ƘUDURORI DA BAYANAN

Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta Duniya

Ƙarƙashin

Ƙungiyar Taimakekeniyar Ƙasashen Musulmai

Tarurrka: (2 – 24)

Ƙudurori: (1 – 238)

(1406 – 1441 H / 1985 – 2019)

Tarjama:

Salihu Abubakar Kaura

Faculty of Language and Translation,

Al Azhar University, Cairo

ƘUDURORI DA BAYANAN

CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

ƘARƘASHIN

ƘUNGIYAR TAIMAKEKENIYAR ƘASASHEN MUSULMAI

TARURRKA 2 – 24

ƘUDURORI: 1 – 238

1406 – 1441 H / 1985 – 2019

Tarjama

Salihu Abubakar Kaura

Faculty of Language and Translation,

Al Azhar University, Cairo

Haƙƙoƙin mallaka © Cibiyar Fiƙihun Musulunci Ta Duniya

1444 – 2023

DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA DA JINƘAI

(Idan waɗannan munafukai suka ga wani abu na tsaro, ko na tsoro da yake da jiɓi da ƙarfin Musulmai, ko rauninsu, sai su yayata shi da nufin ruɗar da Musulmai, ko jefa tsoro da razani a cikin zukatansu, ko saboda su isar da labarinsu zuwa ga maƙiyansu, da a ce waɗannan munafukai sun mayar da duk wani al'amari na tsaro, da na tsoro zuwa ga Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam), da shugabanni, da manyan saahabbai, da dakarun yaƙi, su kuma nemi sanin haƙiƙanin al'amari ta wurinsu, da waɗannan da suke ƙoƙarin neman labarai da yaɗa su sun san gaskiya a wurin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam), da wurin shugabanni. Lallai ba domin falalar da Allah ya yi maku na tabbatar da zukatanku akan imani, da daƙile fitina, da kuma rahamarsa na damƙa maku dukan dalilan da za su sanya ku sami nasara ba, da mafi yawanku sun faɗa cikin tarkon shaiɗan, babu waɗanda za su tsira daga halakarwarsa sai mutane kaɗan daga cikinku) [an- Nisa'i: 83]

GABATARWA

DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA DA JINƘAI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga shugaban Manzanni, Annabinmu Muhammad, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka:

Lallai Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ɗaya ce daga cikin muhimman rassan ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai (OIC)([1]), kaman yanda take a matsayin madogarar Fiƙihu ta farko ga ƙasashen da suke mambobi ne a ƙungiyar, da ma al'ummomin Musulmai da suke rayuwa a wajen ƙasashen Musulmai, bugu da ƙari kuma, ita ce ƙungiyar da take koma wa zuwa gare ta a duk abubuwan da suka shafi Shari'a.

A tsawon shekaru kusan arba'in da suka wuce, cibiyar ta bayar da gudummuwa ta hanyar ƙudurorinta na Fiƙihu masu haske, da mazhabobin Musulunci -da ake la'akari da su- suka haɗu a kai, wajen bayyana hukunce- hukuncen Shari'a game da sababbin abubuwan da suka bayyana a wannan zamani, da matsalolinsa, kaman yanda cibiyar ta iya yin tafiya kafaɗa da kafaɗa da cigaban zamani, da sauye- sauyen rayuwa, ta hanyar ijtihadin gamayyar malamai, waɗanda suke taimakekeniya tare da ƙwararru a dukan fagagen ilimin da ɗan Adam ya iya isa zuwa gare su, suna kuma taƙaituwa da ƙa'idojin aƙidar Musulunci masu rangwame, da dogaro da abubuwan da Shari'ar Musulunci mai haske ta ƙunsa na dawwamammun karantarwa, wanda suke da ikon tabbatar wa ɗan Adam da jin daɗin duniya da sa'ada a kowane zamani, da kuma kowane wuri.

([1]) Organization of Islamic Cooperation

A nan ya kamata mu bayyana cewa; lallai wannan cibiya –tun lokacin da aka kafa ta- ta rungumi ɗabi'un tsaka- tsaki (al- Wasaɗiyya) da daidaito, da kuma kyautata zaman tare da waɗanda ake da saɓani da su, da kuma yin watsi da ɗabi'un ta'assubanci, da wuce gona da iri, da tsaurin ra'ayi.

Saboda haka, abubuwan da wannan littafi ya ƙunsa na ƙudurori da bayanai na musamman, kuma cikakku yana wakiltar abubuwan da fitattun masana Fiƙihu, da kuma ƙwararrun cikin al'ummar Musulmai suka cin ma ne, tun daga taron shekara- shekara na biyu, har zuwa na ashirin da huɗu da cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta shirya (1406 – 1441 H/ 1985 – 2019), kuma hakan sakamako ne na taimakekeniya, da cika juna tsakanin masana Fiƙihun Shari'ar Musulunci, da masana, kuma ƙwararru a sauran fagagen ilmomin bil'adama.

A daidai wannan lokaci da nake gabatar da wannan bugun na ƙudurori da bayanan wannan cibiya mai albarka, ina farin cikin –a madadin mambobi da ƙwararrun cibiyar, da madadin ni kai na- in gabatar da cikakkiyar godiya kuma mai girma zuwa ga shugaba na, Khadimul Haramaini al- Sharifaini, Sarki Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya ƙarfafe shi-, da Amintaccen yarimansa, mai martaba Muhammad Bn Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya kiyaye shi- akan kulawa ta musamman, kuma cikin karamci da suke yi wa cibiyar, da bayar da tallafi mara iyaka tun lokacin da aka kafa ta har zuwa wannan lokaci, ina roƙon Allah ya ba su lada masu yawa, ya kuma dawwamar wa masarauta, da sauran ƙasashen Musulmai, da ma al'ummar Musulmai, ni'imomin tsaro, da aminci, da haɓakar arziki, da cigaba.

Haka ma ina farin cikin gabatar da godiya da jinjina ga ɗan uwana mai girma, Sheikh Dr. Saleh Bn Abdullahi Bn Humaid, shugaban majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, kuma mai bai wa Sarki shawara na musamman, kuma mamba a majalisar manyan malamai, limami mai huɗuba a Masallacin Harami, ina gode masa akan

abubuwan da yake gabatarwa na jan aiki mai albarka, da aiki tuƙuru ba dare ba rana a cibiyar.

Haka ma ina farin cikin gabatar da godiya ta mai girma zuwa ga masu girma da daraja, mambobin cibiyar da suke wakiltar ƙasashen Musulmai, da ƙwararru kuma masana na cibiyar, saboda gudummuwa mara yankewa da cibiyar take samu daga gare su.

A ƙarshe, ina taya sakataren cibiyar, ɗan uwana mai daraja, mai girma Farfesa Ƙudub Mustapha Sano murna wannan jan aiki mai girma da aka gudanar a ɗan ƙanƙanin lokaci da hawansa wannan muƙami na sakatare, ina roƙon Allah ya yi masa jagoranci, ya kuma datar da shi wajen gabatar da aikinsa.

Allah ya sanya mu dace.

Dr. Yusuf Bn Ahmad al- Usaimin
Sakataren ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai

GABATARWAR

Mai girma, shugaban majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, Sheikh Dr. Saleh Bn Abdullahi Bn Humaid, mai bai wa Sarki shawara na musamman, mamba a majalisar manyan malamai, limami kuma mai huɗuba a Masallacin Harami

DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA DA JINƘAI

Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya ɗaukaka darajar malamai, da matsayin masu imani, ya sanya suka zamo shugabannin da suke shiryatar da bayinsa da shiryatarwar Alƙur'ani, gami da shiriyar Annabinsa fiyayyen halitta (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka:

A cikin abubuwan da suka kamata a sani akwai cewa: lallai abu ne mai sanya jin daɗi a ce mutum ya san Fiƙihun addininsa, ya kuma yi aiki da abin da ya sani, hasali ma a cikin alamun samun dacewa da alhairai ne mutum ya zamo ya fahimci addini da kyau, ya kuma yi aiki da shi saboda Allah Ubangijin talikai, saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Duk mutumin da Allah yake sonsa da alhairi sai ya fahimtar da shi addini)** [al-Bukhari da Muslim]; saboda fahimtar addini hanya ce ta sanin hukunce- hukunce, da manufofin Shari'a, da kuma bambance tsakanin halal da haram, da kuma gabatar da abubuwan da suka wajaba, da isar da haƙƙoƙi zuwa ga inda suka kamata, saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki ya tuna wa Annabinsa Sulaiman (AlaiHis Salam) ni'imar da ya keɓance shi da ita na zurfin fahimta, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Sai muka fahimtar da Sulaiman, dukansu mun ba su hukuncin da ilimi)** [al- Anbiya': 79].

Lura da irin yanda ake samun cigaba a kai- a kai, da kuma saurin samun sauye- sauye masu bibiyan juna, da kuma irin yanda fagage suke shiga cikin juna, inda hakan yake samar da matuƙar buƙatar yin bayanin hukunce-hukuncen Shari'a akan sababbin abubuwan da suke faruwa, da kuma la'akari da muhimmancin yin ijtihadi na bai ɗaya kuma a tare, inda masana Fiƙihu za su haɗu a

wuri ɗaya tare da ƙwararru, malamai su tattauna tare da waɗanda suke da tajriba; saboda duka waɗannan dalilai ne cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya take kai- goro da mari –tun sanda aka kafa ta- wajen tabbatar da an sami wannan haɗuwa da yake cika juna tsakanin masana Fiƙihun mazhabobi da junansu, a ɗaya ɓangaren kuma, tsakanin masana Fiƙihun da ƙwararru masana a sauran fagagen ilimi. Godiya ta tabbata ga Allah, lallai wannan jan aiki na ilimi mai albarka ya haifar da samar da ƙudurori ɗari biyu da talatin da takwas (238), da suka shafi mabambanta sababbin abubuwa da suka faru a wannan zamani, kuma waɗannan ƙudurori sun sifantu da kallo na diƙin- diƙin, da kuma fahimtar komai a yanda suke, da kuma kyautatawa, inda cibiyar take bin nagartacciyar hanyar masana Fiƙihu a wajen hararo mas'ala, da yin ijtihadi akansu cikin sababbin abubuwan da suka faru. Abin da kowa ya sani ne cewa shi wannan kallon yana farawa ne daga suranta mas'ala, sannan sanin haƙiƙaninta, sannan sifanta abin da ya faru, sannan kuma a yi aiki da asalin hanyoyin kafa hujja, da kuma ƙa'idojin ilimi saboda a gina akansu, sannan istinbaɗi daga cikinsu, sannan a ƙarshe a saukar da hukuncin akan abin da ya farun, ƙarƙashin wani tsararren manhaji na ilimi.

Haka ma ƙudurori da bayanan cibiyar sun sami ƙarɓuwa a wurin malamai masana Fiƙihu na ƙasashen Musulmai, abin da hakan ya sanya suka zamo madogara ta Fiƙihu mai matuƙar muhimmanci ga Musulmai a ciki da wajen ƙasashen Musulunci. Bugu da ƙari, ga adadi masu yawa na masu girma da daraja cikin shaihunai da malaman Shari'a, da masu nazarin Musulunci a jami'o'i, da cibiyoyin ilimi, da tsangayoyi, da cibiyoyi a ciki da wajen ƙasashen Musulunci da suke muhimmanta waɗannan ƙudurori da bayanan, inda suka sanya su zamo cikin abubuwan da ɗalibansu za su rinƙa gudanar da bincike da nazari akansu, inda hakan zai sanya ɗaliban su iya haɗa tsakanin ilimi hasashen fannin Fiƙihu, da kuma Fiƙihun a aikace, da

kuma samun horaswa ta musamman akan hanyoyin da ake bi wajen saukar da hukunce- hukunce ƙarƙashin madubin wannan ijtihadi na bai ɗaya da aka yi shi a tare.

Haka ma a cikin ƙoƙarin kyautata kulawa da Nassoshin Shari'a, da ƙa'idojin ilmin Fiƙihu da suka zo a cikin waɗannan ƙudurori da bayanan ne muka haɗa da tattaunawar da mujallar cibiyar take fitarwa.

Wannan kenan, saboda haka Cibiyar tana farin cikin gabatar da sabon bugu, da aka yi masa bita na dukan ƙudurori da bayananta tun daga taron shekara – shekara karo na biyu, har zuwa taron shekara- shekara karo na ashirin da huɗu na ƙarshe (1406 – 1441 H/ 1985 – 2019), bayan wucewa kusan shekaru goma da buga ƙudurori da bayanan Cibiyar a shekarar (1413 H/ 2011).

Ina son in yi amfani da wannan dama mai albarka; saboda in gabatar da yabo gami da jinjina da irin tallafi, gami da goyon bayan da Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta samu daga shugabannin ƙasashen Musulunci masu daraja, gudummuwa ta kuɗi, da ta ƙarfafawa da suka bai wa Cibiyar daman gabatar da aikinta da isar da saƙonta, da cimma manufofinta, da kuma zartar da ayyukanta wajen hidimta wa addinin Musulunci da Musulmai a duk inda suke a faɗin duniya.

Haka ma ina gabatar da jinjina ta musamman ga ƙasar da Cibiyar take da Helkwata, wato ƙasar Saudiyya; saboda kulawa ta karamci da take samu, daidai da umurnin da Khadimul Haramaini al- Sharifaini, Sarki Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya yi masa jagora-, da yarimansa, Amintacce mai martaba Muhammad Bn Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya kiyaye mana shi- suka bayar, haka ma ina gabatar da cikakkiyar godiya da mai girma sakataren ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, ɗan uwana mai daraja, Dr. Yusuf Bn Ahmad al-Usaimin, akan gudummuwa mara yankewa da yake bai wa cibiyar wajen gabatar da dukan ayyukanta.

Haka ma a nan, ina son in gabatar da godiya, da jinjina da addu'ar neman gafara da rahama ga waɗanda suka gabace mu cikin masana Fiƙihu da malamai, mai girma Sheikh Dr. Bakr Abu Zaid, tsohon shugaban cibiyar, da mai girma Dr. Muhammad al- Habib Bil'khuja, tsohon sakataren cibiyar, da mai girma Farfesa Abdussalam al-Abbadiy, tsohon sakataren cibiyar, Allah ya yi masu rahama baki ɗaya, ya kuma sanya dukan abubuwan da suka gabatar wa cibiyar na ilimi, da ayyuka, da kuma jagoranci, a cikin ma'aunan kyawawan ayyukansu, kada kuma ya haramta mana ladansu, kada ya fitine mu a bayansu, ya kuma gyara masu bayansu, ya sanya ilimi ya cigaba da wanzuwa a cikin tsatsonsu; haka ma muna ƙara isar da godiya, da jinjina ga mai girma Sheikh Dr. Ahmad Khalid Babakr, tsohon sakataren cibiyar –Allah ya ƙara masa lafiya.

A ƙarshe, wannan ma dama ce da zan yi amfani da ita wajen gabatar da cikakkiyar godiya, da jinjina ga sakataren Cibiyar, mai girma Farfesa Ƙuɗub Mustapha Sano, da dukan mataimakansa akan wannan jan aiki mai albarka, da samar da wannan aiki mai ƙima da suka yi a ɗan ƙanƙanin lokaci daga hawarsa muƙamin sakataren Cibiyar, ƙasa da watanni biyu.

Ina roƙon Allah ya amfanar da al'umma da wannan bugu, ya kuma shiryatar da mu zuwa ga hanya madaidaiciya, ya kuma ƙare mu da taimako, gami da dacewarsa, ya samar mana da nasara, da rabo a duniya da lahira.

Allah ya yi tsira da aminci ga shugabanmu Annabi Muhammad, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Dr. Saleh Bn Abdullahi Bn Humaid
Shugaban Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya.

GABATARWAR
MAI GIRMA SAKATAREN
CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA
FARFESA ƘUƊUB MUSTAPHA SANO

DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA DA JINƘAI

Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya shiryatar da mu zuwa ga wannan addini, mu kam babu yanda za a yi mu iya shiryuwa, ba domin Allah ne ya shiryatar da mu ba, godiya ta tabbata ga Allah, wanda albarkacin ni'imarsa ce kyawawan ayyuka suka kammaluwa, tsira da amincin Allah su tabbata ga mai shiryatar da mutane, rahamar da Allah ya bai wa ɗaukacin bayi, haske mai haskaka duhu, Annabi Muhammadu wanda ya fi kowa, da alayensa tsarkaka, da sahabbansa zaɓaɓɓu, da masu bin turbarsa har zuwa tabbatacciyar rana.

Bayan haka:

Abu ne da kowa ya sani cewa: Saƙon Musulunci shi ne saƙon Allah na ƙarshe zuwa ga bayi, abin da yake nuna cewa shi ne saƙo na ƙarshe kuwa shi ne sauƙin Shari'arsa da yake daidai da kowane zamani, da kuma kowane wuri, da kuma faɗin hukunce- hukuncensa, da nagartar karantarwarsa ta yanda ya dace da zamunna da wurare, bugu da ƙari kuma, ga ƙarfi, gami da ikon da manyan tobula da ginshiƙansa, da manyan manufofinsa, da kuma manyan ƙa'idojinsa suke da su wajen fuskantar da dukan yanayi, da daidaita duk wani sabon abu da rayuwa ta zo da shi, da jagorantar sauye- sauyen zamani, daidai da wani tabbataccen manhaji na ilimi, wanda ya ginu akan ginshiƙai, aka kuma yi masa kuri da manufofi, aka kuma kare shi da ƙa'idoji, masu la'akari da abubuwan da za su je- su- dawo.

Haka ma cikin abubuwan da suke nuna cewa shi ne saƙon ƙarshe akwai: irin yanda hukunce- hukuncensa suka ginu akan kulawa da maslahohin bayi a rayuwarsu ta duniya da ta lahira, da tsayar da adalci, da yaɗa tausayi da rangwame, da kiyaye haƙƙoƙi, da tsara 'yanci, da raya

doron ƙasa, da sanya jin daɗi da farin ciki a cikin zukatan bil'adama.

Ganin irin cigaba, da kuma sauri da ake samu a dukan fagagen rayuwa a wannan zamani namu, da kuma irin yanda fagagen na dangantaka suka cakuɗa da juna, da yawan faruwan sababbin abubuwa, waɗanda suke wajabta aiki domin cika juna, suke kuma nuna muhimmancin yin taimakekeniya tsakanin malaman Fiḳihu na mazhabobi da junansu, da kuma tsakaninsu da masana da ƙwararru a ɗaya ɓangare, saboda bayyana hukunce- hukuncen Shari'a game da sauran mas'alolin da suka shafi Musulmai a dukan faɗin duniya, saboda waɗannan dalilan ne, cibiyarmu ta shirya tarurrukan shekara- shekara na ilimi –a tsawon shekaru kusa arba'in da suka shuɗe-, inda aka kai zuwa ga fitar da ƙudurori na ilimi guda ɗari biyu da talatin da takwas (238), da suka taɓo mas'alolin kuɗi, da na ayyukan kasuwanci, da al'amurran da suka shafi mata, da iyalai, da ƙananan yara, da mas'alolin tunani, da na tarbiyya, da na al'adu, da rayuwar zamantakewa, da siyasa.

A kwaɗayin da muke da shi na isar da waɗannan ƙudorori masu haske, da ingantattun bayanai zuwa ga al'umma –ƙasashe, da ƙungiyoyi, da ɗaiɗaikun mutane-, ofishin gudanarwar wannan cibiya take farin cikin ta gabatar da wannan sabon bugu, da yake ƙunshe da dukan ƙudurorin Cibiyar, da bayananta tun daga taron shekara-shekara karo na biyu har zuwa taron shekara- shekara karo na ashirin da huɗu (1406 – 1441 H/ 1985- 2019), waɗanda aka yi masa bita, zuwa ga masana ilimin Fiḳihu, da malamai, da masu tunani, da wayayyu a dukan faɗin duniya. Akwai buƙatar a sani cewa an gudanar da buga waɗannan ƙudurori da bayanai na ƙarshe ne –kafin wannan- a shekarar (1432 H/ 2011), kuma bugun a lokacin yana ɗauke da ƙudurori da bayanai (185) ne kawai; amma wannan sabon bugu –da taimakon Allah- yana ƙunshe da ƙudurori da bayanai ɗari biyu da talatin da takwas ne.

Lallai an gudanar masa da bita na diƙin- diƙin, gami da lura, ƙarƙashin kwamitin ilimi da ta ƙunshi manyan malamai, ƙarƙashin jagorancin Dr. Abdulƙahir Muhammad Ahmad Ƙamar, daraktan ofishin bincike da bayar da fatawa, da kundayen- sha- kundum, da kuma Ƙamusoshi, mambobin kwamitin sun haɗa da: Dr. Isma'il Jibajiy, shugaban sashen bincike da Kundayen- sha- kundum, da Dr. Muhammad Mustapha Ahmad Shu'aib, shugaban sashen nazari da fatawa, da Malam Khalid Hussain Jarbin, shugaban sashen ɗab'i; Allah ya saka masu da mafificin sakamako.

Zan yi amfani da wannan dama domin in yi wa masu girma malamai, da masana Fiƙihu, da ƙwararru albishir na da cewa an kammala tarjama waɗannan ƙudurori da bayanai zuwa harsunan Turanci, da Faransanci; saboda a bai wa masu magana da harshen da ba Larabci ba daman amfana da su, kuma –da ikon Allah- aiki na nan na cigaba wajen ƙoƙarin tarjama su zuwa ga muhimman harsunan da Musulmai suke magana da su a Afrika, da Asiya, da yankin Turai, idan Allah ya yarda tarjamomi za su isa zuwa ga al'umma nan ba da daɗewa ba; saboda kowa ya amfana.

A ƙarshe, a madadin mambobi, da ƙwararrun wannan cibiya, da ma ni kai na, ina farin cikin gabatar da godiya mai yawa, da jinjina, da girmamawa zuwa ga mai martaba Khadimul Haramaini, Sarki Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya ƙara masa lafiya-, da yarimansa Amintacce, mai martaba Muhammad Bn Salman Bn Abdul'aziz Alu Sa'ud –Allah ya kiyaye mana shi- saboda irin kulawa mai girma, da kuma muhimmantawa da cibiyar take samu daga ƙasar da cibiyarta take –Allah ya kare ta-, ina roƙon Allah ya saka masu da kyakkyawan sakamako, ya kuma dawwamar wa ƙasar da cibiyar take – Saudiyya- da ma sauran ƙasashen da suke mambobi ne a cibiyar, da ni'imomin tsaro, da kwanciyar hankali, da cigaba.

Haka ma ina farin cikin gabatar da godiya mai yawa, da jinjina ga sakataren ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, ɗan uwana mai girma Dr. Yusuf Bn Ahmad al-Usaimin, sakamakon irin muhimmin matsayin da yake bai wa cibiyar, da kuma gabatar da goyon- baya da tallafi ga ayyukan da take gabatarwa.

Haka ma ina son in yi amfani da wannan dama, domin na kwararo da godiya mai yawa, da yabo, da jinjina ta gaskiya, ga mai girma Sheikh Dr. Saleh Bn Abdullahi Bn Humaid, shugaban majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, mai bai wa Sarki shawara na musamman, kuma mamba a majalisar manyan malamai, limami kuma mai huɗuba a Masallacin Harami, saboda kulawa ta musamman da cibiyar take samu daga gare shi, da shawarwari masu muhimmanci, da kuma tallafi mai girma, ina roƙon Allah ya saka masa da kyakkyawan sakamako, ya kuma cigaba da kiyaye shi domin amfanar Musulunci da Musulmai.

A ƙarshe, gaba ɗayanmu muna sake miƙa hannayenmu cikin ƙasƙantar da kai zuwa ga Allah Mabuwayin Sarki, muna roƙonsa mai girma da karamci ya ba mu lada, mu da dukan manyan malaman Fiƙihu, da ƙwararrun wannan cibiya masu girma, da malamanta masu karamci da suka koma zuwa ga Allah, bayan sun gabatar da gagarumin hidima da gudummuwa ga cibiyar wajen cigabanta; musamman masu girma da daraja marigaya: Sheikh Dr. Bakr Abu Zaid, tsohon shugaban cibiyar, da mai girma Dr. Muhammad al- Habib Bil'khuja, tsohon sakataren cibiyar, da mai girma Farfesa Abdussalam al- Abbadiy, tsohon sakataren cibiyar, da Sheikh Muhammad Aliyu al-Taskhiriy, mamba, da Sheikh Abdussattar Abu Gudda, mamba, da Sheikh Anas Abdunnur Kalisa, mamba, da Sheikh Dr. Wahba al- Zuhailiy, mamba, da Farfesa Ja'afar Abdussalam, tsohon sakataren ƙungiyar jami'o'in Musulunci, kuma ƙwararre a cibiyar, da Farfesa Muhammad Abdulhalim Umar, ƙwararre a cibiyar, da

sauran mambobi da ƙwararru, ina roƙon Allah ya sada su da Annabawa, da siddiƙai, da shahidai, da salihai waɗanda haɗuwa da su shi ne abu mafi kyau.

Godiya da jinjinarmu ba za su tsaya ba sai sun isa zuwa ga Farfesa Ahmad Khalid Babakr, tsohon sakataren cibiyar, da duka waɗanda suke aiki a cikinta, da suka haɗa da daraktoci, da shugabannin sassa, da masu gudanarwa; saboda irin yanda suke gudanar da aiki tuƙuru ba dare ba rana cikin ikhlasi; domin hidimta wa al'umma da cibiyar.

Ina roƙon Allah ya ƙara tsira, da aminici, da albarka ga shugabanmu Annabi Muhammadu, da alayensa da sahabbansa.

Farfesa Ƙuɗub Mustapha Sano
Sakataren Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya.

BAYANI GAME DA CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya hukuma ce ta ilimi, wadda aikinta ya shafi ƙasa da ƙasa, tana aikin ne a ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai (OIC), an kafa ta ne a garin Makka, saboda zartar da ƙudurin taron ƙoli na ƙasashen Musulmai na uku (Lamba: 3/8 –Th.Q. A) da ya gudana a tsakanin ranakun: (19 – 22 ga watan Rabi'ul Awwal, 1401 H/ 25- 28 ga watan Junairu, 1981), mazaunin cibiyar shi ne garin Jidda na ƙasar Saudiyya, ƙungiya ce da take da matsayi a dokoki, mambobinta kuma sun haɗa da malamai masana Fiƙihu, da malamai da masu tunani a fagagen ilmomin Fiƙihu, da al'adu, da tarbiyya, da kimiyya, da tattalin arziki, da zamantakewa, waɗanda suka fito daga dukan ƙasashen Musulmai, cikin wani tsari na cikakken cin gashin- kai, cibiyar tana gabatar da ayyukanta akan karantarwar Alƙur'ani mai girma, da Hadisan Annabi masu daraja, wajen bayyana hukunce – hukuncen Shari'a a dukan mas'alolin da suka shafi al'ummar Musulmai a duk inda suke a faɗin duniya, kaman yanda suke gudanar da nazari, da bincike game da matsalolin rayuwar zamantakewa na zamani, da kuma yin ijtihadi na asali kuma muhimmi a cikinsu, saboda a samar da mafita wadda aka ɗauko ta daga ilmomin Musulunci, da suke marhabin da cigaban tunani a Musulunci.

A cikin kusan shekaru arba'in da suka shuɗe, cibiyar – cikin falala da yarjewar Allah- ta sami daman shirya tarurruka ashirin da huɗu, a cikinsu ta sami daman fitar da ƙudurori ɗari biyu da talatin da takwas (238) da suka taɓo fagage mabambanta na sababbin abubuwan da zamani ya zo da su.

MAHANGA

Cibiyar tana fatan ta zamo madogara ta Fiƙihu ta farko ga ƙasashen Musulmai, gami da al'ummar Musulmai da suke zaune a ƙasashen da ba na Musulunci ba inda za su rinƙa komawa zuwa gare ta wajen bayyana hukunce-hukuncen Shari'a game da mas'alolin da suka shafi Musulmai, da niyyar samar da mafitar da suka dace da rayuwar zamani, waɗanda suka samo asali daga Alƙur'ani mai girma, da Sunnonin Annabi masu daraja, da ilmomin Musulunci masu cike da haske.

SAƘO

Saƙon cibiyar shi ne gabatar da Shari'ar Musulunci da kyau, kuma a daidaice, da fito da abubuwan masu kyau da suke ciki, da bayyana ikon da take da shi wajen magance matsalolin rayuwa, da samar da jin daɗi, da kwanciyar hankali, da tsaro, da aminci ga ɗan Adam a duniya da lahira, ta mahanga mai faɗi da ta yi daidai da tushen addinin Musulunci, da madogara, da manufofi, da ƙa'idojinsa, da kuma hukunce- hukuncensa.

ƊABI'U

* Tsaka- tsaki (al-Wasaɗiyya)
* Aiki da ƙa'idoji (al-Indhibaɗ)
* Rashin ƙunbuya – ƙunbuya
* Adalci (al- Adlu)
* Sanin ya kamata (al-Insaf)
* Taimakekeniya da cika juna
* Ƙwarewa da Gwaninta
* Haɓaka al'amurra
* Kyautatawa
* Zartar da ayyuka

MANUFOFI

1) Samar da cikakkiyar haɗuwa ta cika ilmomin juna tsakanin masana Fiƙihu na mazhabobin Musulunci

da ake la'akari da su, da kuma malamai a sauran fagagen ilmi; saboda bayyyana matsayar Shari'a akan matsalolin da suka shafi rayuwar zamani.

2) Bayyana fahimta ta Shari'a, da kuma zartar da ita game da maudhu'an da suke da jiɓi da rayuwar yau da kullum, abin da zai taimaka wajen yi wa dokoki, da tsare – tsare gyara da kwaskwarimar da za su yi daidai da hukunce- hukuncen Musulunci.

3) Ḳarfafa yin Ijtihadi na bai-ɗaya game da mas'alolin da suka shafi rayuwarmu ta zamani, da matsalolin da take ḳunshe da su, da kuma zaɓar ra'ayoyin Fiḳihu da za su samar da maslahar Musulmai a matsayinsu na ɗaiɗaiku, da matsayinsu na al'ummomi da na ḳasashe, daidai da hujjojin da suke tabbatar da manufofin Shari'ar Musulunci.

4) Yin watsi da ɗabi'un: ta'assubanci na mazhaba, da tsaurin ra'ayi, da kafirta mazhabobi da mabiyansu, ta hanyar yaɗa daidaito (al-Wasaɗiyya), da sauḳin kai da rangwame tsakanin mazhabobi da mabambanta ḳungiyoyin Musulunci.

5) Mayar da martani akan fatawowin da suka saɓa da tabbatattun Nassoshin Musulunci, da ḳa'idojinsa na Ijtihadi da ake la'akari da su, da abubuwan da suka tabbata a wurin malaman mazhabobi, ba tare da wani dalili, ko hujja na Shari'a da ake la'akari da su ba.

6) Bai wa al'ummomin Musulmai da suke rayuwa a ḳasashen da ba na Musulmai ba fatawowin da za su kiyaye ɗabi'un Musulunci, da al'adunsa, saboda su kiyaye sifofinsu na Musulunci, tare kuma da bin doka- da- oda a ḳasar da suke rayuwa a ciki a matsayinsu na 'yan ḳasa da suke rayuwa a ḳasashen da ba na Musulmai ba.

7) Ḳarfafa tsarin taimakekeniya, da cika juna, da kuma muḳarana tsakanin Fiḳihun mazhabobin Musulunci da ake la'akari da su akan abubuwan da suke sanannun ne a cikin al'amurran addini, da girmama

abubuwan da aka haɗu a kai, da girmama saɓani da bambance- bambance, da kuma kiyaye ladubban saɓani, da kuma muhimmancin yin amfani ra'ayoyin mazhabobi wajen fitar da fatawowi da ƙudurorin cibiyar.

8) Samar da tsarin tuntuɓar juna tsakanin hukumomin bayar da fatawa, da ƙungiyoyin ilmomin Fiƙihu a ciki da wajen ƙasashen Musulmai, saboda kauce wa cin karo da juna a mas'ala guda, musamman a cikin mas'alolin da suka shafi kowa da kowa a dukan matakai.

9) Aiki wajen jaddada Fiƙihun Musulunci ta cikin gida, da haɓaka shi ta hanyoyin bin manhaji da tsarin Istinbaɗi, da ƙa'idoji, da hujjoji, gami da manufofin Shari'a.

10) Tattaunawa mai ma'ana tsakanin mabambanta addinai, da al'adu da niyyar gudanar da taimakekeniyar da za ta samar da alhairi ga rayuwar ɗan Adam ta zamantakewa.

HANYOYI

1. Bayar da fatawa akan abubuwan da suka shafi al'ummar Musulmai na bai- ɗaya, da tarjama su zuwa harsuna mabambanta, sannan a yaɗa su a ko'ina domin ƙarfafa rungumar manhajin daidaito (al-Wasaɗiyya) na Musulunci, wanda zai shiga tsakanin Musulmai da wuce gona da iri, ko tsaurin ra'ayi, da kuma rashin muhimmanta addini, da bin baƙin ra'ayoyi da suka saɓa da ra'ayoyi masu ƙarfin hujja.

2. Shirya manya, da ƙananan tarurruka na ƙara wa juna sani; domin tattaunawa game da wasu keɓantattun mas'aloli, ko maudhu'ai da suke da matsalolin da akwai buƙatar a gudanar da bincike, da tattaunawa na Fiƙihu masu faɗi da zurfi sama da yanda majalisar cibiyar take iya bayarwa.

3. Bayyana hukuncin Shari'a game da dokoki, da tsare-tsaren da ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai take fitarwa, da ma wasu ƙungiyoyin na Musulunci na ƙasa da ƙasa, da ma waɗanda ba na Musulmai ba a duk sanda aka buƙaci hakan.
4. Sanin hukumomin bayar da fatawa, da cibiyoyi da manyan ƙungiyoyin Fiƙihu da suke a ciki da wajen ƙasashen Musulmai, domin bayyana hukumomin da za iya gudanar da taimakekeniya da tuntuɓar juna da su tare da cibiyar.
5. Kafa cibiyoyin bincike, da nazarin Shari'ar Musulunci a wasu muhimman wurare a wajen ƙasashen Musulmai, da kuma yin taimakekeniya tare da cibiyoyin da suke akwai su, saboda hidimta wa manufofin cibiyar, da kuma bibiyan abubuwan da ake yaɗawa da sunan Musulunci a wuraren da ayyukanta suka shafa, da kuma raddi game da shubuhohin da ake kawowa.
6. Samar da kundayen- sha- kundum a fannin Fiƙihun Musulunci masu sauƙin fahimta (da harsuna uku) da za su mayar da hankali wajen muhimman mas'alolin zamani a fagagen rayuwa mabambanta, za kuma su mayar da hankali akan mas'alolin da suka fi fitowa a litattafan Fiƙihu, a rubuta su da salo mai sauƙi; domin kusanta ilimin Fiƙihu zuwa ga jamhur dîn mutane da suke aiki a fagen fanni, da wayewa, da aikin jarida.
7. Ƙarfafa yin bincike, da nazari a fage ilimin Fiƙihu, ta hanyar sassa, da kwamitocin Cibiyar, da kuma a jami'o'i da cibiyoyin ilimi akan abubuwan da suka shafi ƙalubalen da zamani ya zo da su, da kuma sababbin mas'aloli na zamani.
8. Samar da tsarin dokoki na gwaji (da harsuna uku) a dukan fagagen da suke buƙatar samar da tsararrun dokoki na Shari'a, inda za a yi la'akari da bambancin mazhabobi, sannan a tarjama, a kuma yaɗa a ƙasashen Musulmai, domin su zamo suna da sauƙin

komawa zuwa gare su wajen sauya dokoki, da tsare-tsaren da ake da su a ƙasa.

9. Raya ilmomin Musulunci a fannin ilimin Fiƙihu, tare da bayar da kulawa ta musamman ga litattafan ilimin sanin makamar Fiƙihu (Usulul Fiƙh), da ilimin manufofin Shari'ar Musulunci (Maƙasidus Shari'atil Islamiyya), da Fiƙihu, da Gwama tsakanin mazhabobin Fiƙihu (Fiƙihul Muƙaran), da kuma yaɗa litattafan da ba a yaɗa su ba a waɗannan fagage, bayan an yi masu tahƙiƙi, da kuma tarjama muhimman litattafan Fiƙihu zuwa muhimman harsunan da Musulmai suke amfani da su, da ma manyan harsunan duniya.

10. Samar da ƙamusoshin masu faɗi (mai harsuna uku) na kalmomi na musamman a fannonin Fiƙihu da ilimin sanin makaman Fiƙihu (Usulul Fiƙh), inda za a kula matuƙa wajen bayyana ma'anoninsu, da kuma kyautata salo wajen bayyana su.

11. Yaɗa dukan ayyukan cibiyar, da ƙudurorinta da fatawowin da ta bayar, da muhimman binciken da aka gabatar a mujallar cibiyar, a shafin cibiyar na Intanet; saboda a amfana da su, da kuma tarjama su zuwa muhimman harsunan Musulmai da ma manyan harsunan duniya.

12. Neman taimakon ƙwararru, da masana a fagagen ilmomi mabambanta, da waɗanda suke gudanar da su a aikace saboda a gudanar da nazari da binciken da ake gabatar wa Cibiyar.

OFISOSHI DA SASSA

Sakateriyar cibiyar ta ƙunshi ofisoshi da sassa, kaman haka:

(1) Ofishin gudanar da al'amurran sakateriya, da tarbar baƙi, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, waɗanda su ne: sashen tarbar baƙi, da sashen al'amurran iyali, da mata,

da ƙananan yara, da masu yawan shekaru, da sashen tarjama.

(2) Ofishin tsare- tsare da taimakekeniya na ƙasa da ƙasa, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, waɗanda su ne: sashen tsare- tsare da cigaba, da sashen taimakekeniya na ƙasa da ƙasa da hulɗa da harkokin waje, da kuma sashen adana da bibiya da kuma tantancewa.

(3) Ofishin al'amurran ma'aikata da hada – hadar kuɗi, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, waɗanda su ne: sashen ma'aikata da bayar da horaswa, da sashen kuɗi da lissafi, da sashen ajiye- ajiye da laburare.

(4) Ofishin yaɗa labarai da hulɗa da jama'a da bayanai da tuntuɓa, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, wanda suka haɗa da: sashen yaɗa labarai, da sashen hulɗa da jama'a, da sashen bayanai da tuntuɓa.

(5) Ofishin bayar da tallafi, da zuba jari, da gudanar da ayyuka, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, waɗanda su ne: sashen al'amurran waƙafi, da sashen bayar da tallafi da zuba jari, da sashen gudanar da ayyuka.

(6) Ofishin bincike da nazari da bayar da fatawa da kundayen- sha- kundum, da ɗab'i, akwai sassa uku a ƙarƙashinsa, da suka haɗa da: sashen bincike da kundayen sha- kundum, da sashen bayar da fatawa da nazari, da sashen ɗab'i da yaɗawa.

(7) Ofishin tsara manya da ƙananan tarurrukan ƙara wa juna sani, a ƙarƙashinsa akwai sassa uku, kaman haka: sashen tsara manyan tarurrukan ƙara wa juna sani, da sashen tsara ƙananan tarurrukan ƙara wa juna sani, da sashen tarurrukan horaswa da lakcoci.

KUDURORI DA BAYANAI

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA BIYU([1])
MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA
JIDDA (SAUDIYYA)
10 -16 GA WATAN RABI'UL AKHIR, 1406 H
22 – 28 GA WATAN DISAMBA, 1985

([1]) Taron shekara – shekara na farko: dukan ƙudurorin da aka ɗauka na tsare- tsaren gudanarwa ne

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 1 (1/2)([1])
GAME DA ZAKKAR BASHI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai (OIC), a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan ta duba nazari, da binciken da aka gabatar mata game da zakkar bashi, bayan tattaunawa mai zurfi da ta taɓo wannan maudhu'i ta dukan ɓangarorinsa mabambanta([2]), ta gano cewa:

- **Na farko:** Lallai babu wani nassi a cikin littafin Allah Maɗaukakin Sarki, ko a cikin Hadisan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da ya yi bayani dalla- dalla akan zakkar bashi.
- **Na biyu:** An sami bayanai masu yawa daga sahabbai da tabi'ai (Allah ya ƙara yarda da su) da suke bayyana fahimta mabambanta akan hanyoyin fitar da zakkar bashi.

([1]) Mun sanya wa dukan ƙudurorin da aka samar da su a dukan tarurrukan shekara- shekara lambobi a jere, kaman yanda muka bai wa kowane taro lamba ta musamman da muka sanya cikin baka biyu (..), lamba ta farko tana nuni zuwa ga ƙuduri, lamba ta biyu kuma tana nuni zuwa ga taron shekara- shekara.

([2]) Duba: Nazarce - Nazarce da tattaunawa, a mujallar Cibiyar (Fitowa ta biyu: 1/61)

- **Na uku:** Lallai mazhabobin Musulunci sun yi saɓani game da haka, sakamakon wannan saɓani da ya bayyana.
- **Na huɗu:** Lallai dukan saɓanin ya ginu ne akan saɓaninsu akan ƙa'idar: "Shin za a iya bai wa dukiyar da za a iya samunta hukuncin dukiyar da an riga an same ta?".

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** Wajibi ne akan wanda yake bin bashi ya fitar wa bashin da zakka a kowace shekara, idan yana da wadata da yalwa.
- **Na biyu:** Wajibi ne wanda yake bin bashi ya fitar wa da bashin zakka idan shekara ta kewayo, daga ranar da ya amshi bashinsa, idan mai bin bashin talaka ne, ko wanda ake bi bashi mai taurin bashi.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 2 (2/2)
GAME DA ZAKKAR TABBATATTUN ABUBUWA DA FILAYEN HAYA DA BA A NOMA BA([1])

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai (OIC), a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan ta saurari nazarce- nazarcen da aka gudanar akan maudhu'in zakkar tabbatattun abubuwa da filayen haya da ba a noma ba,

Bayan cikakkiyar tattaunawa, kuma mai zurfi([2]) da aka gudanar akan wannan batu, an gano cewa:

- **Na farko:** Ba a sami wani Nassi na ƙarara da ya wajabta bayar da zakka akan tabbatattun abubuwa da filayen haya ba.
- **Na biyu:** Haka ma ba a sami wani Nassi da ya wajabta fitar da zakka ta gaggawa akan gallar tabbatattun abubuwa, da filayen haya da ba noma ba.

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** Lallai zakka ba ta wajaba akan asalin tabbatattun abubuwa da filayen haya ba.

([1]) Game da al'amarin zakka akan filayen nona (Zakkar noma) an fitar da ƙuduri mai lamba 91 (2/13)

([2]) Mujallar Cibiyar (fitowa ta biyu, 1/115)

- **Na biyu:** Zakka ta wajaba akan galla, wato rubu'in ɗaya cikin goma bayan shekara ta kewayo, tare da la'akari da samuwar sharuɗɗan zakka, da kuma tabbatar da cewa abubuwan da suke hana zakka ba su kasance ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 3 (3/2)
GAME DA TAMBAYOYIN DA CIBIYAR TUNANIN MUSULUNCI TA DUNIYA DA TAKE WASHINGTON, D.C.([1])

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Inda kwamitin mambobin cibiyar ya rubuta littafi domin duba tambayoyin da suka zo daga Cibiyar Tunanin Musulunci ta duniya da take Washington, D.C.

Bayan lura da abin da aka gabatar game da wannan al'amari na amsoshi, an gano cewa:

- **Na farko:** Lallai an rubuta amsoshin ne a taƙaice ƙwarai, da ba za su iya gamsarwa, ko su kawo ƙarshen saɓani, da rashin amincewar da ake ciki ba.
- **Na biyu:** Dole ne Cibiya ta tsaya wajen kawar da dukan ruɗanin da 'yan uwanmu Musulmai da suke rayuwa a ƙasashen Turai suke ciki.

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** An ɗaura wa sakateriya alhakin isar da waɗannan tambayoyi zuwa ga waɗanda take gani sun dace cikin mambobi da ƙwararru; saboda su samar da

([1]) Mujallar Cibiya (fitowa ta biyu, 1/199); da (fitowa ta uku, 2/1087)

amsoshin da suke ɗauke da hujjoji, da dalilai, su kuma dogara da hujjojin Shari'a, da maganganun malaman Fiƙihun Musulunci da suka gabata, da samar da su ta yanda za su gamsar, tare kuma da bayyanannun hujjoji.

- **Na biyu:** An ɗaura wa sakateriya alhakin kawo sakamakon wannan aiki a taron shekara – shekara karo na uku([1]).

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 23 (11/3)

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 4 (4/2)([1])
GAME DA AL'AMARIN ƘADIYANIYYA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan nazari akan tambayar da malajisar Fiƙihun Musulunci ta Cape Town, ƙasar Afrika ta Kudu ta bijiro da ita game da hukunci akan Ƙadiyaniyya da wata ƙungiya da ta fito daga cikinta mai suna: Lahoriyya, shin za a kalle su a matsayin Musulmai, ko kuwa a'a? Da kuma ingancin a ce wanda ba Musulmi ba ne zai yi hukunci akan irin wannan mas'ala,

Ƙarƙashin abin da aka gabatar wa mambobin wannan cibiya na bincike, da takardun tabbatarwa game da wannan maudhu'i akan Miraza Ahamd al- Ƙadiyaniy, wanda ya bayyana a ƙasar Indiya a ƙarnin da ya gabata, wanda ake danganta addinin Ƙadiyaniyya, da Lahoriyya zuwa gare shi,

Bayan kallo na lura zuwa ga abubuwan da aka ambata na bayanai game da wadannan addinai guda biyu, bayan tabbatar da cewa lallai Miraza Ahmad ya yi da'awar Annabta, na cewa shi annabi ne da aka aiko shi, ana kuma

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 1/ 209)

yi masa wahayi, an kuma tabbatar da wannan daga cikin litattafansa da ya riya cewa wasu daga cikinsu wahayinsu aka yi masa, ya kuma ɗauki tsawon rayuwarsa yana yaɗa wannan da'awa, yana kuma kiran mutane a cikin litattafansa da maganganunsa zuwa ga su yi imani da annabtarsa da manzancinsa, haka ma an tabbatar da cewa yana inkarin tabbatattun abubuwan da aka sansu a cikin addini, irinsu jahadi,

Haka ma bayan cibiyar ta duba bayanin da ya fito daga cibiyar Fiƙihu da take garin Makka akan wannan maudhu'in, a**n tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Lallai da'awar da "Miraza Gulam Ahmad" ya yi na: annabta, da manzanci, da saukar masa da wahayi, inkari ne ƙarara akan abubuwan da suka tabbata a cikin addini ta hanyar yankakkun dalilai, da suke nuna cika annabta da manzanci da shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da suke nuna cewa babu wani wahayi da zai sauka wa waninsa bayansa. Wannan da'awa da "Miraza Gulam Ahmad" ya yi, za ta fitar da shi –da ma duk wanda ya amince da ita- daga Musulunci (ridda). Ita ma "Lahoriyya" kaman "Ƙadiyaniyya" take wajen fita daga Musulunci, duk kuwa da cewa sun sifanta "Miraza Gulam Ahmad" da cewa inuwa ne da ya fito daga Annabinmu Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam).
- **Na biyu:** Kotun da ba na Musulunci ba, ko alƙalin da ba Musulmi ba, ba shi da hurumin yin hukuncin da ya shafi tabbatar da Musulunci, ko tabbatar da ridda, musamman ma cikin abubuwan da suka saɓa da abin da al'ummar Musulmai suka haɗu akansa ta hanyar manyan cibiyoyinsu da malamansu, wannan kuwa saboda hukuncin tabbatar da Musulunci, ko tabbatar da ridda ba za a amshe shi ba sai idan Musulmi kuma malami masani game da abubuwan da suke tabbatar da shiga Musulunci, ko fita daga cikinsa ne ya yi, ya

kuma zamo ya san mene ne haƙiƙanin Musulunci, kuma mene ne haƙiƙanin kafirci, ya kuma san dukan abubuwan da suka tabbata a cikin Alƙur'ani da Hadisi da Ijma'i, saboda haka, hukuncin da irin wannan kotu ta yi ɓatacce ne.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 5 (5/2)([1])
GAME DA JARIRAN KWALBA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan an bijiro da binciken da manyan malamai masana Fiḳihu, da manyan likitoci da suka gabatar akan jariran kwalba, ta fuskokinsa guda biyu: Fiḳihu, da ta aikin likitanci, an kuma tattauna akan waɗannan bincike da nazari da kyau, da kuma tambayoyi mabambanta da maudhu'in ya kawo,

Bayan cibiyar ta gano cewa lallai wannan maudhu'in yana buƙatar ƙarin bincike da nazari a fagen likitanci da fagen ilimin Fiḳihu, da kuma sake bita akan nazarce-nazarcen da bincike- binciken da suka gabata, da samar da cikakkiyar sura ta dukan fuskokin maudhu'in, a**n tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Jinkirta wannan maudhu'i zuwa taron shekara- shekara mai zuwa da cibiyar take gudanarwa([2]).

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 1/ 233)
([2]) Duba: Ƙuduri mai lamba 16 (4/3).

- **Na biyu:** An ɗaura wa mai girma Sheikh Dr. Bakr Abu Zaid –shugaban cibiyar- alhakin samar da cikakken bincike akan wannan maudhu'i da ya haɗo duk abubuwan da suka shafi ɓangaren ilimin Fiḱihu da ilimin likitanci.
- **Na uku:** Bai wa sakateriya umurnin isar da duk abubuwan da suka iso zuwa gare ta zuwa ga ɗaukacin mambobin cibiyar kafin a gudanar da taron shekara-shekara mai zuwa da watanni uku alal aƙalla.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 6 (6/2)([1])
GAME DA BANKUNAN ADANA NONO (Human Milk Bank)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan an gabatar wa cibiyar da bincike na Fiḳihu, da na likitanci game da bankunan adana nono (Human Milk Bank),

Bayan la'akari da tunani game da abubuwan da wadannan bincike guda biyu suka ƙunsa, da kuma cikakkiyar tattaunawa akan kowanne daga cikinsu, tattaunawar da ta taɓo dukan sassan maudhu'in, an gano cewa:

- **Na farko:** Lallai bankunan adana nono (Human Milk Bank) wani sabon tsari ne da ya faru a tsakankanin al'ummar Turawan yamma, wanda sannu a hankali aka gano wasu kura-kurai na gudanarwa da na ilimi, hakan ya sanya tsarinsu ya ja da baya, muhimmancin da yake tare da su ya ragu.
- **Na biyu:** Lallai addinin Musulunci yana kallon shayarwa a matsayin 'yan uwantaka ne da yake

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 1/ 383)

daidai da ‘yan uwantakar nasaba, Musulmai sun yi Ijma’in akan cewa: duk abin da nasaba ya hana, shayarwa ma ya hana shi. Lallai a cikin muhimmai, kuma manyan manufofin Shari’a akwai kiyaye nasaba, su kuwa bankunan adana nono (Human Milk Bank) suna kai wa ne zuwa ga cakuɗa nasaba, ko sanya shakku akanta.

- **Na uku:** Lallai dangantar zamantakewa a ƙasashen Musulmai ta samar wa bakwaini, ko jaririn da nauyinsa ya yi ƙaranci, ko wanda yake buƙatar nonon uwa a cikin wasu yanayi na musamman duk abubuwan da yake buƙata wajen shayarwa ta hanyar ɗabi’a, al’amarin da ya sanya aka wadata ga barin bankunan adana nono (Human Milk Bank).

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** An hana kafa bankunan adana nonon iyaye mata a ƙasashen Musulmai
- **Na biyu:** Haramun ne a shayar da yara da nonon da aka adana a waɗannan bankuna.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 7 (7/2)([1])
GAME DA NA'URAR SAMAR DA KARSASHI (I.C.U)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan cibiyar ta duba nazarce- nazarcen Fiḳihu, da na ilimin likitanci da aka gabatar mata akan maudhu'in "Na'urar samar da karsashi" (I. C. U),

Bayan cikakkiyar tattaunawar da aka gudanar, da irin yanda maudhu'in ya haifar da tambayoyi mabambanta, musamman game da al'amarin rayuwa da mutuwa, duba da yanda idan aka cire "Na'urar samar da karsashi" (I. C. U), daga jikin wanda ake ba shi karsashin yake rasa rayuwarsa, da duba da rashin bayyanar fuskoki masu yawa na wannan maudhu'i,

Duba da irin yanda ƙungiyar Musulunci mai kula da ilimin likitanci da take ƙasar Kuwait ta gudanar da cikakken bincike game da wannan maudhu'in, wanda dole ne a koma zuwa gare ta, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Jinkirta fitar da maganar ƙarshe game da wannan maudhu'in zuwa taron shekara- shekara na cibiyar mai zuwa([1]).

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 1/ 383)

- **Na biyu:** Daura wa sakateriyar cibiya alhakin tattaro nazarce- nazarce, da kudurorin kungiyar Musulunci mai kula da ilimin likitanci da take kasar Kuwait ta yi, da gabatar wa mambobin cibiya da cikakken bayani a taikaice da yake bayyana abin da suka kunsa.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Duba: Kuduri mai lamba 17(5/3).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 8 (8/2)([1])
GAME DA TAMBAYOYIN BANKIN MUSULUNCI MAI LURA DA AYYUKAN RAYA ƘASA (IsDB)([2])

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan ta saurari bayanin da bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) ya gabatar, mai ƙunshe da wasu tambayoyi, da neman ƙarin haske, da nufin a bayar da fatawa game da su,

Bayan ta saurari rahoton ƙaramin kwamitin da aka kafa a lokacin taron shekara- shekara da ya ƙunshi masu girma mambobin da suka shiga gaba wajen bayar da amsa game da mas'alolin da aka yi tambaya akansu, da ma waɗanda aka ƙara haɗuwa da su,

Ganin cewa wannan maudhu'in yana buƙatar nazari mai faɗi kuma cikakke, ya sanya dole ne a sake tuntuɓar bankin a tattauna da shi akan sassan mabambanta nasa a kwamitin da shi ne zai kafa ta ɓangarensa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Jinkirta wannan maudhu'i zuwa taron shekara- shekara mai zuwa([1]).

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 1/ 383)
([2]) Islamic Development Bank

- **Na biyu:** Neman bankin da ya gabatar da rahoton da hukumar kula da Shari'a na bankin ya gabatar.

Allah ya sa mu dace;;

(1) Duba: Kuduri mai lamba 13 (1/3).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 9 (9/2)([1])
GAME DA INSHORA DA DAWO DA INSHORA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan bibiyan jawabin da malaman da suka halarci taron shekara- shekara akan inshora da dawo da inshora,

Bayan an yi muhawara akan nazarce- nazarcen da aka gabatar,

Bayan an zurfafa bincike akan sauran surori da nau'o'insa, da kuma ƙa'idojin da ya ginu akansu, da manufofin da yake son cimma,

Bayan lura da bayanan da manyan cibiyoyin Fiḳihu da hukumomin ilimi suka fitar game da wannan al'amari, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Lallai ƙulla inshora ta kasuwanci da take da tabbataccen kaso, wanda kamfanonin inshoran kasuwanci suke mu'amala da shi yana da garari mai yawa da yake kai wa zuwa ga ɓata ƙulla inshoran kanta. Saboda haka, wannan haramun ne a Shari'ance.
- **Na biyu:** Lallai yarjejeniyar da za ta kwafe makwafinta, wadda kuma za ta mutunta tushen

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/ 545)

mu'amala a Musulunci ita ce ƙulla inshora ta taimakekeniya; wadda ta ginu akan harsashen bayar da taimako da taimakekeniya, haka ma abin yake a ɓangaren dawo da inshora wadda ta ginu akan harsashen inshoran taimakekeniya.

- **Na uku:** Kiran ƙasashen Musulmai zuwa ga yin aiki tuƙuru wajen kafa hukumomin inshora na taimakekeniya, da ma hukumomin taimakekeniya wajen dawo da inshora, saboda tattalin arzikin ƙasashen Musulmai ya samu ya 'yantu daga barin yin amfani da shi ba ta hanyar da ta dace ba, ya kuma kuɓuta ga barin saɓa wa tsarin da Allah ne ya zaɓar wa wannan al'umma.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 10 (10/2)([1])
GAME DA MU'AMALA DA ƘARIN DA BANKUNA SUKE YI DA HUKUNCIN MU'AMALA DA BANKUNAN MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan bincike mabambanta da aka gabatar akan mu'amala da bankuna a wannan zamanin,

Bayan lura da abubuwan da aka gabatar, da kuma tattaunawa akansa da ya kai zuwa ga fito da mummunan tasirin da wannan mu'amala take haddasawa a tsarin tattalin arzikin duniya, da zaman lafiyar tsarin, musamman a ƙasashe masu tasowa,

Bayan lura da abin da wannan tsari ya jawo na rusa rayuwa, sakamakon kawar da kai ga barin abin da ya zo a cikin littafin Allah na haramta kuɗin- ruwa (riba) ta kowace fuska, kuma a bayyane ƙarara, da har ya kai ga kira zuwa ga tuba akan abin da ya faru a baya, da kuma taƙaita akan dawo da uwar kuɗin bashin, ba tare da ƙari,

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/735 da 813)

ko tawaya, kaɗan ko mai yawa ba, da kuma tsoratarwar da ya zo na yin yaƙi mai halakarwa da Allah da Manzonsa za su yi da masu bayar da kuɗin ruwa (riba), **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Lallai duk wani ƙari, ko fa'ida akan bashin da lokacin biyansa ya yi, wanda ake bi bashin kuma ya gaza wajen biya, inda za a yi masa ƙari saboda ƙara masa lokaci da aka yi, haka ma ƙari, ko fa'ida akan bashi tun lokacin ƙulla yarjejeniyar bayar da bashin, duka waɗannan surori guda biyu riba ne da Shari'a ta haramta.
- **Na biyu:** Lallai makwafin da zai samar da lamunin hada- hadar kuɗi, da kuma ƙara wa tsarin tattalin arziki nishaɗi daidai da surar da Musulunci ya amince da shi, shi ne gudanar da mu'amala akan hukunce-hukuncen Shari'a.
- **Na uku:** Cibiyar ta bayar da umurnin ƙara ƙarfafa kiran hukumomin Musulunci zuwa ga ƙarfafar bankunan Musulunci da suke aiki da Shari'ar Musulunci, da bayar da daman kafa su a dukan ƙasashen Musulmai, domin su biya buƙatun Musulmai, ta yanda Musulmi ba zai rayu a tsarin da ake samun cin- karo da juna tsananin halin da yake rayuwa da kuma abubuwan da ya yi imani da su ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 11 (11/2)([1])
GAME DA SAMAR DA HAƊIN- KAI WAJEN FARAWAR WATANNI ƘAMARIYYA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan an gabatar da binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar akan samar da haɗin- kai wajen farawar watannin Ƙamariyya,

Bayan tattaunawa mai faɗi, da kuma zurfi akan abubuwan da aka gabatar na wannan maudhu'i, da kuma sauraron ra'ayoyi masu yawa game da yin la'akari da ilimin Hisabi wajen tabbatar da farawar watanni Ƙamariyya, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Ɗaura wa sakateriyar Cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya alhakin samar da tabbatattun nazarce- nazarce da bincike daga ƙwararru, kuma amintattu a fannin ilimin Hisabin Falaki, da hasashen yanayin sararin samaniya.
- **Na biyu:** Sanya maudhu'in samar da haɗin kai wajen farawar watannin Ƙamariyya a cikin ajandar zama mai zuwa, domin kammala bincike akansa ta mahanga biyu, na ƙwarraru da na Fiḳihun Shari'ar Musulunci([2]).

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/839)
([2]) Duba: Ƙuduri mai lamba 18 (6/3).

- **Na uku:** Ɗaura wa sakateriya nauyin ɗaukan isasshen adadin ƙwararrun da aka ambata, saboda su haɗu su yi tarayya da malaman Fiƙihu wajen suranta wannan maudhu'i gaba ɗayansa, ta yanda za a samar da bayanin da zai kai zuwa ga bayyana hukuncin Shari'ar Musulunci.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 12 (12/2)([1])
GAME DA TAKARDAR LAMUNI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara- shekara, karo na biyu a garin Jidda, wanda ya gudana daga ranar 10 zuwa 16 ga watan Rabi'ul Akhir, 1406 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 zuwa 28 ga watan Disamba, 1985,

Bayan an duba bincike da nazarce- nazarcen da aka gudanar game da takardar lamuni, bayan an gabatar da cikakkiyar tattaunawa akansu, wanda a tattaunawar aka gano cewa:

- **Na farko:** Lallai dukan nau'o'in takardar lamuni, na share fage, da na ƙarshe ba za su fita daga: ko dai ta zamo akwai wani abu da yake mara mata baya, ko kuma babu wani abu da yake mara mata baya ba, idan babu wani abu da yake mara mata baya, to ta zamo: Haɗa zimmar mai bayar da lamuni da zimmar waninsa akan abin da zai hau kansa a yanzu, ko a nan gaba, wannan shi ne ma'anar da ake kira a cikin Fiḳihun Musulunci da sunan: Lamuni ko "Kafala".

  Idan kuma takardar lamunin tana da wani abu da yake mara mata baya, to dangantakar da take tsakanin takardar lamunin da wanda yake bayar da lamunin ita ce: wakilci "al-wakala", shi kuwa wakilci ya halatta a

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/1035)

yi shi da lada, ko kuma kyauta ba tare da lada ba, inda dangantakar wakilcin za ta cigaba da zama amfani ga wanda aka wakilta.

- **Na biyu:** Lallai kafala yarjejeniya ce da ake yi ba tare da an biya komai ba, manufa ita ce taimako da kyautatawa. Malaman Fiƙihu sun bayyana cewa bai halatta mai kafala ya karɓi komai a matsayin lada ba, saboda a lokacin da kafili zai amshi kuɗin lamuni daidai yake da wanda ya bayar da bashin da ya jawo masa riba, wannan kuwa abu ne da Shari'a ta hana.

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** Lallai bai halatta a amshi lada idan an bayar da takardar lamuni domin yi wa mutum lamuni ba – wanda a al'adance ake kulawa da yawan kuɗin, da kuma tsawon lokacin bayar da lamunin- shin akwai abin da yake mara masa baya, ko babu.
- **Na biyu:** Amsar kuɗaɗen da ofis yake yi kafin fitar da dukan nau'o'in takardar lamuni ya halatta a Shari'ance, amma dole ne a yi la'akari da cewa kada kuɗin ya zarta ƙimar irin wannan aiki, idan kuma an sami abin da zai mara masa baya na gaba ɗaya, ko a wasu sassa, ya halatta a wurin ƙaddara kuɗin fitar da takardar lamunin a kula da ayyukan da za a gabatar a aikace wajen wannan mara baya ɗin.

Allah shi ne mafi sani;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA UKU NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

AMMAN (JORDAN)
8 -13 GA WATAN SAFAR, 1407 H
11 – 16 GA WATAN OKTOBA, 1986

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 13 (1/3)([1])
GAME DA TAMBAYOYIN BANKIN MUSULUNCI MAI LURA DA AYYUKAN RAYA ƘASA (IsDB)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan nazari da tattaunawa masu zurfi, da kuma fadi akan dukan tambayoyin da Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) ya gabatar wa Cibiyar, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

(a) Game da abin da ya shafi ladan hidimomin bayar da bashi a Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB):

- **Na farko:** Ya halatta a karɓi ladan hidimomin bayar da bashi, da sharaɗin kada ladan yake ƙetare haƙiƙanin hidimomin da aka gabatar.
- **Na biyu:** Duk wani ƙari akan ladan hidimomin da aka gabatar a aikace haramun ne, domin yana cikin kuɗin-ruwa (riba) wanda Shari'a ta haramta.

(b) Game da ayyukan bayar da haya:

- **Na farko:** Lallai alƙawarin da Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) yake yi na bayar da hayar kayan aiki ga abokin huldа, bayan Bankin ya

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/527); da (Fitowa ta uku, 1/77)

mallaki kayan aikin, abu ne da Shari'a ta amince da shi.

- **Na biyu:** Lallai wakilcin da Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) yake bai wa ɗaya daga cikin abokan hulɗarsa na saya wa Bankin abubuwan da shi abokin hulɗar yake buƙata na kayan aiki da makamantansu, waɗanda an riga an san sifofinsu, da kuma kuɗinsu, da nufin Bankin ya ba shi haya bayan kayan sun shiga hannun wakili, wannan wakilci ne da Shari'a ta amince da shi, sai dai abin da ya fi kyau shi ne: a wakilta wanin abokin hulɗar ba wannan da aka ambata za a ba shi hayar ba, idan har akwai yiwuwar haka.
- **Na uku:** Lallai dole ne ƙulla yarjejeniyar bayar da haya ya zamo bayan an sami cikakkiyar mallakar kayan aikin, a kuma ƙulla yarjejeniyar a gefe ba a haɗe da yarjejeniyar wakilci da alƙawarin bayar da hayar ba.
- **Na huɗu:** Lallai yin alƙawarin cewa za a bar wa mai hayan kayan aikin kyauta idan lokacin hayar ya ƙare ya halatta, amma ya zamo da sabon yarjejeniya ne ba a cakuɗe ba.
- **Na biyar:** Lallai rasa kayan hayar, ko samun aibi a ciki alhaki ne da Bankin zai ɗauka a matsayinsa na mai mallakan kaya, muddin ba wanda aka ba shi hayar ne da gangan ya halaka, ko kuma rashin kulawar da ta dace ya jawo haka ba, a irin wannan hali shi ne zai ɗauki alhakin haka.
- **Na shida:** ya kamata Bankin ya ɗauki nauyin biyan kuɗin inshora na kamfanonin Musulunci, in zai yiwu.

(c) Game da aikin sayar da kaya zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya (Installment sales):

- **Na farko:** Lallai alƙawarin da Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) yake yi na sayar da kayan aiki ga abokin hulɗarsa, bayan Bankin ya

mallaki kayan aikin, abu ne da Shari'a ta amince da shi.

- **Na biyu:** Lallai wakilcin da Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) yake bai wa ɗaya daga cikin abokan hulɗarsa na saya wa Bankin abubuwan da shi abokin hulɗar yake buƙata na kayan aiki da makamantansu, waɗanda an riga an san sifofinsu da kuma kuɗinsu, da nufin Bankin ya sayar masa da waɗannan kayan bayan sun shiga hannun wakili, wannan wakilci ne da Shari'a ta amince da shi, sai dai abin da ya fi kyau shi ne: a wakilta wanin abokin hulɗar ba wannan da aka ambata za a sayar masa da kayan ba, idan har akwai yiwuwar haka.
- **Na uku:** Lallai dole ne ƙulla yarjejeniyar sayarwar ta zamo bayan an sami cikakkiyar mallakar kayan aikin, a kuma amshe su a hannu, a kuma ƙulla yarjejeniyar a gefe ba a haɗe da yarjejeniyar wakilci da alƙawarin sayarwa ba.

(d) Game da bayar da kuɗin ƙarfafa kasuwancin ƙetare:

Ƙa'idojin da ake aiki da su wajen aikin sayar da kaya zuwa wani lokaci, tare da rarraba lokacin biya (Instalment sales) su ne dai za a yi aiki da su a nan.

(e) Game da yanda za a yi da fa'idojin ajiya da ya zama dole Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) ya kai ajiyarsu a bankunan ƙetare:

Haramun ne Bankin ya kare haƙiƙanin ƙimar kuɗinsa daga tasirin tangal- tangal ɗin farashin kuɗaɗe ta hanyar fa'idojin da ya samu ta hanyar ajiya. Saboda haka dole ne a yi amfani da waɗannan fa'idojin a abin da zai amfani kowa da kowa, kaman bayar da horaswa, da gudanar da bincike, da samar da hanyoyin bayar da tallafi da taimako, da samar da taimakon kuɗi ga ƙasashen da suke mambobi ne, da gabatar masu da taimakon kayan aiki, haka ma da cibiyoyin ilimi da makarantu, da duk wani fage da yake da jiɓi da yaɗa ilmomin Musulunci.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 14 (2/3)([1])
GAME DA ZAKKAR HANNUN- JARI A KAMFANONI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan tattaunawa akan maudhu'in zakkar hannun- jari a kamfanoni ta dukan fuskokinsa, da kuma duba binciken da aka gabatar game da wannan al'amari, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Jinkirta fitar da ƙudurin da ya shafi wannan al'amari zuwa taron majalisar na shekara- shekara karo na huɗu([2]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 3/705).
([2]) Duba: Ƙuduri mai lamba 28 (3/4).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 15 (3/3)([1])
GAME DA YIN AMFANI DA KUƊIN ZAKKA A MANYAN AYYUKA DA SUKE SAMAR DA RIBA BA TARE DA AN MALLAKA SU GA MUTUM ƊAYA CIKIN WAƊANDA SUKA CANCANTA BA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar akan maudhu'in yin amfani da kuɗin zakka a manyan ayyukan da suke samar da riba, ba tare da an mallaka su ga mutum ɗaya cikin waɗanda suka cancanta ba, bayan majalisar Cibiyar ta saurari ra'ayoyin mambobi da ƙwararrunta, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- A asali ya halatta a yi amfani da dukiyar zakka a manyan ayyukan zuba jari da a ƙarshe suke zamowa mallaka ga waɗanda suka cancanci cin zakka, ko ya zamo yana ƙarƙashin hukuma ta Shari'a da alhakin tara zakka, da raba ta yake hannunta, da sharaɗin cewa hakan ya kasance ne bayan an biyan buƙatun gaggawa na waɗanda suka cancanci cin zakka, a

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta uku, 1/309).

kuma sami cikakken lamunin cewa ba za a yi asara ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 16 (4/3)([1])
GAME DA JARIRAN KWALBA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar akan maudhu'in jariran kwalba (Artificial Insemination), da sauraron sharhin da ƙwararru, da likitoci suka gabatar,

Bayan tattaunawa, majalisar cibiyar ta gano cewa: akwai hanyoyi guda bakwai da ake samar da jariran kwalba (Artificial Insemination) a wannan zamanin, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko: Shari'a ta haramta hanyoyi guda biyar masu zuwa, ta kuma hana su kwata – kwata saboda su kansu hanyoyin, ko saboda abin da suke haifarwa na: cakuɗa nasaba, da tozartar da matsayin uwa, da sauransu cikin abubuwan da Shari'a ta hana:**
  - **Na farko:** A gwana tsakanin miniyyin da aka ɗauko daga miji, da ƙwayayen da aka ɗauko daga matar da ba tasa ba, sannan a shigar da su a cikin mahaifar matarsa.

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta uku, 1/423).

- **Na biyu:** A gwama tsakanin miniyyin da ba na mijinta ba da ƙwayayen matar, sannan a shigar cikin mahaifar matar.
- **Na uku:** A gwama tsakanin maniyyin miji da ƙwayayen matarsa a waje, sannan a shigar cikin mahaifar wata matar da ta yarda ta ɗauka.
- **Na huɗu:** A gwama tsakanin maniyyin wani namiji na daban da ƙwayayen wata matar ta daba na waje, sannan a sanya a cikin mahaifar matar.

- **Na biyar:** A gwama tsakanin miniyyin miji da ƙwayayen matarsa a waje, sannan a shigar cikin mahaifar wata mata ta daban.
- **Na biyu: Babu laifi idan aka yi amfani da hanyoyi na shida da na bakwai idan akwai tsananin buƙata, tare da tabbatar da cewa dole ne a ɗauki duk wani matakin da hakan yake buƙata:**
  - **Na shida:** A ɗauko maniyyin miji da ƙwayayen matarsa, a haɗa su a waje, sannan a shigar da shi cikin mahaifar matar.
  - **Na bakwai:** A ɗauko maniyyin miji, a sanya shi a wurin da ya dace a al'aurar matar ta hanyar allura, ko a mahaifarta ta ciki.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 17 (5/3)([1])
GAME DA NA'URAR SAMAR DA KARSASHI (I.C.U)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan tattaunawar da ta gudanar a sauran sassan da aka taɓo game da maudhu'in: Na'urar samar da karsashi, bayan sauraron sharhi mai zurfi da likitoci ƙwararru suka gabatar, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

Shari'a tana kallon mutum ya rasu, kuma dukan hukunce- hukuncen da ta tanadar waɗanda suke biyo bayan rasuwa sun tabbata a lokacin ne, idan ɗaya daga cikin alamomi guda biyu masu zuwa ta tabbata:

1- Idan zuciyarsa da numfashinsa suka tsaya gaba ɗaya, likitoci kuma suka bayyana cewa lallai wannan tsayawa ce da ba za su dawo su cigaba da aiki ba.

2- Idan dukan ayyukan da ƙwaƙwalwa take yi suka tsaya kwata- kwata, likitoci ƙwararru kuma suka bayyana cewa lallai wannan tsayawa ce da ba za ta dawo ta cigaba da aiki ba, ƙwaƙwalwar kuma ta fara zuganyewa.

A irin waɗannan yanayi za a iya cire na'urar samar da karsashin da aka sanya wa mutumin, koda kuwa wasu

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyu, 2/523).

daga cikin gaɓoɓi –kaman zuciya- suna aiki sakamakon na’urar da aka sanya masa.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 18 (6/3)([1])
GAME DA SAMAR DA HAƊIN- KAI WAJEN FARAWAR WATANNI ƘAMARIYYA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta bijiro da maudhu'in samar da hadin- kai wajen farawar watannin Ƙamariyya, a matsayin mas'aloli guda biyu:

- **Na farko:** Irin tasirin da mahuda wata take da shi wajen hada lokacin farawar watanni.
- **Na biyu:** Hukukuncin tabbatar da farawar watanni Ƙamariyya ta hanyar ilimin Hisabin Falaki.

Bayan ta saurari binciken da mambobi da ƙwararrunta suka gabatar game da wannan mas'alar, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Idan an tabbatar da ganin wata a wani gari, dole ne Musulmai su yi aiki da shi, ba a la'akari da saɓanin mahuda wata; saboda Nassin da ya bayar da umurnin yin azumi, da shan ruwa Nassi ne da ya game kowa da komai.
- **Na biyu:** Wajibi ne a dogara da gani da ido, za a iya neman taimakon ilimin Hisabin Falaki da na sararin

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta uku, 2/811).

samaniya, za a yi haka ne saboda muhimmanta Hadisan Annabi, da abubuwan da ilimi ya tabbatar.

Allah shi ne **mafi sani;;**

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 19 (7/3)([1])
GAME DA ƊAUKAN HARAMIN MAHAJJACI DA MAI UMURAN DA SUKA ZO TA JIRGIN- SAMA KO JIRGIN ƘASA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar game da maudhu'in ɗaukan haramin wanda ya zo yin aikin hajji da umura ta hanyar jirgin sama, ko jirgin ƙasa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Lallai wajibi ne a ɗauki harami a wuraren da Hadisan Annabi masu daraja suka tabbatar ga duk wanda yake da niyyar gabatar da aikin hajji, ko umura, idan ya bi ta wurin a ƙafa, ko in ya ƙetare daidai wurin ta ƙasa, ko ta sararin samaniya, ko ta kogi; saboda umurnin da ɗaukan harami da ya zo a cikin Hadisan Annabi masu daraja, umurni ne gamamme.

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta uku, 3/1419).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 20 (8/3)
GAME DA BAYAR DA ZAKKA GA ASUSUN MUSULUNCI NA BAYAR DA TALLAFI DA TAIMAKON GAGGAWA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta saurari jawabin mataimakin sakataren ƙungiyar ƙasashen Musulmai akan maudhu'in: ayyukan da Asusun Musulunci na bayar da tallafi da taimakon gaggawa, da irin yanda asusun yake matuƙar buƙatar taimako na kuɗi, da shawarar da ya kawo na ya zamo hanya ɗaya daga cikin hanyoyin da za a ba su zakka, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Ɗaura wa sakateriyar cibiyar alhakin samar da nazari da binciken da ake buƙata wurin sanin wannan maudhu'in, tare da taimakekeniya da Asusun Musulunci na bayar da tallafi da taimakon gaggawa, a kuma gabatar da wannan nazari a taron majalisar cibiyar na shekara- shekara mai zuwa([1]).

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba: 27 (2/4).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 21 (9/3)([1])
GAME DA HUKUNCE- HUKUNCEN TAKARDUN KUƊAƊE DA SASSAUYARWAR DARAJAR KUƊI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in hukunce- hukuncen takardun kuɗaɗe, da sassauyawar darajar kuɗi, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko: Game da hukunce – hukuncen tarkadun kuɗaɗe:** Lallai kuɗi ne da ake la'akari da shi, tana da cikakkiyar sifar da kuɗi yake da ita, tana da dukan hukunce- hukuncen da aka tabbatar wa zinare, da azurfa a wurin hukunce- hukunce: riba, da zakka, da salam, da sauran hukunce- hukuncensu.
- **Na biyu: Game da sassauyawar darajar kuɗi kuwa:** An jinkirta duba wannan mas'alar har zuwa lokacin da za a gudanar da cikakken nazari ta dukan fuskokinsa, inda za a duba a taron shekara- shekara karo na huɗu da majalisar take gudanarwa.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiyar (Fitowa ta uku, 3/1650); da (Fitowa ta biyar, 3/1609).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 22 (10/3)([1])
GAME DA SHAHADUN MALLAKAR BASHI (CREDIT BOND) DA SHAHADUN MALLAKAR KASUWANCI (INVESTMENT BOND)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar akan maudhu'in: Shahadun mallakar bashi (Credit Bond) da Shahadun mallakar kasuwanci (Investment Bond) ta kuma saurari tattaunawar da aka yi akansa,

A cigaba da tsarin cibiyar na wajibcin samar da nazari masu yawa akan maudhu'i guda ɗaya,

Lura da muhimmancin wannan maudhu'in, da kuma wajibci kammala bincike a dukan fuskokinsa, da kuma cika dukan bayanansa dalla- dalla, da sanin duka ra'ayin da aka faɗi akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- An ɗaura wa sakateriya alhakin umurtar wadanda ta ga sun dace da su gudanar da bincike akansa, saboda cibiyar ta sami damar ɗaukan ƙudurin da ya dace a taronta na shekara- shekara karo na huɗu([2]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiyar (Fitowa ta huɗu, 3/1809).
([2]) Duba: Ƙuduri mai lamba 30 (5/4).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 23 (11/3)([1])
GAME DA TAMBAYOYIN DA CIBIYAR TUNANIN MUSULUNCI TA DUNIYA DA TAKE WASHINGTON, D.C.

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan ta duba tambayoyin da Cibiyar tunanin Musulunci ta duniya da take Washington D.C, da amsoshin da aka samar ta hanyar mambobi da ƙwararrun cibiyar, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- An ɗaura wa sakateriyar cibiyar alhakin isar wa da Cibiyar tunanin Musulunci ta duniya da take Washington D.C da amsoshin da majalisar ta tabbatar da su.

Da sunan Allah mai yawan rahama da jinkai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

AMSOSHIN DA CIBIYAR TA TABBATAR DA SU GAME DA TAMBAYOYIN DA AKA YI([2])

([1]) Mujallar Cibiyar (Fitowa ta uku, 2/1087); da (Fitowa ta biyu, 1/199).

([2]) An dakatar da ɗaukan ƙuduri akan tambayoyi: 1, 2, 7, 15, 22.

- **Tambaya Ta Uku:** Mene ne hukuncin mace Musulma ta auri wanda ba Musulmi ba, musamman idan tana kwaɗayin ya Musulunta bayan auren, saboda da yawa daga cikin mata Musulmai ba sa samun wanda ya dace da ya aure su a cikin Musulmai a mafi yawan lokuta, kuma suna fuskantar barazanar yiwuwar kauce hanya, ko kuma su rayu cikin matsananciyar damuwa?
- **Amsa:** Alƙur'ani, da Hadisan Annabi, da Ijma'in malamai sun hana aure tsakanin mace Musulma, da wanda ba Musulmi ba. Idan har ma an yi, to auren ɓatacce ne, babu wani abu na shari'a da yake biyo bayan aure da zai tabbata a ciki, 'ya'yan da aka haifa ta wannan aure ba 'ya'yan halal ba ne. Kwaɗayi, ko fatan mazaje za su Musulunta ba zai sauya komai a cikin wannan hukunci ba.
- **Tambaya Ta Huɗu:** Mene ne hukuncin cigaba da zaman aure tsakanin matar da ta amshi Musulunci, mijinta kuma ya cigaba da zama a kafirci, tana da 'ya'ya tare da shi da take tsoron kada su tozarta, su kauce hanya, tana kuma kwaɗayin shi kansa mijin ya Musulunta idan igiyar auren ta cigaba da kasancewa a tsakaninta da shi?

Kuma yaya hukuncin zai kasance idan ba ta kwaɗayin ya shiga Musulunci, amma dai yana kyautata mata, tana kuma tsoron idan ta bar shi ba za ta sami Musulmi ta aura ba?

- **Amsa:** Da zarar mata ta Musulunta, shi kuma miji ya ƙi ya Musulunta za a raba aure a tsakaninsu, bai halatta ya kwanta da ita ba, amma tana da damar ta jira lokacin idda, idan ya Musulunta a tsakanin lokacin, sai ta dawo masa ba tare da ɗaura sabon aure ba. Amma ida lokacin idda ya wuce bai Musulunta ba, aure ya yanke tsakaninsu. Idan ya Musulunta –bayan ta gama idda- suka ku yi sha'awar dawo da aurensu, za su iya dawo da shi ta hanyar sake sabon ɗaura aure. Abin da aka

kira kyautatawa a rayuwar aure ba shi da tasiri wajen halatta cigaba da zaman aure.

- **Tambaya Ta Biyar:** Mene ne hukuncin rufe Musulmi a maƙabartar da ba ta Musulmai ba, ganin cewa ba a yarda a rufe wani a wajen maƙabartar da aka samar domin rufe mamata ba, su kuma Musulmai ba su da keɓantacciyar maƙabarta tasu a mafi yawan jahohin Amurika da yankin ƙasashen Turai?
- **AMSA:** Lallai rufe Musulmi a maƙabartar da ba ta Musulmai ba, a ƙasashen da ba na Musulmai ba ya halatta a halin lalura.
- **Tambaya Ta Shida:** Mene ne hukuncin sayar da Masallaci idan Musulmai sun tashi daga yankin da yake, suka kuma ji tsoron kada ya salwanta, ko wasu su yi kaka- gida akansa? Sau da yawa Musulmai sukan sayi gida ne, sai su mayar da shi Masallaci, idan mafi yawan Musulman suka tashi daga yankin, ko unguwar saboda yanayin aiki, sai a ƙaurace wa Masallacin, ko a wofintar da shi, ta yiwu wasu ne za su zo su yi kaka-gida akansa. Zai yiwu a sayar da shi a sayi wani wurin a wurin da yake akwai Musulmai a mayar da shi Masallaci. Mene ne hukuncin sayar da shi, ko musanya shi da wani? Idan kuma ba a sami daman sauya shi ta hanyar samar da wani Masallacin ba, wace hanya ce ta fi dacewa da a shigar da kuɗin Masallaci a ciki?
- **Amsa:** Ya halatta a sayar da Masallacin da aka dakatar da amfani da shi, ko Musulmai suka yi ƙaura daga wurin da yake, ko aka ji tsoron kada kafirai su yi kaka-gida akansa, da sharaɗin a sayi wani wajen da za a mayar da shi Masallaci da kuɗin.
- **Tambaya Ta Takwas:** Wasu mata, ko ‘yan mata suna samun kansu a cikin wani yanayi na aiki, ko na karatu da zai tilasta masu su zauna su kaɗai, ko tare da mata waɗanda ba Musulmai ba, mene ne hukuncin irin wannan zama?

- **Amsa:** A Shari'ar Musulunci bai halatta mace Musulma ta zauna ita ɗaya a gari, ko ƙasar da take a matsayin baƙuwa ba.
- **Tambaya Ta Tara:** Mata da yawa a nan, suna cewa ƙarshen abin da suke da daman su suturta a jikinsu shi ne: fuska, da tafukan hannaye, wasu daga cikinsu ma wuraren ayyukansu suna hana su suturta kawunansu, mene ne ƙarshen abin da Shari'a ta amince da a bayyana shi a sassan jikin mace tsakanin waɗanda ba muharramanta ba a wuraren aiki, ko a makarantu?
- **Amsa:** Lallai hijabin mace Musulma – a wurin jamhur ɗin malamai- shi ne rufe gaba ɗayan jikinta, banda fuska, da tafukan hannaye, idan ba ta ji tsoron fitinar wasu ba, amma idan ta ji tsoron kada wasu su fitinu dole ne su ma ta rufe su.
- **Tambaya Ta Goma Da Ta Goma Sha Ɗaya:** Da yawa daga cikin ɗalibai Musulmai a waɗannan ƙasashen sukan sami kawunansu a yanayin da zai sa dole su nemi aiki; saboda su samu su biya kuɗin makaranta, da kuma gudanar da rayuwa, saboda abin da iyayensu suke aiko masu ba ya isan da yawa daga cikinsu, abin da yake sanya tilas su nemi aiki, ba za su iya rayuwa ba tare da aiki ba, sau da yawa kuma ba sa samun aiki sai a gidajen siyar da abinci da suke sayar da giya, ko suke gabatar da abinci da naman alade da sauransa cikin abubuwan da haramun ne, mene ne hukuncin yin aiki a irin waɗannan shaguna?

Mene ne hukuncin Musulmi ya sayar da giya, da alade, ko ya sana'anta giya ya sayar wa waɗanda ba Musulmai ba? Musamman ganin cewa wasu daga cikin Musulmai sun ɗauki haka a matsayin sana'a.

- **Amsa:** Idan Musulmi bai sami halattaccen aiki da Shari'a ta amince da shi ba, yana da daman ya yi aiki a gidajen abincin kafirai, da sharaɗin: kada ya zamo da kansa ne yake zuba wa mutane giyar, ko ya ɗauke ta, ko ya yi kasuwanci da ita, haka ma hukuncin yake game

da gabatar wa jama'a da naman alade da makamantan haka cikin abubuwan da aka haramta.

- **Tambaya Ta Goma Sha Biyu:** Akwai magunguna masu yawa da suke ɗauke da mabambanta nau'o'in sinadarin alkahol tsakankanin ƙimar: 0.01% da 25% a mafi yawancin magungunan: mura, da maƙaƙin maƙogoro, da tari da sauransu ne cikin sanannun cututtuka. Za a iya cewa waɗannan magunguna tamkar wata kwasfa ce ta sinadarin alkahol da ya kusan kai kashi 95% na magungunan da ake da su a wannan fage, abin da ya sanya samun magungunan da babu sinadarin alkahol a cikinsu abu ne mai matuƙar wahala, ko ma ba zai yiwu a samu ba, mene ne hukuncin yin amfani da waɗannan magungunan?
- **Amsa:** Mara lafiya yana da daman yin amfani da magungunan da suke ɗauke da wani kimmiyya na sinadarin alkahol, idan bai sami magungunan da babu alkahol a cikinsu ba, ya kuma zamana wanda ya rubuta maganin likita ne amintacce akan aikinsa.
- **Tambaya Ta Goma Sha Uku:** Akwai wasu nau'o'i na "yis" (Yeasts) da "gilatin" (Gelatin) da ake samun su daga fatar alade, sai dai kaɗan ne ƙwarai, shin ya halatta a yi amfani da waɗannan "yis" (Yeasts) da "gilatin" (Gelatin) ɗin kuwa?.
- **Amsa**: Bai halatta Musulmi ya yi amfani da "yis" (Yeasts) da "gilatin" (Gelatin) ɗin da aka samo su daga aladu ba a cikin abinci, lallai makwafinsu wanda shi ne "yis" (Yeasts) da "gilatin" (Gelatin) ɗin da aka samo su daga tsirrai, ko dabbobin da akan yi masu yanka ta Shari'a sun wadatar.
- **Tambaya Ta Goma Sha Huɗu:** Mafi yawan Musulmai suna samun kawunansu a yanayin da za su gudanar da bikin 'ya'yansu mata a Masallatansu, sau da yawa kuma ana samun raye- raye, da kiɗe- kiɗe, da waƙe-waƙe a wurin waɗannan bukukuwa, babu kuma wuraren da za su isa a gabatar da ire- iren waɗannan

bukukuwa a waje, mene ne hukuncin gudanar da waɗannan bukukuwa a cikin Masallatai?

- **Amsa:** An so a ɗaura aure a cikin Masallatai, bai halatta a gudanar da bukukuwa a cikinsu ba idan akwai abubuwan da Shari'a ta hana, kaman cakuɗeɗeniya tsakanin maza da mata, ko akwai bayyana tsaraici, da rawa, da waƙa.
- **Tambaya Ta Goma Sha Shida:** Mene ne hukuncin auren ɗalibi, ko ɗaliba da ba a yi niyyar ya dawwama ba, hasali ma an riga an ɗaura niyyar cewa da zaran an kammala karatu da ɗaukan harmar komawa zuwa gida na dindindin za a kawo ƙarshen auren, sai dai an saba akan ƙulla ɗaurin auren ne kaman yanda aka saba, da sigar da ake ɗaura auren da ake yi da niyyar dawwama, mene ne hukuncin irin wannan aure?
- **Amsa**: Asali a aure shi ne cigaba da wanzuwa da dawwama, da samar da iyali mai cike da kwanciyar hankali, matuƙar ba wani abu ne ya bijiro da zai kawo ƙarshensa ba.
- **Tambaya Ta Goma Sha Bakwai:** Mene ne hukuncin bayyanar mace a shagunan aiki, ko makarantu bayan ta aske gashin gira, ta kuma sanya tozali?
- **Amsa:** Sanya tozali ga namiji da mace ya halatta a Shari'ance. Shi kuwa aske gashin gira bai halatta ba, sai idan gashin girar ya lalata halittar macen.
- **Tambaya Ta Goma Sha Takwas:** Wasu daga cikin mata Musulmai suna samun kawunansu a cikin damuwa sakamakon rashin gaisawa hannu da hannu da mazan da ba muharramansu ba ne da suke zuwa wuraren da suke aiki, ko makarantun da suke koyarwa, hakan sai ya sanya su gaisa da maza hannu da hannu saboda kaucewa wannan damuwar, mene ne hukuncin yin irin wannan musafaha?

  Haka ma abin yake a tare da Musulmai maza masu yawa da matan da ba muharramansu ba suke miƙa

masu hannun wajen gaisawa, idan kuma suka ƙi amsa masu suna shiga cikin damuwa matuƙa, kaman yanda duka maza da matan suke fadi?

- **Amsa:** Gaisuwa namiji da macen da ba muharramiyarsa ba, kuma balagaggiya hannu da hannu haramun ne a Shari'ar Musulunci, haka ma akasin haka.
- **Tambaya Ta Goma Sha Tara:** Mene ne hukuncin yin hayar Coci- coci a matsayin wuraren yi salloli biyar, ko sallar Juma'a da na Idi ƙarama da babba, duk kuwa da akwai mutum- mutumi da ba kasafai ake rasa Coci- coci da su ba.. hayar Coci- coci a wurin Kiristoci –a mafi yawan lokuta- ya fi sauƙi akan sauran wurare, wasu ma jami'o'i, ko ƙungiyoyin bayar da tallafi da jinƙai ne suka bayarwa; domin a yi amfani da su a lokuta na musamman ba tare da an biya su ba?
- **Amsa:** Shari'a ba ta hana a hayi Coci domin gudanar da sallah ba, idan hakan ya zamo a hali ne na lalura, sai dai dole ne a nesanci wurin mutum- mutumi da hotuna a lokacin sallah, a rufe su da ƙyalle idan suna sashen alƙibla ne.
- **Tambaya Ta Shirin:** Mene ne hukuncin dabbobin da Ahlul Kitabi na Yahuduwa da Kiristoci suka yanka, da abubuwan da suke gabatarwa a gidajen abincinsu, duk kuwa da cewa an san ba su ambaci sunan Allah a lokacin yankar ba?
- **Amsa:** A Shari'a cin yankar Ahlul kitabi ya halatta, idan sun yanka ne ta hanyar da Shari'a ta amince da ita, koda kuwa ba su ambaci sunan Allah ba a lokacin yankar. Cibiyar tana bayar da umurnin ƙara bincike mai zurfi game da wannan maudhu'in a gabatar mata da shi a taron shekara- shekara mai zuwa([1]).
- **Tambaya Ta Ashirin Da Ɗaya:** A tarurruka masu yawa da suka shafi kowa da kowa da ake gayyatar Musulmai su halarta, ana gabatar da giya, ana kuma samun

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 95 (3/10) rukuni na shida da mai biye masa

cakuɗuwa tsakanin mata da maza, ƙaurace wa irin waɗannan bukukuwa da wasu daga cikin Musulmai suke yi zai iya sanyawa a mayar da su saniyar- ware a cikin al'ummar da suke rayuwa, zai kuma sanya su rasa wasu fa'idoji da ake samu.

Mene ne hukuncin halartar ire- iren waɗannan bakukuwa, ba tare da an yi tarayya da su wajen shan giya, ko raye- raye, ko cin naman alade ba?

- **Amsa:** Game da halartar bukukuwan da ake gabatar da giya, sam bai halatta ga Musulmi, ko Musulma su halarci tarurrukan da ake aikata saɓon Allah, da munkari ba.
- **Tambaya Ta Ashirin Da Uku:** Yana da wahala matuƙa, ko ma mu ce sam ba zai yiwu ido ya iya ganin watan Ramadhan, ko Shawwal ba a ƙasar Amurika, da ma yankin Turai, cigaban ilimin da yake a mafi yawan waɗannan ƙasashen yana bayar da daman sanin lokacin da aka haifi jinjirin wata, ta hanyar ilimi Hisabin Falaki, shin ya halatta a dogara da ilimin Hisabin Falaki a waɗannan ƙasashen?

Shin ya halatta a yi amfani da ilimin sanin yanayin sararin samaniya, da amsar maganar kafirai da su ne jagorori a waɗannan hukumomi, duk kuwa da cewa mafi rinjayen zato a mafi yawan abubuwan da suke faɗi game da waɗannan al'amurra gaskiya ne?

Ya kuma kamata a lura da cewa: irin yanda Musulmai a Amurika suke bin wasu daga cikin ƙasashen Musulmai na gabashin duniya wajen yin azumi, da shan ruwa yana haifar da saɓani mai yawa, sau da yawa ma hakan yakan kore muhimman fa'idojin da Idi yake samarwa, inda yake haifar da matsalolin da suke dawwama, idan an yi amfani da ilimin Hisabin Falaki za a sami abin da zai kawo ƙarshen wannan rikici a ganin wasu, ko kuma zai kusan kawo ƙarshensa.

- **Amsa:** Wajibi ne a dogara da gani da ido, a kuma nemi taimako daga ilimin Hisabin Falaki, da hukumomin da

suke lura da sararin samaniya, saboda la'akari da Hadisan Annabi, da haƙiƙar da ilimi ta tabbatar.

Idan an ga wata a gari ɗaya wajibi ne Musulmai su yi aiki da shi, ba a la'akari da saɓanin mahudar watan, saboda nassoshin da suka bayar da umurnin yin azumi, da shan ruwa gamammu ne([1]).

- **Tambaya Ta Ashirin Da Huɗu:** Mene ne hukuncin Musulmi ya yi aiki a ofisoshi, da ma'aikatu, da hukumomin ƙasar Amurika, ko wasu gwamnatocin da ba na ƙasashen Musulmai ba, musamman a fagage masu muhimmanci irinsu: sana'anta Nukiliya, ko nazarin akan tsare- tsare masu dogon zango da makamantansu?
- **Amsa:** Ya halatta Musulmi ya yi halattaccen aiki a hukumomi, da ma'aikatu, da gwamnatocin da ba na ƙasashen Musulmai ba ne, idan aikin nasa ba zai kai zuwa ga cutar da Musulmai ba.
- **Tambaya Ta Ashirin Da Biyar Da Ta Ashirin Da Shida:** Mene ne hukuncin Injiniya Musulmin da ya zana gine- ginen Kiristoci, kaman Coci – coci da sauransu, sai dai wannan wani sashe ne na aikinsa a kamfanin da yake aiki, idan ya ƙi zanawa hakan na iya kai wa zuwa ga raba shi da aikinsa.

  Mene kuma hukuncin Musulmi –a karan kansa, ko a matsayin hukuma- ya bayar da taimako wajen gina cibiyoyin karantarwa na wasu addinai, ko na yaɗa addinin Kiristanci, ko gina Coci?
- **Amsa:** Bai halatta Musulmai ya zana, ko ya gina wajen bautar kafirai, ko ya bayar da taimako na kuɗi, ko ya shiga a yi da shi a aikace ba.
- **Tambaya Ta Ashirin Da Bakwai:** Ana samun gidaje masu yawa na Musulmai da mazajen gidan suke aiki a wajen sayar da giya, da alade, da makamantansu, matansu da 'ya'yansu ba su son haka, su kuma suna

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 18 (6/3).

rayuwa ne da dukiyar mijin, shin suna da laifi akan haka?

- **Amsa:** Mata da ‘ya’yan da ba su da ikon neman halal, suna da daman su ci dukiyar mijinsu da yake samun ta haramtacciyar hanya saboda lalura, kaman sayar da giya, da alade, da sauransu cikin hanyoyin samu na haram, bayan sun yi iya ƙoƙarinsu wajen fahimtar da shi muhimmanci nema ta halatacciyar hanya, da neman wani aikin.
- **Tambaya Ta Ashirin Da Takwas:** Mene ne hukuncin siyan gidan zama, da motar hawa, da kayayyakin gida ta hanyar bashin bankuna, da hukumomin da suke ƙara tabbataccen riba a irin wannan bashin, suke amsar jingina asalin mallakar, ya kamata a san cewa a halin sayen gidaje, ko motoci, ko kayayyakin gida, idan bashin bai yiwu ba, sai a sauya bashin zuwa hayar da za a rinƙa biyan wani kaso na shi a wata wata, inda a mafi yawan lokuta kaso- kason yakan haura kaso-kason saye da bankin yake amsa?
- **Amsa:** Bai halatta ba a Shari’ance.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 24 (12/3)
GAME DA MANYAN AYYUKAN ILIMI NA CIBIYAR

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan nazarin rahoton da sashen tsare- tsare na taronsa a ranakun 8 da 9 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 da 12 ga watan Oktoba, 1986, taron da aka duba wasu al'amurra da aka shigar da su cikin jadawalin ajandar ayyuka, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko: An amince a gudanar da ayyuka masu zuwa, bayan an yi masu wasu 'yan gyare- gyare:**

1- Kundin- sha- kundun na Fiƙihu da tattalin arziki
2- Ƙamus na kalmomi na musamman a Fanni ilimin Fiƙihu
3- Jagoran ƙa'idojin Fiƙihu
4- Kundin hujjojin hukunce- hukuncen Fiƙihu
5- Raya tsofaffin littattafan Fiƙihu
6- Tsarin kuɗaɗen zartar da aikin Kundin- sha- kundun na Fiƙihu da tattalin arziki
7- Tsarin kuɗaɗen zartar da aikin Ƙamus na kalmomi na musamman a Fanni ilimin Fiƙihu
8- Tsarin kuɗaɗen zartar da aikin Raya tsofaffin littattafan Fiƙihu

9- Manhajin tafiyar da aiki da tattaunawa da shugabancin zaman majalisa.

- **Na biyu: Kafa kwamitin ilimi na mutane huɗu da za su sanya tsarin gudanar da ayyukan: "Jagoran ƙa'idojin Fiƙihu", da "Kundin hujjojin hukunce-hukuncen Fiƙihu" ta hanyar shawara da tuntuɓar juna tsakanin: shugaban majalisa, da sakatare.**

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 25 (13/3)
GAME DA BAYANIN BAYAN TARON SHEKARA-SHEKARA NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA KARO NA UKU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na uku a garin Amman, babban birnin ƙasar Jordan, wanda ya gudana daga ranar 8 zuwa 13 ga watan Safar, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 zuwa 16 ga watan Oktoba, 1986,

Bayan sauraron bayani daga mai martaba, Yariman ƙasar Jordan, Yarima Alhassan Bn Ɗalal, game da matsalolin da Musulmai suke matuƙar fama da su a fagagen haɓaka tattalin arziki, da zamantakewa, da kuma irin yanda ya zama dole a tsaya tsayin – daka wajen biya wa Musulmai buƙatunsu wajen yaƙi da talauci, da cututtuka, da jahilci, da samar wa ɗan Adam da kyakkyawar rayuwa,

Bayan duba kiran da mai martaba Yariman ƙasar Jordan ya yi zuwa ga ƙasashen Larabawa da na Musulmai domin a taimaka wa ƙasar Sudan,

Bayan irin yanda ta ji, a lokacin da take gudanar da taronta a kusa da Masjidul Aƙsa mai mai albarka na muhimmancin ruɓanya ƙoƙarin da ake yi na ceto farkon alƙibla, kuma harami na uku,

A ƙarƙashin abin da ta yi amanna da shi na muhimmanta dukan al'amurran da suke da jiɓi da rayuwar Musulmai ta zamantakewa, da tattalin arziki, da taimakon juna, da kuma muhimmancin zurfafa bincike, da nazari akansu ta hanyar mayar da hankali wajen tsara tarurrukan

ƙara wa juna sani, da kwanakin karatu, da makamantansu, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko**: Muhimmancin samar da wani tsarin Musulunci na gabatar da ayyukan jinƙai mai faɗi, da za a samar da asusu na musamman mai cin gashin kansa saboda gudanar da shi, ta hanyar kuɗaɗen zakka, da bayar da taimako, da tsarin waƙafi.
- **Na biyu:** Roƙon ɗaukacin al'ummar Musulmai –'yan ƙasa, da gwamnatoci- akan su yi aiki tuƙuru wajen ceto farkon alƙiblar Musulmai, harami mai girma na uku, da 'yanto ƙasa ta hanyar haɗa- ƙarfi da ƙarfe, da gina kai, da haɗin- kai, da daidaita sahu, da kuma girmar duk wani abu da zai kai zuwa ga saɓani a tsakaninsu, da kuma yin aiki da Shari'ar Allah Maɗaukakin Sarki a cikin ɗaukacin rayuwarsu.
- **Na uku:** Cibiyar ta bayar da muhimmanci matuƙa wajen ayyukanta na fagagen bincike da nazari, da bayar da fatawa, da samar da manyan ayyuka da suke da muhimmanci a wurin al'ummar Musulmai, suke kuma da jiɓi da rayuwarsu ta: zamantakewa, da tattalin arziki, da haɗin- kawunansu, da zamowarsu tsintsiya maɗaurikin ɗaya, da samar masu da abubuwan da za su sanya su yi taimakekeniya da juna, su kuma taimaka masu wajen fuskantar dukan ƙalubalen da suke fuskantarsu, da tsayar da rayuwarsu akan shiryatarwar Shari'ar Allah Maɗaukakin Sarki.
- **Na huɗu:** Bambance tsakanin mas'alolin da suke buƙatar nazari da bincike, da maudhu'an da suke buƙatar fatawa, wannan zai kasance ne ta hanyar mayar da hankali akan bincike da nazari a tarurrukan ƙara wa juna sani, da kwanakin karatu, daidai da tsare- tsaren da sashen samar da tsare- tsare na cibiyar za su samar su gabatar wa majilasa.

Allah ya sa mu dace;;

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA HUƊU NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

JIDDA (SAUDIYYA)
18 -23 GA WATAN JIMADAL AKHIR, 1408 H
6 – 11 GA WATAN FABRAIRU, 1988

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 26 (1/4)([1])
GAME DA MAS'ALAR MUTUM YA AMFANA DA GAƁOƁIN JIKIN WANI DA YAKE A RAYE KO A MACE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba bincike na Fiƙihu, da na likitanci da aka kawo wa cibiyar game da mas'alar: mutum ya amfana da gaɓoɓin jikin wani da yake a raye, ko a mace,

Ƙarƙashin tattaunawar da ta karkato da hankula zuwa ga cewa: lallai wannan mas'ala ce da take faruwa a aikace, wadda cigaban ilimin likitanci ne ya haifar da ita, an kuma sami sakamako masu kyau da amfani, da wasu sakamakon kuma masu cike da ruɗani a mafi yawan lokuta, inda suka bar cututtuka na ƙwaƙwalwa da na zamantakewa, saboda gudanar da wannan aiki ba tare da bin ƙa'idoji, ko yi wa iyakokin Shari'ar Musulunci da suke kare haƙƙoƙin bil'adama biyayya ba, ba kuma tare da aiki da manufofin Shari'ar Musulunci da suke sun isa su samar da alhairi, gami da maslaha ga mutum a matsayinsa na shi ɗaya, da matsayinsa na ɗaya daga cikin al'umma ba, manufofin da

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 1/89).

suke kira zuwa ga taimakekeniya da tausayin juna, da fifita wasu akan kai,

Bayan an tattaro wannan maudhu'in a wasu muhimman mas'aloli da akansu ne aka gano mahallin binciken da iyakance ƙa'idojinsa, da surorinsa, da yanayin da yake faruwa, waɗanda hukunci akansu yakan bambanta daidai da haka, **an tabbatar da ƙudurori masu zuwa:**

Ta ɓangaren ma'anarsa da rabe- rabensa:

- **Na farko: Abin da ake nufi da gaɓa a nan shi ne:** kowane irin sashe daga jikin mutum, waɗanda suka haɗa da ƙwayoyin halitta da jini, da makamantansu, kaman ƙwayar ido (Cornea), shin yana ɗamfare da shi mai jikin, ko ya rabu da shi.
- **Na biyu: Amfanar da ake magana akansa a wannan binciken ita ce:** amfanar da yanayin lalura wadda za ta sanya a kiyaye rayuwa, ko kiyaye manyan ayyuka daga cikin ayyukan jikin ɗan Adam, kaman gani da makamantan shi ne ya sanya a yi. Kuma dole ne wanda zai amfana ɗin ya zama yana rayuwa ne wadda Shari'ar Musulunci take mutuntawa.
- **Na uku: Rabe- raben surori, ko fuskokin wannan amfanar sun kasu zuwa kashe- kashe masu zuwa:**
  1. Ciro gaɓar daga rayayye.
  2. Ciro gaɓar daga mamaci.
  3. Ciro gaɓar daga ɗan tayi, ko ɓari
     - **Fuska ta farko: Ciro gaɓar daga rayayye, ta ƙunshe yanayi masu zuwa:**

a) Ciro gaɓar daga wani sashe na jiki, a sanya a wani sashe na jikin mutumin kansa, kaman ciro fata, da gaɓar ƙashin baya, da ƙashi, da jijiya, da jini da makamantansu.

b) Ciro gaɓar daga wani sashe na jikin mutum mai rai, a sanya a jikin wani mutum ɗin na daban. A nan gaɓar ta kasu zuwa: gaɓar da rayuwa ba za ta yiwu ba sai da ita, da gaɓar da ba a rasa rayuwa saboda an rasa ta.

Wadda rayuwa ba za ta yiwu ba sai da ita, za ta iya zamo guda ɗaya ce, kaman yanda za ta iya kasancewa ba ɗaya ba ce, **na farkon**, irinsu: zuciya, da hanta, **na biyun kuma**, irinsu: ƙoda, da kunhu. Game da wanda rasa ta ba ya zamowa sanadin rasa rayuwa kuwa, a cikinsu akwai: waɗanda suke gabatar da muhimman aiki a cikin jiki, akwai kuma: waɗanda aikinsu ba muhimmi ba ne. Kaman yanda a cikinsu akwai: waɗanda suke sabantuwa kai-tsaye, kaman jini, akwai kuma: waɗanda ba sa sabantuwa, a cikinsu akwai: waɗanda suke da tasiri a nasaba da gado, da ma shi mutum kansa, kaman gwaiwa, da ƙwayayen halitta na mace, da ƙwayoyin halittar manifkin abinci (Digestiɓe system), akwai kuma: wadda ba ta da kowane irin tasiri a wannan fage.

- **Fuska ta biyu: Ciro gaɓar daga mamaci:** a nan za a iya lura da cewa, mutuwa ta ƙunshi yanayi ne guda biyu:
  - **Yanayi na farko:** Mutuwar ƙwaƙwalwa sakamakon tsayawar dukan ayyukan da take yi, tsayawar da likitoci suka tabbatar da cewa ba za su sake dawowa su yi aiki ba
  - **Yanayi na biyu:** Tsayawar zuciya da numfashi na gaba ɗayan da likitoci suka tabbatar da cewa ba za su taɓa sake dawowa su yi aiki ba, a cikin duka waɗannan yanayi guda biyu an yi la'akari da ƙudurin Cibiyar a taronta na shekara-shekara karo na uku([1]).
- **Fuska ta uku: Ciro gaɓar daga ɗan tayi ko ɓari, ana amfana da ita ne a nan ta yanayi guda uku:**
  - Yanayin ɓari da ya sauko da kansa.
  - Yanayin ɓarin da aikin likita, ko aikata laifi ne ya yi sanadiyyar saukarsa.
  - Yanayin gwamin da ake yi tsakanin maniyyin miji da ƙwayayen mata a wajen mahaifa.

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 17 (5/3).

Ta ɓangaren hukunce- hukuncen Shari'a:

- **Na farko:** Ya halatta a ciro gaɓa daga wani sashen jiki a sanya a wani sashe na jikin mutumin kansa, tare da tabbatar da cewa amfanin da ake fatan za a samu ya fi cutar da cirowar za ta haifar, da kuma sharaɗin hakan ya zamo: saboda samar da wata gaɓa ce da aka rasa, ko dawo wa da gaɓar sifarta, ko aikinta da aka sani, ko gyara wani aibi, ko cire munin da ya sanya mai shi cikin hali na damuwa ta zuciya, ko ta gaɓa.
- **Na biyu:** Ya halatta a ciro gaɓa daga wani sashe na jikin mutum a sanya a jikin wani mutum na daban, idan wannan gaɓar mai sabantuwa ce kai- tsaye, kaman jini, da fata, amma dole ne a kula da sharaɗin mai bayarwar ya zamo ya kai munzalin da shari'a ta hau kansa, da kuma samuwar sharuɗɗan da shari'a take la'akari da su.
- **Na uku:** Ya halatta wani ya amfana da gaɓar da aka cire ta daga jikin wani saboda wata illa ta cuta, kaman yin amfani da ƙwayar idon mutumin da aka cire masa ita saboda rashin lafiya.
- **Na huɗu:** Haramun ne a ciro gaɓar da rayuwa ba ta yiwuwa sai da ita, kaman a cire zuciya daga mutum a sanya wa wani mutum na daban.
- **Na biyar:** Haramun ne a ciro wata gaɓa daga jikin rayayyen da cirewar za ta haifar da dakatar da wani muhimmin aiki a rayuwarsa, koda kuwa asalin wanzuwar rayuwar ba ta dogara akansa ba, kaman cire ƙwayar ido ɗaya, ko duka biyu, amma idan cirewar za ta haifar da dakatawar wani sashe ne na muhimmin aikin gaɓar, to wannan abin dubawa da bincike ne akansa, kaman yanda zai zo a sakin layi na takwas.
- **Na shida:** Ya halatta a ciro gaɓa daga mamaci a sanya wa mai ran da rayuwarsa za ta tsaya saboda rashin wannan gaɓar, ko za a rasa muhimmin aikin gaɓar. Da

sharaɗin mamacin ne ya amince da haka, ko magadansa bayan rasuwarsa, ko sharaɗin amincewar shugaban al'ummar Musulmai idan ba a gane wane ne mamacin ba, ba kuma shi da magada.

- **Na bakwai:** Ya kamata a lura da cewa: amincewa da cirar wata gaɓa a dukan yanayin da aka gabatar da bayanai akansu, akwai sharaɗin cewa kada su kasance ta hanyar sayar da gaɓar ne; saboda sam bai halatta a sanya gaɓoɓin ɗan Adam a cikin hajar sayarwa ba ta kowace irin hanya.
  Amma idan wanda ya amfana ya sanya kuɗi, saboda ya sami gaɓar da yake buƙata saboda yanayi na lalura, ko ya samar da lada na girmamawa ga wanda zai ba shi, to wannan abin dubawa da gudanar da ijtihadi ne.
- **Na takwas:** Dukan yanayi da surorin da suka saɓa da waɗanda muka ambata, waɗanda suka shiga cikin asalin wannan maudhu'in, suna nan ana gudanar da bincike akansu, dole ne a gabatar da su a taron shekara- shekara mai zuwa saboda a yi nazari da bincike akansu daidai da irin sababbin abubuwan da aka cimma a fannin ilimin likitanci, da hukunce-hukuncen Shari'a.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 27 (2/4)([1])
GAME DA BAI WA ASUSUN MUSULUNCI NA BAYAR DA TALLAFI DA AYYUKAN JINƘAI ZAKKA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba bayanan fassara game da al'amarin Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jinƙai, da waƙafinsa, da aka gabatar wa Cibiya a taron shekara-shekara na uku, da bincike gami da nazarin da aka gabatar wa cibiyar a taronta na wannan karo game da maudhu'in bai wa Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jinƙai zakka, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Bai halatta a bayar da zakka domin ƙarfafa waƙafin Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jinƙai ba; saboda yin hakan takure zakka ne, da hana isar da ita ta hanyoyin da Shari'ar Musulunci ta ƙididdige a cikin Alƙur'ani mai girma.
- **Na biyu:** Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jinƙai zai iya zama wakilin mutane, ko ƙungiyoyin wajen raba zakka da isar da ita a hanyoyinta, da sharuɗɗa masu zuwa:

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 1/517).

(a) A sami cikan sharuɗɗan wakilci da Shari'a ta sanya a tare da wanda ake wakilta da wanda yake wakilcin.

(b) Asusun ya gudanar da gyare- gyare a tsarinsa da yake a matsayin ginshiƙin kafa shi, da manufofinsa, gyare-gyaren da za su ba shi daman gudanar da irin wannan aiki na wakilci.

(c) Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jiƙai ya wace asusun ajiya na banki da za a keɓance shi saboda sanya zakka; gudun kada ta haɗe da sauran kuɗaɗen da suke zuwa ga asusun ta wasu hanyoyin, abin da zai iya kai wa zuwa ga a shigar da kuɗin zakka a hanyoyin da ba su Shari'a ta bayyana ba, kaman manyan kayan amfani na kowa da kowa da sauransu.

(d) Bai halatta Asusun ya yi amfani da wani abu na dukiyar zakka da ya zo a ayyukan gudanarwa na ofis, ko wajen biyan albashin ma'aikata, da makamantan haka ba waɗanda ba su a cikin sassan da Shari'a ta amince a ba su zakka.

(e) Wanda ya bayar da zakka yana da haƙƙin ya sanya wa Asusun sharaɗin inda yake son a bayar da zakkarsa cikin hanyoyi takwas da shari'a ta bayyana, kuma dole ne Asusun –idan hakan ya faru- ya zartar da wannan sharaɗi.

(f) Dole Asusun ya isar da dukiyar wannan zakkar zuwa ga waɗanda suka cancanta a kan kari, saboda waɗanda za su amfana da ita su same ta cikin sauƙi, kada ta wuce shekara ba isar ba.

Majalisar cibiyar tana bayar da wasici da abu mai zuwa:

Saboda aikin da zai bai wa Asusun Musulunci na bayar da tallafi da ayyukan jiƙai daman zartar manufofinsa na alhairi –waɗanda aka bayyana su a tsarin gudanar da shi-, waɗanda saboda su aka kafa shi, da kuma yin aiki da ƙudurin taron ƙoli na ƙasashen Musulmai na biyu, wanda ya bayyana kafa wannan Asusun da taimaka masa ta

hanyar gudummuwar da ƙasashen da suke mambobi ne a ƙungiyar za su rinƙa bayarwa, lura da irin yanda wasu ƙasashe ba su lizimci bayar da gudummuwarsu kaman yanda aka tabbatar ba, cibiyar tana kira zuwa ga ƙasashe da gwamnatoci, da ƙungiyoyi da masu hannu da shuni cikin Musulmai da su gabatar da abin da ya wajaba akansu na taimaka wa wannan Asusun saboda ya samu ya gudanar da manufofinsa masu girma da nagarta wajen hidimta wa al'ummar Musulmai.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 28 (3/4)([1])
GAME DA ZAKKAR HANNUN- JARI A KAMFUNA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in zakkar hannun- jari a kamfuna, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Zakkar hannun- jari ta wajaba akan masu hannun- jarin, shugabancin da yake jagorantar kamfanin ne zai fitar da zakkar a madadin masu su, idan tsarin gudanar da kamfanin ya bayyana haka, ko ya zamana an samar da wani ƙuduri akan haka daga babban zauren kamfanin, ko ya zama dokokin ƙasar da kamfanin yake sun wajabta wa kamfuna fitar da zakka, ko ya zama kamfanin ya sami wakilci daga masu mallakar hannayen- jarin akan cewa shugabannin kamfanin su fitar wa hannayen jarin da zakka.
- **Na biyu:** shugabannin kamfanin za su fitar da zakkar hannayen- jarin ne kaman yanda mutane na ɗabi'a suke fitar da zakkar dukiyoyinsu, ma'ana za a kalli jimillar dukiyar da suke su ne masu hannayen – jarin a

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 1/705).

matsayin tamkar dukiyar mutum ɗaya, sai a fitar mata da zakka ta wannan mahangar, inda za a yi la'akari da: nau'in dukiyar da zakka ta wajaba akanta, da kuma nisabi, da kuma gwargwadon abin da za a cire, da sauran abubuwan da suka yi kama da haka cikin abubuwan da ake lura da su a lokacin da mutum na ɗabi'a zai fitar da zakka, za a yi haka ne daidai da ƙa'idar nan ta Cakuɗa, a wurin masana Fiƙihun da suka game ta a cikin dukan dukiyoyi.

Za a cire rabon hannayen jarin da zakka ba ta wajaba akansu ba, irinsu: hannayen- jarin asusun gwamnati, da hannayen – jarin waƙafin taimako, da hannayen jarin ƙungiyoyin bayar da tallafi, haka ma da hannayen jarin waɗanda ba Musulmai ba.

- **Na uku:** Idan kamfanin bai fitar wa dukiyarsa zakka ba saboda kowane irin dalili, to abin da ya wajaba akan masu hannayen- jari shi ne kowa ya fitar da zakka akan adadin hannayen- jarin da yake mallaka, idan ya sami daman sanin jimillar dukiyar kamfanin da zakka ya hau kan hannayen- jarin gaba ɗaya, idan ya fitar da zakkar daidai da tsarin da muka faɗi, a nan sai ya yi wa nasa hannayen- jarin zakka ta wannan fuska; saboda yin haka shi ne asali wajen fitar da zakkar hannayen- jari.

Idan kuma mai hannayen- jarin bai sami daman sanin haka ba:

To idan da ma ya saka hannun- jarinsa a kamfanin da niyyar ya amfana da ribar da hannayen- jarin za su kawo masa ne a shekara- shekara, ba wai da niyyar kasuwanci ba, to a nan zai fitar da zakka ne irin ta wanda ya sami galla, a nan kaman yanda ƙudurin da Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta bayyana a taronta na shekara-shekara karo na biyu([1]) game da zakkar tabbatattun abubuwa da filayen haya da ba a noma ba, babu zakka

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 2 (2/2).

akan wanda ya mallaki irin wannan hannayen- jari a asalin hannayen jarinsa; tana dai wajaba ne akan ribar da hannayen- jarin suka haifar, wato "rubu'in ushiri" bayan kewayowar shekara daga ranar da aka amshi wannan ribar, idan sharuɗɗan zakka sun cika, ba kuma a sami wani abu cikin abubuwan da suke hana yin zakka ba([1]).

Amma idan mai mallakar hannayen- jarin ya mallaka ne da niyyar yin kasuwanci, to zai yi masu zakka ne irin yanda ake yi wa kayan kasuwanci zakka, idan shekara ta kewayo suna kuma nan a ƙarƙashin mallakarsa, sai ya yi masu zakka daidai da ƙimar su ta kasuwa a lokacin, idan kuma ba su da kasuwa, sai ya yi masu zakkar daidai da yanda ƙwararru a fannin kasuwanci suka bayyana, ya fitar da "rubu'in ushiri" (2.5%) na wannan ƙimar da ribar, idan hannayen- jarin suna da riba.

- **Na huɗu:** idan mai mallakar hannayen jari ya sayar da hannayen- jarinsa a cikin shekara kafin ta zagayo, sai ya shigar da kuɗinsu cikin dukiyarsa ya yi masu zakka a tare idan shekarar da yake yin zakkar da zagayo. Shi kuwa wanda ya sayi hannayen- jarin daga wurinsa zai yi wa hannayen- jarin zakka ne kaman yanda muka bayyana a baya.

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) An fitar da ƙuduro mai lamba 120 (3/13) da yake ƙarin haske da daidai abin da ake nufi da ribar zakkar hannayen- jari.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 29 (4/4)([1])
GAME DA ƘWACE MALLAKAR ƊAIƊAIKUN MUTANE SABODA MASLAHAR AL'UMMA TA GABA ƊAYA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba binciken da aka kawo wa Cibiyar game da maudhu'in ƙwace mallakar ɗaiɗaikun mutane saboda maslahar al'umma ta gaba ɗaya,

Ƙarƙashin abubuwan da suke sanannu ne a cikin asali da tushen Shari'ar Musulunci, na girmama mallakar ɗaiɗaikun mutane, abin da har ya kai ga cewa hakan ya zamo cikin yankakkun hukunce- hukuncen da duk wani wanda ya san addini ya san a tare suke, kuma lallai kiyaye dukiya yana cikin manyan muhimman abubuwa guda biyar da Musulunci yake muhimmantawa, waɗanda aka san cewa ba su kariya yana cikin manyan Manufofin Shari'ar Musulunci, Nassoshi na Alƙur'ani da Hadisai suka zo domin ba su kulawa ta musamman, tare kuma da hararo da tabbatattun dalilai da hujjoji daga Sunnar Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da ayyukan Sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) na amshe mallakan

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 2/897).

filaye, ko gidaje daga hannun ɗaiɗaikun mutane saboda maslahar al'umma ta baki ɗaya; domin aiki da manyan ƙa'idojin Shari'ar Musulunci wajen kiyaye maslahohi, da ɗaukan maslaha, ko buƙatar al'umma ta bai ɗaya a matsayin lalura, da jure wa ɗaukan cutuwar mutum ɗaya domin kauce wa cutuwar da za ta sami kowa da kowa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Dole ne a kiyaye mallakar ɗaiɗaikun mutane, a kuma ba su kariya ga barin duk wani zalunci, ko fin ƙarfi, bai kuma halatta a takura ta, ko a yi mata iyaka ba, mai ita shi ne yake da wuƙa- da-nama akan abin da ya mallaka, yana da ikon ya yi duk abin da ya ga dama da ita, daidai da yanda Shari'a ta iyakance, na amfani da mallakarsa ta yanda Shari'a ta tanadar, ko kyautarwa, ko sayarwa.
- **Na biyu:** Bai halatta a ƙwace mallakar tabbatattun abubuwan mallaka (Real estate) ba, sai dai idan an yi la'akari da sharuɗɗa masu zuwa da Shari'a ta tanadar:
  (1) Ya zamana an amshi gida, ko filin ne bayan an biya shi kuɗin da zai yi daidai da abin da aka amsa nan take, kuma ya zamo ƙwararru ne suka bayyana kuɗin da sharaɗin kada ya yi ƙasa da kuɗin irinsa.
  (2) Wanda ya amsa ya zamo shugaba ne na al'umma, ko wanda yake wakiltarsa a wannan fagen.
  (3) Ya zamana an amsa ne saboda amfani da maslahar al'umma gaba ɗaya, wadda kuma lalura, ko buƙata ce suka sanya yin haka, kaman saboda gina Masallaci, ko hanya, ko gina gadoji.
  (4) Kada a yi amfani da fili ko gidan da aka amsa daga mai shi wajen kasuwanci da sunan al'umma, ko da sunan wasu ɗaiɗaikun mutane, kada kuma a yi gaggawar amshe shi daga hannunsa kafin lokacin amfani da shi.

Idan aka rasa waɗannan sharuɗɗa dukansu, ko wasu daga ciki, to amsar mallakar a wannan hali zalunci ne a

bayan ƙasa, yana kuma cikin ƙwacen da Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa mai tsira da aminci suka hana.

Haka ma idan an sake ɗaukan matakin fasa yin amfani da gida, ko filin da aka amsa saboda maslahar al'umma, to mai mallakar wurin na asali shi ne ya fi cancanta da a mayar masa da wurin, ko magadansa idan sun biya kuɗin wurin cikin adalci.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 30 (5/4)([1])
GAME DA SHAHADUN MALLAKAR BASHI (CREDIT BOND) DA SHAHADUN MALLAKAR KASUWANCI (INVESTMENT BOND)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata game da maudhu'in: Shahadun mallakar bashi (Credit Bond) da Shahadun mallakar kasuwanci (Investment bond), waɗanda sakamako ne na taron ƙara wa juna sani da Cibiyar ta gabatar, tare da haɗin- gwiwar Cibiyar Musulunci mai bincike da bayar da horaswa na Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB) a ranakun 6 zuwa 9 ga watan Almuharram, 1408, waɗanda suka yi daidai da ranakun 2 zuwa 8 ga watan Satumba, 1987, saboda zartar da ƙuduri mai lamba 22 (10/3), wanda aka ɗauka a taron shekara- shekara na Cibiyar, karo na uku, inda adadi mai yawa cikin mambobi da ƙwararrunta, da masu bincike a Cibiyar (IsDB) da sauran cibiyoyin ilimi da na tattalin arziki suka halarta, saboda irin yanda wannan maudhu'in yake da matuƙar muhimmanci, da kuma buƙatar a kammala bayyana duk wani abu da ya

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 3/1809).

ƙunsa da dukan fuska, da kuma irin muhimmiyar rawar da wannan salo yake takawa wajen ƙara ƙarfi da haɓaka arzikin al'umma ta hanyar haɗa tsakanin dukiya da aiki,

Bayan an bijiro da bayanin bayan taro da yake ɗauke da muhimman abubuwa guda goma, waɗanda aka sami matsaya game da su a taron ƙara wa juna sani, aka kuma tattauna akansu ƙarƙashin binciken da aka gabatar wa taron na ƙara wa juna sani, da ma wasu tarurrukan, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko: Game da karɓaɓɓiyar sigar da Shari'a ta amince da ita wajen rubuta Shahadun Sukuk (Credit Bond Certificate):**

1- (Credit bond) hanya ce da ake amfani da ita wajen haɓaka dukiya ta hanyar kasuwanci, an gina ta ne akan rarraba uwar kuɗi ko jarin bashin (mudaraba) zuwa, ta hanyar samar da shaidar mallakar (Sukuk) daidai da yawan uwar kuɗi, ko jarin, akan ƙima iri ɗaya daidai- wa- daida, a kuma yi wa kashe- kashen rijista da sunayen masu su, a matsayinsu na waɗanda suke mallakar wani kaso daga cikin uwar kuɗi, ko jarin wannan bashi, da duk abin da zai shiga cikinsa, kowa daidai gwargwado yawan kason da yake mallaka.

An fi son a kira wannan hanya ta haɓaka dukiya da ƙara mata yawa da sunan (Sukuk): wato shaidar mallakar bashi.

2- Dole ne surar shahadun mallakar bashin (Credit Bond) da Shari'ar Musulunci ta amince da shi ya zamo ya cika ginshiƙan al'amurra masu zuwa:

Ginshiƙi na farko:

Kowane kaso na shaidar mallakar bashin ya zamo yana wani sashe ne na mallakar wani kaso daga cikin babban aikin da aka samar da shaidun mallakar bashin wajen samar da shi, ko zuba jari a cikinsa, kuma wannan mallaka ta cigaba da kasancewa tun daga farkon shirin har zuwa ƙarshensa.

Ya kuma zamana tana da wani haƙƙi na yin amfani da dama (tasarrufi) da Shari'a ta tabbatar wa wanda yake mallakar wani abu akan abin da ya mallaka, na daman ya sayar, ko ya yi kyauta da shi, ko ya bayar da jingina, ya kuma gadar wa magada da makamantan haka, dole ne kuma a yi la'akari da cewa (Sukuk) shaidar mallakar bashin gaba ɗaya shi ne uwar kuɗi ko jari a tsarin (Mudaraba).

Ginshiƙi na biyu:

Hanyar ƙullar yarjejeniyar samar da shaidar mallakar bashi ta ginu ne akan cewa: Bayanan da za su samar da shaidar mallakar bashin su ne za su bayyana sharuɗɗan yarjejeniyar samar da shaidar, inda tayi (al- Ijab) zai zo ne a rubuce cikin wannan shaidar (Sukuk), amsa (al- Ƙabul) kuma ita ce: amincewar da hukuma, ko cibiyar da ta samar da shaidar za ta yi.

Dole ne bayanin samar da shaidun mallakar su ƙunshi dukan bayanan da shari'ar Musulunci ta nemi a samar wajen gudanar da kasuwanci a tsarin mudaraba, da za su haɗa da: bayanin da zai sanya a san uwar kuɗi, ko jari, da yanda za a raba riba, tare kuma da keɓantattun sharuɗɗan da suka shafi samar da shaidun mallakar, amma fa dole ne duka sharuɗɗan su yi daidai da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci.

Ginshiƙi na uku:

Dole ne shaidun mallakar bashin su zamo za a iya hulɗar hada- hada da su bayan wucewar lokacin da aka iyakance a rubuce, hakan a matsayin cewa mai gudanar da kasuwancin mudarabar ya amince da shi wajen samar da waɗannan shaidun, tare kuma da la'akari da sharuɗɗa masu zuwa:

a- Idan dukiyar bashin da aka tara bayan wannan rubutaccen neman, da kafin aiwatar da aikin a aikace yana nan a matsayi kuɗi, domin hulɗa da shaidar mallakar bashi daidai yake da hulɗa da kuɗi hannu-

da- hannu, za a yi aiki da hukunce- hukuncen bayar da kuɗi a cikinsu.

b- Idan kuɗin bashin ya zama bashi, za a yi aiki da hukunce- hukuncen mu'amala da bashi wajen hulɗa da hada- hada da shaidun mallakar.

c- Idan kuɗin bashin ya zama wasu abubuwa ne a cakuɗe da suka haɗa da kuɗi da bashi, da kayan amfani da kuma kadarori, to ya halatta a gudanar da hulɗa da shaidun mallakar daidai da farashin da aka yi yarjejeniya akansa, amma a wannan yanayi dole ne a rinjayar da kayayyakin amfani, da kadarori. Amma idan abin da ya fi rinjaye shi ne kuɗi, ko basussuka, to za a yi la'akari da hukunce- hukuncen Shari'a da bayanan tsare- tsaren fassara, wanda Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya za ta samar a taron shekara-shekara mai zuwa za ta bayyana su.

A dukan yanayi da halayen da ake ciki dai dole ne a yi rijistar hulɗar hada- hadar a daftarin hukuma, ko cibiyar da ta samar da shaidar mallakar.

Ginshiƙi na huɗu:

Lallai wanda zai amshi kuɗin rubutattun takardun neman shiga cikin wannan tsari na samun shahadun Sukuk da ake kasuwanci da su, da samar da tsayayyen kasuwancin kansa shi ne mai mudaraba, ma'ana wanda shi da jikinsa ne zai gudanar da kasuwancin, ba shi ne yake mallakar shirin ba sai gwargwadon abin da zai iya na sayen wasu daga cikin hannayen- jari, zai iya zama mai mallakar jari, ko uwar kuɗi ne na gwargwadon abin da ya zuba na hannun jari, bugu da ƙari, kuma shi mai mudarabar ɗaya ne daga cikin waɗanda za a yi tarayya da su a cikin ribar da aka samu, daidai gwargwadon da aka iyakance a bayanan samar da tsarin hannayen- jari, inda wannan ne zai bayyana abin da yake mallaka a cikin wannan kasuwanci.

Mai gudanar da mudaraba amintacce ne game da kuɗin shahadun kasuwanci na Sukuk, da duk wasu abubuwa da

suke da jiɓi da wannan tsarin na kasuwanci, ba za a nemi ya lamunci biya waɗannan abubuwa idan aka rasa su ba, sai idan an rasa ɗaya daga cikin dalilan lamunin da shari'ar da gindaya.

3- Tare da lura da ƙa'idojin da suka gabata wajen hada-hada: ya halatta a yi hada- hada da hulɗa da shahadun hannayen jari na Sukuk ɗin bashi a kasuwannin hada- hadar tarkardun kuɗi, idan an same su, daidai da ƙa'idojin da Shari'a ta gindaya, daidai da yanda suke a kasuwa, da kuma irin buƙatarsu da ake yi, da kuma yardar mai saye da mai sayarwa. Haka ma ya halatta a gudanar da hada- hadar ta hanyar fitar da sanarwa bijiro da su ga jama'a daga hukuma, ko cibiyar da take samar da shahadun hannayen- jari a wasu sanannun lokaci, inda za su yi riƙo da sayen waɗannan shahadun na wani iyakantaccen lokaci daga ribar kuɗin mudarabar a sanannen farashi, yana da kyau ta nemi taimakon ƙwararru wajen iyakance farashinsu daidai da yanayin kasuwa da kuma matsayin kuɗin a cikin harkar, haka ma ya halatta a sanar da daman sayensu ga hukumomi, ko cibiyoyin da ba su ne suke samar da shahadun ba, kaman yanda muka nuna a baya.

4- Bai halatta takardar shiga cikin mudaraba, ko shahadun Sukuk na bashi su ƙunshi nassin da yake ɗaura alhakin uwar kuɗi, ko jarin mudaraba akan mai gudanar da mudaraba ba, ko kuma a ɗaura masa alhakin wani riba da ake da tabbacin samunsa, ko wanda aka jingina wa uwar kuɗi ba, idan an sami irin wannan sharaɗi, ko nassi ƙarara, ko a fakaice, to sharaɗin ne ya ɓaci, shi kuma mai gudanar da harkar mudarabar yana da ribar da ta yi daidai da irin kai-komo da wahalhalunsa.

5- Bai halatta takardar yarjejeniyar samun shahadun, ko su kansu shahadun Sukuk ɗin su ƙunshi wani

nassi, ko sharaɗi da zai tilasta sayarwa, ko ratayar da sayarwar akan wani abu, ko a jingina shi da nan gaba ba. Kawai dai ya halatta shahadar Sukuk ɗin ta bashi ta ƙunshi alƙawarin sayarwa ne, idan kuma hakan ya faru, sayarwar ba zai tabbata ba sai da wata yarjejeniyar da za ta kasance daidai da ƙimar da ƙwararru suka bayyana, da kuma yardar ɓangarorin guda biyu.

6- Bai halatta takardar shiga cikin shirin, ko shahadar Sukuk ɗin da ake samarwa su zama sun ƙunshi wani nassi da zai nuna yiwuwar kamfanin ya iyakance riba ba, idan haka ya faru to yarjejeniyar tun asali ta ɓaci.

Inda abubuwan da za su biyo bayan haka, sun haɗa da:

a- Rashin halaccin sanya wani adadi na kuɗi ga waɗanda suke ɗauke da shahadun Sukuk, ko wanda yake gudanar da mudaraba a takardar samar da shahadun, ko a shahadun Sukuk da aka samar da su saboda ita.

b- Abin da ake rabawa shi ne riba –da ma'anar da Shari'a take nufi da haka-, wanda shi ne abin da ya ƙaru akan uwar kuɗi, ko jari, ba wai abin da aka samu da ya shigo, ko galla ba. Kuma ana sanin gwargwadon ribar ne ko dai ta hanyar sauya uwar kuɗin zuwa tsabar kuɗi, a aikace, ko a lissafe, ko ta hanyar ƙididdige harkar, da yi masa kuɗi, duk abin da ya ƙaru akan uwar kuɗi, ko jari lokacin wannan sauya uwar kuɗin zuwa tsaba, a aikace, ko a lissafe shi ne ake rarrabawa tsakanin waɗanda suke mallakar shahadun Sukuk da wanda yake aikin mudaraba, daidai da sharuɗɗan ƙulla yarjejeniyar.

c- Lissafa riba da faɗuwar da shirin kasuwancin na mudaraba ya fuskanta, a kuma sanar da haka a

fili ta yanda dukan waɗanda suke ɗauke da shahadun Sukuk ɗin za su iya mu'amala da shi.

7- Cancantar samun riba tana tabbata ne da zaran ta bayyana, ana kuma mallaka wa masu ita ne da zaran an mayar da shahadun zuwa tsabar kuɗi, ko idan an tabbatar da lissafi, bai hallata masu shahadun Sukuk su yi ma'amala da ita ba sai bayan an rarraba. Game da shirin kasuwancin da yake haifar da wani amfani, ko galla kuwa, ya halatta a raba gallar, abin da ake rarrabawa tsakanin sassan yarjejeniyar kafin mayar da shahadun zuwa kuɗi, yana matsayin kaman wani kuɗin da aka fara bayar wa wanda daga baya za a yi lissafi a cire.

8- A Shari'a babu abin da zai hana a sami wani nassi a cikin takardar amincewa da shiga cikin tsarin kasuwancin da zai nuna a yanke wani kaso a ƙarshen kowane zango, ko dai daga cikin kason masu ɗauke da shahadun Sukuk a cikin ribar da za a samu, idan ya zamana ana mayar da shahadun mallakar hannayen- jari zuwa tsabar kuɗi a zango-zango, ko kuma daga kasonsu cikin abubuwan da suke shigowa da galla da ake rarrabawa kafin a kai zuwa ga ƙarshen tsarin, a adana shi saboda fuskantar hatsarin da zai iya faɗowa uwar kuɗi, ko jarin.

9- A Shari'a babu abin da zai hana a sami wani nassi a cikin takardar amincewa da shiga cikin tsarin kasuwancin, ko a cikin shahadun mallakar Sukuk da zai nuna alƙawarin wani da ba ya cikin ɓangarorin yarjejeniyar (mutum na uku) na bayar da kyauta ba tare da an bashi komai ba, domin a cike giɓin asarar da za ta iya faɗawa cikin wani tsarin kasuwancin, sai dai wannan kyauta da za a wajabta wa kai dole ne ta zamo an yi ta ne da yarjejeniya mai zaman kanta ba a gwama ta da

mudaraba ba, ma'ana biyan giɓin da aka samu da zai yi ba sharaɗi ne wajen zartar da yarjejeniyar da har hukunce- hukuncensa za su shafi ɓangarorin yarjejeniyar ba, saboda haka masu ɗauke da shahadun Sukuk da mai aikin gudanar da kasuwancin mudaraba ba su da haƙƙin su yi da'awar ɓacin mudaraba, ko su ƙi zartar da abin da ya wajaba akansu saboda kawai wanda ya yi alƙawarin bayar da kyautar cika giɓi ya ƙi cika alƙawarinsa, suna kafa hujja da cewa alƙawarin nasa yana da muhimmanci a cikin yarjejeniyar.

- **Na biyu: Majalisar Cibiyar ta bijiro da wasu sigogi huɗu da bayanin bayan taron ƙara wa juna sani da cibiyar ta gabatar ya ƙunsa, shawarwari ne da za a amfana da su wajen raya "waƙafin kasuwanci" ba tare da wofintar da sharuɗɗan da suke kiyaye dawwamar da waƙafi ba, waɗanda su ne:**
  a) Kafa gamayya tsakanin masu waƙafi da ƙimar kayan waƙafi, da kuma msu dukiya da za su yi amfani da ita wajen raya waƙafin.
  b) Gabatar da kayayyakin waƙafi –a matsayin tabbatattun abubuwa- zuwa ga wanda yake aikin raya shi da dukiyarsa da zai sami wani kaso daga ribar da waƙafin ya samar.
  c) Raya waƙafi ta hanyar yarjejeniyar sana'antawa tare da bankin Musulunci, da zai sami makwafin ribar da waƙafin ya samar.
  d) Bayar da hayar waƙafin da ladan kayayyaki da akansa shi kaɗai za a gina, ko tare da lada kaɗan.

Lallai ra'ayin majalisar cibiyar ya yi daidai da bayanin bayan taron ƙara wa juna sanin game da waɗannan sigogi ta ɓangaren buƙatar ƙara bincike da nazari akansu, an kuma ɗaura wa sakateriya alhakin neman malaman da za su yi rubutu da bincike akan wasu daga cikin sigogin da shari'a ta amince da su a wurin kasuwanci da haɓaka dukiya, da kuma shirya taron ƙara wa juna sani da za a

gabatar da sakamakon da suka cimma ga Cibiyar a taron shekara- shekara mai zuwa.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 31 (6/4)([1])
GAME DA MAKWAFIN BARI (KEY- MONEY)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba bincike na Fiḳihu da aka gabatar wa Cibiyar game da makwafin bari (key- money), **akan haka ne aka tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Surorin yarjejeniyar makwafin bari sun kasu gida huɗu, waɗanda su ne:

1- Yarjejeniyar ta kasance tsakanin mai mallakar gidan hayar da ɗan haya lokacin ƙulla yarjejeniyar hayar.

2- Yarjejeniyar ta kasance tsakanin ɗan haya da mai gidan, a lokacin da ake gudanar da hayar a aikace, ko bayan ƙarewar lokacin hayar.

3- Yarjejeniyar ta kasance tsakanin ɗan haya da wani sabon ɗan haya, a lokacin da ake gudanar da hayar a aikace, ko bayan ƙarewar lokacin hayar.

4- Yarjejeniyar ta kasance tsakanin sabon ɗan haya da mai gidan a tare da ɗan hayar farko, kafin lokacin hayar ya ƙare, ko bayan ya ƙare.

- **Na biyu:** Idan mai gida da ɗan haya suka yi yarjejeniya akan cewa ɗan hayan zai bai wa mai gida

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 3/2171).

wani tabbataccen kuɗi, ƙari akan kuɗin da yake biya duk bayan zagayowar lokaci –abin da a wasu ƙasashen ake kiransa da suna "Bari"- to a Shari'a dai babu laifi wajen biyan wannan kuɗi da suka tabbatar, amma dai dole ne a shigar da shi cikin lissafin kuɗin iya lokacin da aka yi ittifaƙi akansa, idan kuma an rusa yarjejeniyar ta haya, to za a zartar da hukunce-hukuncen kuɗin haya ne akan wannan kuɗi da aka biya.

- **Na uku:** Idan an sami yarjejeniya tsakanin mai gida da ɗan haya a cikin lokacin da ake haya akan cewa mai gida zai bai wa ɗan haya kuɗi a madadin shi kuma ya bar haƙƙinsa da yarjejeniyar da tabbatar na mallakar amfana da sauran lokacin hayar, to a nan biyan makwafin barin (key- money) ya hallata a shari'ance; saboda bai wuce kuɗi ne da aka bayar da shi saboda sauka daga haƙƙin da ɗan haya ya yi da yardarsa na ya bar haƙƙinsa na cigaba da amfana, wanda a nan ya sayar da haƙƙin ga mai gida.

Amma idan lokacin hayan ya ƙare, ba kuma a sabunta yarjejeniyar ƙarara, ko a dunƙule ta hanyar sabuntawa ta kai- tsaye daidai da sigar da take nuna haka ba, to a nan bai halatta ya amshi makwafin bari ba, saboda mai gidan shi ne ya fi cancanta da ya karɓi kayansa bayan ƙarewar haƙƙin ɗan haya.

- **Na huɗu:** Idan an riga an yi yarjejeniya tsakanin ɗan haya na farko da wani sabon ɗan haya a lokacin da ake hayar akan ya sauka akan haƙƙinsa na sauran lokacin haya da aka yi yarjejeniya, akan wani kuɗi da zai zamo ƙari akan kuɗin hayar da ake biya a duk sanda lokaci ya zagayo, to makwafin barin ya halatta a shari'ance, amma dole ne a yi la'akari da yarjejeniyar ƙulla hayar tsakanin mai gidan da ɗan haya na farko, a kuma yi la'akari da dokokin da ake aiki da su, waɗanda suka yi daidai da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci.

Amma a haya mai dogon zango abin ya saɓa da yanda nassin yarjejeniyar haya yake tabbatarwa, daidai da yanda wasu dokoki suka bayyana, inda bai halatta ɗan haya ya bayar da hayar abin da yake haya ga wani ɗan haya ba, bai kuma halatta ya amshi makwafin bari ba sai idan mai kayan hayar ya amince.

Amma idan an yi ittifaƙin tsakanin ɗan haya na farko, da sabon ɗan haya ne bayan lokacin hayar ya wuce, to sam bai halatta ya amshi makwafin bari ba, saboda haƙƙin ɗan hayan farko akan kayan hayar ya riga ya ƙare.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 32 (7/4)([1])
GAME DA SAYAR DA SUNAN KASUWANCI (TRADE NAME) DA LASI (LICENCING)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan ta duba bincike da nazarce- nazarcen da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in sayar da sunan kasuwanci (Trade Name) da lasi (Licencing), waɗanda suka bambanta da juna wajen taɓo wannan maudhu'i, suka kuma sassaɓa da juna wajen kalmomi na musamman (Terms ko musɗalahat) da aka yi amfani da su, daidai da asalin harshen da aka tarjamo waɗannan sababbin sigogi na zamani, ta yanda bincike ba su zo akan maudhu'i ɗaya ba, aka kuma sami bambancin fahimta da mahanga, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Jinkirta duba wannan maudhu'i zawa taron shekara- shekara na biyra da majalisa take gabatarwa, saboda a sami daman kammala nazari da bincike ta dukan fuskoki, tare da la'akari da al'amurra masu zuwa:
  - **a-** Bin manhajin da suke kusa da juna wajen bincike, inda za su fara da gabatarwar bincike da za a

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 43 (5/5).

bayyana ainihin mas'alar da ake magana a kanta, a kuma bayyana iyakokin binciken, tare da taɓo dukan kalmomi na musamman da ake amfani da su cikin binciken dokoki da kalmomin da suke da ma'anoni iri ɗaya.

b- Ishara zuwa ga maudhu'ai da suke yi kama da wannan da suka faru a tarihi, da kuma abubuwan da aka bayyana na mahangar Shari'a, ko na dokoki suna da tasiri matuƙa wajen fito da surar, da kuma hukunce- hukuncen rarrabawar.

- **Na biyu:** Koƙarin shigar da maudhu'in sayar da sunan kasuwanci da sayar da lasi cikin babban maudhu'i kuma gamamme, saboda nazarin ya fi inganci, fa'idar da za a samu kuma ya yawaita, ya kuma faɗaɗa, inda za a yi haka ƙarƙashin kanu (Unwani) "Haƙƙoƙi na Ma'ana", domin kalmomi irinsu: "Haƙƙin ta'alifi", da "haƙƙin ƙirƙira", da "haƙƙin fasaha", da "haƙƙin saƙo", da "haƙƙin zane" da misalai na sana'a, da kasuwanci, kaman su alamomi, da bayanai da sauransu su sami shiga.
- **Na uku:** masu bincike za su iya taƙaita bincikensu akan kalma ɗaya cikin haƙƙoƙin da aka yi ishara, kaman yanda za su iya faɗaɗa sassan bincikensu ta yanda za su ƙunshi kalmomin da suke da jiɓi da juna a taswirar maudhu'in na bai ɗaya.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 33 (8/4)([1])
GAME DA HAYAR DA TAKE ƘAREWA DA MALLAKA, DA ƉAURA WA WANDA AKA BAI WA SAUTU, KO SAƘO RIBA DA SASSAUYAWAR DARAJAR KUƉI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Jinkirta duba dukan maudhu'an: "hayar da take ƙarewa da mallaka"([2]), da "ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba"([3]), haka ma da jinkirta fitar da maganar ƙarshe game da maudhu'in: "sassauyawar darajar kuɗi"([4]), saboda buƙatar da ake da ita na samun cikakken bayani ta dukan fuskoki, zuwa taron shekara- shekara na gaba.
- **Na biyu:** Ɗaura wa sakateriya alhakin samar da bincike da nazari game da maudhu'an nan guda biyu, da kuma kawo abin da aka gabatar na bincike akan

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 43 (5/5).
([2]) Duba: Ƙuduri mai lamba 44 (6/5), da Ƙuduri mai lamba 110)4/12) wanda ya kawo surorin da aka hana da surorin da aka halatta na hayar da take ƙarewa da mallaka.
([3]) Duba: Ƙuduri mai lamba 40 -41)2/5 da 3/5).
([4]) Duba: Ƙuduri mai lamba 42 (4/5), da Ƙuduri mai lamba 115 (9/12) wanda ya kawo hanyoyin hana faruwar badago (inflation).

maudhu'in "hayar da take ƙarewa da mallaka", da ƙudurorin da suka shafi haka da taron Fiƙihu na ƙara wa juna sani na Gidan Zakkar ƙasar Kuwait (Baitut Tamwilil Kuwaitiy) ya fitar, wanda aka gudanar a shekarar 1407 H, da ta yi daidai da 1987. Da ma binicke da nazarin da aka gabatar game da maudhu'in "ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba", a taron muhimman al'amurra game da zuba hannun jari a bankunan Musulunci, wanda aka yi a Amman shekara ta 1407 H, da ta yi daidai da 1987 tare da hadin gwiwa da Cibiyar Musulunci mai bincike da horaswa na bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB), da Cibiyar masarauta mai lura da cigaban Musulunci.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 34 (9/4)([1])
GAME DA "ALBAHA'IYYA"

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Lura da ƙudurin taron ƙolin ƙasashen Musulmai mai lamba biyar, wanda aka yi a ƙasar Kuwait a ranakun 26 zuwa 29 ga watan Jimadal Ula, 1407 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 26 zuwa 29 ga watan Junairu, 1987, wanda ya ƙarƙare da ƙudurin da Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta fitar mai bayyana ra'ayin akan gurɓatattun ƙungiyoyin da suke cin karo da karantarwar Alƙur'ani mai girma, da Sunnar Annabi mai tsarki.

- Lura da irin hatsarin da Albaha'iyya take da shi a farfajiyar Musulunci, da kuma irin gudummuwa da goyon bayan da take samu daga sassan da suke adawa da addinin Musulunci.
- Bayan duba da la'akari masu zurfi akan abubuwan da wannnan ƙungiya ta yi imani da su, da tabbatar da cewa shi Baha'u –wanda shi ne ya kafa wannan ƙungiya- yana da'awar cewa shi manzo ne, yana kuma riya cewa rubuce- rubucensa wahayi ne da aka saukar masa, yana kuma kiran ɗaukacin mutane

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 3/2189).

zuwa ga imani da saƙonsa, yana kuma inkarin cewa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) shi ne cikamakin Manzanni, yana kuma cewa lallai litattafan da aka saukar masa sun shafe abubuwan da Alƙur'ani mai girma ya zo da shi, haka ma ya yi imani da kara-kainan ruhi daga waɗanda suka shuɗe zuwa waɗanda suke biyo bayansu.

- Lura da irin yanda Baha'u ya sabar wa kansa na soke da sassauya hukunce- hukuncen Fiƙihu, kaman yanda ya sauya adadin sallolin da suka wajabta da lokutansu, inda ya mayar da su tara, da ake yinsu a lokuta uku, safiya, da maraice da kuma lokacin zawali, ya kuma sauya taimama, inda ya sanya duk mai bin Baha'iyya kawai zai ce (BismilLahil Aɗɗaharil Aɗɗahari) a maimakon taimama, ya mayar da azumi kwanaki goma sha tara, inda za a ƙare shi a ranar Nairuz a ranar ashirin da ɗaya ga watan Maris na kowace shekara, ya kuma sauya alƙibla zuwa gidan Baha'u da yake garin Aka na ƙasar Falasxinu da Isra'ila take yi wa mulkin mallaka. Ya haramta jahadi, ya kuma yi watsi da haddi, ya daidaita tsakanin namiji da mace a wurin gado, ya kuma halatta kuɗin ruwa (riba).

Bayan lura da bincike da nazarce- nazarcen da aka gabatar akan maudhu'in (Fagagen haɗin kan Musulunci), waɗanda suka ƙunshi gargaɗi akan gurɓatattun ƙungiyoyi da suke rarraba kawunan al'umma, suke kuma raunata haɗin- kanta, su mayar da ita ƙungiyoyi da jam'iyyu masu adawa da juna, da kuma irin yanda hakan yake kai wa zuwa ga yin ridda da nesantar addinin Musulunci, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Kallon abubuwan da Baha'u yake yi na da'awar cewa an aiko shi da saƙo a matsayin manzo, da cewa ana saukar masa da wahayi, kuma wai litattafan da aka saukar masa sun shafe Alƙur'ani mai girma, da shigar da sauye- sauye a sassan Shari'a da suka tabbata ta

hanyar tawaturi, duka waɗannan inkarin sanannen abin da akan sani yana tare da addini ne, kuma duk wanda ya yi irin wannan inkarin za a zartar masa da hukunce- hukuncen kafirci kaman yanda ɗaukacin Musulmai suka yi Ijma'i akan haka.

An kuma yi wasici da abu mai zuwa:

- Wajibi ne hukumomin Musulunci a gaba ɗayan duniya su yi amfani da dukan damammakin da suke da su wajen yaƙar hatsurran da waɗannan ƙungiyoyi suke da su, na yaɗa Ilhadiyanci da manufarsu ita ce gurgunta addinin Musulunci a fagen aƙida da shari'a da tsarin rayuwa

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 35 (10/4)
GAME DA TSARIN SAUƘAƘA ILIMIN FIƘIHU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan duba da nazarin rahoton da aka samar game da tsarin sauƙaƙa ilimin Fiƙihu, wanda ya ƙunshi shawarwarin samar da tsarin kaman yanda ya zo daga kwamitin da aka ɗaura masa alhakin kula da shi,

Bayan duba rahoton ƙaramin kwamitin da aka kafa a lokacin taron shekara- shekara da aka yi nazarin akan tsarin sauƙaƙa ilimin Fiƙihu, da shawarwarin da ya bayar na amincewa da tsarin da aka yi ishara zuwa gare shi, da ɗaura wa sakateriyar Cibiya alhakin bibiya da zartarwa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Amincewa da tsarin da ya zo a rahoton kwamitin da yake kula da tsarin sauƙaƙa ilimin Fiƙihu, daidai da sauye- sauyen da aka bayar da shawarwari akansu, da kuma ɗaura wa sakateriyar Cibiyar alhakin bibiya da zartarwa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 36 (11/4)
GAME DA TSARIN KUNDIN- SHA- KUNDUM NA FIƘIHU DA TATTALIN ARZIKI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan an gudanar da nazari game da rahoton da kwamitin da aka kafa domin samar da tsarin zartar da shirin samar da kundin- sha- kundum na Fiƙihu, da na tattalin arziki ya gabatar, wanda ya ƙunshi matakan da aka bayar da shawarar bi wajen zartar da shirin, da kuma taswirar da aka bayar da shawara bi domin farawa (Tsare-tsaren tarayya), da kuma tsare- tsare da za a bi,

Bayan duba rahoton ƙaramin kwamitin da aka kafa lokacin taron shekara- shekara da aka gudanar domin nazari akan tsarin samar da kundin- sha- kundum na Fiƙihu, da na tattalin arziki, da shawarwarinsa na amincewa da tsarin da aka samar domin zartar da shirin daidai da gyare- gyaren da aka bayar da shawara, da kuma sassan abubuwan da aka bayar da shawarar shigar da su cikin maudu'ai da manazarta da aka ƙara a cikin jerin litattafan da aka dogara da su, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Amincewa da tsarin zartarwa na shirin samar da kundin- sha- kundum na Fiƙihu, da na tattalin arziki,

wanda ya zo a cikin rahoton kwamitin da aka ɗaura wa alhakin samar da shi, daidai da shawarwarin da ƙaramin kwatimin ya bayar, an kuma ɗaura wa sakateriyar Cibiya alhakin bibiya da zartarwa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 37 (12/4)
GAME DA SHIRIN "JAGORAN ƘA'IDOJIN FIḲIHU"

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Bayan an gudanar da nazari akan rahoton da aka samar domin samar da shirin Jagoran ƙa'idojin Fiḳihu, da duba rahoton ƙaramin kwamitin da aka kafa a lokacin gudanar da taron shekara- shekara, domin nazari akan shirin samar da jagoran ƙa'idojin Fiḳihu, da matakan da za a gudanar da aiki a ciki, wanda ya ƙunshi tsarin shirin na ƙarshe, sannan matakai bakwai da aka bayar da shawarar bi a lokacin samar da jagoran ƙa'idojin Fiḳihu, da abin da yake mataki na farko da na biyar na bambancin ra'ayi, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Amincewa da sigar ƙarshe na shirin samar da jagoran ƙa'idojin Fiḳihu, da matakan da dukan ra'ayoyi suka haɗu a kansu cikin shawarwarin da kwamitin samar da shirin ya bayar.
- **Na biyu:** Ɗaura wa sakateriyar Cibiya alhakin bibiya da zartarwa, da zaɓar ra'ayoyin da ta ga sun dace cikin ra'ayoyi guda biyu da kwamitin samar da tsarin shirin ya kawo game da matakin farko da na biyar cikin matakan samar da shirin.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 38 (13/4)([1])
GAME DA HANYOYIN YAƘI DA LALACEWAR ƊABI'U, DA FAGAGEN HAƊIN- KAI NA MUSULUNCI DA HANYOYIN AMFANA DA SU, DA MUSULUNTAR DA ILIMI A ƘASASHEN MUSULMAI A WANNAN ZAMANI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na huɗu a garin Jidda, ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 18 zuwa 23 ga watan Jimadal Akhir, 1408 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 zuwa 11 ga watan Fabrairu, 1988,

Na farko:

Bayan duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in hanyoyin yaƙi da lalacewar ɗabi'u, waɗanda suka bayyana abubuwan da ɗaukacin duniya take fama da shi na lalacewar ɗabi'u, waɗanda sun fara yaɗuwa a ƙasashenmu na Musulmi da yanayin da Allah Maɗaukakin Sarki bai yarda da su ba, ba kuma su yi daidai da nauyin jagoranci da aka ɗaura wa wannan al'umma na jagorantar bil'adama zuwa ga tsarki a fagen aƙida da ɗabi'u da tsarin rayuwa ba.

Lura da kuwa haɗewar da sifofin Musulunci da suke cikakku, da kuma kasancewar ɓangaren kyawawan ɗabi'u a Musulunci yana cikin muhimman ɓangarorin addini, inda ba zai yiwu a sami cikakkun alhairan kasancewa a

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 3/2354 da 2487).

cikin addinin Musulunci sai idan an zartar da Shari'ar Musulunci a aikace daidai da dukan ƙa'idojinsa da hukunce- hukuncensa, a kuma dukan sassan rayuwa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

a- Aiki tuƙuru wajen gyara imani da ƙarfafa shi a cikin zukata, ta hanyar wayar da kai na baki ɗaya, da kuma shigar da tasirin ingantacciyar aƙida a cikin zukata.

b- Aiki wajen tsarkake aikin jarida –wanda ake karantawa, da wanda ake kallo, da wanda ake ji- da ma tallace- tallacen kasuwanci a ƙasashenmu na Musulunci, daga barin dukan saɓon Allah Maɗaukakin Sarki, da tace shi daga barin duk wani abu da zai tayar da sha'awa, ko ya zamo sanadin karkacewa, wanda yake jefa mutane cikin lalacewar ɗabi'u.

c- Samar da tsare- tsare a aikace da za su kai zuwa ga kiyaye asalin tarbiyyar Musulunci da aka gada, da kuma kawo ƙarshen duk wani yunƙuri na kwaikwayon Turawa da sauya ɗabi'un Musulunci wajen koyi da su, da kuma ƙalubalantar duk wani yunƙuri na yaƙin tunani, da na al'adu waɗanda suka ci- karo da ƙa'idoji gami da ɗabi'un Musulunci.

Kuma dole ne a sami tsarin sanya ido akan fagagen yawon buɗe ido, da kuma tura 'ya'yanmu zuwa ƙasashen waje domin nemo ilimi, gudun kada hakan ya zamo hanyar rusa tarbiyyar Musulunci da ɗabi'unsa.

d- Sanya ilimi akan gwadaben Musulunci, da karantar da dukan ilmomi ta mahangar Musulunci, da sanya maddojin Musulunci su zamo ginshiƙai a dukan matakai da sassan ƙwarewa, abin da zai kai zuwa ga ƙarfafa aƙidar Musulunci da dasa kyawawan ɗabi'un Musulunci a cikin zukata, kaman yanda ya wajaba al'umma ta yi duk abin da ya kamata na ta zamo jagora a dukan fagagen ilmomi mabambanta.

e- Gina iyali Musulma akan ingantacciyar turba, da sauƙaƙa hanyoyin yin aure, da kuma kwaɗaitar da

jama'a akansa, da kira zuwa ga iyaye maza da mata akan su kula wajen samar da nagartattun 'ya'ya maza da mata, ta yanda za su taso a matsayin al'umma mai ƙarfi da za su bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki kaman yanda ya kamata, su kuma ɗauki alhakin dawwama wajen yaɗa addinin Musulunci da kira zuwa gare shi, a kuma samar da mace da sifofin da za su ba ta dama wajen taka-rawar da ta dace da ita a matsayinta na uwa, kuma uwar gida, daidai da yanda Shari'ar Musulunci ta tanadar, da kawo ƙarshen abin da ya zama ruwan dare na yaɗuwar masu rainon 'ya'ya da suka zo daga ƙasashen waje, musamman waɗanda ba Musulmai ba.

f- Samar da dukan hanyoyin da za su tabbatar da tarbiyyar yara masu tasowa akan tsarin tarbiyyar Musulunci, ta yanda za su yi riƙo da rukunnan Musulunci da tsarinsa a fagen gudanar da rayuwa, su kuma fahimci abubuwan da suka wajaba akansu da suka shafi Ubangijinsu da al'ummarsu, su kuma kuɓuta daga talaucin ruhi, wanda shi ne yake kai wa zuwa ga shaye- shaye, da lalacewar ɗabi'u ta mabambantan hanyoyi, da shagaltar da matasa da abubuwa masu muhimmanci, da ɗaura su akan alhakin da yake a kansu, kowa gwargwadon iko, da daman da yake da su, da shagaltar da lokutansu da abubuwa masu amfani, da samar masu da hanyoyin shaƙatawa da na wasannin motsa- jiki da kacici-kacici masu tsafta, duka dai a fuskantar da su zuwa ga cikakken inda Musulunci ya dosa.

Na biyu:

Bayan duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar akan maudhu'in Haɗin kan al'umma da hanyoyin fa'idanta da shi, tare da la'akari da muhimmancin gabatar da 'yan uwantaka ta Musulunci tsakanin ɗaukacin al'ummar Musulmai, inda hakan yake a matsayin igiyar da ba za ta

taɓa yankewa ba, kuma ita ce harsashen taimakekeniya da goyon bayan da ake fata, kuma ita ce tabbatacciyar ƙa'idar gina kowane irin cigaba da yake nufin samar da haɗin- kai da daidaita sahu, da kuma haɗa dukan ƙoƙarin da ake yi wajen fuskantar ƙalubalen zamani, da samar da izza gami da cigaba,

Ganin cewa 'yan uwantakar Musulunci ita ce ginshiƙi mafi ƙarfi, ko dawwamammen dalili da zai kai zuwa ga kyautata mafuskanta, da tuntuɓar juna wajen haɗa siyasar ƙasashen Musulunci a dukan fagagen ayyukan raya ƙasa da haɓaka tattalin arziki da rayuwar zamantakewa, da kuma ƙarfafa dangantakar taimakekeniya da taimakon juna, da sanya tausayi tsakanin al'umma wajen kawar da duk wani abu da zai zama cikas a tafiyarta, cikin abubuwan da suke sanya ta ta zamo mai bi ba wanda ake bi ba, su kuma taimaka mata wajen fuskantar ƙalubalen zamani da suke gabanta, a yunƙurin isa zuwa ga cigaba da haɓakar tattalin arziki da ɗaukaka, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **a.** Bai wa aƙidar Musulunci kariya, da tabbatar da ita kaman yanda take cikin tsafta ba tare da an bar wani abu ya yi mata hazo- hazo ba, da kuma yin gargaɗi akan duk wani abu da zai kai zuwa ga rusa ta, ko sanya shakka akan tushe gami da asalinta, ya kuma kai zuwa ga rusa haɗin- kan da yake tsakanin Musulmai, ya sanya su zamo masu saɓani da junan da za su rinƙa cin- duduniyar juna.
- **b.** Ƙarfafa kulawar da Cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya take yi da bincike da nazarce- nazarce a fagen Fiƙihu, waɗanda suke fuskantar ƙalubalen da ake fuskanta a fagen tunani, musamman waɗanda zamani ne ya zo da su, da sanya Fiƙihun Musulunci ya zamo yana muhimmanta matsalolin rayuwar zamantakewa, da dogara da shi a matsayinsa na ginshiƙi wajen farfaɗo cigaba al'umma a fagen tunani, da faɗaɗa shi ta yanda ƙasashen Musulmai za su

dogara da shi wajen sanya dokoki a dukan sassan da suka shafi rayuwar zamantakewa.

c. Wajibcin tuntuɓar juna mai ƙarfi a fagen tarbiyya da karantarwa, sawa'un a cikin abubuwan da suka ƙunsa ne, ko wajen bin manhaji, akan daidaitacciyar hanyar cigaba a fagen tunanin da Musulunci ya gina, ta yanda za a samar da al'umma Musulma da suka haɗu akan madogarar wurin bauta, masu kuma kusanci da juna wajen tunani, masu haɗin gwiwa da tarayya wajen alfahari da zamowarsu abu ɗaya wajen dangantaka da cigaba.

d. Bai wa bincke na ilimi muhimmanci mai girma a dukan fagagen ilmomi da sani, da keɓance kashi 1% na ɗaukacin arzikin al'umma wajen ɗaukan nauyin tsare- tsaren bincike, da samar da ɗakunan gwaje-gwaje na ilimi akan wata turba na cikasa juna da taimakekeniya tsakan jami'o'in Musulunci.

e. Aiki tare da jami'o'in Musulunci wajen ƙayyade tsarin karantarwa da zai ƙunshi manyan ginshiƙai, inda za su zamo fagen binciken Fiƙihu, da samar da kwamitin ƙoli da zai haɗa manyan malaman Musulunci domin bibiyar waɗannan bincike da amincewa da su, a kuma wajen kyaututtuka ga waɗanda suka fi kyau daga cikinsu.

f. Sanya gaba ɗayan aikin jarida (jarida da talebiji da radiyo) a ƙasashen Musulmai su zamo suna da manufar da take kai wa zuwa ga tabbatar da bauta wa Allah a doron ƙasa, da yaɗa alhairi da kyawawan ɗabi'u, su kuma kuɓuta daga ƙa'idojin da suke rusa tunani da kyawawan ɗabi'u, waɗanda suke kai wa zuwa ga yi wa addinin Allah tawaye da ilhadiyanci, da waɗanda suka karkace ga barin madaidaiciyar hanya. Da kuma ƙarfafa ayyukan da suke yi.

g. Samar da tsarin tattalin arziki na Musulunci, ba wanda zai dogara da wani ba, in ba tsantsar Musulunci, tare da samar da kasuwar Musulunci ta

tarayya, inda Musulmai za su yi taimakekeniya wajen samar da kayan cikinta, da kuma tallata su ba tare da sun buƙaci waninsu ba, saboda tattalin arziki babban ginshiƙi ne wajen kafa al'ummomi, da cikansu wajen samar da hadin kai tsakanin al'ummar Musulmai.

Na uku:

Bayan la'akari da cewa tabbas Musuluntar da karantarwa a ƙasashen Musulmai a wannan zamanin wajibi ne da babu makawa sai an yi shi; saboda gina nagartacciyar al'umma da take cika juna a fagagen tunani da hangen- nesa da tsarin rayuwa da gunadar da ayyuka, **an sake tabbatar da wasici mai zuwa:**

Sanya dukan ilmomi su zamo suna tafiya ne daidai da Musulunci a wajen farawarsu da manufofinsu, ya kuma zamo addinin Musulunci da tsare- tsarensa da ƙa'idojinsa su ne suka kewaye waɗannan ilmomin, aƙidar Musulunci kuma ta zamo ita ce ƙa'ida kuma asali wajen gina manhajin tarbiyya da karantarwa, za a iya taƙaita muhimman ginshiƙan manhajin da ake fata a wajen Musuluntar da karantarwa a cikin abubuwa masu zuwa:

a- Sanya aƙidar Musulunci ta zamo ita ce mahangar da za a sanya a gaba wajen hango gaba ɗayan halittun Allah, da ɗan Adam, da rayuwa, kaman yanda take karantar da ɗan Adam yanda zai san mahaliccin wannan rayuwar, take kuma bayyana dangantakarsa da waɗannan halittun, da ma dangantakar ɗan Adam da Ubangijinsa, da ma al'ummar da yake gudanar da rayuwarsa ta zamantakewa tare da su.

b- Daukan Musulunci a matsayin shi ne tushen dukannin ilmomin zamantakewa da na mutuntaka da tattalin arziki da siyasa, da fito da hasashensa game da mutuntaka da dangantakarsu da mahaliccin halittu da ɗan Adam da rayuwa, tare da tuntuɓa da taimakekeniya tsakanin ƙungiyoyin Musulunci da suke aiki a wannan fage, kaman ƙungiyar Musulunci

mai kula da ilmomin likitanci (IOMS)([1]), da ƙungiyar Musulunci mai kula da karantarwa da ilmomi da al'adu (ISESCO)([2]).

c- Aiki tuƙuru wajen bayyana ɓacin abubuwan da suka saɓa da aƙidar Musulunci cikin ilmomin da suke muhimmanta rayuwar duniya kawai, da yaɗa ilhadiyanci, da duk ilmomin da suke ɓatar da al'umma, kaman bokanci, da tsafi, da duba, da yin gargaɗi akan ilmomin da Musulunci ya haramta su, haka ma da ilmomin da suka ginu akan fasiƙanci da aikata saɓo.

d- Sake rubuta tarihin ilmomi, da bayyana matakan da suka bi wajen cigaba da haɓaka, da gudummuwar da Musulmai suka baya a cikinsu, da kuma tsarkake su ga barin abubuwan da aka cusa a cikinsu na hasashe-hasashen turawan yamma da suke gurɓata tarihinsu na gaskiya, da sake duba yanda aka tsara ilmomi da manhajojin bincike, daidai da yanda Musulunci yake kallonsu, ta hanyar ayyukan da cibiyoyi da manyan makarantun binciken ilimi da cibiyoyin tattalin arziki na Musulunci a ko'ina a ƙasashen Musulmai suke yi.

e- Dawo da dangantaka tsakanin ilmomin da suke bincike akan halittu da ɗan Adam da rayuwa, da Mahaliccinsu, lallai ya kamata malamin da yake bincike a waɗannan fagage ya duba irin yanda Allah gwani ya gudanar da halittarsa, cikin wani yanayi na ƙwarewa mai cike da hikima.

f- Samar da ƙa'idojin da za a ciro su daga karantarwar addini, ko waɗanda suka yi daidai da manufofinsa, saboda su zama ƙa'idoji a dukan ilmomi ko wani ilimi guda ɗaya, da kuma bayyana aibobin manhajojin Turawa waɗanda suka shiga tsakanin addini da ilimi suka yi masu katanga, ko suka sanya

([1]) Islamic Organization for Medical Sciences
([2]) Islamic Educational, Scentific and Ciltural Organization

aka gina wasu ilmomin a karkace, kaman ilimin tarihi da na tattalin arziki da na zamantakewa.

Ya kamata a sani cewa lallai akwai wani shiri mai girma da yake a matsayin madogarar Musulunci wajen Musuluntar da karantarwa, hasali ma yana ɗaya daga cikin muhimman ayyukan da dole ake buƙatarsu, wannan shiri kuwa shi ne shirin "Musuluntar da ilimi" wanda Cibiyar duniya ta tumanin Musulunci([1]) take gudanar da shi wajen tsare- tsare da shata taswiyar hanyoyin zartarwa ta hanyar maƙalu da rubuce- rubuce da tarurrukan ƙara wa juna sani.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) The International institute of Islamic Thought

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA BIYAR NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

KUWAIT

1 - 6 GA WATAN JIMADAL ULA, 1409 H

10 – 15 GA WATAN DISAMBA, 1988

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 39 (1/5)([1])
GAME DA TSARIN IYALI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in tsarin iyali, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa,

Bayan la'akari da cewa lallai haihuwa da kiyaye nau'in ɗan Adam ɗaya ne daga cikin manyan manufofin aure a Shari'ar Musulunci, kuma sam bai halatta a yi watsi da wannan manufar ba, saboda yin watsi da ita ya saɓa da Nassoshin Shari'a da karantarwarsa da take kira zuwa ga yawaitar tsatso, da kuma kiyaye shi, da bashi kulawa ta musamma, ganin cewa kiyaye tsatso ɗaya ne daga cikin manyan manufofin Shari'a guda biyar wadanda Shari'o'i suka zo domin su ba su kulawa ta musamman, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Bai halatta a yi doka da za ta taƙaita 'yancin ma'aura biyu wajen haihuwa ba.
- **Na biyu:** Haramun ne a dakatar, ko a cire damar da na namiji, ko mace suke da ita na haihuwa (dandaƙa), abin da ake kiransa da (sterilization), matuƙar ba halin

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta huɗu, 1/73).

lalura ne ya sanya a yi hakan ba, shi ma dole ne ya kasance ƙarƙashin ma'aunan da Shari'a ta sanya.

- **Na uku:** Ya halatta a yi tsari na wucin- gadi wajen haihuwa da niyyar bayar da tazara tsakanin lokutan ɗaukan ciki, ko dakatar da ɗaukan cikin na wani lokaci, idan akwai buƙatar da Shari'a take la'akari da shi, daidai da ƙaddarawar ma'aurata ta hanyar shawara da yarda a tsakaninsu, da sharaɗin kada yin hakan kuma haifar da cutuwa, ya kuma zamana hanyar da aka bi aka yi hakan halattacciyar hanya ce da Shari'a ta amince da ita, kada kuma ya zamo zaluntar cikin da ya riga ya tabbata ne.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 40 - 41 (2/5 DA 3/5)([1]) GAME DA CIKA ALƘAWARIN GUDANAR CINIKAYYA A NAN GABA DAGA ƁANGARE ƊAYA, DA ƊAURA WA WANDA AKA BAI WA SAUTU KO SAƘO RIBA([2])

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar akan maudhu'in cika alƙawari da ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba, ta kuma saurari tattaunawar da ta gudana akansu, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** lallai idan cinikin ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba ya faru ne bayan kayan ya riga ya shiga hannun wanda aka bashi umurnin saye, ya zama ya karɓa kaman yanda Shari'a ta gindaya, to wannan ciniki ya halatta, matuƙar dai alhakin lalacewar kayan kafin ya miƙa wa mai bayar da umurnin, da abubuwan da suke biyo bayan cinikin

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 2/754 da 965).

([2]) Abin da ake nufi da: ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba a nan shi ne: Mutum ya nemi banki ya saya masa wani abu daidai da sifofin da shi ne ya zayyana, akan cewa shi ya yi alƙawarin zai sayi abin a aikace bayan ya ƙara wa bankin ribar da za su haɗu shi da bankin su yi ittifaƙi a kansa. Wannan ne a harshen Shari'a ake kira da sunan المرابحة للآمر بالشراء

irinsu mayar da kaya saboda bayyanar aibi da makamantan haka, da suke dalilai ne na mayar da kaya bayan an amsa suna kan wanda aka bai wa umurnin ne, ya kuma zamana an cika sharuɗɗa ciniki, inda babu abubuwan da suke hana gudanar da shi.

- **Na biyu:** Alƙawari wanda mai bayar da umurni, ko wanda aka bai wa umurnin ya yi a karan kansa, zai zamo yana kan wanda ya yi a addinance, wajibi ne a cika shi idan an rataya shi da wani dalili, ya kuma zamana wanda aka yi wa alƙawarin ya shiga cikin wani hali sakamakon alƙawarin da aka yi. A wannan yanayi wannan wajibi yana cika ne, ko dai ta hanyar zartar da alƙawarin da aka yi, ko kuma a biya makwafin cutuwar da ta auku sakamakon rashin cika alƙawarin ba tare da wani hanzari ba.
- **Na uku:** Alƙawarin da duka ɓangarori biyun suke yi wa juna ya halatta a cikin cinikin ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba da sharaɗin cewa dukansu suna da zaɓi, a matsayinsu na su biyu a haɗe, ko kowanne daga cikinsu a matsayinsa na shi ɗaya, idan babu wannan haƙƙi na zaɓi, to cinikin bai halatta ba, saboda shi alƙawarin da ya wajaba a cika shi a cikin cinikin ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba yana kama da kasuwanci kansa, inda kuma a irin wannan yanayi an sanya sharaɗin dole mai sayarwa ya zama yana mallakar abin da yake sayarwa, gudun kada a saɓa wa hanin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi na kada mutum ya sayar da abin da bai mallaka ba.

An kuma bayar da wasici mai zuwa:

Bayan an lura da cewa ɗaukacin bankunan Musulunci sun fi mayar da hankali wajen sanya kuɗinsu ta hanyar ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba.

- **Na farko:** Ya kamata ayyukan bankunan Musulunci ya ƙara faɗaɗa cikin salo mabambanta na haɓaka tattalin arziki, musamman samar da shirye- shirye na

masana'antu, ko na cinikayya, da ƙoƙarin kansu, ko kuma ta hanyar yin tarayya da mudaraba, tare da wasu ɓangarorin.

- **Na biyu:** A gudanar da nazari akan nau'o'in gudanar da cinikin ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba a aikace kaman yanda bankunan Musulunci suke yi, domin a samar da ƙa'idojin da za su hana aukawa cikin kuskure a lokacin aiwatarwa, su kuma taimaka wajen kulawa da hukunce- hukuncen Shari'a na bai ɗaya, da keɓaɓɓu waɗanda suka shafi cinikin ɗaura wa wanda aka bai wa sautu, ko saƙo riba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 42 (4/5)([1])
GAME DA SAUYAWAR DARAJAR KUƊI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in sauyawar darajar kudi, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa,

Bayan ta duba ƙudurin Cibiyar mai lamba 21 (9/3) na taron shekara- shekara karo na uku, wanda ya tabbatar da cewa: lallai takardar kudi, kudi ne da ake la'akari da shi, tana da cikakkiyar sifar da kudi yake da ita, tana da dukan hukunce- hukuncen da aka tabbatar wa zinare, da azurfa a wurin hukunce- hukunce: riba, da zakka, da salam, da sauran hukunce- hukuncensu, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Abin da za a yi la'akari da shi wajen biyan basussukan da suka tabbata da wani nau'i na takardun kudi shi ne kwatankwacinsa ba ƙimarsa ba, saboda shi bashi ana biyansa ne da kwatankwacinsa, bai halatta a hada basussukan da suka hau kan zimma da darajar farashi ba, ko mene ne kuwa ya kai zuwa ga bashin.

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 3/1609).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 43 (5/5)([1])
GAME DA HAƘƘOƘI NA MA'ANA (MORAL RIGHTS)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in haƙƙoƙi na ma'ana (moral rights), ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Sunan kasuwanci, da adireshin kasuwanci, da alamar kasuwanci, da wallafa, da ƙirƙira daga wani abu da yake akwai shi, da ƙirƙira daga abun da babu shi, duka waɗannan haƙƙoƙi ne da masu shi suka keɓanta da su, inda a al'adar da wannan zamanin ya tabbatar suna da ƙima na kuɗi da ake la'akari da su, inda mutane suke sanya kuɗi akansu, waɗannan haƙƙoƙi ne da Shari'a take la'akari da su, sam bai halatta a kutsa cikinsu da zalunci ba.
- **Na biyu:** Ya halatta a yi tasarrufi a cikin sunan kasuwanci, ko adireshin kasuwanci, ko alamar kasuwanci, ko a sauyi kowanne daga cikinsu da kuɗi, idan babu ruɗi, ko rufa- rufa, ko algushi a ciki, saboda hakan ya riga ya zama haƙƙi ne na kuɗi.

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 3/2267).

- **Na uku:** Haƙƙoƙin wallafa, da na ƙirƙira dukansu suna da kariya da Shari'a ta ba su, masu su suna da haƙƙin tasarrufi a cikinsu, sam bai halatta a kutsa cikinsu da zalunci ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 44 (6/5)([1])
GAME DA HAYAR DA TAKE ƘAREWA DA MALLAKA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in hayar da take ƙarewa da mallaka, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa,

Bayan ta duba ƙudurin Cibiyar mai lamba 31 (1/3) na taron shekara- shekara na uku, game da tambayoyin da bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa([2]) (IsDB) ya yi, a sakin layi (b), wanda ya keɓanci ayyukan haya, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Abin da ya fi shi ne a wadata ga barin surorin hayar da take ƙarewa da mallaka da wasu hanyoyin da za su kwafe makwafinsu, a cikin hanyoyin da za su iya kwafewa makwafinsu akwai wadannan guda biyu masu zuwa:

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 4/2593).
([2]) Islamic Deɓelopment Bank

- **(Na ɗaya):** Aikin sayar da kaya zuwa wani lokaci, tare da rarraba lokacin biya (Instalment sales), tare da samun cikakken lamuni.
- **(Na biyu):** Ƙulla yarjejeniyar haya tare da bai wa ɗan haya zaɓi akan ɗaya daga cikin abubuwa masu zuwa, bayan ya biya dukan kason kuɗin hayan da ya yi a tsawon lokacin da ya yi yana hayar:
  - Ƙara lokacin hayar.
  - Kawo ƙarshen yarjejeniyar hayar da mayar da abin da aka haya zuwa ga mai shi.
  - Sayen abin da aka haya da farashin kasuwa na lokacin ƙarewar hayar.

- **Na biyu:** Akwai sura guda ɗaya ta hayar da take ƙarewa da mallaka da aka sami saɓani akanta, an ɗauki ƙudurin jinkirta duba ta zuwa taron shekara-shekara mai zuwa, bayan an gabatar da fom ɗin yarjejeniya akanta, da bayanan da suke kewaye da ita na ƙaidi da yanayi, tare da taimakekeniya da bankunan Musulunci, saboda a yi nazarinta, a kuma fitar da ƙuduri game da ita.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 45 (7/5)
GAME DA BAYAR DA BASHI DOMIN SAYEN TABBATACCEN ABU (Mortgage Finance) SABODA GINA MATSUGUNI DA SAYENSA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta bijiro da maudhu'in bayar da bashi domin sayen tabbataccen abu (Mortgage Finance) saboda gina matsuguni da sayensa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- An jinkirta duba maudhu'in bayar da bashi domin sayen tabbataccen abu (Mortgage Finance) saboda gina matsuguni da sayensa, har zuwa a fitar masa da ƘUDURI MAI LAMBAsa na musamman a taron shekara- shekara karo na shida, saboda a ƙara nazari da bincike akansa([1]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta Biyar, 4/2773) da (Fitowa ta Shida, 1/81).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 46 (8/5)
GAME DA IYAKANCE RIBAR 'YAN KASUWA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in iyakance ribar 'yan kasuwa, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Asalin abin da Nassoshi da ƙa'idojin Shari'a suka tabbatar shi ne a bar mutane da cikakken 'yancinsu wajen saye da sayarwarsu da tasarrufi cikin abubuwan da suka mallaka da dukiyoyinsu, ƙarƙashin hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci mai haske da ƙa'idojinta, saboda aiki da maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada ku kuskura ku ci dukiyoyin junanku ta hanyar ɓarna, sai dai idan hakan ya kasance ta hanyar kasuwanci ne da ya sami cikakkiyar yarda daga gare ku..)** [an- Nisa'i: 29].
- **Na biyu:** Ba a ƙayyade iyaka, ko kaso na riba da dole ɗan kasuwa ya yi aiki da shi wajen mu'amalolinsa na kasuwanci ba, hasali ma an bar haka ne ya zamo daidai da yanayin kasuwa, da yanayin ɗan kasuwa da kuma hajar da yake cinikayya da ita, tare da lura da

abubuwan da ladubban Shari'a suka tabbatar na yin rangwame da wadatuwar zuci, sa tausayi gami da saukaƙawa.

- **Na uku:** Nassoshin Shari'ar Musulunci masu yawa sun zo akan wajibcin kauce wa dalilan da suke kai wa zuwa ga abubuwan da aka haramta irinsu algushi, da yaudara, da rufa- rufa, da shammatan mutane, da sauya haƙiƙanin riba, da ɓoye kayan amfani saboda ya yi tsada a fito da shi a sayar, abubuwan da suke cutar da ɗaukacin al'umma da keɓantattu.
- **Na huɗu:** Shugaba ba zai sanya farashin kayayyaki ba sai idan an sami bayyanannen giɓi wajen sanya farashi a cikin kasuwa, shi ma hakan ya zamo ƙirƙirarren abu ne, to a nan shugaba zai shiya ta hanyoyin daidaito da adalci, ta yanda zai toshe wannan giɓi ya kawo ƙarshe dalilan tsada da tashin goron zaɓin da kayayyakin suka yi.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 47 (9/5)([1])
GAME DA AL'ADA (AL- URFU)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in al'ada (al- Urfu), ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Abin da ake nufi da al'ada shi ne abin da mutane suka saba da shi, rayuwarsu ta wajen magana, ko aiki, ko bari ta ginu akansa, za ta iya zamowa abin la'akari a Shari'a, ko wadda Shari'a ba ta la'akari da ita.
- **Na biyu:** Idan al'ada ta zamo keɓantacciya, to kuwa tana da matsayi a wurin masu ita, idan kuma ta gama-gari ce to kuwa tana da matsayi a wurin kowa da kowa.
- **Na uku:** Al'adar da Shari'ar Musulunci take la'akari da ita, ita ce wadda ta cika sharuɗɗa masu zuwa:
  - **a.** Kada ta saɓa wa Shari'a, idan al'ada ta saɓa wa Nassin Shari'a, ko wata ƙa'ida cikin ƙa'idojin Shari'a, to ta zama ɓatacciyar al'ada kenan.

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 4/2921).

b. Ya zamo ana cigaba da aiki da ita ba tare da yankewa ba, ko a yanayi mafi rinjaye.
c. Ya zamo akwai al'adar a lokacin fara mu'amalar.
d. Ya zamo masu ƙulla yarjejeniyar su biyu ba su bayyana manufarsu da saɓa mata ba, idan sun bayyana saɓa mata, to ba a la'akari da ita.

- **Na huɗu:** Bai halatta masanin Fiƙihu –shin mai bayar da fatawa ne, ko alƙali- ya takure kansa akan abin da ya zo a cikin litattafan malaman Fiƙihu, ba tare da la'akari da sassauyawar al'adu ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 48 (10/5)([1])
GAME DA AIKI DA HUKUNCE- HUKUNCEN SHARI'AR MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba binciken da mambobi, da ƙwararru suka gabatar mata akan maudhu'in aiki da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar game da haka,

Ganin cewa Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta samu ne sakamakon kyakkyawar manufa daga taron ƙoli na ƙungiyar ƙasashen Musulmai (OIC) mai lamba uku da aka gudanar da shi a gari Makka, da niyyar samar wa matsalolin al'ummar Musulmai da mafita ta Shari'a, da kuma saita al'amurran da suka shafi rayuwar Musulmai ƙarƙashin karantarwar Shari'ar Musulunci, da kuma kawar da duk wani abu da zai kawo cikas wajen yin aiki da Shari'ar Allah, da kuma samar da dukan yanayi da damammaki da za su bayar da daman a yi aiki da ita, saboda bayyana cikakken mulkin Allah Madaukakin Sarki, da kuma tabbatar da jagorancin Shari'arsa, da kawar da cin- karon da ake samu tsakanin shugabannin Musulmai

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 4/3471).

da al'ummominsu, da kuma kawar da dalilan da suke kai wa zuwa ga tashin hankali da cin- karo gami da rikice-rikice a ƙasashensu, saboda a samar da cikakken aminci da tsaro a ƙasashen Musulmai, **an tabbatar da ƙudiri mai zuwa:**

Lallai farkon abin da ya wajaba akan duk wani wanda yake jagorantar al'amurran Musulmai shi ne ya yi aiki da Shari'ar Allah a cikinsu.

Majalisar tana kira zuwa ga ɗaukacin hukumomi a ƙasashen Musulmai da su fara aiki da Shari'ar Musulunci, su sanya ta zamo ita ce abin koma wa zuwa gare ta a komai, a kuma dukan fagagen rayuwa, tana kuma kira zuwa ga al'ummomin Musulmai, ɗaiɗaikun mutane da al'ummomi, da ƙasashe akan su yi riƙo da addinin Allah Maɗaukakin Sarki, su zartar da Shari'arsa a aikace, ganin cewa wannan addini ne da yake da ɓangarorin aƙida, da Shari'a, da tsarin rayuwa a aikace.

Ta bayar da wasici da abubuwa masu zuwa:

a) Cigaba da bincike da nazari masu zurfi akan dukanin sassai da suke da jiɓi da maudu'in yin aikin da Shari'ar Musulunci, da kuma bibiyan abubuwan da aka cimma game da wannan al'amari a ƙasashen Musulmai.

b) Tuntuɓar juna tsakanin Cibiyar da wasu cibiyoyin ilimi da suke bai wa wannan maudhu'i na yin aiki da Shari'ar Musulunci muhimmanci, da samar da tsare-tsare, da hanyoyi, gami da bincike da za su iya kawar da duk wata matsala da shubuha da za ta ita kawo cikas wajen yin aiki da Shari'a a ƙasashen Musulmai.

c) Tattara ayyukan tsara dokokin Musulunci waɗanda an riga an samar da su a ƙasashen Musulmai mabambanta, saboda a yi nazari akansu a amfana da su.

d) Kira zuwa ga yin gyara a tsarin manhajojin tarbiyya da karantarwa da hanyoyin yaɗa labarai mabambanta, da yin amfani da su wajen yin aiki da

Shari'ar Musulunci, da kuma samar da matasa Musulmai masu tasowa da za su yi aiki da Shari'ar Allah Maɗaukakin Sarki.

e) Faɗaɗa bayar da horaswa ga ɗalibai da waɗanda suka gama karatun jami'a cikin alƙalai da wakilan hukumomin shigar da ƙara, da lauyoyi, saboda a samar da cikakken ƙarfin da ake buƙata wajen yin aiki da Shari'ar Musulunci a aikace.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 49 (11/5)
GAME DA KWAMITIN MUSULUNCI NA ƘASA DA ƘASA MAI LURA DA DOKA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na biyar a ƙasar Kuwait, wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Jimadal Ula, 1409 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 10 zuwa 15 ga watan Disamba, 1988,

Bayan ta duba bayanin da aka rubuta game da muhimman tsare- tsare na kafa kwamitin Musulunci na ƙasa da ƙasa mai lura da doka, wanda taron ƙara wa juna sani na goma sha bakwai da ministocin harkokin wajen ƙasashen Musulmai, wanda aka gudanar a Amman na ƙasar Jordan ya bayar da umurnin kafawa da ƙuduri mai lamba (45/17- S), an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

An amince da gudanar da nazari game da muhimman tsare- tsaren kafa kwamitin Musulunci na ƙasa da ƙasa mai lura da doka, da miƙa ayyukan da aka wakilta zuwa ga kwamitin, saboda ya zamo cikin ayyukan da cibiyar take gabatarwa.

Allah ya sa mu dace;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA SHIDA NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

JIDDA (SAUDIYYA)

17 - 23 GA WATAN SHA'ABAN, 1410 H

14 – 20 GA WATAN MARIS, 1990

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 50 (1/6)([1])
GAME DA BAYAR DA BASHI DOMIN SAYEN TABBATACCEN ABU (Mortgage Finance) SABODA GINA MATSUGUNI DA SAYENSA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in bayar da bashi domin sayen tabbataccen abu; saboda gina matsuguni da sayensa, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Lallai samun matsuguni yana cikin manya, kuma muhimman buƙatun da ɗan Adam yake da su, ya kuma zama dole a biya wannan buƙatar da halattaciyar hanya, da kuɗin halal. Kuma lallai hanyar da bankunan gidaje da matsugunai da makamantansu suke bi na bayar da bashi da ruwa –mai yawa ko kaɗan- ita ce ainihin hanyar da Shari'a ta haramta, saboda akwai mu'amala da riba a ciki.
- **Na biyu:** Akwai halattatun hanyoyin samar da matsuguni ta hanyar mallaka da za su wadatar ga barin bin haramtattun hanyoyi, (akwai kuma yiwuwar

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta biyar, 4/2773) da (1/81).

su samar da su ta hanyar haya), a cikin hanyoyin akwai:

a- Gwamnati ta bai wa waɗanda suke sha'awar mallakar matsugunai bashin da aka keɓance su saboda samar da gidaje, inda su kuma za su biya sannu a hankali kashi- kashi ba tare da ɗaura masu riba ba, shin wannan riba an ambace ta ƙarara, ko kuwa an saya ta ƙarƙashin wani suna (kuɗin hidima), idan ma akwai buƙatar a amshi kuɗin hidindumun da aka yi wajen bayar da bashin da bibiyansa, to dole ne a taƙaita akan daidai abin da aka kashe a aikace, kaman yanda aka bayyana a sakin layi na (a) cikin ƙuduri mai lamba 13 (1/3) na taron wannan Cibiyar na shekara- shekara karo na uku.

b- Ƙasashen da suke da ƙarfi kuma gwamnatocinsu su ɗauki alhakin gina matsugunai, sai su sayar wa waɗanda suke da sha'awar su mallaka da kuɗin da za su rinƙa biya kaso- kaso cikin mabambanta lokuta, daidai da sharuɗɗan da aka bayyana a ƙuduri mai lamba 51 (2/6) na taron shekara-shekara na wannan karo.

c- Haka ma masu zuba jari (ɗaiɗaikun mutane ko kamfanoni) su shiga kasuwancin gina gidajen da za a sayar da su bashin da za a rinƙa biya lokaci-lokaci.

d- A mallaka wa mutane matsugunan ta hanyar ƙulla yarjejeniyar jinga (Istisna'a contract) –akan cewa shi ne ya wajaba-, da haka za sayi gidan kenan kafin a gina shi, daidai da sifofin da aka bayyana waɗanda za su kawar da jahiltar da za ta iya kai wa zuwa ga rikici, ba kuma tare da an wajabta gaggauta biyan dukan kuɗin ba, hasali ma ya halatta a jinkirta biya a kuma karkasa shi daidai da yarjejeniyar da aka haɗu a kai, tare da lura da sharuɗɗa da kuma yanayin da aka tabbatar da

tsarin jinga (Istisna'a contract) a wurin malaman Fiƙihun da suke bambanta shi da cinikin salam.

An kuma bayar da wasicin:

Cigaba da bincike saboda a samar da wasu halattattun hanyoyin da za a iya mallaka gidajen ga masu sha'awar mallaka.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 51 (2/6)([1])
GAME DA SAYAR DA KAYA ZUWA WANI LOKACI, TARE DA RARRABA LOKACIN BIYA (INSTALMENT SALES)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in sayar da kaya zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya (Instalment sales), ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Ya halatta a yi wa farashin da aka jinkirta biyansa ƙari akan farashin da za a biya nan take, kaman yanda ya halatta a ambaci farashin saye kuɗi- hannu, da kuma farashinsa idan an rarraba lokutan biya zuwa wani lokaci sananne, sai dai irin wannan kasuwanci ba ya zama ingantacce sai idan mai saye da mai sayarwa sun yi riƙo ko dai kuɗi – hannu, ko kuma za a jinkirta biya. Idan cinikin ya faɗa duk kuwa da cewa akwai kokwanto tsakanin biya kuɗi- hannu da kuma jinkirtawa, ma'ana ba a kai zuwa ga samun yankakkiyar yarjejeniya akan hanyar biyan kuɗin

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 1/193) da (Fitowa ta bakwai, 2/9).

guda ɗaya ba, to wannan cinikayya ba ta halatta ba a Shari'anci.

- **Na biyu:** A cinikin da aka yi za a biya zuwa wani lokaci, sam bai halatta a ambaci ƙarin fa'idar rarraba lokacin biya a cikin yarjejeniyar, da zai zama an ware shi daga farashin kuɗi- hannu ba, ta yanda zai zamo yana rataye ne da lokacin, shin mai saye da mai sayarwa sun cinma yarjejeniya akan kason fa'idar ne, ko kuwa sun haɗe ta da fa'idar da aka saba ta'amuli da ita, duk ɗaya ne.
- **Na uku:** Idan mai sayen da ake bi bashi ya yi jinkiri wajen biyan kason da aka rarraba a lokacin da aka iyakance, sam bai halatta a tilasta masa biyan wani ƙari akan bashin da yake a kansa sakamakon wani sharaɗi da ya gabata, ko kuma ba ma da sharaɗi ba; saboda hakan riba ne da Allah ya haramta.
- **Na huɗu:** Haramun ne wanda ake bi bashin –da yake da abin da zai sauke nauyin bashin- ya yi taurin-biyan bashi idan lokacin biyan kason ya zo, sai dai duk da haka bai halatta a sharɗanta masa wani ƙari idan ya yi jinkirin biya ba.
- **Na biyar:** Ya halatta mai sayar da kaya zuwa wani lokaci ya sanya sharaɗin da zai sanya cancanta biyan kason kafin lokacin biyan, idan wanda ake bi bashin ya yi jinkirin biyan wani sashe na bashin, matuƙar wanda ake bi bashin ya yarda da wannan sharaɗin a lokacin ƙulla yarjejeniyar.
- **Na shida:** Mai sayarwa ba shi da haƙƙin cigaba da riƙe abin da ya sayar bayan sayarwa, sai dai ya halatta mai sayarwar ya sanya wa mai saye sharaɗin bayar da jingina domin ya sami lamunin haƙƙinsa wajen biya kason da aka jinkirta.

An bayar da wasici mai zuwa:

Jinkirta nazarin wasu mas'aloli da suke da jiɓi da sayar da kaya zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya

(Instalment sales), har zuwa a sami matsaya akansu bayan an gudanar da cikakkun nazari da bincike akansu, irinsu:

a- Zamiyen kason da aka rarraba a banki da mai sayar da "Kanbiyala"([1]) zai yi.

b- Gaggauta biyan bashin da sharaɗin yafe wani sashe nasa, wato mas'alar (Yafe wani sashe, ka amshi bashinka nan take)

c- Tasirin mutuwa wajen kusanto da lokacin biyan sauran kason da aka jinkirta.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) *Kanbiyala:* tana nufin: wata takarda ce ta kasuwanci da take da ɓangarori uku, umurni ne daga ɓangare na farko zuwa ga ɓangare na biyu akan ya bai wa ɓangare na uku wani adadi na kuɗi idan ya ga wannan takarda, ko zuwa wani lokaci ba tare da sanya wani tarnaƙi ko sharaɗi ba.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 52 (3/6)([1])
GAME DA HUKUNCIN GUDANAR DA HULƊODI DA YARJENIYOYI TA SABABBIN HANYOYIN SADARWA NA ZAMANI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in gudanar da huldodi da yarjeniyoyi ta sababbin hanyoyin sadarwa na zamani,

Duba da irin gagarumin cigaban da aka samu a hanyoyin sadarwa, inda ake aiki da su wajen ƙulla kasuwanci, da yarjeniyoyi saboda saurin gudanar da mu'amalolin kudi da na hada- hada,

Bayan an hararo abubuwan da malaman Fiḳihu suka bijiro da su a fagen ƙulla cinikayya ta hanyoyin jawabin baki baka- da baka, ko ta rubutu, ko nuni, ko ta hanyar ɗan saƙo, da kuma abubuwan da suka tabbata na cewa lallai ƙulla kasuwanci tsakanin wadanda suke a wuri ɗaya yana buƙatar sharaɗin –in banda a wurin wasiyya da wakilci- samun haɗuwa tayi da yarda, da rashin fitowar wani abu da zai nuna fasawa daga ɗaya daga cikin masu cinikayyar, a kuma sami bibiya tsakanin tayi da amsawa daidai da yanda al'ada ta tabbatar, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Idan aka ƙulla cinikayya, ko yarjejeniya tsakanin mutanen da ba su kusa da juna, ba su a wuri

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 2/785).

ɗaya, dukansu ba su san junansu ba, ba kuma su ji maganar juna ba, ya kuma zamana hanyar da suka tuntuɓi juna ita ce rubutu, ko wasiƙa, ko ɗan saƙo, a nan wasiƙar gidan waya ta kar- ta- kwana, da telefaks da faks da allon fuskar kwamfuta duk sun shiga, to a irin wannan hali kasuwanci, ko yarjejeniyar sun ƙullu idan tayin ya isa zuwa ga wanda aka yi masa, ya kuma amshi tayin da aka yi masa.

- **Na biyu:** Idan aka ƙulla cinikayya, ko yarjejeniya tsakanin ɓangarori biyu a lokaci ɗaya, alhalin suna wurare biyu da suka yi nesa da juna, inda anan wayar talfon, da mobile sun shiga, to wannan ƙulla cinikayya, ko yarjejeniya daidai yake da cinikayya, ko yarjejeniyar da aka gudanar tsakanin ɓangarori biyun suke a wuri ɗaya, a irin wannan hali za a zartar da hukunce- hukuncen asali ne waɗanda malaman Fiƙihu suka tabbatar, wanda aka yi nuni zuwa gare su a cikin muƙaddima.
- **Na uku:** Idan mai talla ya gabatar da hajarsa ta waɗannan hanyoyi, idan ya sanya iyaka na lokaci, to dole ne ya zama akan tallarsa da ya yi na tsawon lokacin da ya sanya, ba shi da haƙƙin sauya ra'ayinsa akan haka.
- **Na huɗu:** Lallai ƙa'idodjin da suka gabata ba su haɗe da ƙulla aure ba, saboda akwai sharaɗin sanya shaidu a cikinsa, haka ma ba su haɗa da miƙa kuɗi ba, saboda sharaɗi amsa hannu da hannu, haka ma ba su haɗa da Salam ba, saboda sharaɗin gaggauta bayar da uwar kuɗi, ko jari.
- **Na biyar:** Duk wani abu da yake da jiɓi da yiwuwar samun maguɗi, ku sauya gaskiya, ko kuskure, za a koma ne zuwa ga ƙa'idojin tabbatarwa da aka sani.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 53 (4/6)([1])
GAME DA AMSA HANNU DA HANNU: SURORINSA –MUSAMMAN SABABBI- DA HUKUNCE-HUKUNCENSA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in: Amsa hannu da hannu: surorinsa – musamman sababbi- da hukunce- hukuncensa, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akai, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Kaman yanda amsar kuɗi yake kasancewa ƙiri- ƙiri ta hanyoyin hannu da hannu, ko ta hanya awo na mudu, ko na auna nauyi a cikin abinci, ko ta hanyar sifiri da sauya wuri ta yanda zai zamo ƙarƙashin ikon mai amsa, haka ma yana tabbata ta hanyoyin hukunci, ko da bari bayan an bai wa wanda aka bari masa daman sanya hannu da yin abin da ya so da shi, ko da kuma ba a sami amsa na ƙiri- ƙiri ba. Ana samun bambancin yanda ake amsar abubuwa daidai da yanayin abin da za a amsa, da kuma bambancin al'adu a cikin abubuwan da ake amsar.

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 1/453).

- **Na biyu:** Lallai a cikin surori amsa a hukunce wanda shari'a, da al'ada suke la'akari da su akwai:
  1- Sanya kuɗi a asusun bankin abokin huldɑ̂ a cikin halaye masu zuwa:
  a- Idan ya sanya kuɗi a asusun abokin huldɑ̂ kai-tsaye, ko ta hanyar tiransifa ta bankuna.
  b- Idan abokin huldɑ̂ na kar- ta- kwana ya ƙulla yarjejeniya tsakaninsa da banki cewa idan ya sayi takardar kuɗi da wata takardar kuɗin su shiga cikin asusun abokin huldɑ̂.
  c- Idan banki ya cire wani adadi na kuɗi daga asusun abokin huldɑ̂ zuwa wani asusun a cikin wannan bankin, ko a waninsa, bayan umurnin da abokin huldɑ̂ ya ba shi, saboda amfanin shi kansa abokin huldɑ̂r, ko saboda amfanin wani, dole ne bankin ya kula da ƙa'idojin fitar da kuɗi a shari'ar Musulunci.

  Ana kawar da kai idan an ɗan jinkirta shigar da bayanai da banki yake yi wanda zai bai wa wanda zai amfana daman amsar kuɗin a aikace, zuwa lokutan da aka saba da su a kasuwannin mu'amala, sai dai bai halatta wanda zai amfana da kuɗin ya yi tasarrufi da su a cikin lokacin wannan jinkirin ba, sai bayan ya sami bayanin cewa zai iya amsar kuɗin a aikace.
  2- Amsar cek([1]) idan yana da kuɗin da za a iya cire, da takardar kuɗin da aka rubuta lokacin biyansa da kiyaye shi a cikin banki.

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Takardar izinin da ke bai wa banki nay a bai wa wanda sunansa yake ciki adadin kiɗin da aka rubuta a cikin takardar daga asusun mai bayar da umurnin da yake a bankin.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 54 (5/6)([1])
GAME DA DASHEN ƘWAƘWALWA (BRAIN TRANSPLANT) DA JIJIYOYI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasicin da suke da jiɓi da wannan maudhu'i, wanda ɗaya ne daga cikin maudhu'an taron Fiḳihun likitanci na ƙara wa juna sani, karo na shida wanda aka gudanar a ƙasar Kuwait, daga ranar 23 zuwa 26 ga watan Rabi'ul Awwal, 1410 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 26 ga watan Oktoba, 1990, tare da taimakekeniya tsakanin Cibiyar da ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci,

Ƙarƙashin abubuwan da taron da aka yi nuni zuwa gare shi ya cimma na cewa manufar ba wai shi ne cire ƙwaƙwalwar wani mutum a dasa wa wani mutum ɗin na daban ba, manufar wannan dashe ita ce magance tangarɗar da wasu sanannun ƙwayoyin halitta na ƙwaƙwalwa wajen fitar da sinadarinta na kimiyya, ko na ƙwayoyin gina jiki daidai gwargwado, inda ake sanya wasu ƙwayoyin halitta irinsu da aka samo a wani wuri a wurinsu, ko magance

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 3/1739).

tazarar da ake samu a jijiyoyi sakamakon wasu raunuka da aka samu, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Idan daga jikin mara lafiyan ne aka samo ƙwayoyin halitta wanda su ne: (Adrenal gland), ya zama tana da sifar amsar garkuwan jiki, saboda daga jikin ne kansa aka samo ƙwayoyin, to a nan Shari'a ba ta hana ba.
- **Na biyu:** Idan an samo su ne daga ƙwayoyin halittar dabbobi, to shi ma Shari'a ba ta hana bin wannan hanya ba, idan akwai yiwuwar samun nasara, kuma babu wani abu da shari'a ta hana da zai zai gitto a ciki. Lallai likitoci sun bayyana cewa an sami nasara a wannan hanya da aka bi inda aka haɗa tsakanin ƙwayoyin halitta na dabbobi mabambanta, ana kuma fatan ganin cewa za a sami nasara ma idan aka gudanar akan mutum ɗan Adam, amma dole ne a yi taka- tsantsan ɗin da aikin likitanci yake buƙata, gudun kada ya ƙi amsar garkuwar jikin.
- **Na uku:** Idan an samo ƙwayoyin halittar ne daga ƙwaƙwalwar jaririn da aka haifa kafin lokacin haihuwarsa (a mako na goma, ko na goma sha ɗaya), to a nan hukunci ya danganta ne da hanyoyin da aka bi, waɗanda su ne kamar haka:
  a- **Hanya ta farko:** A ciro su kai- tsaye daga jaririn ɗan mutum daga cikin mahaifiyarsa, ta hanyar yin tiyata a mahaifarta, abin da yake faruwa a wannan hanya shi ne jaririn yana mutuwa da zaran an cire ƙwayoyin daga ƙwaƙwalwarsa, wannan kam Shari'a ta haramta yinsa, sai dai idan ya faru ne bayan ɓarin da ba da gangan aka yi ba, ko kuma ɓarin da ya halatta a yi shi da gangan saboda tseratar da rayuwar uwa, aka kuma tabbatar da cewa jaririn ma ya koma zuwa ga Allah, tare kuma da yin la'akari da sharuɗɗan da za su zo a maudhu'in yiwuwar amfana da jariran da

halittarsu ba su gama kammala ba (ɗan tayi) a ƙuduri mai lamba 59 (8/6) na wannan taron.

b- **Hanya ta biyu:** Wannan hanya ce da za ta iya bayyana nan gaba kaɗan, wanda take ƙunshe da shuka ƙwayoyin halitta a gonar likitanci saboda a amfana da su, lallai Shari'a ba za ta hana bin wannan hanya ba, idan inda aka samo irin ƙwayoyin halittar wuri ne da Shari'a ta amince, an kuma same su ta halattacciyar hanya.

- **Na huɗu:** Jaririn da aka Haifa ba tare da ƙwaƙwalwa ba: matuƙar dai an haife shi a raye, to kuwa sam bai halatta a cire komai daga cikin gaɓoɓin jikinsa ba, sai bayan an tabbatar da cewa ya rasu ta hanyar samun tabbacin cewa mutuwar tushen ƙwaƙwalwa ɗin ƙwaƙwalwarsa, a nan babu bambanci tsakaninsa da masu lafiya a wannan fage, idan ya mutu kuma dole ne a yi aiki da hukunce- hukunce da sharuɗɗan yin amfani da wata gaɓa daga cikin gaɓoɓin mamaci, kaman samun cikakken izini, da kuma rashin samun abin da zai kwafe makwafinsa, a kuma tabbatar da cewa ana tsananin buƙata ta lalura da sauransu, kaman yanda ya zo a ƙuduri mai lamba 26 (1/4) cikin ƙudurorin taron shekara- shekara karo na huɗu da Cibiyar ta gabatar. Shari'a ba ta hana a bar wannan jariri da aka haifa ba tare ƙwƙwalwa ba a cikin na'urorin bayar da kuzari (I.C.U) har zuwa lokacin da ran tushen ƙwaƙwalwa zai yi halinsa –wanda za a iya gane shi- domin kiyaye rayuwar sauran gaɓoɓin da za a iya dasa wa wasu, a matsayin shimfiɗa na sanya su a jikin waɗanda za su amfana da su, da dai sauran sharuɗɗan da muka yi nuni zuwa gare su.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 55 (6/6)([1])
GAME DA ƘWAYAYEN DA AKA ƘYANƘYASA WAƊANDA YAWANSU YA WUCE WANDA AKE BUƘATA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasicin da suke da jiɓi da wannan maudhu'i, wanda ɗaya ne daga cikin maudhu'an taron Fiḳihun likitanci na ƙara wa juna sani, karo na shida wanda aka gudanar a ƙasar Kuwait, daga ranar 23 zuwa 26 ga watan Rabi'ul Awwal, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 26 ga watan Oktoba, 1990, tare da taimakekeniya tsakanin Cibiyar da ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci,

Bayan ta duba wasiyyoyi guda biyu (na goma sha uku, da na goma sha huɗu) da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani na uku da ƙungiyar Musulunci ta ilmomin likitanci ta shirya a ƙasar Kuwait daga ranar 20 zuwa 23 ga watan Sha'aban 1407 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 18 zuwa 21 ga watan Afrilu, 1987 game da makomar ƙwayayen halittar da aka ƙyanƙyasa, da wasici na biyar na taron ƙara wa juna sani, farko da ƙungiyar Musulunci ta

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 3/1791).

ilmomin likitanci ta shirya a ƙasar Kuwait daga ranar 11 zuwa 14 ga watan Sha'aban 1403 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 24 zuwa 27 ga watan Mayu, 1982 akan dai wannan maudhu'i, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Ƙarƙashin abin da ilimi ya tabbatar na yiwuwar adana ƙwayayen halittar da ba a haɗa su aure ba, saboda a iya amfana da su, wajibi ne a lokacin da za a haɗa auren a ɗebi adadin da ake buƙatar a dasa kawai a duk lokacin da za a haɗa su, gudun kada a sami ƙarin ƙwayoyin halittar da aka yi masu aure da ba amfana za a yi da su ba.
- **Na biyu:** Idan an sami ƙarin ƙwayayen halittar da aka ƙyanƙyasa ta kowace hanya ce kuwa, to za a bar su haka nan ne ba tare da ba su wata kulawa ta likitanci ba har su mutu da kansu.
- **Na uku:** Haramun ne a yi amfani da ƙwayayen a jikin wata macen ta daban, dole ne a ɗauki dukan matakan da za su hana yin amfani da ƙwayayen da aka yi masu aure wajen ɗaukan cikin da ba na halal ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 56 (7/6)([1])
GAME DA AMFANI DA 'YAN TAYI A MATSAYIN WURIN SAMO GAƁOƁIN DA ZA A DASA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasicin da suke da jiɓi da wannan maudhu'i, wanda ɗaya ne daga cikin maudhu'an taron Fiḳihun likitanci na ƙara wa juna sani, karo na shida wanda aka gudanar a ƙasar Kuwait daga ranar 23 zuwa 26 ga watan Rabi'ul Awwal, 1410 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 26 ga watan Oktoba, 1990, tare da taimakekeniya tsakanin Cibiyar da ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Bai halatta a ɗauki 'yan tayi su zamo su ne wajen samo gaɓoɓin da da ake buƙata domin dasa wa wani mutum na daban ba, sai a wasu halaye, su ma dole ne a cika wasu sharuɗɗa:
  - **a-** Bai halatta a samar da ɓari da gangan saboda kawai ana son a yi amfani da ɗan tayi wajen dasa gaɓoɓinsa a jikin wani mutum ba, dole ne ɓarin da za a iya amfani da shi ya zamo ɓari ne na Allah da

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 3/1791).

Annabi, ba da gangan aka yi shi ba, ko kuma ya zamo an yi shi ne saboda wani uzuri daga cikin uzurorin da Shari'a ta amince, ba za a koma zuwa ga hanyar yin tiyata domin a ciro jariri a cikin mahaifiyarsa, ba sai idan hakan ya zama kawai shi ne hanyar da za a iya tseratar da rayuwar mahaifiyarsa.

b- Idan akwai yiwuwar ɗan tayin ya cigaba da rayuwa, to dole ne a yi masa magani ta yanda za a kiyaye rayuwarsa, bai wai ƙoƙarin amfana da shi ta hanyar dasa gaɓoɓinsa ba, idan kuma babu yuwuwar ya cigaba da rayuwa, to bai halatta a amfana da gaɓoɓinsa wajen dasa su a jikin wani ba sai bayan ya yi wafati, shi ma da sharuɗɗan da suka zo a ƙuduri mai lamba 26 (1/4) na wannan cibiyar.

- **Na biyu:** Sam bai halatta aikin dashen gaɓoɓi ya zamo harka ne ta kasuwanci ba kwata- kwata.
- **Na uku:** Dole a samar da hukumar ƙwararru da aka amince da su da za su rinƙa kula da aikin dashen gaɓoɓi.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 57 (8/6)([1])
GAME DA DASHEN AL'AURA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasicin da suke da jiɓi da wannan maudhu'i, wanda ɗaya ne daga cikin maudhu'an taron Fiḳihun likitanci na ƙara wa juna sani, karo na shida wanda aka gudanar a ƙasar Kuwait, daga ranar 23 zuwa 26 ga watan Rabi'ul Awwal, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 26 ga watan Oktoba, 1990, tare da taimakekeniya tsakanin Cibiyar da ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko: Dasa jijiyoyin al'aura:** Ganin cewa gwaiwa da ƙwayayen halitta suna cigaba da ɗauka, gami da fitar da sifofin da ake gadar da su (genetic code) a tare da wanda aka yi wa dashen har bayan an dasa su a jikin wanda ya amfana da su, to Shari'a ta haramta a yi dashen su.
- **Na biyu: Dasa gaɓoɓin al'aura:** Idan akwai hali na lalaura da Shari'a ta amince da shi a matsayin lalura, ya halatta a yi dashen wasu daga cikin gaɓoɓin al'aura

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 3/1975).

waɗanda ba sa ɗaukan sifofin gado (genetic code) – amma fa banda al'auran kanta-, sai dai dole ne a kula da sharuɗɗa da ƙa'idojin Shari'a da aka bayyana a ƙuduri mai lamba 26 (1/4) na wannan Cibiya.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 58 (9/6)([1])
GAME DA DASA GAƁAR DA AKA YANKE TA WAJEN ZARTAR DA HADDI KO ƘISASI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar game da maudhu'in dasa gaɓar da aka yanke ta wajen zartar da haddi, ko ƙisasi, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar game da haka,

Bayan la'akari da manufofin Shari'a wajen zartar da haddi, wanda gargadi ne da izina, da kuma wanzar da uƙubar ta hanyar barin tasirinta ya zamo wa'azi da izina gami da kan-da- garki, da kuma kawo ƙarshen aikata laifin, ganin cewa dawo da gaɓar da aka yanke yana buƙatar aikin likitanci na gaggawa daidai da tsarin likitanci na zamani, inda hakan bai zai yiwu ba sai da cikakken shirin likitanci na musamman, wanda yake nuna rashin muhimmanta zartar da haddin, da ma tasirinsa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Shari'a ba ta halatta dawo da gaɓar da aka yanke ta wajen zartar da haddi ba, saboda barin tasirin haddi wani yanki ne na cikar wannan uƙubar

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 3/2161).

da Shari'a ta tabbatar, hakan kuma zai hana rashin muhimmanta hukuncin haddi, da kuma kauce wa cin-karo tsakanin hukunce- hukuncen Shari'a a zahiri.

- **Na biyu:** Ganin cewa an shar'anta yin ƙisasi ne saboda tabbatar da adalci, da kuma yi wa wanda aka yi wa laifi adalci, da kiyaye haƙƙin rayuwa ga ɗaukacin al'umma, da samar da tsaro, gami da kwanciyar hankali, saboda haka sam bai halatta a dawo da gaɓar da akan yanke ta ta hanyar zartar da ƙisasi ba, sai a halaye masu zuwa:
  - **a-** Idan wanda aka yi masa laifin bayan an zartar da ƙisasin ya amince a dawo da gaɓar da aka yanke wa mai laifin.
  - **b-** Idan wanda aka yi masa laifin shi ma ya sami daman dawo masa da nasa gaɓar da aka yanke.
- **Na uku:** Ya halatta a dawo da gaɓar da aka yanke ta wajen haddi, ko ƙisasi; saboda gano kuskure a wurin yanke hukunci, ko wurin zartar da hukuncin.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 59 (10/6)([1])
GAME DA KASUWANNIN HADA- HADAR KUƊI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasiyoyin da sakamakon taron ƙara wa juna sani akan (Kasuwannin hada- hadar kuɗi) da aka yi a garin Rabat daga ranar 20 zuwa 24 ga watan Rabi'u Sani, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 20 zuwa 24 ga watan Oktoba, 1989, tare da hadin gwiwa da wannan Cibiyar, da Cibiyar Musulunci mai bincike da horaswa na bankin Musulunci mai kula da ayyukan raya ƙasa (IsDB), wanda Ma'aikatar Auƙaf da al'amurran Musulunci na ƙasar Maroko ta karɓi bakwancinsa.

Ƙarƙashin abin da Shari'ar Musulunci ta tabbatar na kwadaitarwa game da neman halal, da kasuwanci domin haɓakar dukiya, da kuma haɓakar dukiyoyin da aka ajiye su akan tsarin zuba jari na Musulunci wanda ya ginu akan yin tarayya wajen ɗaukan nauyi, da kuma raba asara, cikinsu har da hatsurran da suke tattare da bashi,

Ganin irin rawar da kasuwannin hada- hadar kuɗi suke takawa wajen shige da ficen kuɗi, da haɓaka kasuwanci, da ganin cewa ba su muhimmanci, da bincike akan hukunce-

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 2/1273), da (Fitowa ta bakwai, 1/73).

hukuncensu abu ne da yake biya wa mutane buƙatunsu na sanin hukunce- hkuncen addininsu akan abubuwan da suke sababbi ne na zamani, kuma hakan ya haɗu da ainihin ƙoƙarin da malaman Fiƙihu suke yi na bayyana hukunce- hukuncen ma'amaloli na kuɗi, musamman hukunce- hukuncen kasuwanni da tsarin Hisba a cikin kasuwanni, haka ma da muhimmanci da kasuwannin suke da shi na bai wa masu zuba jari daman su sake shiga cikin harkar kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe, su kuma sami daman samun shige- da- ficen kuɗaɗe, da bayar da ƙarfin gwiwa wajen sanya kuɗi, wanda yake tattare da daman fita daga cikin kasuwar a duk sanda buƙatar hakan ta taso,

Bayan ta duba abubuwan da binciken da aka gabatar mata suka taɓo game da tsari da dokokin gudanar da kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe da ake da su, da hanyoyin da ake bi, da kuma tsare- tsarenta, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- **Na farko:** Lallai bai wa kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe muhimmanci rukuni ne cikin rukunnan da suka wajaba a gabatar wajen bai wa dukiya kariya, da haɓaka ta, lura da abin da yake biyo bayan haka na taimakekeniyar da ake yi wajen biyan buƙatun al'umma, da kuma fitar da haƙƙoƙi na addini da na duniya da suke ɗamfare da dukiya.
- **Na biyu:** Lallai waɗannan kasuwanni na hada- hadar kuɗaɗe –duk kuwa buƙatar da ake na asalin tunanin da ya kafa ta- kaman yanda suke a yanzu, ba za su iya tabbatar da manufofin haɓaka dukiyoyi da kasuwanci kaman yanda addinin Musulunci yake so ba. Lallai wannan yanayin da ake ciki yana buƙatar gabatar da jan ƙoƙari na haɗin- gwiwa tsakanin malaman Fiƙihu da masana tattalin arziki domin bita akan ginshiƙai da tsarin ya ginu akansu, da abubuwan da ya dogara da sun a dokoki da tsare- tsare, da sauya abubuwan da suka kamata a sauya ƙarƙashin karantarwar Shari'ar Musulunci.

- **Na uku:** Lallai kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe sun ginu ne akan tsare- tsaren ofis da wasu matakai, saboda haka ne wajibcin yi masu biyayya ya ginu akan zartar da ƙa'idar "al- Masalihul Mursala" akan abubuwan da za su iya shiga cikin wani asali na Shari'a waɗanda ba su saɓa da wani Nassi, ko wata ƙa'ida na Shari'a ba, saboda haka wannan tsarin yana babin tsare- tsaren da shugaba ne zai tsattsara su a fagen sana'o'in hannu, da sauran abubuwan da al'umma take buƙata, bai halatta wani ya saɓa wa tsarin da shugaba ya yi ba, bai kuma halatta a yi wasu 'yan dabarbaru domin kauce wa tsarin ba, matuƙar dai sun cika sharuɗɗa da asalin da Shari'a ta gindaya.

An yi wasici da abu mai zuwa:

- Cigaba da bincike da nazari game da kayayyaki, da sigogin da ake amfani da su a kasuwannin hada-hadar kuɗaɗe, a rubuta bincike da nazari mai zurfi a fagagen Fiƙihu da tattalin arziki da za su gamsar([1]).

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 63 (1/7).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 60 (11/6)([1])
GAME DA SHAHADU (BONDS)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba bincike da wasiyoyin da sakamakon taron ƙara wa juna sani akan (Kasuwannin hada- hadar kuɗi) da aka yi a garin Rabat daga ranar 20 zuwa 24 ga watan Rabi'u Sani, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 20 zuwa 24 ga watan Oktoba, 1989, tare da hadin gwiwa da wannan Cibiyar, da Cibiyar Musulunci mai bincike da horaswa na bankin Musulunci mai kula da ayyukan raya ƙasa (IsDB), wanda Ma'aikatar Auƙaf da al'amurran Musulunci na ƙasar Maroko ta karɓi bakwancinsa.

Bayan an duba cewa Shahada (Bond) wata takarda ce da wanda ya fitar da ita yake ɗaukan alhakin biyan ƙimar da take ɗauke da shi ga wanda yake ɗauke da takarda, tare kuma da biyan fa'idar da suka yi yarjejeniya akanta ƙari akan ƙimar da take rubuce a cikin takardar, ko ya sanya wani amfani da sharaɗi, shin kyaututtuka ne da ake rarraba su ta hanyar yin ƙuri'a, ko ta hanyar yanke wani adadi na kuɗi daga ciki, ko zamiye, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

([1]) Mujallar Cibiya (Fitowa ta shida, 2/1273), da (Fitowa ta bakwai, 1/73).

- **Na farko:** Lallai shahadun nan tamkar wani alƙawari ne na biyan wani adadi na kuɗi tare da fa'idar da aka danganta masa ƙari akan abin da yake cikin takardar, ko ya sanya wani amfani da sharaɗi, Shari'ar Musulunci ta haramta fitar da waɗannan shahadun, ko sayar da su, ko yin musanyen kasuwanci da su; saboda bashi ne da ruwa, shin waɗanda suka fitar da ita keɓaɓɓiyar hukuma ce, ko ta gaba ɗaya da take da jiɓi da gwamnati. Duk sunayen da za a sanya masu ba zai yi tasiri ba, sawa'un an kira su shahadu, ko Sukuk, ko kuɗin ajiya, ko an kira fa'idar kuɗin ruwa da za a biya da sunan riba, ko galla, ko abin da ya biyo baya.
- **Na biyu:** Haka ma Shari'a ta haramta shahadun da suke ɗauke da fatsi- fatsin tiket a matsayinsu na bashin da ake sayarwa da kuɗin da bai kai kuɗin da yake a rubuce ba, inda waɗanda suke ɗauke da su suke amfana da bambancin da yake a tsakani inda za su zame daga cikin waɗannan shahadun
- **Na uku:** Haka ma Shari'a ta haramta shahadun da suke ɗauke da kyaututtuka a matsayinsu na bashin da aka shardanta amfanuwa da shi, ko ƙari ga jumlar masu bayar da bashin, ko ga wasu daga cikinsu ba tare da an ambace su ba, bugu da ƙari hakan yana kama da caca.
- **Na huɗu:** Cikin abubuwan da suke kwafe makwafin shahadun da aka haramta –fitarwa, ko sayarwa, ko yi mu'amala da su- akwai shahadu, ko Sukuk da aka samar da su akan ƙa'idar mudaraba a wani shirin kasuwanci da ake zuba jari a cikinsa, ta yanda mai kuɗin ba shi da wani tabbatacciyar fa'ida, ko amfani da zai samu, kawai zai zamo yana da kaso ne daga cikin ribar da shirin ya samar gwargwadon abin da yake mallaka na shahadu ko Sukuk, kuma ba zai sami rib aba sai idan tabbar shirin ya sami riba. Zai yiwu a iya amfana da wannan daga sigar da aka amince da

ita a ƙuduri mai lamba 30 (5/4) na wannan Cibiyar game da shahadun bashi([1]).

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 30 (5/4).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 61 (12/6)
GAME DA MAUDHU'AI DA TARURRUKAN ƘARA WA JUNA SANI DA SASHEN TSARE- TSARE YA BAYAR DA SHAWARA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Bayan ta duba rahoton da sashen tsare- tsare ta gabatar wa sakateriyar Cibiyar, wanda aka rarraba wa mambobin majalisar Cibiya, rahoton da yake ƙushe da maudhu'an da aka bayar da shawarar cewa majalisar ta gudanar da bincike da nazari akansu, da aka yi masu jadawali gwargwadon muhimmancinsu, waɗanda suka ƙunshi maudhu'ai mabambanta da aka shigar da su cikin alamu masu zuwa:

- Haƙƙoƙin ƙasa da ƙasa a Fiƙihun Musulunci na zamani
- Aurace- aurace da gado a Fiƙihun Musulunci na zamani
- Tunanin Musulunci na zamani
- Ibadu a Fiƙihun Musulunci na zamani
- Ma'amaloli da tsumi- da- tanadi a Fiƙihun Musulunci na zamani
- Ilimin sanin makamar Fiƙihun Musulunci (Usulul-Fiƙh) a mahangar zamani

- Likitanci da ilmomi
- Sababbin abubuwa da suka faru waɗanda ba a ambata ba

Kaman yanda rahoton ya ƙunshi shawarar shirya tarurruka akan maudhu'ai masu zuwa:

- Haƙƙoƙin mace a Musulunci da wajiban da suke kanta
- Haƙƙoƙin ƙasa da ƙasa a Musulunci
- Haƙƙoƙin bil'adama tare da haɗawa da ƙoƙarin da Ƙungiyar ƙasashen Musulmai (OIC) take yi
- Haƙƙoƙin ƙananan yara a Musulunci tare da gabatar da tsokaci akan yarjejeniyar ƙasa da ƙasa game da haƙƙoƙin ƙananan yara
- Waɗanda ba Musulmai ba a ƙarƙashin mulkin Musulunci: haƙƙoƙinsu da abubuwan da suka wajaba akansu
- Musulmai tsakanin riƙo da Musulunci da kwaikwayon wasu a wannan zamani
- Nazari akan misalan kundin tsarin mulki na Musulunci
- Matsayar Musulunci game da sababbin fannoni (Zane, da waƙa, da kaɗe- kaɗe, da wasan kwaikwayo)
- Tsarin shugabanci a Musulunci: asalinsa da ƙa'idojinsa da manyan mas'alolinsa a wannan zamani
- Aikin jarida da hanyoyinsa a wannan zamani ta mahangar Musulunci
- Hukunce- hukuncen takardar kudî da darajarta yake hawa da sauka a Fikihun Musulunci
- Taimakon marasa shi a Musulunci ƙarƙashin tsare-tsarensa a aikace a wannan zamani
- Shahadun asusun gwamnati da shahadun zuba jari
- Zaɓi da sauye- sauye da ake amfani da su a kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** A kula da waɗannan shawarwari da aka bayar, tare da bai wa sakateriya daman zaɓa daga ciki,

daidai da ikon da take da shi wanda ya yi daidai da maslaha, musamman waɗanda aka bayar da shawarar gudanar da nazarin akansu a taron shekara- shekara da ya gabata.

- **Na biyu:** Sakateriya ta shirya tarurrukan ƙara wa juna sani, tare da bai wa maudhu'an da aka gabatar a tarurruka muhimmanci gwargwadon daman da ake da ita.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 62 (13/6)
GAME DA WASIYYOYIN BAYAN TARON SHEKARA-SHEKARA NA SHIDA DA MAJALISAR CIBIYAR FIḲIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA TA GABATAR

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na shida a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 17 zuwa 23 ga watan Sha'aban, 1410 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 20 ga watan Maris, 1990,

Ta yi wasici da abubuwa masu zuwa:

- **Na farko:** Kiran Musulmai a duk inda suke zuwa ga taimakon juna, da hadin- kai, da kuma riḳo da mafitar da Musulunci yake bayarwa wajen fita daga matsalolinsu, da kuma su tashi tsaye wajen sauke abin da ya wajaba akansu na gabatar da Musulunci zuwa ga duniya a matsayin shi ne mafita daga dukan matsaloli, maimakon komawa zuwa ga ƙa'idojin 'yan maddiyya da tuni suka karkace ga barin hanya madaidaiciya, kuma rashin alfanunsu ya riga ya bayyana, haka ma tana kira ga ɗaukacin Musulmai kan su bayar da muhimmanci na musamman ga mas'alolin da suka shafi 'yan uwansu a ƙasashen gabashin duniya, da nuna masu goyon baya game da halattattun haƙoƙƙinsu na su cigaba da kasancewa akan addininsu, da kuma haƙƙoƙinsu na mutane.
- **Na biyu:** Cibiyar tana Allah wadai da hijirar da Yahudawan Tarayyar Sufiyet suke yi zuwa ƙasa mai

albarka, ƙasar Isra'i da Mi'iraji, tana kuma kallon hakan a matsayin babban hatsarin da yake yi wa gaba ɗayan al'ummar Musulmai barazana, tana kira zuwa ga ƙasashen Larabawa da na Musulunci da su haɗa-kai, su ƙalubalanci wannan hatsarin da ya tunkaro, su kuma ɗauki dukan matakan da suka dace wajen 'yanto garuruwan da aka mamaye, da 'yantar da wuraren ibada masu tsarki, a tseratar da inda Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi Isra'insa zuwa gare shi daga hannun azzalumai da suka ƙwace shi, a kuma goya wa gwagwarmayar da suke tunkarar azzaliman Yahudawa baya, ta yanda za ta cimma manufarta, ta kuma kiyaye cigabanta.

- **Na uku:** Bai wa dukan kafafen yaɗa labarai muhimmanci a ƙasashen Musulmai, da yin aiki wajen sanya su a hanya ta yanda za su amfani al'umma, su kuma hidimta wa Musulunci, da ƙalubalantar matsalolin zamani masu hatsari, kuma akwai buƙatar sakateriyar Cibiya ta shirya taro na musamman game da kafafen yaɗa labarai.
- **Na huɗu:** Shirya taron ƙara wa juna sani game da fannonin da suka fi yaɗuwa a wannan zamani, irin su: wasan kwaikwayo, da waƙe- waƙe, da kaɗe- kaɗe, da raye- raye da sauransu, waɗanda babu wata kafar yaɗa labarai da ba su.
- **Na biyar:** Gabatar da cikakkun bincike da nazari akan maudhu'in yawaitar kaffarar kisa, saboda a tsayar da magana ɗaya, a gabatar da ƙuduri game da shi.
- **Na shida:** Jinkirta maudhu'in hannun jari saboda a ƙara bincike da nazari akansa.
- **Na bakwai:** Shirya taro akan maudhu'in Zaɓi da sauye- sauye da ake amfani da su.
- **Na takwas:** Kafa kwamiti, ƙarƙashin kulawar sakateriyar Cibiya, da suka haka malaman Fiƙihu da

masana tsumi da tanadi, domin amsa tambayoyin bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa (IsDB), game da shiga cikin kamfanonin bayar da gudummuwa (joint- stock company).

Allah ya sa mu dace.

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA BAKWAI NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

JIDDA (SAUDIYYA)

7 - 12 GA WATAN ZUL- ƘIDA, 1412 H

9 – 14 GA WATAN MAYU, 1992

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 63 (1/7)([1])
GAME DA KASUWANNIN HADA- HADAR KUƊAƊE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa Cibiyar akan maudhu'in: (Kasuwannin hada- hadar kuɗaɗi) hannayen zuba jari, da gwaje- gwaje, da haja, da katin lamuni,

Bayan ta saurari tattaunawar da akan gabatar game da su, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Hannayen jari

1- Hannayen jari a kamfuna:

a. Ganin cewa asali a cikin harkokin mu'amala shi ne halacci, za mu iya cewa lallai kafa kamfunan haɗin gwiwa da suke da manufofi da kuma ayyuka abu ne da ya halatta a Shari'a.

b. Babu wani saɓanin tsakanin malamai akan haramcin sanya hannu a cikin kamfunan da manyan manufofin haramun ne a Shari'a, kaman mu'amala da riba, ko samar da kayayyakin da shari'a ta haramta, ko yin kasuwanci da su.

c. A asali harumun ne sanya hannu a cikin kamfunan da a wasu lokuta suke mu'amala da

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta shida, 2/1273) da (Fitowa ta bakwai, 1/73) da (Fitowa ta tara, 2/5).

abubuwan da Shari'a ta haramta, irinsu riba da makamantanta, duk kuwa da cewa shari'a ta halatta manyan ayyukan suke yi([1]).

2- Lamunin fitarwa **(Under writing):**

Lamunin fitarwa (Under writing): Yarjejeniya ce a lokacin kafa kamfani tare da wanda zai ɗauki alhakin lamunin bayar da dukan hannayen jari, ko wani sashe na bayar da hannayen jarin, wato wani alƙawari da wanda zai ɗauki wannan alhakin yake ɗauka na ɗaukan dukan sauran hannayen da babu wanda ya ɗauka, wannan abu ne da shari'a ba ta hana ba, idan wannan alƙawarin ya ɗauke shi ne da ƙimar da aka ambata, ba tare da an biya wani lada akan alƙawarin ba, ya kuma halatta wanda ya ɗauki alƙawarin ya karɓi lada akan wani aiki da ya gabatar – banda wannan lamunin-, alal misali idan ya gudanar da wani bincike, ko ya tallata hannayen jarin.

3- Rarraba biyan ƙimar hannayen jari a lokacin ɗaukan alhakin:

A shari'a babu laifi a rarraba biyan ƙimar hannayen jarin da aka ɗauki alhakin, da jinkirta biyan sauran kashe – kashen, saboda hakan daidai yake da gabatar da kaso a cikin abin da aka gaggauta biyan, da kuma yin alƙawarin ƙari a jari uwar kuɗi, shari'a ba ta hana haka ba, domin wannan ɗin ya haɗa da dukan hannayen jarin, kuma a haka alhakin da yake kan kamfanin zai cigaba da kasancewa a dukan jari ko uwar kuɗin da ta sanar da ta bayyana a wurin sauran mutane, saboda wannan ne abin da mutanen da suke mu'amala da kamfanin suka sani, suka kuma yarda da shi.

4- Hannun jarin wanda yake ɗauke da shi (Bearer Shares):

Ganin cewa kasuwanci a cikin (hannun jarin wanda yake ɗauke da shi) shi ne: kaso n agama- gari a cikin abubuwan da suke mallaki ne na kamfani, kuma shahadar hannun

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 77 (8/8), da ƙuduri mai lamba 87 (4/9)

jarin shi ne takardar da take tabbatar da cancantar samun wannan kason, to lallai shari'a ba ta hana fitar da irin wannan hannun jarin daga kamfani ta irin wannan hanyar ba, ba kuma ta hana yi ta'amuli da shi ba.

5- Wurin da ake ƙulla yarjejeniya a wajen sayar da hannun jari:

Lallai wurin da ake ƙulla akansa a wajen sayar da hannun jari shi ne kaso na gama gari daga cikin asalin uwar kuɗin kamfani, shahadar hannun jarin shi ne takardar da take bayyana haƙƙin mai shi akan wannan kason.

6- Hannayen jari na musamman:

Bai halatta a fitar da wasu hannayen jari na musamman, da suke da wani fifiko na kuɗi da suke kai wa zuwa ga bai wa uwar kuɗinsu lamuni, ko lamunin akan riba, ko a gabatar da su a lokacin da za a rufe kamfani, ko a lokacin da za a raba riba ba.

Ya halatta a bai wa wasu daga cikin hannayen jari fifiko na musamman da suke da jiɓi da tsarin gudanarwa, ko matakan zartarwa.

7- Ta'amuli da hannayen jari ta hanyar ruwa (riba):

a. Ba ya halatta a sayi wani kaso da rancen riba da dillali ko wani ya bayar ga mai saye don yin jinginar da kaso, saboda hakan ya shafi riba kuma an rubuta shi ta hanyar jinginar gida, kuma suna daga cikin haramtattun ayyukan da mai saye ya yi. rubutun da ya zagi wanda ya ci riba, da wanda ya biya, da wanda ya rubuta, da shaidunsa guda biyu.

b. Haka nan bai halatta a sayar da wani kason da mai sayarwa ba, sai dai ya samu alkawari daga dillalin da zai bashi kason a lokacin da aka kawo shi, domin yana daga sayar da abin da ba shi da shi. kuma haramcin ya qarfafa ne idan ya ce za a karvi farashin ga dillali domin ya amfana da shi ta

hanyar ajiye shi da ribar domin samun lamunin lamuni.

8- Sayar da hannun jari, ko Bayar da jinginansa:

Ana iya siyar da kaso ko jinginar la'akari da tanade-tanaden dokokin kamfanin, kamar idan ka'idar ta hada da hujjar siyarwar kwata-kwata ko bisa la'akari da fifikon tsoffin masu hannun jari a cikin siyan.Haka kuma, tanadin a cikin Ana la'akari da ƙa'idar yiwuwar jinginar gida daga abokan tarayya ta hanyar jinginar da kaso na gama gari.

9- Bayar da hannun jari tare da kudaden bayarwa:

Babu wani ƙin yarda da ƙara wani kaso na ƙimar rabon don biyan kuɗin fitar da kayayyaki, in dai an ƙididdige wannan kaso daidai.

10-Bayar da hannun jari akan kari ko rangwamen bayarwa:

Za a iya fitar da sabbin hannun jari don kara yawan jarin kamfani idan an fitar da su a halin yanzu na tsohon hannun jari bisa kimar da masana suka yi na kadarorin kamfanin, ko kuma da darajar kasuwa.

11-Kamfanin ya bada tabbacin siyan hannun jari:

Majalisar ta yi la'akari da jinkirta yanke shawara kan wannan batu zuwa zama na gaba don ci gaba da bincike da nazari.

12-Kaddara alhaki na kamfani mai iyaka:

Babu wani abin da doka ta hana a kafa kamfanin hada-hadar hannayen jari mai iyaka da jarin sa, domin wannan sananne ne ga masu mu’amala da kamfanin, kuma ta hanyar samun ilimi, babu yaudara a cikin masu mu’amala da kamfanin.

Har ila yau, babu wani ƙin yarda na doka game da alhakin wasu masu hannun jari mara iyaka game da masu karɓar bashi ba tare da la'akari da wannan wajibcin ba. Kamfanoni ne da ke da abokan haɗin gwiwa da abokan haɗin gwiwa masu iyaka.

13-Kayyade cinikin haja ga dillalai masu lasisi, da kuma kayyade kudaden mu'amala a kasuwannin su:

Ya halatta ga hukumomin da ke da iko su tsara yadda ake cinikin wasu hannayen jari ta yadda za a iya yin hakan ne ta hanyar ƙwararrun dillalai waɗanda ke da lasisin yin hakan, domin wannan yana ɗaya daga cikin ayyukan hukuma da ke cimma buƙatu na halal.

Haka nan, ya halatta a kayyade kudade na kasancewar dan kasuwa a kasuwannin hada-hadar kudi, domin wannan yana daya daga cikin al'amuran da suka shafi ka'ida da aka dorawa alhakin tabbatar da maslaha ta halal.

14-Haƙƙin fifiko:

Majalisar tana tunanin jinkirta yanke shawara kan wannan batu zuwa wani zama na gaba don ci gaba da bincike da nazari.

15-Takaddar Haƙƙin mallaka:

Majalisar tana tunanin jinkirta yanke shawara kan wannan batu zuwa wani zama na gaba don ci gaba da bincike da nazari.

Na biyu: Zaɓuka:

a) Kwafin kwangilar zaɓi:

Abin da ake nufi da kwangilar zaɓuɓɓuka shine maye gurbin wajibcin sayarwa ko siyan wani takamaiman abu da aka bayyana akan takamaiman farashi a wani takamaiman lokaci ko a wani takamaiman lokaci, ko dai kai tsaye ko ta hanyar wata hukuma da ke tabbatar da haƙƙin ɓangarorin biyu.

b) Hukuncinsa:

Kwangilar zabuka - kamar yadda yake a yau a kasuwannin hada-hadar kudi na duniya - sabbin kwangiloli ne da ba su fadowa a karkashin duk wata kwangilar da ake kira halaltacciyar kwangila.

Kuma da yake abin da aka yi kwangilar ba kudî ba ne ko riba ko haƙƙin kudî da za a iya musanya shi da shi, kwangila ce da ba ta halatta ba.

Tun da tun farko waɗannan kwangilolin ba su halatta ba, ba a halatta a yi ciniki da su ba.

Na uku: Ma'amala da kayayyaki, kudade da fihirisa a kasuwannin da aka kayyade:

(1) Kaya:

Ana magance kayayyaki a cikin kasuwannin da aka tsara ta ɗayan hanyoyi huɗu masu zuwa:

Hanya ta farko:

Cewa kwangilar ta haɗa da haƙƙin karɓar abin da aka sayar da kuma karɓar farashin nan da nan, tare da kasancewar kaya ko rasit ɗin da ke wakiltar su a hannun mai sayarwa da rasidin.

Wannan kwangilar ta halatta bisa doka ƙarƙashin sanannun sharuɗɗan siyarwa.

Hanya ta biyu:

Cewa kwangilar ta ƙunshi haƙƙin karɓar abin da aka sayar da kuma karɓar farashin nan da nan, tare da ikon tabbatar da su daga Hukumar Kasuwa.

Wannan kwangilar ta halatta bisa doka ƙarƙashin sanannun sharuɗɗan siyarwa.

Hanya ta uku:

Cewa kwangilar ta kasance kan isar da wani samfurin da aka siffanta a hannun a ranar da aka jinkirta da kuma biyan farashin lokacin bayarwa da kuma cewa ya haɗa da yanayin da ke buƙatar cewa a zahiri ya ƙare tare da bayarwa da karɓa.

Wannan kwangilar ba ta halatta a dage musanya biyun ba, kuma za a iya gyara ta don saduwa da sharuɗɗan aminci da aka sani, kuma idan ta cika sharuddan aminci ya halatta.

Haka nan, baya halatta a sayar da kayan da aka siya da aminci kafin a mallake shi.

Hanya ta huɗu:

Cewa kwangilar ta kasance a kan isar da kayan da aka siffanta a hannun a ranar da aka jinkirta da kuma biyan farashin lokacin bayarwa ba tare da kwangilar ba tare da

sharaɗin da ke buƙatar ta ƙare tare da ainihin bayarwa da karɓa, amma ana iya rushewa. ta hanyar kwangilar kishiyar.

Wannan shi ne nau'in da ya fi yawa a kasuwannin kayayyaki, kuma wannan kwangilar ba ta halatta ba tun farko.

(2) Ma'amala da kuɗaɗe:

Ana magance kuɗaɗe a kasuwannin da aka tsara ta ɗaya daga cikin hanyoyi huɗu da aka ambata wajen mu'amala da kayayyaki.

Ba za a iya siye da sayar da kudi ta hanyoyi na uku da na huɗu ba.

Amma hanyoyin farko da na biyu, ya halatta a siye da siyar da kuɗaɗe, in dai an cika sharuɗɗan musayar da aka sani.

(3) Ma'amala da mai nuni:

Ma’auni mai nuni shi ne lambar ƙididdiga da ake ƙididdige ta ta amfani da hanyar ƙididdiga ta musamman da aka yi nufin sanin girman canjin a wata kasuwa, kuma ana yin ciniki akansa a wasu kasuwannin kudi.

Ba ya halatta a saya da sayar da fihirisa domin caca ce tsantsa, kuma tana sayar da wani abu na hasashe ne wanda ba zai wanzu ba.

(4) Halaltacciyar madadin haramtacciyar mu'amala a cikin kayayyaki da kuɗaɗe:

Kasuwar Musulunci ta kayayyaki da kudade ya kamata a tsara ta a kan hada-hadar Sharia, musamman tallace-tallacen sallama, musayar kudi, alƙawarin sayarwa a lokacin da aka jinkirta, Istisna’a, da sauransu.

Majalisar tana ganin ya zama wajibi ta gudanar da cikakken nazari kan yanayin wadannan hanyoyin da hanyoyin aiwatar da su a cikin tsarin kasuwar Musulunci.

Na huɗu: Katin Kiredit:

a) Ma'anarsa:

Katin kiredit wata takarda ce da mai bayar da ita ke bayarwa ga mutum na halitta ko na shari'a - bisa wata

yarjejeniya da ke tsakaninsu - wanda ke ba shi damar siyan kaya ko ayyuka daga duk wanda ya amince da takardar ba tare da ya biya kudinsa nan take ba, kamar yadda ya wajaba mai bayarwa. biya. Daya daga cikin nau'ikan wannan takarda shine abin da ke ba da damar cire kudi daga bankuna. Don katunan kuɗi:

- Wasu daga cikinsu su ne cirewa ko biyan kuɗi bisa ga shi daga asusun mai ɗaukar kaya a banki ba daga asusun mai bayarwa ba, don haka ana rufe su. Wasu daga cikinsu akwai biyan kuɗi daga asusun mai fitar da kaya sannan a mayar da su ga mai ɗaukar kaya a kan lokaci-lokaci.
- Wasu daga cikinsu suna sanya ribar riba akan jimlar ma'aunin da ba a biya ba a cikin ƙayyadadden lokaci daga ranar da'awar. Ciki har da wadanda basu sanya amfani ba.
- Yawancinsu suna sanya kuɗin shekara ga mai ɗaukar kaya, wasu kuma waɗanda ba a sanya su a hukumance ba.

b) Karɓar katunan kuɗi na Sharia:

Bayan tattaunawa, majalisar ta yanke shawarar dage yanke shawarar kan daidaitawa ta doka na katunan bashi da hukuncinta zuwa zama na gaba don ci gaba da bincike da nazari([1]).

Allah shi ne mafi sani;;

([1]) Duba quduri mai lamba 96 (4/10)

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 64 (2/7)([1])
GAME DA SAYAR DA KAYA ZUWA WANI LOKACI TARE DA RARRABA LOKACIN BIYA (INSTALLMENT SALES)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar akan maudhu'in: sayar da kaya zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya (Installment sales), saboda a kammala ƙuduri mai lamba 51 (2/6) game da shi,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar game shi, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** Sayar da kaya zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya (Installment sales) ya halatta a Shari'ar Musulunci, koda kuwa kuɗin da za a biya bayan lokacin ya fi na wanda za a biya nan take.
- **Na biyu:** Takardun kasuwanci (cek, da shahadun bayar da umurnin biya, da shahadun cire kuɗi) dukansu nau'o'i ne na tabbatar da halaccin bashi ta hanyar rubutu.
- **Na uku:** Lallai yin zamiye a takardun kasuwan kasuwanci abu ne da bai halatta ba a shari'ar

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta shida, 1/193) da (Fitowa ta bakwai, 2/9).

Musulunci; saboda yana kai wa zuwa ga ribar nasi'a da shari'a ta haramta.

- **Na huɗu:** Biyan sauran kuɗin kayan da aka siyar zuwa wani lokaci tare da rarraba lokacin biya (Installment sales), kafin lokacin da aka yanke ya yi, bayan an rage yawan bashin saboda an gaggauta biya ya halatta a Shari'ar Musulunci, babu bambanci tsakanin wanda ya nemi a yi hakan, shin wanda ake bi bashin ne, ko wanda yake bin bashin, saboda hakan ba zai shiga cikin riba wanda aka haramta ba tun da ba a yi ittifaƙi akan haka tun farko ba, matuƙar dai dangantaka tsakanin wanda ake bi bashin da mai bin bashin dangantaka ce ta su biyu. Amma idan an sami wani na uku ya shiga tsakani, to a nan bai halatta ba, domin a irin wannan hali hukuncin takardun kuɗi na kasuwanci ne zai shigo.
- **Na biyar:** ya halatta waɗanda ake bi bashi da waɗanda suke bin bashi su yi ittafaƙi akan biyan sauran kason idan wanda ake bi bashin ya ƙi biyan kowane kaso daga cikin kason da suke a kansa, matuƙar dai ba yana shiga cikin halin rashi ba ne.
- **Na shida:** Idan an kai ga kusanto da lokacin biyan bashi sakamakon mutuwar wanda ake bi bashi, ko kuwa tsiyacewarsa, ko kuma taurin bashin da ya nuna, to a nan ya halatta a rage yawan abin da yake kansa, ta hanyar yarjejeniya da junansu.
- **Na bakwai:** Ƙa'idar tsiyacewar da ya wajaba a jinkirta neman biyan bashi ita ce: ya zamana wanda ake bi bashin ba shi da wata dukiya da ta wuce buƙatunsa na asali da za ta iya biyan bashin da ake binsa, sawa'un farin kuɗi ne, ko kadara.

Allah ne masani.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 65 (3/7)([1])
GAME DA BAYAR DA JINGAR SANA'ANTAWA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar akan maudhu'in: bayar da jingar sana'antawa,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar a kai, da kuma la'akari da manufofin Shari'ar Musulunci wajen maslahohin bayi, da kuma ƙa'idodjin ilimin Fiḳihu wajen kasuwanci da dangantaka tsakanin 'yan kasuwa, lura da cewa lallai yarjejeniyar jingar sana'antawa yana da babban muhimmanci wajen haɓaka masana'antu, da ma kayan da ake sana'antawa, da kuma buɗe ƙofofi masu yawa na bayar da jari, da kuma haɓaka tattalin arzikin Musulunci, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Na farko:** Lallai yarjejeniyar bayar da jingar sana'antawa –wanda ake yinsa akan aiki, da wani ayyanannen abu da yake hawa zimma- tana zama

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta bakwai, 2/223).

wajiba akan ɓangarori biyu (wanda ya bayar da jingar da wanda aka bai wa) idan an cika rukunnai da sharuɗɗa.

- **Na biyu:** A cikin yarjejeniyar bayar da jingar sana'antawa an sanya sharuɗɗa masu zuwa:
  - **a.** Bayyana jinsin abin da za a sana'anta da nau'insa da sifofin da ake buƙata.
  - **b.** Iyakance lokacin da za a sana'anta.
- **Na uku:** A yarjejeniyar bayar da jingar sana'antawa ya halatta a jinkirta bayar da gaba ɗayan kuɗi, ko bayar da shi a rarrabe kaso kaso a sanannun lokuta.
- **Na huɗu:** Ya halatta mai bayar da jingar da wanda aka bai wa jingar su samar da wani sharaɗi na hukunci ga wanda bai cika abin da aka yi yarjejeniya akansa ba, matuƙar dai ba wani abu ne da ya wuce ƙarfinsu ya shigo ba.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

KUDURI MAI LAMBA: 66 (4/7)([1])

GAME DA KASUWANCIN WAFA'I (cika alkawari)([2])

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar akan maudhu'in: Kasuwanci wafa'i,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar game da kasuwanci wafa'i, wanda ma'anarsa ita ce: (Sayar da kuɗi da sharaɗin cewa a duk sanda mai sayarwa ya mayar da kuɗin da aka sayam shi kuma wanda ya saya zai mayar masa da abin da ya saya), an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- Na farko: lallai haƙiƙanin wannan kasuwanci shi ne bashin da ya jawo wa mai bayar da shi amfani, shi ɗin bai wuce 'yan dabarbaru na riba ba, kuma jamhur ɗin malamai sun tafi akan rashin ingancinsa.
- Na biyu: Lallai wannan yarjejeniya ba ta halatta ba a shari'ar Musulunci

Allah shi ne masani;;

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta bakwai, 3/9).

([2]) Ma'anarsa it ace: Mutum ya sayar da wani abu akan farashi kaza, da sharaɗin cewa a duk sanda wanda ya saya ya dawo masa da abin da ya saya shi kuma zai mayar masa da kuɗin da ya saya.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 67 (5/7)([1])
GAME DA MAGANIN ASIBITI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ḳida, 1412 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar akan maudhu'in: maganin Asibiti,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar game da shi, ta tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Yin magani:

A asali halal ne a yi magani, saboda ayoyin Alƙur'ani da Hadisai na magana da na aiki da suka tabbatar da haka, da kuma ganin cewa a cikin yin magani akwai (kiyaye ran ɗan Adam) wanda hakan ɗaya ne daga cikin manyan manufofin Shari'ar Musulunci.

Hukunce- hukuncen yin magani yana da bambanci daidai da yanayi da kuma waɗanda za a yi wa maganin:

- Zai iya zama dole "Wajibi" ne a yi magani ga mutumin da idan bai yi maganin ba zai iya rasa rayuwarsa, ko zai iya rasa wata gaɓa daga cikin gaɓoɓin jikinsa, ko ya kai ta zuwa ga yin rauni, ko idan cutar za ta ita harbar waninsa, kaman irin cututtukan da ake iya ɗauka daga wani.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta bakwai, 3/563).

- Zai iya zama abin da aka so a yi "Mandubi" idan rashin yin maganin zai kai zuwa ga samun raunin jiki ne kawai, ba zai kai zuwa ga abubuwan da aka ambata a yanayin da suka gabata ba.
- Zai iya zama halal "Mubahun" idan bai shiga cikin yanayi da halaye biyun da suka gabata ba.
- Zai iya zama abin ƙi "Makruhi", idan ya zama ana jin tsoron kada yin maganin kada ya haifar da tsananin da yake sama da wadda cutar da ake son a yi mata maganin ya haifar.

Na biyu: yin magani a halin da ake ɗebe ƙauna, ko aka cire rai:

a- Aƙidar Musulmi tana gadar masa da cewa lallai cuta da warkewa duka suna hannun Allah mai girma da buwaya ne, shi yin magani da amfani da shi duka ba su wuce yin amfani da sababi da Allah Maɗaukakin Sarki ya samar da su a cikin halittu ba, kuma sam bai halatta mutum ya ɗebe ƙauna da rahamar Allah da tausayinsa ba, hasali ma dole ya cigaba da fatan samun waraka da ikon Allah.

Dole ne likitoci da da iyalai da makusantan mara lafiya su yi duk abin da za su iya wajen ƙarfafa masa gwiwa, da kuma ba shi kulawar da ta dace, da rage masa raɗaɗi da zafin ciwo da yake ji a ransa ko a jikinsa, ba tare da la'akari da suna fatan ya sami waraka ko kuma akasin haka ba.

b- Ana ɗaukan halin mara lafiya ya shiga cikin yanayin da ba a tunanin samun waraka ne daidai da yanda likitoci suka bayyana, da kuma irin cigaban da aka samu a fannin likitanci a dukan zamuna da lokuta, kuma daidai da yanayin mara lafiya.

Na uku: Neman izinin mara lafiya:

a. Kafin a yi wa mara lafiya magani dole ne a sami izininsa idan yana da cikakken iko da shari'a ta gindaya, idan kuma ba shi da iko, ko kuma ikon nasa ragagge ne to a nan ana buƙatar izinin waliyyinsa, daidai da tsarin walitaka ta shari'a da hukunce-

hukuncenta da suke ƙayyade abubuwan da waliyyi zai iya yin na amfanar wanda yake yi wa walitaka daidai da maslaharsa, ko nesanta shi da kowace irin cutarwa.

Amma fa ba a la'akari da rashin izinin waliyy idan cutar da take damun wanda ake walikatan a bayyane take, a nan sai walitakar ta tashi a hannun wannan waliyyi ta koma zuwa wurin waninsa cikin waliyyai, kai har dai ta kai zuwa ga shugaba.

b. Shugaba yana da daman tirsasa a yi magani a wasu halaye, Kaman wajen yaƙar cututtukan da suke tsallakawa zuwa wasu, ko riga- kafi da bai wa kai kariya.

c. A halin matsanancin rashin lafiyan da ake buƙatar taimakon gaggawa, inda ake ganin cewa rayuwar mara lafiya tana cikin wani hatsari, to ba za a jira sai an sami izini kafin a yi masa magani ba.

d. A wurin gabatar da bincike a fannin likitanci dole ne a sami cikakken izinin mutumin da za a yi gwaji akansa, ya kuma zama yana da cikakken ikon bayar da izini, babu kuma wani abu da zai iya sanya shakkar cewa ko dole aka yi masa –alal misali Kaman fursunoni a gidan yari- ko ya zamana an ruɗe shi da dukiya –kaman yanda za a iya yi wa talakawa da miskinai-. Kuma dole a tabbatar da cewa babu wata cuta da za ta biyo bayan wannan bincike da gwajin.

Sam bai halatta a gabatar da gwaji na likitanci akan wanda ba shi da cikakken iko na shari'a ba, ko kuma wanda ikon nasa bai cika ba, ko da kuwa waliyyansa sun amince da haka.

Majalisar ta yi wasici da cewa:

Ɗaura wa sakateriyar majalisar alhakin nemo malamai da za su yi bincike akan maudhu'ai na likitanci masu zuwa, saboda a gabatar da su a tarurruka masu zuwa.

- Yin magani da abubuwan da aka haramta, ko da najasa, da kuma ƙa'idojin yin amfanin da waɗannan magunguna.

- Maganin ƙara kyau.
- Alhakin da ya rataya akan likita, da abubuwan da yake lamuninsu.
- Namiji ya yi wa mace magani, ko mace ta yi wa namiji magani, da kuma wanda ba Musulmi ba ya yi wa Musulmi maganani.
- Magani ta hanyar ruƙiyya.
- Dabi'un da suka wajaba likita ya sifantu da su – za a rarraba su a tarurruka da dama idan akwai buƙatar haka.
- Cinkoso wajen magani, da kuma tsarin wanda za a fara gabatarwa.
- Bincike akan wasu nau'o'in cututtuka da a mafi yawan lokuta likitoci sukan gaza samar masu da magani, ko kuma suke tantama game da magungunansu, irinsu:
    - Mutumin da ciwon kansa (daji) ya fantsama a cikin jikinsa, shin za a iya yi masa magani, ko kuwa za a cigaba da ba shi maganin samun sauƙi da rage raɗaɗi ne kawai?
    - Yaron da yake fama da mutuwar ƙwaƙwalwa, wanda yake haɗe da shan- inna, kuma ƙwaƙwalwar za ta iya yanƙwanewa –ma'ana har yanzu wasu sassa nata suna aiki- shin za a yi wa irin wannan yaro aiki? Shin idan wannan yaro ya kamu da gwambo a ciki, ko a huhu za a yi masa magani ne ko kuwa za a ƙyale shi?
    - Tsohon da ya kamu da ciwon zuciya na farat ɗaya, sannan kuma yana fama da wani nau'I na cutar shan –inna, sannan kuma ya kamu da rashin aikin ƙoda, shin za a yi masa maganin rashin aikin ƙoda da ta hanyar wankin ƙoda? Idan zuciyarsa ta tsaya cak ba zato ba tsammani za a yi ƙoƙarin yi masa magani ne, ko kuwa za a ƙyale shi? shin idan ya kuma kamu da gyambon

huhu za a yi masa magani ne, ko kuwa za a ƙyake shi?

- Mutumin da ya samu rauni mai tsanani a ƙwaƙwalwarsa, amma duk daga wasu sassa nata suna cigaba da aiki –ƙwaƙwalwar ba ta shiga cikin ma'anar mutuwar ƙwaƙwalwa ba- amma kuma ya rasa gane komai, ba kuma a fatan cewa zai sami sauƙi, shin idan irin wannan mutumi ya kamu da tsayawar aikin zuciyarsa, za a yi masa magani ne, ko kuwa za a ƙyale shi? Haka ma idan ya kamu da gyambon huhu za a yi masa magani? Wane ne yake da alhakin bayar da umurnin a dakatar da yin magani a irin waɗannan halaye, shin kwamitin likitoci ne, ku kuwa kwamitin lura da ɗabi'u, ko kuwa likitoci tare da iyalai?

- Bayyana matsayar Shari'ar Musulunci da Sunnar Annabi game da waɗannan halaye da nau'o'i.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 68 (6/7)([1])
GAME DA HAƘƘOƘIN ƘASA DA ƘASA A MAHANGAR MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na ƙasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in" Haƙƙoƙin ƙasa da ƙasa a mahangar Musulunci,

Bayan yabo da jinjina da ta yi wa ƙoƙarin da aka gabatar akan waɗannan bincike da aka gabatar da su, aka kuma tattauna akansu a taron shekara- shekara karo na bakwai akan wannan maudhu'i, lallai ta ga cewa lallai muhimmanci da faɗin da wannan maudhu'in yake da su, sun sanya ta ƙara neman a faɗaɗa bincike da nazari akan sa ta dukan ɓangarori masu yawa, wanda har yanzu maudhu'in yana buƙatar haka,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akan maudhu'in, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: A kafa kwamitin tsare- tsare domin shirya takardun tsare- tsaren taro na musamman domin magance wannan maudhu'in inda a ƙarshe za a fitar da dokoki na

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta bakwai, 4/9).

haƙƙokin ƙasa da ƙasa a mahangar Musulunci, a kuma gabatar wa majalisar a taron shekara- shekara mai zuwa.

Na biyu: Sassan wannan takardar aiki ya taɓo abubuwa masu zuwa:

1- Asalin da ake ciro dokokin ƙasa da ƙasa na Musulunci, da ma dangantaka tsakanin ƙasa da ƙasa su ne: Alƙur'ani mai girma, da Hadisan Annabi masu daraja, da kuma ayyukan da Khulafa'ur Rashidin suka gabatar a aikace, haka ma ana amfana da ijtihadodin malamai masana Fiƙhu a wannan fage.

2- Manufofi da manyan sifofin Shari'ar Musulunci, waɗanda suka bar tasiri na ƙarara akan dukan yanayin da ake da su wajen sanin:

a. Ilimin manufofin Shari'ar Musulunci.

b. Sifofin Musulunci na musamman.

3- Ma'anar al'umma da hadin kanta a Musulunci.

4- Mazhabobin malaman Fiƙihu wajen karkasa garuruwa da ƙasashe.

5- Asalin tarihin yanayin da ake ciki a wannan zamani a ƙasashen Musulmi.

6- Dangantakar tsarin rayuwar zamantakewa a cikin ƙasashen Musulmai (al'umma da 'yan tsirarun cikinta).

7- Dangantakar ƙasar Musulunci da sauran ƙasashe.

8- Matsayar ƙasar Musulunci game da yarjejeniyoyi da ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa.

Na uku: Kuma kwamitin shirye- shiryen ya samar da littafin da yake ƙarin haske akan dukan waɗannan sassa, saboda masu bincike su amfana da shi a cikin watannin masu zuwa.

Allah ya sanya mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

KUDURI MAI LAMBA: 69 (7/7)([1])
GAME DA BAYANAN BAYAN TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA BAKWAI DA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA GAME DA YAKIN TUNANI

Lallai majalisar cibiyar Fikihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na bakwai a Jidda na kasar Saudiyya, wanda ya gudana daga ranar 7 zuwa 12 ga watan Zul Kida, 1412 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 9 zuwa 14 ga watan Mayu, 1992,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: yakin tunani, wanda ya bayyana farkon lokacin fara wannan yaki, da hatsarinsa, da kuma sassan da yake shafa, da abubuwan da ya cimma a kasashen Larabawa da na Musulmai, ya kuma bijiro da fuskokinsa da ya haifar da shubuhohi da soke- soke, da zatra da shirye- shirye da da ma can manufarsu ita ce kawo ruɗani a cikin al'ummar Musulmai, da dakatar da yaɗuwa da kiran Musulunci, kaman yanda waɗannan bincike sun bayyana rawar da addinin Musulunci ya taka wajen kiyaye al'umma, da kuma cigaba da tabbatarta wajen kalubalantar wannan yaki, da kuma irin yanda ya dakile shirye- shirye da makirce- makircen wannan yaki yake kitsawa, lallai waɗannan bincike sun muhimmanta kawo bayanai game da hanyoyin kalubalantar wannan yaki, da kuma yanda za

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta bakwai, 4/311).

a bai wa alumma kariya daga barin duk wani tasiri da zai iya bari a dukan fagage.

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gabatar akan waɗannan bincike, ta bayar da wasici mai zuwa:

Na farko: Yin aiki tuƙuru wajen yin aiki da shari'ar Musulunci da ɗaukanta a matsayin manhajin da za ta tsara siyasarmu ta cikin gida da ta waje.

Na biyu: Mayar da hankali wajen tace da tsabtace manhajojin tarbiyya da na karantarwa da haɓaka su, da nufin gina al'umma masu tasowa akan nagartaccen harsashe na tarbiyyar Musulunci da zai yi daidai da zamani, ta yanda zai samar da su daidai da yanda ya kamata, ya kai su zuwa ga sanin addininsu, ya kuma kare su daga duk wani salon a yaƙin tunani da ake kawowa.

Na uku: Ƙara haɓaka manhajojin samar da masu da'awa, ta yanda za su fahimci ruhin Musulunci, da manhajojinsa wajen gina rayuwar zamantakewa ta mutuntaka, bugu da ƙari kuma ya ba su dama sanin cigaban zamani, saboda su yi mu'amala da al'ummomin wannan zamani akan ilimi da basira.

Na huɗu: Bai wa Masallaci daman taka rawa wajen bayar da cikakkiyar tarbiyya a rayuwar Musulmai, ta yanda zai iya ƙalubalantar duk wasu sassa da fuskokin wannan yaƙi na tunani da tasirinsa, da kuma sanar da Musulmai haƙiƙanin addininsu.

Na biyar: Yi wa dukan shubuhohin da maƙiya Musulunci suka kawo raddi ta ingantattun hanyoyi, waɗanda suke ɗauke da cikakken yaƙini da imani da cikan wannan addini, ba tare da bin hanyoyin masu rauni wajen bayar da kariya ba.

Na shida: Muhimmanta gabatar da nazari akan tunani da baƙin fahimtar da suke haurowa zuwa ƙasashen Musulmai, da bayyana haƙiƙaninsu, da kuma inda suka gaza, cikin amana ta ilimi.

Na bakwai: Muhimmanta farkawar Musulunci da ake ciki, da ƙarfafa cibiyoyi da suke aiki wajen kira zuwa ga

Allah da gabatar da ayyuka na Musulunci, wajen gina da samar da nagartaccen Musulmi da zai iya zama cikakkiyar sura mai haske da take nuni zuwa ga zartar da karantarwar Musulunci a aikace, a matakin mutum ɗaya, da matakin al'umma a dukan fagagen siyasa da zamantakewa da al'ada da tattalin arziki.

Na takwas: Bai wa harshen Larabci muhimmanci, da yin aiki tuƙuru wajen yaɗa ta, da ƙarfafa masu aikin koyar da ita a ko'ina duniya, ganin cewa ita ce harshen Alƙur'ani mai girma, da sanya ta zama harshen karantarwa a ƙananan makarantu da manya da cibiyoyi da jami'o'i a ƙasashen Larabawa da na Musulmai.

Na tara: Mayar da hankali wajen bayyana sauƙi da rangwamen Musulunci, da bayyana alhairan da ya zo waɗ an Adam da su wajen samun jin daɗin duniya da na lahira. A kuma yi haka ta yanda zai karaɗe duniya da dukan rayayyun harsuna.

Na goma: Yin cikakken nazari kuma mai amfani akan yanda za a amfana da sababbin salon ayyukan jarida da na yaɗa labarai wajen isar da kalmar gaskiya da alhairi zuwa ko'ina a faɗin duniya, ba kuma tare da an wofintar da sauran hanyoyin da ake da su ba.

Na goma sha ɗaya: Muhimmanta gabatar da bincike akan sababbin abubuwan da suke bayyana, da samar masu da mafita na Musulunci, da kuma yin aiki wajen zartar da waɗannan mafita da aka cimma a aikace, saboda zartar da abu a aikace shi ne hanya mafi kyau wajen isar da kira zuwa ga Allah da kuma bayani.

Na goma sha biyu: Yin aiki tuƙuru wajen ƙara tabbatar da haɗin kan Musulmai, da yanda suke cika juna a dukan fagage, da warware rikici da saɓanin da suke tsakaninsu ta hanyoyi na ilimi, kuma daidai da hukunce – hukuncen Shari'ar Musulunci da aka sani, saboda haka ya zama wani aiki ne na daƙile da lalata makirce- makircen da wannan yaƙi na tunani yake ƙullawa wajen rarraba kawunan Musulmai da dasa saɓani da rikice- rikice a tsakaninsu.

Na goma sha uku: Aiki tuƙuru wajen samar da ƙarfin Musulmai, da yanda za su dogara da kansu a fagen tattalin arziki da na soji.

Na goma sha huɗu: Ƙara kira ga ƙasashen Larabawa da na Musulmai wajen taimaka wa Musulman da suke fuskantar zalunci da kama- karya a ko'ina a faɗin duniya, da ƙarfafa su, da kuma tunkuɗe zalunci ga barinsu da duk hanyoyin da ake da su.

Haka ma majalisar tana ƙara bayar da wasici da cewa:

Sakateriyar cibiyar ta cigaba da muhimmanya gabatar da muhimman mas'alolin wannan maudhu'in a tarurrukan cibiyar na ƙara wa juna sani masu zuwa, saboda irin yanda maudhu'in: yaƙin tunani yake da matuƙar muhimmanci, da kuma samar da hanyoyi yaƙi da shi ta dukan fuskoki da fagage, da ma sababbin salon da yake sake bayyana da su, zai yiwu a fara da yunƙurinsa na: Kiristantar da Musulmai, da Istishraƙ a taro mai zuwa.

Allah ya sa mu dace;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA TAKWAS NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

BANDAR SERI BEGAWAN (BRUNEI – DARUS SALAM)

1 - 7 GA WATAN AL MUHARRAM, 1414 H

21 – 27 GA WATAN YUNI, 1993

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 70 (1/8)[1]
GAME DA AIKI DA SAUƘI DA RANGWAME DA HUKUNCINSA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Aiki da sauƙi da rangwame da hukuncinsa,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, ta tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1- Sauƙi ko rangwame na shari'ar Musulunci shi ne: hukunce- hukuncen da aka samar da su a halin uzuri da lalura, saboda a sauƙaƙa wa baligi mukallafi, a lokacin da dalilan da suke wajabta hukuncin asali suka samu.

Babu wani saɓani akan halaccin yin aiki da sauƙi da rangwame na shari'a idan dalilan hakan sun samu, da sharaɗin abubuwan da za su sanya a yi hakan sun faru, da kuma taƙaita yin aiki da sauƙin a wuraren da aka bayyana, tare kuma da lura da ƙa'idojin da shari'a ta shimfiɗa wajen amfana da wannan sauƙi da rangwamen.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 1/41).

2- Abin da ake nufi da sauƙi da rangwamen Fiƙihu shi ne wanda ya zo sakamakon ijtihadi manzabobi saboda ya halatta wani abu da a wani ijtihadin yake haramtawa. Shi riƙo da sauƙi da rangwamen fiƙihu da ma'anar bin magana mafi sauƙi a cikin maganganun malaman Fiƙihu, abu ne da ya halatta daidai da sharuɗɗa da ƙa'idoji masu zuwa a lamba ta (4).

3- Ana yin mu'amala da sauƙi da rangwamen da suke cikin mas'alolin na gama gari ne daidai da yanda ake yin mu'amala da mas'alolin Fiƙihu na asali idan hakan zai tabbatar da maslahar da shari'a take la'akari da ita, ya kuma zamana hakan ya zo ne daga ijtihadi na jama'an da suke cika sharuɗɗa da ƙa'idojin da za su ba su dama iya zaɓen fatawa, ya kuma zama sun sifantu da tsoron Allah da kuma amana ta ilimi.

4- Bai halatta a yi amfani da sauƙi gami da rangwame na Fiƙihu saboda tsananin son zuciya ba, saboda yin haka guje wa wajiban Shari'ar Musulunci ne, kawai ya halatta a yi amfani da sauƙi da rangwame ne idan an yi la'akari da ƙa'idoji masu zuwa:

- **a.** Maganganun malaman Fiƙihun da suke tabbatar da sauƙi da rangwamensu zama shari'a tana la'akari da su, ba a sifanta su da cewa maganganu ne na shazi([1]) ba.
- **b.** Ya zama lallai akwai bukatar da zai sanya a yi aiki da sauƙi da rangwamen, saboda a kawar da wahala, babu bambanci tsakanin bukata ta gaba ɗaya, ko bukata ta ɗaiɗaiku.
- **c.** Wanda zai yi amfani da sauƙi da rangwamen ya zama yana da ikon yin zaɓi, ko ya dogara da wanda yake da ikon yin haka.

([1]) Ma'anar Shazi ita ce: Maganar malami siƙa ta sava da maganar wani malamin da ya fi shi zama siƙa.

d. Kada riƙo da sauƙi da rangwamen ya zama sanadin jefa shi cikin sahun "Talfiƙ" wato masu zaɓen sauƙin da suka ga dama daidai da son zuciya, wanda an riga an hana yinsa, bayanin sa zai zo a lamba na (6).

e. Kada kuma yin amfani da sauƙi da rangwamen ya zama hanya ce na isa zuwa ga wata haramtacciyar manufa.

f. Zuciyar mai amfani da sauƙi da rangwamen ta sami natsuwa da abin da take yi.

5- Ma'anar "Talfiƙ" wajen bin mazhabobi ita ce: mai bin mazhabobin ya bibiyi sassan mas'ala guda ɗaya da take da sassa biyu ko sama da haka, ya ɗauki abin da yake so ya bar saura, ta yanda a ƙarshe mas'alar za ta fito da ma'anar da babu wani malami mai ijtihadi –da yake riya cewa su yake bi- da ya faɗi haka akan mas'alar.

6- An hana yin "Talfiƙ" ne a halaye masu zuwa:

a) Idan tsantsar son zuciya ne ya kai shi da ɗaukan sauƙi da rangwamen, ko hakan ya kai shi ga watsi da ƙa'idojin yin amfani da sauƙi da rangwamen a mas'alar da aka bayyana.

b) Idan hakan ya kai shi ga warware hukuncin shari'a na kotu.

c) Idan hakan ya kai shi ga warware abin da aka koyi da shi a irin wannan mas'alar.

d) Idan hakan ya kai shi ga saɓa wa ijma'in malamai, ko yana lizimta saɓawar.

e) Idan hakan ya kai ga samar da wata haɗakar da babu wani malami mai jitihadi da ya amince da shi.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

KUDURI MAI LAMBA: 71 (2/8)([1])
GAME DA HATSURRAN HANYA

Lallai majalisar cibiyar Fikihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: hatsurran hanya,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gabatar akansu, lura da irin yanda hatsurran hanya suka kagama, hatsari akan rayukan mutane da dukiyoyinsu kuma suka kara yawa, maslaha kuma ta sanya dole a samar da dokoki da za su tsara yanda za a bayar da lasisi ga abubuwan hawa ta yanda za su zama sun cika sharuɗɗan tsaro da aminci, kaman lafiyar abubuwan hawan, da ka'idojin mallaka, da lasisin tuki, da ɗaukan isassan matakai wajen bayar da izinin tuki da wasu sharuɗɗa na musamman da suka shafi shekaru da gani da ma sanin ka'idojin tuki da bin hanya, da kuma kayyade saurin abin hawa, da yawan kayan da za ta ɗauka, an tabbatar da kuduri mai zuwa:

Na farko:

a- Yin aiki da waɗannan tsare- tsare waɗanda ba su saɓa wa hukunce – hukuncen Shari'at Musulunci ba wajibi

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 2/171).

ne, saboda yin haka biyayya ne ga shugabanni cikin abubuwan da sukan tsara na tsare – tsare da matakai daidai da maslahar al'umma "Masalihul Mursala", kuma ya kamata waɗannan tsare – tsaren su zama suna ƙunshe da hukunce- hukuncen Shari'a da ba a yi aiki da su a wannan fagen ba.

b- Kuma maslaha za ta wajabta a samar da dukan nau'o'i na dokokin da za su zama sun tsoratar, irinsu uƙubar biyan tara na kuɗi, ga duk wanda ya karya tsare- tsaren da suke gudanar da yanda za a yi amfani da hanyoyi, saboda hakan ya zama izina ga duk wanda yake nufin jefar tsaron mutane cikin hatsari a hanyoyi da kasuwanni, cikin masu abubuwan hawa nan a dakon kayayyaki daidai da tabbatattun hukunce – hukuncen Hisba

Na biyu: A yi aiki da hukunce- hukuncen manyan laifuffuka da Shari'ar Musulunci ta tanadar a cikin hatsarurrukan da suke faruwa ta hanyar abubuwan hawa, duk kuwa da cewa mafi yawansu suna faruwa ta hanyar kuskure, saboda haka direba shi ne zai ɗauki alhakin duk abin da ya haifar wa wani na cutarwa, shin a jiki ne ko a dukiya matuƙar ƙa'idojin ɗaukan alhakin sun haɗu, waɗanda su ne: kuskure da kuna cutarwa, ba za a yafe wannan alhakin ba sai a halaye masu zuwa:

a. Idan hatsayin ya faru ne sakamakon wani abu da ya fi ƙarfin ɗan Adam, ta yanda ba zai taɓa iya hana faruwarsa ba, wato duk wani abu da ya fi ƙarfin ɗan Adam ya yi komai na hana faruwarsa.

b. Idan wanda ya cutu ɗin ne ya yi sanadiyyar hatsarin, ko shi ne yake da tasiri mafi girma na faruwansa.

c. Idan hatsarin ya faru ne saboda kuskuren wani mutum na uku, ku zaluncin da ya yi, inda shi ne zai ɗauki dukan alhakin abubuwan da suka biyo baya.

Na uku: Dole ne masu dabbobin gida su ɗauki alhaki da lamunin duka hatsarurrukan da dabbobinsu suka haifarwa

a hanyoyi, idan har akwai sakaci da suke yi wajen kiyaye su, da killace su, kotu ne za ta yi hukunci game da hakan.

Na huɗu: Idan direba da wanda ya cutu dukansu sun taka rawa wajen faruwar hatsarin, kowannensu zai ɗauki alhaki ya kuma lamunci abin da ya faru wa junansu na rasa rai ko dukiya.

Na biyar:

a) Tare da la'akari da bayanai na dalla- dalla masu zuwa, tabba sa asali wanda ya aikata aiki na kai-tsaye shi ne alhaki zai hau kansa koda ba da zalunci ya aikata hakan ba., shi kuwa wanda ya zama sanadi ba zai zama ya ɗauki alhaki, ko ya lamunci abin da ya faru ba, sai idan da gangan ya yi, ko kuma akwai sakacinsa.

b) Idan aka haɗu tsakanin wanda ya aikata hatsari da wanda ya zama sanadi, to wanda ya aikata ɗin ne zai ɗauki alhaki ba wanda ya zama sanadiyya ba, sai dai idan wanda ya yi sanadiyyar ya yi hakan ne saboda zalunci, shi kuma wanda ya yi hatsayin ba shi da nufin cutarwa ta zalunci.

c) Idan an sami sababi guda biyu da suka saɓa da juna suka haɗu, kuma kowanne daga cikinsu yana da tasiri wajen cutarwar da ta auku, to dole ne kowane ɗaya daga cikinsu waɗanda suka zama sanadiyya ya ɗauki alhaki gwargwadon irin tasirin da ya yi wajen cutarwa, idan kuma dukansu tasiri daidai da juna suka yi, ko kuma aka rasa sanin irin girman tasirin da kowanne ya yi, to za a raba alhakin a tsakaninsu daidai wa daida.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 72 (3/8)([1])
GAME DA BIYAN KAFIN ALƘALAMI "DAFOZIT" KO "ARBUN"

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Biyan kafin alƙalami "dafozit" ko "Arbun",

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akan haka, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1- Abin da ake nufi da sayar da haja tare da biyan wani sashe na kuɗi da sharaɗin idan aka amshi hajar za a biya cikon kuɗin, idan kuma wanda ya biya ɗin ya fasa saya kuɗin da aka biya ya zama na mai sayarwar.

Haya ma yana ɗaukan hukuncin sayayya; saboda sayar da amfanin abu ne, kasuwancin da yake togiya akan wannan shi ne duk wata cinikayya da aka sharɗanta amsar ɗaya daga cikin musanyensa a wurin da aka haɗa cinikayyar (Kaman "as- Salamu"), ko amsa dukan musanyen guda biyu (Musanyen kuɗaɗen riba da na canji), ba ya shiga cikin "al Murabaha ga wanda aka umurce shi

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 1/641).

ya wata haja”([1]) a wani mataki na ɗaukan alƙawari, amma ya halatta a matakin biya wanda yake biyo bayan ɗaukan alƙawarin.

2- Ya halatta a yi cinikayya da bayar da kafin alƙalami “defozit” idan an iyakanci lokacin jira, ana kuma yi la’akari da kafin alƙalamin a matsayin wani sashe ne na kuɗin idan an kai ga sayen hajar, kuma zai zama haƙƙi ne na mai sayarwa idan mai sayen ya fasa saye.

Allah shi ne masani;;

([1]) Abin da ake nufi shi ne: Yarjejeniya ce tsakanin vangarori biyu, ana kiran vangare da farko da wanda ya bayar da umurni, ɗayan kuma wanda aka ba shi umurni, na farkon zai nemi na biyun da ya saya masa wata haja, da sharaɗin zai saya a wurinsa ba shi, zai ba shi riba na wani adadi na kuɗi, su kuma rattaba hannu akan zartar da haka akan dukanninsu.

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

KUDURI MAI LAMBA: 73 (4/8)([1])
GAME DA KAƊA KARARRAWA([2])

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Kaɗa ƙararrawa,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akansa,

Ganin cewa saye da sayarwa ta hanyar kaɗa ƙararrawa yana cikin harkokin da suka yaɗu ainun a wannan zamani, kuma an sami kura- kurai da wuce gona da iri a wajen zartar da wasu hanyoyi na gudanar da shi, abin da ya sanya dole a samar da ƙa'idoji da za su daidaita al'amarinsa, su kuma kiyaye haƙƙoƙin masu ta'amu da shi (mai saye da mai sayarwa) daidai da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci, haka ma lura da irin yanda cibiyoyi da hukumomi suka aminta da wannan tsari, suka kuma samar masa da ƙa'idodjin da da tsare- tsare a hukumance, saboda kuma bayanin hukunce- hukuncen da Shari'a a

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 2/25).

([2]) Kulla cinikayya ne ta hanyar tayi, inda wani tayin da ya fi na farko zai biyo baya, haka dai har zuwa lokacin da za a sallama wa wanda tayinsa ya fi yawa, inda dukan sauran tayin da suka gabace shi za su zaman Kaman ba a yi su ba.

shimfiɗa a wannan kasuwanci, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1- **Kasuwancin kaɗa ƙararrawa**: Kasuwanci ne da ya dogara da gayyatar masu so –a rubuce ko da baki- domin su shiga cikin tsarin tayi, wanda a ƙarshe idan mai sayarwa ya aminta a gudanar da shi a aikace.
2- Kasuwancin kaɗa ƙararrawa nau'i- nau'i ne daidai da maudhu'in da za a gudanar da shi a kansa, shin kasuwanci ne, ko kuwa haya da sauransu. Kuma ta sashen ɗabi'arsa ya kasu zuwa kasuwanci na zaɓin kai –irinsu kasuwancin kaɗa ƙararrawar da yake gudana tsakanin mutane da junansu- da kuma na dole –irin wanda shari'a na kotu ne ta wajabta yinsa, kuma cibiyoyin gwamnati da masu zaman kansu, da hukumomi da ɗaiɗaikun mutane duka suna buƙatar wannan tsari na kasuwanci.
3- Lallai dole ne duka matakan da ake ɗauka wajen gudanar da kasuwancin kaɗa ƙararrawa da suka haɗa da: rubuta shi a rubuce, da tsarin yanda ake gudanar da shi, da bin sharuɗɗa da ƙa'idoji na gudanarwa, da na dokoki su zama ba su yi hannun- riga da hukunce-hukuncen Shari'ar Musulunci ba.
4- Ya halatta mutumin da zai shiga cikin wannan kasuwanci ya nemi lamuni, kuma dole ne a mai da wa duk wanda ya shiga ciki aka yi da shi abin da bayar muddin ba shi ne ya yi nasarar samun kasuwancin ba, ana cire lamuni na kuɗi ne daga cikin kuɗin wanda ya sami nasara a kasuwancin.
5- Shari'a ba ta hana a biya kuɗin shiga –kuɗin form ɗin da yake ɗauke da sharuɗɗa- da sharaɗin kada ƙimarsa ya wuce na kuɗinsa na haƙiƙa.
6- Ya halatta bankin Musulunci ko waninsa ya gabatar da shirye- shirye na zuwa jari da kasuwanci da za su kawo masa riba mai yawa, shin zuba jarin a wajen kasuwancin Mudaraba tare da bankin ne, ko kuwa a wani wuri na daban.

7- Yayata haja da Tallata ta ta hanyar ƙarya harumun ne, a cikin surorin yin hakan akwai:

a. Wanda ba saye zai yi ba ya ƙara kuɗin haja saboda kawai ya rudi mai saye akan ya ƙara.

b. Wanba ba saye zai yi ba amma ya bayyana sha'awarsa da hajar yana mai bayyana kyawonta da nagartarta yana kuma yabonta, saboda kawai ya rudi mai saye ya yi ƙari akan kuɗinta.

c. Mai haja, ko wakilinsa, ko kuma dillali ya yi ƙaryar cewa an sayi hajar ne da wani kuɗin, saboda a rudi mai saye.

d. Haka ma a cikin sababbin surori na yayata haja, da tallata ta ta hanyar ƙarya, wadda Shari'ar Musulunci ta haramta akwai: bin hanyoyin sadarwa na ji (irinsu radiyo) da na gani (bidiyo ko talebijin) da na karantawa (jaridu da shafukan intanet na zamani) wajen Ambato wasu sifofi da ba na gaskiya ba, ko kuma su ɗaga ainihin farashin na haƙiƙa saboda a rudi mai saye, hakan kuma ya sanya shi ya shiga cikin wannan ciniki.

Allah ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 74 (5/8)(1)
GAME DA SAMAR DA KASUWAR MUSLUNCI DAIDAI DA HUKUNCE- HUKUNCEN SHARI'A

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Samar da Kasuwar Muslunci Daidai Da Hukunce- Hukuncen Shari'a, wanda ciko ne na maudhu'an kasuwannin hada- hadar kuɗi, da takardun kuɗaɗe da aka gabatar a tarurrukan da suka gabata, musamman ma a taron shekara- shekara na bakwai da aka yi a Jidda(2), da kuma ƙananan tarurrukan ƙara wa juna sani da majalisar ta gudanar saboda wannan manufa, domin isa zuwa ga halattattun ƙa'idoji da suka dace da kasuwannin hada- hadar kuɗi, ganin cewa irin wannan kasuwa ita ce hanyar shige- da ficen kuɗaɗe da aka da ita a ƙasashen Musulmai, yake kuma tabbatar da cimma manufofin ayyukan raya ƙasa, da taimako gami da daidaito a tsakanin ƙasashen Musulmai,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana game da yanda ake amfana da sigogin da suke cika kasuwannin

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 2/373).
(2) Duba Ƙuduri mai lamba 63 (1/7)

Musulunci, waɗanda su ne: hannun – jari, da Sukuk, da kuma kasuwanci na musamman waɗanda da su ne ake samar da kasuwar Musulunci akan hukunce- hukuncen Shari'a, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Hannun- jari:

Majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta fitar da wani ƙuduri mai lamba 63 (1/7) game da kasuwannin hada- hadar kuɗi: Hannun- jari, da zaɓi, da haja, da takardun kuɗaɗe, ta kuma bayyana hukunce- hukuncensu, za a iya amfana da su wajen kafa kasuwar hada- hadar kuɗaɗe ta Musulunci.

Na biyu: "Sukuk": Shahadun Mallakar Bashi (Credit Bond)

a. Shahadun Mallakar Bashi na bayar da bashi, da na zuba jari.

Majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta fitar da wani ƙuduri mai lamba 30 (5/4) game da Shahadun Mallakar Bashi na bayar da bashi.

b. Shahadun Mallakar Bashi na bayar da bashi na haya, ko hayar da take ƙarƙarewa da mallaka, ita ma lallai Majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta fitar da wani ƙuduri mai lamba 44 (6/5), saboda haka irin wannan Sukuk ɗin yana bayar da gudummuwa mai kyau a kasuwar hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci a wajen amfanin da ya yi.

Na uku: Cinikayyar Salam:

Ganin cewa cinikayyar Salam –idan aka yi la'akari da sharuɗɗanta- tana da fagage masu faɗi, saboda mai saye yana amfana da shi ne ta hanyar amfani da dukiyarsa wajen samun riba, shi kuma mai sayarwa yana amfana da kuɗin da aka saya ne, tare kuma da ƙara tabbatar da ƙudurin Majalisa mai lamba 63 (1/7) game da rashin halaccin sayar da abin da aka yi cinikayyar salam akan kafin ya zo hannu, wanda yake cewa: (Bai halatta a sayar da hajar da aka yi cinikinta ta hanyar salam kafin ta zo hannu ba).

Na huɗu: Cinikiyyar bayar da jinga na sana'anta wani abu

Majalisa ta fitar da ƙuduri mai lamba 65 (3/7) game da bayar da jingar sana'antawa.

Na biyar: Cinikayya mai jinkiri:

Ita cinikayya mai jinkiri ɗaya ne daga cikin sigogin zuba jari, da suke sauƙaƙa tsarin gudanar da cinikayya, inda mai saye yake amfana da samun hajarsa a nan take, da biyan kuɗin hajar zuwa wani lokaci, Kaman yanda shi mai mai sayarwa yake amfana da ƙarin kuɗin hajar, a ƙarshe kuma hakan yana kai wa zuwa ga faɗaɗa wuraren sayar da hajar da yaɗuwarta a cikin al'umma([1]).

Na shida: Game da cika alƙawarin da ɓangare ɗaya yake ɗauka, da kuma alƙawarin da ɓangarori biyun suke ɗauka wa juna na gudanar da wata cinikayya a nan gaba.

Majalisa ta fitar da ƙuduri mai lamba 40 da 41 (2 da 3/5) game da game da cika alƙawarin gudanar cinikayya a nan gaba daga ɓangare ɗaya, da ɗaura wa wanda aka bai wa sautu ko saƙo riba.

Majalisar tana yin wasici da:

Kira zuwa ga masu bincike cikin masana Fiƙihu da masana tattalin arziki da su samar da bincike da nazarce – nazarce masu zurfi akan maudhu'an da ba a gudanar da bincike akansu ba, saboda su bayyana irin yanda za a zartar da su a aikace, a kuma amfana da su a Shari'ance wajen samar da kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci, waɗannan maudhu'ai sun haɗa da:

- **a-** Dukan nau'o'in Sukuk na tarayya.
- **b-** Tsara Sukuk a cikin haya, ko hayar da take ƙarƙarewa da mallaka.
- **c-** Sauya bashin cinikayyar Salam, da amsa da kuma tarayya a cikinsa, da kuma sauke nauyinsa, da yin sulhu akansa da sauransu.

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 51 (2/6) da Ƙuduri mai lamba 64 (2/7) game da Cinikayyar da ake rarraba kuɗin biyanta zuwa lokaci lokaci (Installement sales).

d- Alƙawarin gudanar cinikayya a nan gaba daga ɓangare ɗaya wanda ba a cinikayyar Murabaha ba, musamman alƙawarin biya.
e- Sayar da basussuka.
f- Sulhu a kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe (musanya ko makamantan haka)
g- Zameye.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 75 (6/8)([1])
GAME DA MAS'ALOLIN TARKADUN KUDI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Mas'alolin takardun kuɗi,

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan wannan maudhu'in, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ya halatta tsare- tsare da dokokin ƙwadugo, da ma wasu shirye- shirye na musamman da ake ƙayyade albashinsu da takardun kuɗi su ƙunshi sharaɗin "ɗaure albashi da ƙima", da sharaɗin kada hakan ya zama ya cutar da tattalin arzikin na gaba ɗaya.

Abin da ake nufi da "ɗaure albashi da ƙima" shi ne: Sassauyawar albashin daga lokacin zuwa lokaci daidai da irin yanda farashin lokacin ya kama, gwargwadon yanda kwararrun hukumomi da suke a wannan fage suka tabbatar, manufar wannan gyarar ita ce: kiyaye albashin da ma'aikata suke ɗauka daga durƙushewa, da gazawa wajen siyan abubuwan buƙata sakamakon faɗuwar darajar kuɗin, da kuma abin da faɗuwar darajar yake haifarwa na tsadan

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta uku, 3/1650) da (Fitowa ta biyar 3/1609).

kayayyaki da hidimomin yau da kullum. Saboda a asali sanya sharaɗi abu ne da ya halatta, sai dai idan ya kai zuwa ga halatta haramu, ko haramta halal.

Amma ida albashin ya tattaru ya zama bashi, to a nan za a yi aiki ne da hukunce- hukuncen bashi da aka bayyana a ƙudurin Majalsa mai lamba 42 (4/5).

Na biyu: Ya halatta mai bayar da bashi da wanda aka bai wa su yi yarjejeniya a ranar biyan bashin –ba kafin ranar ba- akan cewa za a biya bashin ne da wani kuɗi na daban saɓanin wanda aka basa, amma da farashin wannan kuɗin a ranar biya. Haka ma bashin da aka rarraba lokacin biyansa, da ayyanannen takardar kuɗi, ya halatta a ranar biyan kason a biya shi gaba ɗaya da wani takardar kuɗin na daban, amma da farashinsa a ranar biya.

Amma sharaɗi a dukan nau'o'in shi ne: kada wani nauyi ya yi saura akan wanda ake bi bashin da aka biya a cikin wannan tsari, tare kuma da la'akari da ƙudurin da Majalisa ta fitar mai lamba 50 (1/6) game da amsa hannu da hannu.

Na uku: Ya halatta masu ƙulla cinikayya su yi yarjejeniya a lokacin ƙulla cinikin akan ayyana kuɗin cinikin da za a biya nan gaba, ko kuɗin hayar da za a biya da takardar kuɗi sau ɗaya, (duka), ko a rarrabe da takardun kuɗaɗe mabambanta, ko da wani awo na zinaye, a kuma biya daidai da yanda suka yi yarjejeniya, haka ma ya halatta a biya daidai da abin da ya zo a sakin layi da ya gabata.

Na huɗu: Bashin da aka yi shi da ayyanannen takardar kuɗi bai halatta a yi yarjejeniya akan a rubuta biyansa akan wanda ya amshi bashin da abin da ya daidai da wannan kuɗin na zinate ko wani takardar kuɗi na daban ba, ta yanda zai zama wajibin wanda ake bi bashin shi ne ya biya da zinare ko da wani takardar kuɗi na daban da suka cimma yarjejeniya a kai ba.

Na biyar: Ƙara tabbatar da ƙuduri mai lamba 42 (4/5) da majalisa ta fitar game da sauya ƙimar takardun kuɗaɗe.

Majalisar tana bayar da wasici mai zuwa:

Sakateriya ta binciko waɗanda suka cancanta cikin masu bincike a fannin Shari'ar Musulunci, da masana tattalin arziki da suke bin karantarwar Musulunci saboda su yi nazari mai zurfi akan wasu maudhu'ai da suke da jiɓi da mas'alar kuɗaɗe, saboda a tattauna akansu a taron majalisa na shekara- shekra mai gabatowa in Allah ya yarda, a cikin amudhu'an akwai:

a. Yiwuwar amfani da takardar kuɗi na musamman, Kaman a ce dinaren Musulunci, musannan a cikin mu'amalolin da Bankin Musulunci mai kula da ayyukan raya ƙasa (IsDB) yake gudanarwa, ta yanda za a rinƙa bayar da bashi da biyansa da shi, haka ma da tabbatar da bashin da yake ɗaukan lokaci, ta yanda za a biya daidai da farashin da ya yi daidai da wannan takardar kuɗi na musamman, ma'ana daidai da ƙimarta, da ƙimar kuɗaɗen ƙasashen waje da aka zaɓe su wajen biya, alal misa kaman dalar Amurika.

b. Hanyoyi na Shari'a da za su kwafe makwafin ɗaure bashi da ƙima zuwa wani lokaci daidai da matsakaicin ɗaure farashi da ƙima.

c. Ma'anar Badagon takardar kuɗi, da tasirinsa wajen bayyana haƙƙoƙi da wajibai masu zuwa nan gaba.

d. Iyakan Badagon haja da zai yiwu a ɗauki hakan a matsayin shiga cikin yanayin badagon takardun kuɗaɗe.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 76 (7/8)
GAME DA MATSALOLIN BANKUNAN MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar mata akan maudhu'in: Matsalolin Bankunan Musulunci,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa,

Bayan majalisar ta bijiro da abubuwan da suka zo a cikin bincike da nazarce- nazarcen da aka yi game da matsalolin Bankunan Musulunci, waɗanda suke ƙunshe da shawarwarin da za su magance dukan waɗannan nau'o'i na matsaloli ta ɓangare shari'a da aiki da kuma gudanarwa, da ma matsalolin da suke da dangantaka da ɓangarori da suka saɓa da juna, bayan sauraron tattauwar da ta gudana akan waɗannan matsaloli, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Gabatar wa sakateriyar majalisa da jerin maudhu'an da aka tsara a rukunnai guda huɗu, saboda ta nemo ƙwararru masana su yi rubutu a kai, a kuma bijiro da su a taron shekara- shekara mai zuwa daidai da jerin abubuwan da suka fi muhimmanci da kwamitin tsare- tsare ya shirya:

Rukuni na farko: Ajiye- ajiye da abubuwan da suke da jiɓi da shi:

a- Lamunin ajiye- ajiyen kasuwanci da suka yi daidai da hukunce- hukuncen Musulunci a babin Mudaraba.
b- Musanyen ajiye- ajiye tsakanin bankuna ba a kan tsarin fa'ida ba.
c- Yanda Shari'a take kallon wannan ajiye- ajiye, da hanyoyin magance lissafe- lissafen ciki.
d- Bayar da bashi ga wani mutum da sharaɗin zai yi mu'amala tare da bankin, ko zai sanya shi a cikin wata harkar da aka ƙayyade.
e- Kuɗaɗen Mudaraba da wanda suke akansa (Mai juya kuɗin ko kuwa uwar kuɗin mudarabar).
f- Iyakance dangantaka tsakanin masu bayar da ajiya da masu bayar da kuɗin mudaraba.
g- Shiga tsakani a cikin mudara da haya da kuma lamuni.
h- Iyakance abin da ake nufi da mudaraba a Bankin Musulunci (Masu bayar da kuɗi, ko kuwa majalisar gudanarwa, ko kuwa majalisar da suke zartarwa).
i- Tsarin Musulunci da zai kwafe makwafin buɗaɗɗun asusu.
j- Zakkar da Bankunan Musulunci za su fitar daga cikin dukiyoyinsu da ajiye- ajiyen da yake wurinsu.

Rukuni na biyu: Neman riba (al-Murabaha)([1]):

a. Neman riba a cikin hannayen jari.
b. Jinkirta yin rijistan mallaka a cinikayyar da aka gudanar da ita a tsarin murabaha, saboda a kiyaye wa banki haƙƙinsa na lamuni a lokacin biya.
c. Tsarin cinikayyar Murabaha da aka jinkirta lokacin biya tare da yin wakilci ga wanda aka ba shi umurnin

([1]) Murabaha wani tsari ne na cinikayya a Musulunci wanda yake aiki a matsayin ƙulla cinikayya da aka ƙayyade farashin haja, ko tsare- tsarenta Kaman yanda wanda za a yi ta'amuli da shi ya buƙata, har da ribar da suka cimma yarjejeniya a kai, inda bayan haka ne banki zai sayi abin da ake buƙata, ya kuma rufe wannan cinikayyar tare da mai sayarwar da aka zava, sannan bayan haka kuma ya sayar wa abokin huldarsa akan tsarin raba riba a tsakaninsu, shi kuma abokin huldar zai rinƙa biyan banki sannu a hankali kaso kaso, ko kuma ta dukan sharaɗin da suka gindaya ma kansu.

sayen haja da sharaɗin za a saya a hannunsa a matsayinsa na wakili.

d. Taurin bashi wajen biyan basussukan da suka faru ta hanyar murabaha, ko ta duk wata jinkitacciyar mu'amala.

e. Yi wa basussuka inshora.

f. Sayar da basussuka.

Rukuni na uku: bayar da haya:

a- Sake bayar da haya ga mai kayan da aka yi haya a wurinsa, ko ga waninsa.

b- Bayar da hayar ayyukan mutane, da sake bayar da hayarsu.

c- Bayar da hayar hannayen jari, ko bayar da su a matsayin bashi, ko jingina.

d- Gyara abin da aka haya.

e- Sayen abu daga hannun wani da sharaɗin ba shi hayarsa.

f- Haɗa tsakanin haya da mudaraba.

Rukuni na huɗu: Ƙulla Cinikayya:

a. Sharaɗi na yarjejeniya akan haƙƙin banki na rusa cinikayya idan ba a biya kashe- kashen kuɗaɗen da aka rarraba lokutan biyansu ba.

b. Sharaɗi na yarjejeniya akan sauya yarjejeniyar ƙulla cinikayya daga wata siga zuwa wata idan ba a biya kashe- kashen kuɗaɗen da aka rarraba lokutan biyansu ba.

Majalisar tana wasici da abu mai zuwa:

Na farko: Bankunan Musulunci su cigaba da tuntuɓa da tattaunawa da manyan bankunan ƙasashe a ƙasashen Musulmai saboda bankunan Musulunci su sami damar gabatar da ayyukansu wajen yin kasuwanci da jujjuya dukiyoyin abokan hulɗarsu daidai da ƙa'idoji hukunce-hukuncen Shari'ar Musulunci da a ƙarƙashinsu ne ake gudanar da ayyuka da hada- hadar bankunan, wanda ya yi daidai da ɗabi'unsu na musamman. Kuma dole ne su manyan bankuna na ƙasashe su yi la'akari da abubuwan

da za su sanya bankunan Musulunci su yi nasara wajen gabatar da ayyukansu mai tasiri wajen gabatar da ayyukan raya ƙasa, ƙarƙashin tsare- tsaren sanya ido da lura da ya dace da sharuɗɗa da ƙa'idodjin bankunan Musulunci, da kuma gabatar da kira zuwa ga ƙungiyar ƙasashen Musulmai da bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa na su cigaba da tsara tarurrukan manyan bankunan ƙasashe na ƙasashen Musulmai, abin da zai bayar da dama na zartar da abubuwan da wannan wasicin ya buƙata.

Na biyu: Bankunan Musulunci su kula da bayar da horaswa ta musamman ga jagorori da ma'aikata game da ƙwarewa ta aiki da za ta wayar masu da kai akan ɗabi'ar ayyuka a bankunan Musulunci, da kuma samar da tsare-tsaren horaswa da suka dace tare da taimakekeniya da Cibiyar Musulunci mai lura da bincike da horaswa da sauran sassan da suke da jiɓi da bayar da horaswa a fannin sanin makama a Bankunan Musulunci.

Na uku: Bayar da kulawa ta musamman da cinikayyar Salam da neman sana'antawa (al- Istisna'u), ganin cewa su ne makwafin da Shari'a take gabatarwa a wajen bayar da tallafi na kuɗi wajen cigaban harkar samar da abubuwan da al'umma take buƙata nay au da kullum.

Na huɗu: Rage yin amfani da salon murabaha ga wanda aka ba shi umurnin sayen haja da sharaɗin za a saya a hannunsa gwargwadon iko, da taƙaita da tsare- tsaren da suke ƙarƙashin kulawa da sanya idon banki, waɗanda aka samin tabbacin rashin faɗawa cikin abubuwan da suka saɓa wa Shari'a wanda ita ce take hukuntanta. Da kuma ƙara yawaita sigogin cinikayya da kasuwanci masu yawa irinsu Mudaraba da tarayya da bayar da haya, tare kuma da muhimmanta bibiya, da kawo gyara lokaci zuwa lokaci, kuma ya kamata a amfana da mabambanta karɓaɓɓun halaye a fagen mudaraba, abin da zai bayar da saman killace ita kanta mudarabar da kuma sauƙin bibiya wajen sanin tasirinta.

Na biyar: Samar da kasuwa ta cinikayya domin musanyen kayayyaki tsakanin ƙasashen Musulmai da za ta kwafe makwafin kasuwar kayayyaki na ƙasa da ƙasa wadda ba kasafai take rabo da abubuwan da suka saɓa da Shari'ar Musulunci ba.

Na shida: Fuskantar da ribar da aka samu sakamakon jujjuyawar uwar kuɗi wajen gabatar da manyan manufofin ayyukan raya ƙasa a ƙasashen Musulmai, tare da taimakekeniya tsakanin bankunan Musulunci saboda a ƙarfafi asusun harkokin kasuwanci na haɗin gwiwa da kuma samar da ayyuka da shirye – shiryen cigaba na tarayya.

Na bakwai: Gaggawar samar da manuniya ta hasashe da za ta yi daidai da Shari'ar Musulunci, wadda za ta kwafe makwafin kuɗin ruwa (riba) wajen iyakance riba a cikin mu'amaloli.

Na takwas: Faɗaɗa tsarin kasuwar hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci ta hanyar gabatar da ita tsakanin bankunan Musulunci da junansu, tare da taimakekeniya da bankIN Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa, saboda a ƙara fagen ƙirƙira da kuma kara-kainar hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci a ƙasashen Musulunci mabambanta.

Na tara: Kiran hukumomin da abin ya shafa wajen samar da dokoki da za su zamo ginshiƙai da ƙa'idoji na ƙarfafa mu'amaloli na musamman a fannin sigogin kasuwanci da cinikayya na Musulunci, irinsu mudaraba da musharaka da muzara'a da kuma shayar da amfanin gona da neman sana'antawa da haya.

Na goma: Kiran Bankunan Musulunci zuwa ga su samar da wani rumbu na bayanai da za su ƙunshi cikakkun bayanai game da abokan hulɗat bankunan Musulunci da manyan 'yan kasuwa, saboda hakan ya zama wajen da bankunan Musulunci za su rinƙa komawa zuwa gare shi domin su amfana da bayanan da suke ciki wajen ƙarfafa yin mu'amala tare da su da samun aminci, da kuma nesantar marasa gaskiya.

Na goma sha ɗaya: Kiran bankunan Musulunci zuwa ga tuntuɓar juna wajen sanya ido da kulawa tsakananin hukumomin da suke sanya ido da kulawa a fagen Shari'a da suke da su, shin ta hanyar ƙara jaddada ayyukan hukumar ƙoli ta lura da hukunce- hukuncen Musulunci a bankunan Musulunci ne, ko ta hanyar sake samar da wata hukumar da za ta samar da ƙa'idoji na bai ɗaya a ayyukan sanya ido da kulawa da hukunce- hukuncen Shari'a a bankunan Musulunci.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 77 (8/8)([1])
GAME DA TARAYYA A CIKIN HANNAYEN ZUBA JARIN KAMFANONIN HAƊIN GWIWA DA SUKE MU'AMALA DA KUƊIN RUWA (RIBA)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba bayanin bayan taron ƙara wa juna sanin akan tattalin arziki da sakateriyar majalisa ta shirya a garin Jidda tare da taimakekeniya da Cibiyar Musulunci mai lura da bincike da horasta ƙarƙashin Bankin Musulunci mai lura da ayyukan raya ƙasa game da hukuncin yin tarayya a cikin hannayen zuba jarin da kamfanonin haɗin gwiwa da suke mu'amala da kuɗin ruwa (riba), da kuma bincike- binciken da aka gabatar a wannan taro,

Duba da muhimmancin da wannan maudhu'in yake da shi, da kuma wajibci kamala dukan bayanai da suke shafe shi, ta yanda za a bi shi dalla- dalla a kuma sami sanin dukan ra'ayoyin malamai game da shi, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

An ɗaura wa sakateriyar majalisa alhakin nemo malamai masana da za su rubuta wasu bincike- bincike da nazarce-

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta shida, 2/1273) da (Fitowa ta bakwai 1/73) da (Fitowa ta tara 2/5).

nazarce ta yanda majalisa za ta samu daman ɗaukan ƙudurin da ya kamata a taronta na shekara- shekara mai zuwa([1]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Duba Ƙuduri mai lamba 63 (1/7) da ƙuduri mai lamba 87 (4/9).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 78 (9/8)([1])
GAME DA KATIN AMINCI (Credit card)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisa game da maudhu'in katin aminci (Credit card),

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa,

Duba da muhimmancin da wannan maudhu'in yake da shi, da kuma wajibci kamala dukan bayanai da suke shafe shi, ta yanda za a bi shi dalla- dalla a kuma sami sanin dukan ra'ayoyin malamai game da shi, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

An ɗaura wa sakateriyar majalisa alhakin nemo malamai masana da za su rubuta wasu bincike- bincike da nazarce-nazarce ta yanda majalisa za ta samu daman ɗaukan ƙudurin da ya kamata a taronta na shekara- shekara mai zuwa([2]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 290/571).
([2]) Duba Ƙuduri mai lamba 63 (1/7) da ƙuduri mai lamba 87 (4/9).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 79 (10/8)([1])
GAME DA SIRRI A AIKIN LIKITANCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisa game da maudhu'in: Sirri a aikin likitanci,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Sirri shi ne abin da mutum zai bayyana wa wani ya kuma nemi ya ɓoye masa shi kafin, ko bayan, ya kuma haɗa da abubuwan da suke haɗe da alamun neman a ɓoye a cikin abubuwan da a al'adance ana ɓoye su, haka ma ya haɗa da abubuwan da suke keɓanci mutum da aibobinsa da ba ya son mutane su sani.

Na biyu: Sirri amana ne a wurin wanda aka ba shi shi domin ya kiyaye, saboda yi wa abin da Shari'ar Musulunci ta zo da shi biyayya, da kuma kiyaye mutunci da kyautata ladubban a wajen mu'amala.

Na uku: A asali an haramta yaɗa sirri, saboda haka yaɗa shi ba tare da wani dalili ko hujja da za su kai ga yin hakan ba laifi ne a shari'ar Musulunci.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 3/15).

Na huɗu: Wajibcin kiyaye sirri yana ƙara ƙarfi da tabbata akan wanda yake aiki a fagen da yaɗa sirri yana cutar da sana'ar kanta, kaman aikin likitanci, saboda mutane masu buƙata suna komawa zuwa gare su domin neman nasiha da shawara da neman taimako, hakan yake sanya su faɗa masu sirrinsu da zai taimaka masu su gabatar da aikinsu kaman yanda ya kamata, a cikin wannan sirrin akwai waɗanda mutum ba ya son waninsa ya sani, koda kuwa makusancinsa ne.

Na biyar: A wajibcin kiyaye sirri ana yin togaciyar wasu halaye da yanayi, waɗanda ɓoye sirrin zai kai zuwa ga cutuwar da ta ɗara wadda za ta faru idan aka yaɗa sirri ga mai shi, ko kuma ya zama akwai maslaha a yaɗa sirrin da ya rinjayi cutar da ɓoye shi zai haifar, waɗannan halaye da yanayi suna da fuskoki biyu:

a- Halaye da yanayin da wajibi ne a yaɗa sirri, ƙarƙashin ƙa'idar nan da take cewa: "Aiki da abu mai cutarwa da ya fi sauƙi, saboda a kawar da cutar da ta fi girma", da ƙa'idar: "Samar da maslahar al'umma da take wajabta yin haƙuri da jure wa cutuwar ɗaiɗaiku wajen kawar da cutuwar ɗaukacin al'umma idan kawar da shi ɗin mai yiwuwa ne".

Waɗannan yanayin sun kasu biyu:

- Abin da zai kawar da cutuwa ga ɗaukacin al'umma.
- Abin da zai kawar da cutuwa ga mutum ɗaya.

b- Halaye da yanayin da ya halatta a yaɗa sirri saboda abin da yake cikin yin haka na:

- Samar da maslahar ɗaukacin al'umma.
- ko kawar da cutuwa ga ɗaukacin al'umma.

A duka waɗannan halaye da yanayin dole ne a kiyaye manyan manufofin Shari'ar Musulunci, da abubuwan da take gabatar da su akan komai na kiyaye addini da rai da hankali da tsatso da dukiya.

Na shida: Togiya game da wuraren da ya wajaba a yaɗa sirri, ko halaccin yaɗa shi ya kamata ya zama a rubuce a

tsari da dokokin aikin likita da sauran tsare- tsare, inda za a ambaci haka a fili, kuma su ɗin ne kawai da aka ambata ɗin, tare kuma da bayyana irin yanda aka amince a yaɗa sirri, ko wane ne zai yi haka, kuma hukumar da abin ya shafa dole ne ya wayar da kan al'umma game da haka kowa ya sani.

An bayar da wasici mai zuwa:

Kira zuwa ga ƙungiyoyin likitoci da ma'aikatun lafiya da tsangayoyin ilmomin likitanci kan su shigar da wannan maudhu'in a cikin manyan shirye- shiryensu, su kuma muhimmanta shi su wayar da kan ma'aikatansu da suke wannan fage akan haka. Su kuma sanya shi a cikin tsari da manhajar karantarwa, suna masu amfani da binciken da nazarce- nazarcen da aka gabatar akan wannan maudhu'in.

Allah ya sa mudace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 80 (11/8)([1])
GAME DA ƊABI'UN LIKITA: ALHAKIN DA YAKE KANSA DA ABUBUWAN DA SHARI'A ZA TA KAMA SHI A KAI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisa game da maudhu'in: Ɗabi'un Likita: Alhakin da yake kansa da abubuwan da Shari'a za ta kama shi a kai,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta fitar da ƙuduri akan maudhu'in: "Ɗabi'un Likita: Alhakin da yake kansa da abubuwan da Shari'a za ta kama shi a kai", da maudhu'in: "Yin magani da abin da aka haramta", da "Duba dokokin aikin likitanci da Ƙungiyar Musulunci ta ilmomin likitanci da take Kuwait" da kuma neman sakateriyar majalisa ta sake nemo malamai da za su ƙara gabatar da bincike akan waɗannan maudhu'ai a gabatar da su a taron majalisa na shekara- shekara mai zuwa.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 3/5).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 81 (12/8)([1])
GAME DA LIKITA NAMIJI YA YI WA MACE MAGANI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisa game da maudhu'in: Likita namiji ya yi wa mace magani,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

A asali, idan akwai likita mace ƙwararriya to ita ce ya wajaba ta duba 'yar uwarta mace, idan kuma ba a sami haka ba, sai a koma zuwa ga likita mace amintacciya wadda ba Musulma ba, idan haka bai samu ba, sai a koma zuwa ga likita Musulmi, idan haka bai samu ba zai yiwu a koma zuwa ga likita namiji wanda ba Musulmi ba. Dole ne ga wanda zai kalli jikin mace ya taƙaita kawai a wuraren da dubawan ya zama dole saboda yin magani, kada ya ƙetare haka, dole ne kuma ya rufe idonsa daidai gwargwado, idan kuma za a yi wa mace magani a yi ne a gaban: muharraminta, ko mijinta, ko wata amintacciyar mace, gudun kada a sami keɓancewa.

An bayar da wasici da cewa:

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 3/9).

Hukumomin lafiya su ƙara himma wajen ƙarfafa mata su shiga fagen ilmomin likitanci, su kuma shiga su ƙware a dukan sassansa, musamman a cututtukan da suka shafi mata da haihuwa, duba da irin yanda mata suka yi ƙaranci ainun a cikin waɗannan fagage da sassa na aikin likitanci, gudun kada yin aiki da halin lalura ya tilasta mana aiki da ƙa'idar togaciya.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 82 (13/8)([1])
GAME DA CUTA MAI KARYA GARKUWAR ƊAN ADAM (AIDS KO SIDA)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisa game da maudhu'in: Cuta mai karya garkuwar ɗan Adam (Aids ko sida),

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, wadda ta bayyana cewa aikata laifuffukan alfasha na zina da luwaɗi su ne muhimman dalilai da suke kai wa zuwa ga kamuwa da cututtukan saduwa, wadda mafi hatsarin cikinsu ita ce cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam, kuma lallai yaƙi da munanan ɗabi'u, kuma fuskantar ma'aikatan jarida da yaɗa labarai, da ma'aikatan yawon shaƙatawa da buɗe ido zuwa ga hanyoyi masu kyau suna muhimman hanyoyin sanya ido da samun kariya daga faɗawa cikinsu, babu shakka bin karantarwar Musulunci mai daraja, da yaƙi da munanan ɗabi'u, da kuma kawo gyara a fagen jarida da yaɗa labarai, da hana yaɗa fima-fiman batsa gejeru, da masu dogon zangonsu, da kuma

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 3/9).

sanya ido a sashen yawon shaƙatawa da buɗe ido, suna cikin manyan hanyoyin samun kariya ga barin kamuwa da waɗannan cututtuka, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

Idan ɗaya daga cikin ma'aurata biyu ya kamu da wannan cutar, dole ne ya sanar da ɗayan, ya kuma yi taimakekeniya da shi wajen ɗaukan gaba ɗayan matakan da za su bayar da kariya.

An kuma yi wasici da cewa:

Na farko: Kira zuwa ga hukumomin da abin ya shafa a ƙasashen Musulmai na su ɗauki dukan matakan kariya da riga- kafi da suka kamata wajen kare kai daga cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam, da hukunta duk wani da ya yi yunƙurin yaɗa shi zuwa ga wani da gangan. Kaman yanda muke kira zuwa ga gwamnatin ƙasar Saudiyya da ta cigaba da ƙoƙarinta na bai wa Alhazai kariya, da ɗaukan duk matakan da suka kamata wajen kare su daga yiwuwar kamuwa da cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam.

Na biyu: Bayar da kulawa ta musamman ga waɗanda suka kamu da wannan cuta, kuma dole ga waɗanda suka kamu, ko waɗanda suke ɗauke da wannan cuta su nesanci duk wata hanya da za ta kai ga wasu su kamu ta hanyarsu, kaman yanda ya dole ne a samar makarantu ka ƙananan yaran da suke ɗauke da wannan cuta a kuma karantar da su ta hanyoyin da suka dace.

Na uku: Ɗaura wa sakateriyar majalisa alhakin nemo masana likitoci da masana Fiƙihu su yi rubutu akan maudhu'ai masu zuwa, saboda a kamman binciken da ake buƙata akansu, a kuma gabatar da su a taron shekara-shekara mai zuwa([1]):

- **a-** Killace mai ɗauke da cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam da wanda ya kamu da ita.
- **b-** Matsayar hukumomin da masu kamuwa da cutar aids ko sida suka aiki game da su.
- **c-** Zubar da cikin mace mai ɗauke da cutar aids ko sida.

([1]) Duba Ƙuduri mai lamba 90 (7/9).

d- Bai wa matar mai ɗauke da cutar aids haƙƙi rabuwar aurenta da shi.

e- Shin za a yi la'akari da kamuwa da cutar aids ya zama daidai yake da hukuncin wanda cuta ta kwantar da shi a shimfiɗar mutuwa a fagen matakan da yake ɗauka akan abubuwan da ya mallaka?.

f- Tasirin kamuwar uwa da cutar aids akan haƙƙinta na rainon yaro.

g- Mene ne hukuncin shari'a akan wanda da gangan ya yaɗa wa waninsa wannan cuta?

h- Bayar da diyya ga waɗanda suka kamu da cutar aids ta hanyar ɗaukan jinni, ko abubuwan da suke da jiɓi da shi, ko ta hanyar dashen gaɓoɓi.

i- Gabatar da bincike na likitanci kafin aure saboda a guje wa hatsarurrukan da ake iya ɗauka, musamman cutar aids,

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 83 (14/8)
GAME DA TSARIN NEMO MALAMAI MASU BINCIKE DA SU YI RUBUTU DA TATTAUNAWA AKANSU A TARON SHEKARA- SHEKARA NA MAJALISA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na takwas a Bandar Seri Begawan (Brunei – Darus Salam), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 7 ga watan Al- Muharram, 1414 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 21 zuwa 27 ga watan Yuni, 1993,

Bayan ta duba ƙa'idoji da dokokin yaɗa binciken cibiya, da sharuɗɗan da aka sanya duk wani bincike ya cika su,

Bayan ta saurari yanayi da abubuwan da suke faruwa a lokacin da aka ɗaura alhakin yin rubutu akan wani, da kuma iyakance lokacin gabatar da binciken da ya yi, ta yanda sakateriya za ta sami daman gabatar wa majalisar ciba domin da duba binciken ƙarƙashin ƙa'idojin yaɗa bincike da muka yi nuni akansu, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Idan lokacin da aka ƙayyade na amsar bincike ya wuce, sakateriya tana da haƙƙin ta taƙaita da binciken da aka gabatar mata a lokaci ba kuma tare da ta ɗauki wani alhaki akan waɗanda suka yi jinkiri ba.

Na biyu: Sakateriyar cibiya ba za ta amshi duk wani bincike da masu shi suka yi gaban kansu suka yi ba tare da sakateriya ce ta nemi su yi ba.

Na uku: Za a taƙaita tattaunawa a taron shekara-shekara kawai tare da waɗanda aka gayyato cikin mambobin cibiya da ƙwararrun masanan cikinta da masu bincikenta.

Allah ya sa mu dace;;

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA TARA NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA ABU DHABI (HAƉAƉƉIYAR DAULAR LARABAWA) 1 - 6 GA WATAN ZUL ƘIDA, 1415 H 1 – 6 GA WATAN AFRILU, 1995

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 84 (1/9)([1])
GAME DA KASUWANCIN ZINARE, DA MAFITA TA SHARI'A IDAN CANJI YA HAƉU DA HAWALA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Kasuwancin zinare, da mafita ta shari'a idan canji ya haɗu da hawala,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Game da kasuwancin zinare

a. Ya halatta a sayi zinare da azurfa da cek ɗin da ya sami tabbaci, da sharaɗin tattauwar cinikin ta kasance a wurin.

b. Ƙarfafa abin da ɗaukacin malaman Fiƙihu suka tafi a kansa na rashin halaccin sauya zinaren da aka sana'anta da zinaren da ba a sana'anta ba da ya fi shi yawa, saboda ba a la'akari da nagarta ko sana'antawa a wurin cinikayyar zinare da zinare, saboda haka majalisar cibiya tana ganin babu buƙatar sake duba wannan mas'alar, lura da cewa wannan mas'ala ba ta da fage a aikace, saboda ba a yin ta'amuli da zinare a

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 65/).

matsayin kuɗi, tun sanda takardun kuɗaɗe suka kwafe makwafinsa, kuma inda aka gwama su da zinare sun zama wani jinsin na daban.

c. Ya halatta a yi musanyen wani adadi na zinare da wani adadin da bai kais hi ba da aka cakuɗa shi da wani jinsin na daban, inda za a yi la'akarai da ƙarin da za a samu a cikin yana cikin ɗayan jinsin ne da aka cakuɗa.

d. Ganin cewa mas'aloli masu zuwa suna buƙatar ƙarin haske wajen suranta su, da kuma ƙarin bincike na aiki da na Shari'a, an jinkirta ɗaukan ƙuduri akansu, bayan an tabbatar da bayanai game da abubuwan da suke bambance su, waɗanda su ne:

- Siyan hannayen jarin kamfanin da yake aiki wajen fitar da zinare da azurfa.
- Mallaka da mallakar da zinare ta hanya miƙawa da amsar shahadun da suke ayyana wani adadi da ake da shi a wajen ajiya da su ne suke fitar da shahadun, abin da zai bayar da daman amsar zinaren ko kuma yin tasarrufi da shi a duk sanda a ka so.

Na biyu: Game da mafita ta shari'a idan canji ya haɗu da hawala:

a. Hawalar da ake gabatar da ita da wata takardar kuɗi, inda mai neman a yi masa yake gabatar da irin wannan takarda ta kuɗi halal ce a Shari'ar Musulunci, shin an biya mata ladan jinga ko a ba a biya mat aba, amma dai kada ladan jingar ya zarce na daidai irin wannan aiki, amma idan babu ladan jinga to yana layin sakakkiyar hawala kenan a wurin wanda bai sharɗanta cewa dole ne wanda za a yi masa hawalar ya zama yana bin bashi ba, waɗanda su ne mazhabar Hanafiyya, a wurin waninsu kuma sunansa "saftaja", wato wani mutum ya bai wa wani kuɗi saboda ya biya wa wanda aka bai wa, ko wakilinsa da yake a wani gari. Idan kuma akwai ladan jinga, to wannan shi ake kira wakilta mai lada, idan masu zartar da

hawalar a aikace suna yi wa ɗaukacin al'umma ne aiki, to za su lamunci kuɗaɗen halawar, daidai da yanda aka saba na sanya ɗan hayan da yake cikin tarayya ya lamunci abin da ya yi tarayya akansa.

b. Idan kuma abin da ake buƙata a hawala shi ne a biya ta da takardun kuɗaɗen da ba su ne aka gabatar ba, to a nan abin da zai faru shi ne bayar da canji tare da hawala a haɗe, daidai da ma'anar da aka yi ishara zuwa gare ta a sakin layi na **(a.)**, inda a farko ake farawa da canji kafin a yi halawa, inda abokin huldar zai miƙa kuɗin ga banku, inda banki zai rubuta haka a daftarinsa bayan sun cimma matsaya akan farashin canji da aka tabbatar, sannan kuma a yi hawalar da ma'anar da aka yi ishara zuwa gare ta.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 85 (2/9)[1]
GAME DA SALAM DA YANDA AKE GABATAR DA SHI A ZAMANANCE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Salam da yanda ake gabatar da shi a zamanance,

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Game da (Salam):

a) Kayayyaki da hajojin da cinikayyar salam yake iya shiga cikinsu sun haɗa da dukan abubuwan da suka halatta a sayar da su, waɗanda zai yiwu a iyakance su da sifa, su kuma zama bashi akan zimma, shin suna cikin kayayyakin aiki ne, ko kuma waɗanda aka noma ko waɗanda aka sana'anta.

b) Dole a cikin cinikayyar Salam a iyakance ta da wani sanannen lokaci, ko a iyakance da wani sanannen kwanan wata, ko a ɗaure da wani al'amari da ake da tabbacin faruwarsa, koda kuwa lokacin faruwar nasa

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 1/371).

yakan ɗan saɓa kaɗan daga lokaci zuwa lokaci, ta dai yanda ba zai kai zuwa ga faruwar rikin da saɓani ba, alal misali kaman lokacin girbi.

c) Asali shi ne a gaggauta amsar uwar kudin salam a wurin da aka ƙulla shi, amma ya hallata a jinkirta amsarsa zuwa kwanaki biyu, ko uku koda da sharaɗi ne, amma kada lokacin jinkirin ya zama daidai da lokacin da aka iyakance wa cinikayyar salam ɗin, ko ya zama ya wuce shi.

d) A shari'ance babu laifi mai saye a cinikayyar salam ya amshi jingina, ko wani abu da zai lamunce masa haƙƙinsa a wurin abokin cinikayyarsa a cinikayyar salam (mai sayarwa).

e) Ya halatta mai saye (a cinikayyar salam) ya sauya abin da aka gudanar da cinikayyar salam akansa – ban da kuɗi- bayan lokacin bayar da shi ya yi, shin sauyin da jinsinsa ne, ko da wani jinsi na daban. Saboda babu wani nassi cikin nassoshin da suka zo da ya hana haka, babu kuma ijma'in malamai akan hana haka, amma fa sharaɗi ne abin da aka sauya da shin ya zama nagartacce da ya yi daidai da uwar kuɗi a hajar da aka ƙulla cinikayyar salam ɗin akansa.

f) Idan mai sayarwa a cinikayyar salam ya gaza miƙa abin da aka ƙulla cinikayya akansa a lokacin da aka iyakance, to mai sayen yana da zaɓi, ko dai ya jinkirta har zuwa lokacin da za a sami kayan, ko kuma a rusa cinikayyar ya amshi uwar kudinsa, idan kuma dalili gazawarsa wajen bayarwa rashi ne, to za a jinkirta masa zuwa lokacin da zai sami wadata da yalwa.

g) Bai halatta a gindaya sharaɗin uƙuba sakamakon jinkiri gabatar da abin da aka yi cinikayyar salam akansa ba, saboda shi ɗin bashi ne, bai kuma halatta a sanya sharaɗin ƙari a cikin bashi a lokacin da aka yi jinkiri ba.

h) Bai halatta uwar kuɗi a cinikayyar salam ya zama bashi ba, saboda hakan zai zama an sayar da bashi da bashi kenan.

Na biyu: Game da yanda ake gabatar da Salam a wannan zamanin:

Ganin cewa cinikayyar salam a wannan zamani namu hanya ce na jujjuya kuɗi mai ƙarfi a cikin tsarin tattalin arzki na Musulunci, da hada- hadar kuɗaɗe a bankunan Musulunci, ganin irin yanda take da sauƙi wurin mu'amala, da kuma irin yanda take biyan buƙatu mabambanta a wajen zuba jari, shi zuba jarin na kusa ne mai gajeren zango, ko matsakaicin zango, ko kuma mai dogon zangi, da kuma irin yanda hakan yake biyan buƙatun mutane masu yawa da bambanci cikin abokan hulɗa, shin cikin manoma da suke samar da amfanin gona ne, ko kuma masu yin sana'o'i, ko 'yan kwangila, ko 'yan kasuwa, da kuma irin yanda take biyan buƙatun masu sanya kuɗinsu saboda a jujjuya da kuɗin aiki, da ma wasu uwar kuɗin.

Saboda haka ne fagagen gabatar da cinikayyar salam suka yawaita, a cikinsu akwai:

a. Cinikayyar salam ta dace da sanya jari a harkokin noma mabambanta, inda bankin Musulunci zai yi mu'amala tare da manoman da ake tunanin za su sami amfani a lokacin girbinsu, ko girbin waninsu, wanda zai yiwu su saya su kuma bayar da shi, idan sun gaza bayar da kayayyakin amfanin gonan da suka noma da kawunansu, inda wannan hannun jari da za a gabatar masu zai yi masu matuƙar amfani, zai kuma cike giɓi na dukiya da za su iya fuskanta wajen samar da abubuwan da suke buƙata.

b. Zai yiwu a yi aiki da cinikayyar salam wajen sanya jari a harkokin noma da na sana'o'i, musamman a lokacin da sukan gabaci isa zuwa ga amfanin goma, ko kayan da aka sana'anta, inda za a saye su tun

kafin su zo hannu, a kuma sake tallata su da gamsassun farashi.

c. Za a iya yin amfani da cinikayyar salam wajen sanya jari da ƙarfafa masu sana'o'i, da ƙananan manona da masu masana'antu, ta hanyar samar masu da kayayyakin aiki da suka haɗa da injuna da manyan abubuwan buƙata a matsayin hakan ya zama shi ne jari a cinikayyar salam, akan cewa za a amshi kuɗinsu ne daga cikin abubuwan da suka samar, a kuma sake tallata shi.

Majalisar tana bayar da wasici da: a kamala bayani wajen kawo sauran surorin cinikayyar salam na zamani, bayan an gabatar da bincike mabambanya daga ƙwararru masana([1]).

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Game da cinikayyar Salam, duba ƙuduri mai lamba 63 (1/7), hanya ta uku, da ƙuduri mai lamba 74 (5/8) sakin layi na uku

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 86 (3/9)([1])
GAME DA AJIYAR BANKI (ASUSUN BANKI)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Ajiyar Banki (Asusun banki),

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ajiye- ajiyen da za a iya nemansu a kowane lokaci (Current accounts) a bankunan Musulunci, da ma a bankunan da suke ta'amuli da riba dukansu bashi ne a mahangar ilimin Fiƙihu, inda hannun mai amsarsu hannu ne na lamuni, wajibi ne ya bayar da su a lokacin da aka buƙata. Kasancewar banki wuri ne da yake cike maƙil da dukiya ba zai yi tasiri ya sauya hukuncin kasancewar haka a matsayin bashi ba.

Na biyu: Lallai ajiye a banki ta kasu gida biyu ne daidai da irin yanda bankin yake mu'amalarsa.

a. Ajiyar da ke sanya mata fa'ida, ko ƙari irin yanda ake yi a bankunan da suke ta'amuli da riba, wannan kam bashi da ruwa ne wanda shari'a ta haramta, shin

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 65/667).

wannan ajiyar tana cikin nau'in ajiye - ajiyen da za a iya nemansu ne a kowane lokaci (Current account), ko kuwa ajiyar da ake yi zuwa wani lokaci, ko kuwa ajiyar da ake yi zuwa lokacin da da ba a sanar ba, amma dole ne kafin lokacin buƙatar amsa a sanar da cewa ga lokacin da ake buƙata, ko kuma asusun rahusa

b. Aiye – ajiyen da ake bai wa bankunan da a aikace suke bin hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci, ta hanyar zuba jari akan sharaɗin samun wani kaso daga cikin ribar da aka samu, inda za a bayar da kason ne ga uwar kuɗi, inda ake gudanar da hukunce- hukuncen mudaraba da yake cikin Fiƙihun Musulunci, wanda a cikinsu akwai rashin ɗaura lamuni akan mai gudanar da mudaraba (banki) idan uwar kuɗi ya salwanta.

Na uku: Lallai lamuni a ajiye- ajiyen da za a iya nemansu a kowane lokaci (Current accounts) yana kan waɗanda suka amshi bashin ne (wato bankuna) matuƙar da su ne kawai suke amfana da ribar da ake samu a cikin wannan kasuwanci da ake yi da su, masu ajiyar ba za su shiga cikin lamuni ta yanda za a ce a raba asara tare da su idan kuɗin da suka ajiye a bankunan sun salwanta ba, saboda ba su cikin waɗanda suka amshi bashin, balle har su zama cikin waɗanda suka amfana da ribar da aka samu.

Na huɗu: Lallai bayar da jinginar ajiye- ajiye abu ne da ya halatta, sawa'un suna cikin ajiye- ajiyen da za a iya nemansu a kowane lokaci (Current accounts), ko kuma ajiye- ajiyen kasuwanci, ba zai yiwu a gabatar da su a matsayin jingina ba, sai an bi matakan da za su iya hana mai su yin tasarrufi da su tsawon lokacin da aka jinginar da su. Idan bankin da aka buɗe asusun ne ya jingina, to dole ne ya sauya asusunsu zuwa asusun kasuwanci, ta yanda za su sauya daga yiwuwar lamuni idan bashi ne, zuwa mudaraba, inda mai asusun zai zama yana da daman samun riba da ake samu, domin a kauce wa yiwuwar

amfanar wanda aka ba shi jingina da alhairin da aka samu sakamakon abin da aka jinginar.

Na biyar: Ya halatta a killace wani adadi daga cikin asusun ajiya, idan dai har akwai yarjejeniya tsakanin banki da abukin huldarta akan haka.

Na shida: Asali a dukan mu'amala shi ne a gina shi akan amana da gaskiya wajen bayyana dukan abin da yake da jiɓi da wannan ma'amala ta yanda za a cire duk wani ƙumbiya- ƙumbiya da rudani, ya kuma yi daidai da abin yanda yake, a sami daidaito ta mahangar shari'a, wannan asalin ya fi tabbatuwa a bankuna, inda za su bayyana duk wani abu da yake da dangantaka da ire- iren asusun da suke aiki da su cikin amana, ta yanda ba za su cutar da abokan huldarsu ba.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 87 (4/9)(1)
GAME DA KASUWANCI A HANNAYEN ZUBA JARI DA HANNAYEN KASUWANCI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara- shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Kasuwanci a hannayen zuba jari, da hannayen kasuwanci, abin da ya bayyana wa majalisa shi ne lallai wannan maudhu'in -a wasu daga cikin ginshiƙansa- yana ƙunshe da mas'alar sayen hannayen jarin kamfuna, wadanda manyan manufarsu da ayyukansu halal ne, amma kuma suna bayar da bashi, ko suna ajiye dukiyoyinsu da sharaɗi ƙarin kuɗin ruwa (riba), wadannan ba a kawo maganar ƙarshe game da su ba, duk kuwa da cewa an gabatar da tarurrukan ƙara wa juna sani har guda biyu domin bincika al'amarinsa, an kuma fitar da ƙudurin share- fage akansa a tarorn shekara- shekara na bakwai, sannan aka sake fitar da wani ƙudurin a taron da ya biyo bayansa wato na takwas(2) da yake umurtan sakateriyar cibiya da ta nemo wadanda za su ƙara yin bincike akan

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 2/5); da (fitowa ta shida 2/273); da (Fitowa ta bakwai 1/73).

(2) Duba: Ƙuduri mai lamba 63 (1/7); da Ƙuduri mai lamba 77 (8/8).

wannan maudhu'in, ta yanda majalisar za ta sami daman ɗaukan ƙudurin da ya dace a taron sheka- shekara mai zuwa,

Bayan an fara tattaunawa akan wannan maudhu'i, sai aka gano cewa lallai wannan maudhu'in yana buƙatar a ƙara gudanar da bincike mabambanta kuma masu zurfi, saboda aka samar da ƙa'idodjin da suke da jiɓi da irin wannan nau'I na kamfuna da ya fi yawan faruwa a ƙasashen Musulmai da ma ƙasashen da ban a Musulmai ba, saboda haka an ɗauki ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Jinkirta duba wannan maudhu'i, har zuwa a ƙara gabatar da bincike da nazari akan duk wani abu da ya keɓance shi a sassan ainihin yanda yake, da kuma hukuncinsa a Shari'a; domin majalisa ta sami daman fitar da ƙudurin da ya dace akansa, daidai da wasicin taron shekara- shekara na takwas.

Na biyu: Amfana da abubuwan da bincike guda uku suka ƙunsa game da asusun, da tsarin kasuwanci, saboda a samar da dokokin da ƙuduri mai lamba 30 (5/4)([1]) ya yi wasici da a yi.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Duba: Ƙuduri mai lamba 30 (5/4).

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 88 (5/9)(1)
GAME DA KWANGILA TANDA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Kwangila Tanda

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, ƙarsƙashin tsarin da cibiyar take na wajibcin gudanar da bincike masu dama akan kowane maudhu'I saboda a san dukkan sassansa, a kuma isa zuwa ga dukan fuskokinsa a ilimin Fiḳihu, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Jinkirta fitar da ƙuduri game da maudhu'an da aka gudanar da binicke akansu a wannan maudhu'in saboda muhimmancinsa, da kuma wajibci kamala dukan binciken a dukan fuskokinsa, da saninsa dalla- dalla, da kuma sanin dukan fahimta da ra'ayoyi game da shi, da ƙididdige dukan fuskokin da ake gudanar da Kwangila Tanda a aikace, musamman sashen da ya haramta, irinsu takardun kuɗaɗe na riba, da "treasury bounds".

Na biyu: Mambobin cibiya da ƙwararrunsa su gabatar da wa da sakateriya da duk abubuwan da suke da su na

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 1/179).

fangaren sanin wannan abu, da fuskokinsa na shari'a, shin ta fuskar yanda ake gudanar da shi ne, ko kuma ta sigogin da yanda ake ƙulla hulɗa da shi a aikace.

Na uku: Neman malamai da masana su gudanar da bincike akan maudhu'in Kwangila Tanda da zai taimaka wa ƙwararru da masana Fiƙihu wajen fihimtar wannan maudhu'in a ilmance.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 89 (6/9)(1)
GAME DA ABUBUWAN DA SUKA SHAFI TAKARDUN KUƊAƊE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Abuwan da suka shafi takardun kuɗaɗe,

Bayan ta saurari tattaunawa da suka nuna cewa lallai akwai fuskoki masu yawa game da yanda za a magance karyewar darajar kuɗaɗe, wanda yake kaiwa zuwa ga taɓarɓarewar tattalin arziki da durƙushewar wasu daga cikin kuɗaɗe, waɗanda a cikinsu akwai:

a. Ƙudurin da Cibiya ta gabatar a taronta na shekara-shekara karo na biyar(2) ya game dukan waɗannan halaye da yanayin da aka yi togiya akansu, wannan nassin ƙudurin shi ne: "Abin da za a yi la'akari da shi wajen biyan basussukan da suka tabbata da wani nau'i na takardun kuɗi shi ne kwatankwacinsa ba ƙimarsa ba, saboda shi bashi ana biyansa ne da

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 1/351) da fitowa ta uku, 3/1650) da fitowa ta biyar. 3/1609).
(2) Duba: Ƙuduri 42 (4/5)

kwatankwacinsa, bai halatta a haɗa basussukan da suka hau kan zimma da darajar farashi ba, ko mene ne kuwa ya kai zuwa ga bashin".

b. A yi amfani da ƙa'idar nan ta haɗe ƙima da wahalhalu gami da tsadar rayuwa (lura da darajar kudaɗe).

c. A yi amfani da ƙa'idar haɗe kuɗaɗen takarda da zinare (lura da ƙimar waɗannan kuɗaɗen da zinare a lokacin ƙulla hulɗa da cinikayya).

d. A irin wannan yanayi a yi aiki da ƙa'idar wajibcin yin sulhu, bayan a ƙaddara asarar da dukan ɓangarorin suka yi (wanda ya bayar da bashi da wanda aka ba shi bashin).

e. Bambance tsakanin faɗuwar ƙimar kuɗaɗen da ta faru sakamakon buƙata ta kasuwa, da kuma faɗuwar da gwamnati ne da yi da kansa ta hanyar fitar da ƙuduri mai lamba fili ƙarara akan haka, wanda hakan yake sanya a rage darajar takardun kuɗi sakamakon lura da wannan ƙuduri.

f. Bambance tsakanin faɗuwar darajar kuɗaɗe da bin wata siyasa da gwamnatoci ne ya haifar da ita, da kuma faɗuwar da wasu abubuwa na daban ne suka haifar da ita.

g. A yi amfani da ƙa'idar (matsayin buƙatu) a cikin waɗannan halaye da yanayi da aka yi togiyarsu, ta yanda za a yi la'akari da halayen da suka bijiro ba tare da an yi tsammanin bijirowarsu ba.

A ƙarƙashin waɗannan halaye da fuskoki masu bambanci da juna, da dukansu suke buƙatar a gudanar da bincike a kuma tace su da kyau ne, aka tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Sakateriyar Cibiya –tare da taimakekeniya da ɗaya daga cikin cibiyoyin hada- hadar kuɗi na Musulunci- ta shiyar taro na ƙwararru da za a gayyato ƙwararru a fagen tattalin arziki da ƙwararru a fagen ilimin Fiƙihu, a kuma haɗa da wasu daga cikin mambobi da ƙwararrun

wannan cibiya, saboda su duba mafi ingancin hanyar da ta fi dacewa, wadda za a yi ittifaki akanta wajen biyan basussuka da alhaki a cikin waɗannan halaye da yanayi na togiya da aka yi nuni zuwa gare su a sama.

Na biyu: Jadawalin wannan taron ƙara wa juna sanin ya ƙunshi:

a) Nazari akan haƙiƙanin faɗuwar darajar kuɗaɗe, da nau'o'in faɗuwar darajar kuɗaɗe, da dukan fuskokin da suke da dangantaka da ita.

b) Nazari akan tasirin da faɗuwar darajar kuɗaɗe yake yi a tattalin arziki da zamantakewa, da kuma yanda za a magance ta ta fannin ilimin tsimi- da – tanadi.

c) Kawo mafita a ilimin Fiƙihu da suke magance matsalolin faɗuwar darajar kuɗaɗe, irin wanda aka yi nuni akansu a gabatarwa da shimfiɗar wannan ƙudurin.

Na uku: A gabatar da sakamakon da wannan taro na ƙara wa juna sani ya cimma, tare da bincike binciken da aka gabatar da tattaunawar da aka yi ga babban majalisar wannan cibiya a taron shekara- shekara mai kamawa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 90 (7/9)(1)
GAME DA CUTA MAI KARYA GARKUWAR ƊAN ADAM (AIDS) DA HUKUNCE- HUKUNCEN FIƘIHU DA SUKE DA JIƁI DA ITA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Cuta mai karya garkuwar ɗan Adam (Aids) da hukunce- hukuncen Fiƙihu da suke da jiɓi da ita, da ƙuduri mai lamba 82 (13/8),

Bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Killace mara lafiyar:

Ganin cewa bayanai na ilimin likitanci da ake da su a wannan lokacin sun tabbatar da cewa lallai ƙwayoyin cututtukan da suke raunata garkuwar jikin ɗan Adam, cutar karanci ko karya garkuwa (aids) ba sa kama mutum ta hanyar rayuwa a wuri ɗaya, ko shafa, ko numfashi, ko ta hanyar cizon ƙwari, ko yin tarayya wajen cin abinci, ko shan abin sha, ko wurin wanka a kogi ko kwami ɗaya, ko zama a wuri ɗaya, ko ta hanyar yin amfani da kayayyakin

(1) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 3/9)

cin abinci ɗaya da sauran al'amurra na rayuwar yau da kullum da aka saba da su, ana kamuwa da wannan cuta ne kawai ta ɗaya daga cikin hanyoyi masu zuwa:

1. Kowace irin saduwa ta jima'i
2. Ɗaukan gurɓataccen jinni, da abubuwan da suke da jiɓi da haka.
3. Yin amfani da allurer da ta gurɓata, musamman tsakanin masu shaye- shaye, haka ma da reza ko zaɓirar aski.
4. Ɗauka daga uwar da take ɗauke da cutar zuwa ga jaririn da yake cikinta a lokacin ciki, ko lokacin haihuwa.

Idan muka lura da abin da ya gabata, za mu ga cewa lallai killace waɗanda suka kamu da wannan cuta, a raba su da abokan zamansu masu lafiya -idan ba an ji tsoron za su harbi wasu ba- ba wajibi ba ne a shari'ance, za a yi mu'amala da marasa lafiyan ne daidai da tabbatattun matakan da ilimin likitanci ya samar.

Na biyu: Yaɗa cutar da gangan:

Yaɗa cutar karya ko raunata garkuwar jikin ɗan Adam da gangan zuwa ga lafiyayyen da ba ya ɗauke da wannan cutar haramun ne ta kowace fuska, hasali ma yana cikin manyan zunubai da laifuffuka, bayan uƙuba da hukunci na duniya da ya zama wajibi a ɗauka, inda hukuncin yake sham bambanci daidai da girman laifi da kuma tasirin da ya bari a cikin rayuwar zamantakewar al'umma.

Idan wanda ya yi hakan da gangan ya yi hakan ne da mummunar manufar na cutar da al'umma, to lallai wannan abu da ya aikata yana cikin babi "Haraba da yaɗa ɓarna a bayan ƙasa", saboda haka dole ne a yi masa ɗaya daga cikin hukunce- hukuncen da ayar Alƙur'ani mai girma ta bayyana game da masu yaƙar Allah da manzonsa da suke yaɗa ɓarna a bayan ƙasa, Allah mai girma yana cewa: **(Shi kawai uƙubar waɗanda suke yaƙar Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa Ălihi wa sallam) idan suka yi wa tsarin shugabanci da**

hukunce-hukuncen shari'a tawaye, suka kuma cigaba da yin ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar tare hanya da yin fashi da makami, ko ƙwace dukiyoyin mutane: shi ne a kashe su idan sun kashe, a kuma tsire su idan suka yi kisa, suka kuma ƙwace dukiya, a kuma yanke hannayensu da ƙafafuwansu amma a saɓa tsakani([1]) idan sun tare hanya, suka kuma ƙwaci dukiya amma ba su yi kisa ba, a kuma kore su daga garin zuwa wani garin na daban, a kuma tsare su a gidan fursuna idan tsoratar da al'umma suka yi kawai. Wannan uƙubar ƙasƙanci ne da wulaƙanci a gare su a nan rayuwar duniya, a lahira kuma suna da azaba mai girma wadda ita ce azabar wuta) [al- Ma'ida: 33].

Idan kuma manufarsa ta yaɗa wannan cutar ita ce ya harbi wani mutum shi kaɗai, kuma ya yi nasarar yin haka, amma wanda aka sanya masa cutar bai mutu ba, za a yi masa hukunci ne na ta'aziri da ya dace da shi, idan kuma ya kais hi ga wanda aka sanya wa cutar ya rasu, to shi ma mutumin sai ya fuskanci hukuncin laifin kisan kai.

Amma idan manufarsa ita ce ya cutar da wani mutum guda ɗaya saboda ƙiyayyar da yake yi masa, amma bai kai ga yin nasarar sanya masa cutar ba, to a nan hukuncin ta'azirin da ya dace ne ya wajaba a yi masa.

Na uku: Zubar da cikin uwar da ta kamu da cutar karya garkuwar ɗan Adam ba ya kasancewa a mafi yawan lokaci sai idan cikin ya girma –ma'ana bayan an hura wa jaririn rai-, ko kuma a lokacin haihuwa, shi kuwa a shari'a bai halatta a zubar da ciki ba.

Na huɗu: Uwar da ta kamu da cutar karya garkuwar jikin ɗan Adam ta raini jaririnta mai lafiya, ta shayar da shi:

Ganin cewa bayanan ilimin likitanci da ake da su a yanzu sun bayyana cewa lallai babu wani tabbataccen hatsari na cewa uwar da ta kamu da cutar karya garkuwar jikin ɗan Adam za ta iya harbar ɗanta mai lafiya da take

([1]) Ma'ana a yanke hannun dama da ƙafar hagu, ko hannun hagu da ƙafar dama.

shayarwa, wanda al'amarinta daidai yake da al'amarin cakuɗeɗeniya nay au da kullum, to kuwa lallai a shari'a babu abin da zai hana ta rainonsa da shayar da shi, matuƙar ba an sami rahoto na musamman ne daga wurin masa aikin likitanci ba.

Na biyar: Haƙƙin lafiyayye cikin ma'aurata biyu na ya nemi a raba auren da yake tsakaninsa da abokin zamansa da ya kamu da cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam (aids):

Matar aure tana da haƙƙin neman a raba aurenta da mijinta da ya kamu da cuta mai karya garkuwar jikin ɗan Adam (aids), ganin cewa cutar tana yaɗuwa ta hanyar saduwar alaƙa ta aure.

Na shida: Daukan cutar karya garkuwar jikin ɗan Adam (aids) a matsayin cutar mutuwa, idan har cukan alamunsa suka bayyana, inda har suka kai mara lafiyan zuwa ga gaza aiwatar da rayuwarsa na yau da kullum, a hakan kuma mutuwa ta riske shi.

An bayar da wasici da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Jinkirta batun haƙƙin saduwa ta aure a lokacin da aka kamu da cutar aids, har zuwa lokacin da za a kammala bincike akansa.

Na biyu: Wajibi ce a cigaba da tabbatar da cewa lallai babu wani Alhaji da yake ɗauke da kowace irin cutar da ake iya yaɗa su a lokacin aikin Hajji, musamman cutar karya garkuwar ɗan Adam aids.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 91 (8/9)([1])
GAME DA ƘA'IDAR SHIGA- TSAKANI (AL-TAHKIM) A FIƘIHUN MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Ƙa'idar shiga - tsakani (Al- Tahkim) a Fiƙihun Musulunci

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, ta fitar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Shiga- tsakani (al- Tahkim) yarjejeniya ne tsakanin ɓangarorin da suke rikici da juna akan wani ayyanannen abu, akan naɗa wanda zai yi shari'a da hukuncin da zai warware rikicin da yake a tsakaninsu, ta hanyar fitar da hukuncin da dole ne dukansu su yi na'am da shi, ana kuma yin aiki da shari'ar Musulunci.

Wannan ya halatta a shari'a, shin tsakanin ɗaidaikun mutane ne, ko kuma a fagen rikici tsakanin ƙasa da ƙasa.

Na biyu: Shari'ar shiga- tsakani (al- Tahkim) ba ta zama tilas ga kowa cikin ɓangarorin guda biyu, ko ga shi mai yin shari'ar, saboda haka ya halatta kowanne daga cikinsu ya

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 4/5)

janye ya fasa, matuƙar ba a fara gudanar da shari'ar ta shiga tsakani a aikace ba, haka ma ya halatta mai shari'ar ya fita daga cikin al'amarin –bayan ya amshi shiga ciki a farko- matuƙar bai kai ga fitar da hukuncin ƙarshe ba, bai kuma halatta ya kawo wani ya kwafe makwafinsa ba sai da amincewar ɓangarorin rikicin dukansu, saboda tun farko da shi suka yarda.

Na uku: Bai halatta a gudanar da shari'ar shiga- tsakani akan duk wani abu wanda ba haƙƙi ne na bayi ba kaman haddi, haka ma bai halatta a cikin abin da hukuncinsa zai zarce ya shafi wani mutum na daban da ba shi cikin waɗanda suke nemi a shiga tsakaninsu, shin ta hanyar tabbatar da hukunci ne, ko korewa, Kaman Li'ani, saboda hukuncinsa yana rataye da haƙƙin yaron, haka ma bai halatta a cikin mas'alolin da aka keɓance su da ɓangaren shari'a ne kawai yake da haƙƙin duba al'amarinsu, idan har aka kai ga yanke hukunci na shiga – tsakani a cikin abin da bai halatta a yi hukuncin shiga- tsakani akansa ba, to hukuncin ya ɓaci, ba za a zartar da shi ba.

Na huɗu: A asali dole ne mai shiga- tsakani ya zama ya cika sharuɗɗan da aka gindaya wa alƙali.

Na biyar: A asali ana zartar da hukuncin da mai shiga-tsakani ya yi ne cikin so da biyayya, amma idan ɗaya daga cikin waɗanda suke rikicin ya ƙi zartar da hukuncin, sai a gabatar da al'amarin ga kotu domin a zartar da shi, kotu ba ta da hurumin warwaren shari'ar shiga- tsakani, matuƙar ba hukuncin yana ɗauke da zalunci ƙarara ba ne, ko kuma ya zama ya saɓa da hukuncin shari'ar Musulunci.

Na shida: Idan babu kotunan ƙasa da ƙasa na Musulunci, ya halatta ƙasashe da ƙungiyoyin Musulmai su shigar da ƙarar neman shiga- tsakani a gaban kotunan da ba na Musulunci ba, saboda a cinma abin da yake ja'izi ne a shari'a.

An bayar da wasiya mai zuwa:

Kira zuwa ga dukan ƙasashen da suke mamba ne a ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai na su cigaba

su kammala ɗaukan matakan da suka zama dole wajen kafa kotun Musulunci na duniya, su kuma ba ta duk wata dama da za ta gudanar da ayyukanta da suke rubuce a tsarin da ya kafa ta.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 92 (9/9)([1])
GAME DA TOSHE KAFA (SADDUZ – ZARI'A)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na tara a Abu Dhabi (Haɗaɗɗiyar daular Larabawa), wanda ya gudana daga ranar 1 zuwa 6 ga watan Zul Ƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 1 zuwa 6 ga watan Afrilu, 1995,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Toshe- kafa (Sadduz - zari'a)

Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana akansa, ta fitar da ƙuduri mai zuwa:

1. Toshe- kafa (Sadduz –zari'a) ɗaya ne daga cikin jingogin shari'ar Musulunci, ma'anarsa ita ce: Hana abubuwan da suka halatta, waɗanda ake amfani da su zuwa ga aikata ɓarna, ko abubuwan da aka haramta.
2. Toshe – kafa (Sadduz – zari'a) bai taƙaita kawai a abubuwan da suke da rikitarwa, ko ake rufe masu ƙofa kwata gudun kada ɓarna ta shigo ba, a'a ya haɗa har da duk wani abu da za a iya bi ta hanyarsa a aikata abin da aka haramta.
3. Toshe- kafa (sadduz – zari'a) yana nufin hana duk wasu 'yan dubarbaru da ake amfani da su wajen aikata abubuwan da aka haramta, ko lalata wani abu

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta tara, 3/5)

da shari'a ta nemi a aikata, kawai dai dabara (al-Hila) ta sha bamban da kafa (Zari'a) ne ta wajen shi nafarko da nufi ake yinsa, na biyun kuma babu sharaɗin nufi.

4. Kafafe sun kasu kashi- kashi:

Na farko: Kowa ya yarda da a hana su: Su ne waɗanda ayoyin Alƙur'ani mai girma da Sunnar Annabi mai daraja suka bayyana, ko waɗanda take, ko a mafi yawan lokuta suke kai wa zuwa ga aikata ɓarna, shin hanyar da ake bin halal ce, ko mandubi, ko wajibi. A cikin irin wannan nau'in akwai kasuwanci ko yarjejeniyar da tun farkonsu suke nuna manufar yinsu shi ne aikata abin da aka haramta, domin an bayyana a cikin yarjejeniyar a rubuce.

Na biyu: Kowa ya yarda a buɗe kafafen: Su ne waɗanda maslahar da suke cikinsu sun rinjayi ɓarnar da take ciki.

Na uku: Waɗanda ake da saɓani akansu: Su ne ayyukan da a zahirinsu babu komai sai inganci da nagarta, amma akwai tuhumar cewa za a yi amfani da su a ɓoye wajen aikata abubuwan da aka haramta, ganin irin yanda ake yawan yin hakan.

5. Ƙai'dar halatta kafa (Zari'a) ita ce: Ya zamana ba kasafai ake kai wa zuwa ga aikata ɓarna da ita ba, ko kuma ya zama maslahar da take cikin aikatawar ta rinjayi ɓarnar da take ciki.

Ƙa'idar toshe kafa (Zari'a): Ya zamana take take dai wa zuwa ga aikata ɓarna, kuma babu makawa akan haka, ko kuma a mafi yawan lokuta, ko kuma ya zama ɓarnar da take cikin aikatawar ta rinjayi maslahar da ake tsummani.

Allah ne mafi sani;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA JIDDA (SAUDIYYA) 23 - 28 GA WATAN SAFAR, 1418 H 28 GA WATAN YUNI- 3 GA WATAN YULI, 1997

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 93 (1/10)([1])
GAME DA MAGUNGUNAN DA SUKE KARYA AZUMI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na goma a Jidda (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 23 zuwa 28 ga watan Safar, 1418 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 28 ga watan Yuni zuwa 3 ga watan Yuli, 1997,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Magungunan da suke karya azumi, da kuma bincike- bincike da nazarce- nazarce da bayanan bayan taron ƙara wa juna sani na Fiḳihun ilimin Likitanci karo na tara, wanda ƙungiyar Musulunci ta ilmomin likitanci ta shirya tare da taimakekeniyar wannan cibiyar da wasu ƙungiyoyin a garin Casablanca na ƙasar Marocco a ranakun 9 – 12 ga watan Safar, 1418 H, da suka yi daidai da ranakun 14 – 17 ga watan Yuni, 1997, ta kuma saurari tattaunawar da ta gudana akan wannan maudhu'I, tare da masana Fiḳihu da likitoci, ta kuma duba hujjoji da dalilai daga Alƙur'ani da Hadisi, da maganganun malaman Fiḳihu, an tabbatar da ƙudurori masu zuwa:

Na farko: Abubuwa masu zuwa ba sa cikin abubuwan da suke karya azumi:

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma, 2/7)

1) Ɗiga magani a ido, ko ɗiga magani a kunne, ko wanke kunne, ko ɗiga magani a hanci, ko abin shaƙa na hanci (nasal spray), idan ba su zarce sun shiga maƙogwaro ba.
2) Ƙwayoyin magungunan da ake sanya su a ƙarƙashin harshe domin maganin ciwon zuciya (heart attack) da sauransu, idan ba su zarce sun shiga maƙogwaro ba.
3) Magungunan da ake shigar da su ta gaba, ko ake wanke gaba da su, ko gwaji da binciken da ake tura na'urar yinsa ta gaba , ko ɗan yatsa da ake sanyawa domin yin bincike na likitanci.
4) Shigar da na'urar bincike ta gaba zuwa mahaifa, ko sanya na'urar hana ɗaukan ciki (IUD) cikin mahaifa.
5) Na'urar da ake shigarwa da mafitsarar namiji ko mace, na wani bututu na musamman, ko na'urar bincike, ko sinadarin da yake taimakawa wajen ɗauko hoto, ko magani, ko shigar da wani sinadari domin wanke mara.
6) Yin wushirya, ko cire turamen haƙora, ko tsaftace da wanke haƙora, ko asuwaki da buroshin goge haƙori, idan ba su zarce sun shiga maƙogwaro ba.
7) Kurkure baki da ruwa, ko da magani, da iskan shaƙa ta magani da ake sanya wa a baki, idan ba su zarce sun shiga maƙogwaro ba.
8) Allurar magani da ake yi a fata, ko a damtse, ko a jijiya, banda magungunan ruwa da alluran da suke a matsayin abinci.
9) Iskan oksijin.
10) Allura ko iskar gas da suke ɗauke zafi da raɗaɗi (anesthetic gases), matuƙar ba a yi wa mara lafiyan ƙarin ruwa da yake a matsayin abinci ba.
11) Na'urar da ake shigar da shi a jiki ta fata domin ya zuƙe kitse, da mayukan shafawa na magani, ko abubuwan da ake mannawa a fata da suke ɗauke da sinadaran magani ko na kimiyya.

12) Shigar da bututu da ido bai iya gani a cikin jijiyoyi domin ɗaukan hoto, ko maganin jijiyoyin da suke a zuciya, ko waninta na cikin gaɓoɓi.

13) Shigar da na'urar bincike da fatar ciki domin gudanar da bincike akan hanji, ko yi masu tiyata.

14) Daukan samfuri daga hanta, ko wanin hanta a cikin gaɓoɓi, matuƙar yin hakan ba ya tare da ƙarin ruwan da yake a matsayin abinci.

15) Tura na'urar bincike cikin tunbi, idan ba shi tare da ƙarin ruwan da yake a matsayin abinci, ko wasu sinadarai na daban.

16) Shigar da kowane irin na'ura, ko magani zuwa ga kwanya, ko ɓargo (Bone marrow).

17) Yin amai /haraswa ba da gangan ba.

Na biyu: Ya kamata likita Musulmi ya bai wa mara lafiya shawara da nasiha na jinkirta duk wani abu da jinkirta shi ɗin ba zai cutar ba zuwa bayan buɗa baki, cikin surorin magungunan da suka gabata.

Na uku: Jinkirta fitar da ƙuduri akan abubuwa masu zuwa, saboda akwai buƙatar a ƙara gabatar da bincike da nazari akan tasirinsu a azumi, tare da mayar da hankula zuwa ga waɗanda hukuncinsu suka zo a cikin Hadisai da maganganun sahabbai:

a. Na'urar da take isar da magani zuwa kunhu (inhaler), da shaƙar abin da ta ƙunsa na iska.

b. Ɓallu- ɓallu da ƙaho

c. Ɗaukan samfurin jinni domin gudanar da bincike, ko ɗaukan jinni daga jikin wanda zai bai wa waninsa, ko sanya jinin da aka ɗauko a jikin mutum.

d. Allurer da ake yi wa waɗanda suke da matsalar ƙoda, allura ce da ake yi a fatar ciki ta ƙarshe (peritoneum), ko a ƙodar da aka sana'anta.

e. Allura ko maganin da ake shigar da shi da dubura, ko na'urar ɗauko hoto ko isar da magani, ko ɗan yatsa da ake shigarwa domin bincike na likitanci.

f. Yin allura mai kashe zafi da raɗaɗi nag aba ɗaya ga wanda za a yi masa aikin tiyata, idan mara lafiyan ya kwana da niyyar azumi tun dare, ba kuma a yi masa kowane irin ƙarin ruwa da yake a matsayin abinci ba.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 94 (2/10)([1])
GAME DA KWAIKWAYON HALITTA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na goma a Jidda (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 23 zuwa 28 ga watan Safar, 1418 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 28 ga watan Yuni zuwa 3 ga watan Yuli, 1997,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: kwaikwayon halitta, da kuma bincike- bincike da nazarce- nazarce da bayanan bayan taron ƙara wa juna sani na Fiḳihun ilimin Likitanci karo na tara, wanda ƙungiyar Musulunci ta ilmomin likitanci ta shirya tare da taimakekeniyar wannan cibiyar da wasu ƙungiyoyin a garin Casablanca na ƙasar Marocco a ranakun 9 – 12 ga watan Safar, 1418 H, da suka yi daidai da ranakun 14 – 17 ga watan Yuni, 1997, ta kuma saurari tattaunawar da ta gudana akan wannan maudhu'i, tare da masana Fiḳihu da likitoci, an cimma matsaya mai zuwa:

Gabatarwa:

Lallai Allah ya halicci ɗan Adam akan mafi kyawon tsari, ya kuma girmama da babban matsayi, Allah Mabuwayin Sarki ya ce: **(Lallai mun karrama ɗan Adam da kyakkyawar halitta da kuma furuci da zaɓan abubuwa, mun kuma ba shi karama da izza idan suka yi**

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma, 2/7)

biyayya, mun kuma ba shi dabbobin da zai hau a tudu da tsandauri, a kogi kuma mun ɗaura shi akan jiragen ruwa, mun kuma azurta su da abubuwa masu daɗi, mun kuma yi matuƙar fifita su da hankali da tunani akan halittu masu yawa da muka halitta) [al- Isra'i: 70], ya ƙawata shi da hankali, ya kuma ɗaukaka shi ta hanyar ba shi takalifi, ya kuma sanya ya zama halifansa a bayan ƙasa, ya umurce shi da ya raya doron ƙasa, ya kuma ɗaukaka shi ta hanyar ɗaukan saƙonsa wanda ya yi daidai da fiɗirarsa, hasali ma hakan shi ne haƙiƙanin fiɗira, saboda Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ka tsayar da mafuskantarka zuwa ga addini da kyau cikin tsarkin fiɗira, domin shi ne fiɗirar da Allah ya halicci mutane akanta, sam babu sauyi a cikin halittar Allah, wannan shi ne daidaitaccen addini..)** [al- Rum: 30], lallai addinin Musulunci ya mayar da hankali matuƙa wajen kiyaye fiɗirar ɗan Adam ta yanda za ta cigaba da zama akan daidai, ta hanyar kiyaye manyan manufofinsa guda biyar: addini, da rai, da hankali, da tsatso, da dukiya, da kiyaye su daga barin duk sauyi da zai ɓata su ko ya lalata su, shin a matsayinsa na sababi ne ko sakamakon sababi, abin da yake nuna haka a fili shi ne Hadisi Ƙudusin da Imamul Ƙurɗabiy ya kawo a cikin littafinsa daga ruwayar alƙali Isma'il cewa: **(Lallai na halicci bayi nag aba ɗayansu akan tsarkin fiɗira, shaiɗanu ne suka zo suka gusar da su ga barin addininsu..** har zuwa inda ya ce: **suka umurce su da su sauya halitta ta)** [Tafsirul Ƙurɗabiy: 5/389].

Lallai Allah ya sanar da ɗan Adam abin da bai sani ba, ya kuma umurce shi da yin bincike da nazari da tunani da tadabburi, inda y aba shi wannan umurni ta ayoyi masu yawa, irinsu: **(Shin ba su ganin cewa…)** [Ɗaha: 89], ya kuma cewa: **(Shi ɗan Adam bai san cewa lallai mu ne muka halicce shi daga ɗigon maniyyi ba..)** [Yasin: 77], da inda ya ce: **(Lallai a cikin wannan akwai ayoyi ga mutanen da suke tunani..)** [ar- Ra'ad: 3], ya kuma cewa**: (Lallai a cikin wannan akwai ayoyi ga mutanen da suke**

da hankali..) [ar- Ra'ad: 4], ya kuma cewa: **(Lallai a cikin wannan akwai tunatarwa ga masu hankali da tunani..)** [az- Zumar: 21], ya kuma cewa: **(Ka yi karatu da sunan Ubangijinka wanda ya yi halitta)** [al- Alaƙ: 1].

Addinin Musulunci bai sanya wani cikas ko tarnaƙi akan 'yan ne yin bincike na ilimi ba, saboda yin haka ƙofa ce ta jirkita sunnar da Allah ya halicci hallitunsa a kai. Sai dai duk da haka addinin Musulunci bai bar ƙofar a buɗe sakaka ba tare da ƙa'idoji ba, bai yarda da a yi duk gwaje-gwajen da aka ga dama a cikin rayuwa ba tare da an bi da rariyar shari'ar Musulunci ba, saboda abubuwan da suka halatta su samu su wuce, ta kuma yi wa waɗanda suka haramta burki, ba ta yarda a zartar da komai saboda kawai za a iya zartar da shi ba, dole ne sai ya zama ilimi ne mai amfani, da zai zama maslaha ne ga bayin Allah, zai kuma tunkuɗe masu ɓarna. Kuma dole ne wannan ilimin ya kiyaye mutuncin ɗan Adam da matsayinsa, da kuma manufar da ta sanya Allah ya halicce shi saboda ita, kada kawai a ɗauke shi a matsayin fage ne kawai na gwaje-gwaje, ba za a yarda ya wuce iyaka a ckin rayuwar ɗaiɗaikun mutane da abubuwan da Allah ya kaɓence su da su ba, ba kuma a yarda shi ilimin ya zama sanadin rusa rayuwar zamantakewa, ko ya mayar da tsarin dangi da iyali da zamunci da aka sanin a tsawon tarihi ƙarƙashin inuwar shari'ar Allah da tsararrun hukunce- hukuncensa su shiga cikin garari suna tangal- tangal ba.

Lallai a cikin abubuwan da suka fito wa mutane sababbi a wannan zamani, kafafen yaɗa labarai na duniya suka yi ta kwarmata su akwai abin da ake fi sani da sunan kwaikwayon halitta, ya kuma zama dole a bayyana hukuncin shari'ar Musulunci game da shi, bayan zaɓaɓɓun ƙwararrun malaman Musulunci a wannan fage sun yi bayanai na dalla- dalla game da shi.

Ma'anar: kwaikwayon halitta:

Kowa ya san cewa lallai sunnar Allah wajen halittar ɗan Adam ita ce haɗuwar maniyyin mutane biyu, da

kowannensu yake ƙunshe da wani adadi na ƙwayayen halitta (chromosomes) da suka kai rabin ƙwayoyin halittar da suke a jikin ɗan Adam. Idan ɗigon maniyyin uba (miji) ya haɗu da ɗigon maniyyin uwa (mata), sai su sauya duka a tare zuwa maniyyin da yake tattare da sinadaran mabambanta, da yake ƙunshe da wata jaka da take ɗauke da dukan sifofin da ake gada, suna kuma da daman ƙara yawaita. Idan har aka dasa su a cikin mahaifar uwa sai su ƙara haɓaka da ya waita, har zuwa su samar da cikakken halitta da ikon Allah. A haka tana cigaba, tana ƙara ruɓanya kanta daga ƙwayoyin halitta biyu da suke daidai da juna, zuwa huɗu, zuwa takwas.. a haka za ta cigaba da ruɓanyuwa har ta kai matakin da daga shi ne za su fara samun bambanci da juna. Idan ɗaya daga cikin waɗannan ƙwayoyin halitta da suka haɗe da juna ya rabe biyu daidai da juna a matakin da yake gabatar bambance kansa, sai a haifi tagwaye biyu masu kama da juna. Lallai an gudanar da haka a aikace ga dabbobi inda aka raba wannan cakuɗaɗɗen maniyyi, aka kuma sami haihuwar tagwaye da suka yi daidai da juna, amma ba a gwada hakan a kan mutum ɗan Adam ba. an ɗauki hakan a matsayin ɗaya ne daga cikin nau'o'in kwaikwayon halitta, saboda yana samar da kwafin halittar a dukan sifofi, an kuma yi wa haka suna da (replication by splitting).

Akwai kuma wata hanyar na samar da kwafin cikakken halitta, a wannan hanya ana ɗauka cikakkiyar jakar da take ɗauke da sifofin gado a matsayin ƙwayar halitta ɗaya daga cikin ƙwayoyin halittar da suke cikin jiki, a sanya ta a cikin maniyyin mace da aka cire ƙwayoyin halittar da suke cikinsa, da haka sai su haɗu da sinadarai mabambanta da suke a cikin jakar da take ɗauke da sifofin da ake gada, a kuma daidai wannan lokacin suna da iko gami da daman ƙara yawaita. Idan aka ɗauka a sanya a cikin mahaifar uwa sai su ƙara haɓaka da bunƙasa da cika, har a kai zuwa ga haifuwar cikakken halitta da ikon Allah. A duk sanda aka ambaci kwaikwayon halitta to wannan nau'in ne yake fara

zuwa, domin shi ne ya faru aka samar da tunkiyar nan mai suna (Dolly), sai dai ita wannan sabuwar halittar ba ta yi kama da ta asali a komai da komai ba ne, domin maniyyin uwa da aka cire ƙwayoyin halittar, zai cigaba da zama tare da wasu daga cikinsu, saboda ba duka aka cire ba, kuma wannan da ya rage ɗin yana da tasirin da yake yi wajen sauya sifofi da aka gada daga ƙwayoyin halittar na jiki, amma har yanzu babu wata sanarwa da ta nuna cewa an gabatar da irin wannan akan ɗan Adam.

Saboda haka, kwaikwayon halitta shi ne: Haifar halitta ɗaya ko sama da ɗaya ta hanyar ɗaukan ƙwayar halitta guda ɗaya daga cikin ƙwayoyin halittar da suke cikin jiki a haɗa shi da maniyyin mace da aka cire masa ƙwayoyin halitta da suke cikinsa, ko kuma ta hanyar raba maniyyin mace da aka yi masa Barbara a matakin da yake kafin rarraba ƙwayoyin da gaɓoɓi.

Abu ne a fili ƙarara cewa irin wannan aikin ba za a kira shi da sunan halitta, ko wani sashe na halitta ba, Allah mai girma da buwaya ya ce: **(Ko kuwa ɓatar tasu ta ɗauke su zuwa ga riya cewa waɗannan gumaka abokan tarayyar Allah ne wajen halitta da gudanar da al'amurra, sai suka sami kamanceceniya a cikin al'amarin halitta, kaman yanda suka saki hanya wajen yin ibada, ya Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ka ce masu: lallai Allah shi kaɗai ne ya halicci duk wani abu samamme, shi kaɗai ne ya kaɗaita da yin halittu, shi kaɗai ne kuma ya cancanci a bauta masa, shi ne muka marinjayi akan komai)** [ar- Ra'ad: 6], Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Shin ba za ku yi duba zuwa ga maniyyin da kuke sakawa a cikin mahaifa ba?!. Shin ku ne kuke ƙaddara shi, da kulawa da shi a matakan da yake wucewa da yake bi, har ya zamo mutum, ko kuwa mu ne muke ƙaddara masa komai nashi?!. Mu ne muka hukunta mutuwa a tsakaninku, muka kuma sanya wa mutuwar taku keɓantacce lokaci, babu yadda za a iya yin rinjaye akanmu… Akan mu sauya maku surorin jikinku da wasu**

surorin, mu farar da ku a wata halitta da surorin da ba ku sani ba!.. Lallai tabbas kun tabbatar da cewa Allah ne ya fare ku a farko, shin ba za ku yi tunanin cewa lallai wanda yake da ikon samar da ku a farko, ikon nasa ya fi bayyana wajen sake samar da ku ba?!..) [al- Waƙi'a: 58 - 62].

Allah mai girma da ɗaukaka ya ce: **(Shin ɗan Adam bai ganin cewa: lallai mun halicce shi ne daga ɗigon maniyyi ba, amma kuma ya koma yana husuma da jayayya na ƙiri- ƙiri. Ya buga mana misali, amma shi ya manta da yanda aka halicce shi, sai ya ce: wane ne zai raya ƙasusuwa bayan sun rududduge? Ka ce masa: wanda ya samar da su a karon farko shi ne zai raya su, lallai shi ɗin yana da cikakkiyar masaniya game da kowace halitta. Shi ne wanda ya sanya maku wuta a cikin koriyar bishiya, sai kuma ga shi kuna kunna wuta da ita. Shin ashe wanda ya halicci sammai da ƙasa ba shi da ikon da zai sake halittar kwatankwacinsu? Lallai yana da cikakken iko akan haka, domin shi ne ainihi mahaliccin halittu, mai kuma cikakkiyar masaniya akan komai. Shi fa al'amarinsa idan ya so wani abu ya faru cewa yake da shi kawai faru, kuma nan take yake faruwa)** [Yasin: 77 -82].

Allah mai girma ya ce: (Lallai mun halicci ɗan Adam ne daga wani dangi na tsurɓaya. Sannan muka sanya ya zama maniyyi a wani tabbataccen mazauni. Sannan muka mayar da maniyyin ya koma gudan jinni, muka kuma mayar da gudan jinin ya koma gudan tsoka, daga kuma gudan tsokar ce muka mayar da shi ƙashi, sai muka suturta ƙashi na nama, sannan muka farar da shi ya zama wata halitta ta daban, kai lallai tabarakallah wanda shi ne fiyayyen dukan masu halitta) [al- Mu'uminun: 12 – 14].

Bayan binciken da suka gabata, da tattaunawar da aka yi, da kuma ƙa'idojin shari'ar Musulunci da aka gabatar a gaban majalisar wannan cibiya, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Haramun ne a yi kwaikwayon halitta akan ɗan Adam ta dukan hanyoyi biyun da muka ambata, da ma kowace irin hanya da za ta kai zuwa ga yawaitar ɗan Adam.

Na biyu: Idan an saɓa wa hukuncin shari'a da aka bayyana a sakin layin (Na farko), to abin da hakan ya haifar na sakamako za a gabatar da shi saboda a bayyana hukuncinsa a shari'ar Musulunci.

Na uku: An haramta duk wani yanayi da wani ɓangare na uku zai shigo a cikin dangantakar aure, shin ta hanyar bayar da mahaifa ne, ko maniyyin mace, ko kuma maniyyin namiji, ko ƙwayar halittar jiki domin a yi kwaikwayon halitta.

Na huɗu: Shari'a ta halatta yin amfani da kimiyyar kwaikwayon halitta da ta tsarin gado a fagen ƙwayoyin cuta da sauran ƙananan halittu da tsirrai da dabbobi shi ma ƙarƙashin dokoki da ƙa'idojin Shari'a, daidai da yanda zai tabbatar da maslaha, ya kuma tunkuɗe ɓarna.

Na biyar: Kira zuwa ga ƙasashen Musulmai da su samar da dokoki gami da ƙa'idoji da tsare- tsaren da suka kamata wajen kulle duk wata ƙofa ta kai- tsaye ko ta kaikaice da wasu ƙungiyoyi na cikin gida da na ƙasashen, ko cibiyoyin bincike da ƙwararru daga ƙasashen wajen za su yi amfani da su wajen ɗaukan ƙasashen Musulmai su zama filayen gwaje- gwajen kwaikwayon halitta, ko kuma yaɗa shi da tallata shi.

Na shida: Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya da ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci su haɗa kais u cigaba da bibiyan maudhu'in kwaikwayon halitta da sababbin cigaba na ilimi da aka samu akansa, da kuma tabbatar da ma'anonin kalmominsa na musamman, da shirya tarurrukan ƙara wa juna sani da tarurruka da suka kamata domin bayyana hukunce- hukuncen Shari'a da suke da jiɓi da shi.

Na bakwai: Kira zuwa ga kafa kwamitoci na ƙwararru tare da malaman shari'ar Musulunci saboda su sanya

ƙa'idoji na kyawawan ɗabi'u a fagen bincike da nazari ilmomin likitanci, saboda ƙasashen Musulmai su mayar da su a matsayin doka.

Na takwas: Kira zuwa ga a kafa da kuma ƙarfafar cibiyoyi da ƙungiyoyi na ilimi da suke gudanar da bincike a fagen ilmomin likitanci, da tsarin gado a fagagen da ba na kwaikwayon halitta ba, daidai da ƙa'idoji da dokokin shari'a, gudun kada ƙasashen Musulmai su zama kaya da suka rataya akan waninsu, ko su zama mabiya 'yan amshin shata a wannan fagen.

Na tara: Binciko tushe, gami da da asalin yanda za a yi ta'amuli da sababbin abubuwan da ilimi yake zuwa da su daidai da karantarwar Musulunci, da kuma kira zuwa ga kafafen yaɗa labarai kan su yi aiki da irin yanda imani yake kallonsu wajen ta'amuli da waɗannan mas'aloli, da kuma nesanta yin amfani da su ta hanyar da za su saɓa wa addinin Musulunci, da kuma wayar da kan al'umma saboda su tabbata akan wannan mataki da matsayar; suna masu amsa kiran Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **(Idan waɗannan munafukai suka ga wani abu na tsaro, ko na tsoro da yake da jiɓi da ƙarfin Musulmai, ko raunin su, sai su yayata shi da nufin ruɗar da Musulmai, ko jefa tsoro da razani a cikin zukatansu, ko saboda su isar da labarin su zuwa ga maƙiyan su, da a ce waɗannan munafukai sun mayar da duk wani al'amari na tsaro da tsoro zuwa ga Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa aliHí wa sallam) da shugabanni da manyan saahabbai da dakarun yaƙi, su kuma nemi sanin haƙiƙanin al'amari ta wurin su, da waɗannan da suke ƙoƙarin neman labarai da yaɗa su sun san gaskiya a wurin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa aliHí wa sallam) da shugabanni. Lallai ba domin falalar da Allah ya yi maku na tabbatar da zukatanku akan imani, da daƙile fitina, da kuma rahamarsa na damƙa maku dukan dalilan da za su sanya ku sami nasara ba, da mafi yawanku sun faɗa cikin tarkon shaiɗan, babu waɗanda za su tsira daga**

halakarwarsa sai mutane kaɗan daga cikinku) [an- Nisa'i: 83].

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 95 (3/10)([1])
GAME DA YANKA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na goma a Jidda (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 23 zuwa 28 ga watan Safar, 1418 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 28 ga watan Yuni zuwa 3 ga watan Yuli, 1997,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Yanka, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akan wannan maudhu'i tare da malamai masana Fiƙihu da likitoci da ƙwararru a fannin abinci, ta kuma halarto da bayanin cewa lallai yanka tana cikin al'amurran da suke ƙarƙashin shari'ar Musulunci da suka tabbata ta hanyar Alƙur'ani da Hadisi, kuma lura da hukunce- hukuncenta biyayya ne ga addinin Musulunci, alama ce da take bambance Musulmi da waninsa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya yi sallar da muke yi, ya kuma fuskanci alƙiblarmu, ya kuma ci yankarmu, to wannan shi ne Musulmin da yake akwai zimmar Allah da Manzonsa a tare da shi)**, an tabbatar da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Yankar da Shari'a ta yarda da ita tana tabbatuwa ne ta ɗaya daga cikin hanyoyi masu zuwa:

1. Yanka, tana tabbata ne da zaran an yanke maƙogwaro, da magudanar abinci, da jijiyoyin

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma, 1/53)

jannaye guda biyu. Wannan ita ce ta fi falala a shari'ar Musulunci wajen yanka tumaki da shanu da tsuntsaye da makamantansu, amma sauran hanyoyin ma sun halatta.

2. Suka, tana tabbata ne ta hanyar suka a hujin wuya da yake a ƙasar wuya. Wannan ita ce ta fi falala a Shari'ar Musulunci wajen yanka raƙumi da ire-irensa, amma sauran hanyoyin ma sun halatta.
3. Raunatawa, tana tabbata ne da yi wa dabbar da aka gaza yin ta'amuli da ita raui a wani sashe daga cikin jikinsa, shin dabbar ta daji ce mai wawusan mutane da aka halatta a yi farautarta, ko kuwa dabbar gida ce da ta zama abin tsoro, duk ɗaya ne. Idan mafarauci ya riski dabbar da ranta wajibi ne ya yanka ta, ko ya soke ta.

Na biyu: Kafin yanka ta zama ingantacciya sharaɗi ne a tabbatar da abubuwa masu zuwa:

1. Mai yankan ya zama ya balaga, ko zai iya mayyaze abubuwa, Musulmi ko Ahlul kitabi (Bayahude ko Kirista), ba za a ci yankar masu bautar gumaka, da waɗanda ba su da addini, da mulhidai, da masu bautar wuta (Majusawa), da waɗanda suka yi ridda, da sauran kafiran da ba Ahlul kitabi ba.
2. Yankar ta kasance da kakkaifar abin yanka da za ta yanka nan take da kaifinta, shin abin da za a yi yankar da shi ƙarfe ne, ko wani abu da ake zubar da jinni da shi, banda dai haƙori ko farce.

Dabbar da ta mutu ta hanyar shaƙa, ko maƙura, shin ita ce ta shaƙe kanta, ko kuma shaƙe ta aka yi, da wadda aka yi ta dukanta (da dutse ko sanda da makamantansu) har sai da ta mutu, da wadda ta faɗo daga sama ta mutu, ko ta faɗa wani rami, da wadda ta mutu sakamakon sukar da wata dabbar ta yi mata da ƙaho, da wadda ta mutu sakamakon wata dabbar da tafi ƙarfinta ta far mata, irinsu zakanya ko manyan tsuntsaye masu akaifa da ba a koya masu yanda za su yi farauta ba. Amma duk dabbar da

kuka riske ta da ranta –cikin waɗanda aka halatta maku cin namansu- kuka yanka su, to wannan yankar ta halatta maku su.

3. Mai yankar ya ambaci sunan Allah Maɗaukakin Sarki a lokacin yankar. Yin amfani da abin ɗaukan magana a ɗauki Kalmar Bisimillah a kunna lokacin yanka bai wadatar ba, amma za a iya cin yankar wanda ya manta bai ambaci sunan Allah ba.

Na uku: yanka tana da ladubba da shari'ar Musulunci ta faɗakar akansu, domin a rausasa da tausaya wa dabba kafin a yanka ta, da lokacin yanka ta, da ma bayan an yanka ta.

Kada a wasa abin da za a yi yanka da shi a gaban dabbar da za a yanka, kada kuma a yanka ta a gaban wata dabbar, kada kuma a yi yankar da dakusasshen abin yanka, kada a azabtar da dabbar da za a yanka, kada kuma a yanke wani sashe daga cikin jikinta, ko a feɗe ta, ko a saɓule fatarta, ko a dulmiya ta a cikin ruwan zafi, ko a fiffige mata gashi sai bayan an tabbatar da cewa ranta ya fita.

Na huɗu: Ya kamata dabbar da ake son a yanka ta zama ba ta ɗauke da cutar da za ta iya harbar wasu, ko wadda take kawo sauyi a cikin namanta, ta inda za ta cutar da wanda ya ci, wannan ƙa'ida tana ƙara ƙarfi idan ya zama naman za a kai shi kasuwa ne, ko za a fita da shi ƙasashen ƙetare.

Na biyar:

(a) Yanka a asalin shari'a tana kasancewa ne ba tare da sumar da dabba ba, saboda lura da sharuɗɗa da kuma ladubban yanka a shari'ar shi ne abin da ya fi kyau, domin tausayin dabba, da kuma kyautata wa abin yanka, da rage masa raɗaɗi, za a nemi hukumomin da suke tsaye da al'amurran yanka da su ƙara bincike domin kyautata hanyoyin da ake bi wajen yanka manyan dabbobi, ta yanda za a tabbatar da samuwar wannan asalin a wurin yanka kaman yanda ya kamata.

(b) Tare da la'akari da abin da aka bayyana a (a) na wannan sakin layi, lallai ya halatta a ci dukan dabbobin da aka masu yanka ta shari'a bayan an sumar da su, idan sun cika sharuɗɗan yanka, aka kuma tabbatar da cewa ba su mutu kafin a kai ga yanka su ba, kuma a wannan zamanin namu ƙwararru sun bayyana waɗannan sharuɗɗan kaman haka:

1. A sanya wayoyi biyu na wutar lantarkin a ƙasusuwan kumatu, ko a wajen ƙarshen kai ta baya.

2. Magwajin wutar lantarkin ya kasance tsakanin (100 – 400).

3. Ƙarfin wutar lantarkin ya zama tsakanin (0.75 zuwa 1.0) idan tumaki za a yanka, da tsakanin (2 zuwa 2.5) idan shanu za a yanka.

4. Tsawon lokacin sanya wayoyin lantarkin ya kasance tsakanin sakon 3 zuwa 6.

(c) Bai halatta a sumar da dabbar da ake son a yanka ta hanyar amfani da bindiga mai allurai, koda guduma ko maƙwarƙwasa ba, ko ta hanyar hura masa wani abu Kaman yanda mutanen Ingila suke yi.

(d) Bai halatta a sumar da kaji da wutar lantarki ba, domin tajriba ta tabbatar da cewa da yawansu sukan mutu kafin a kai zuwa ga yanka su.

(e) Ba a haramta dabbobin da aka yanka su bayan an sumar da su ta hanyar haɗa (Carbon Dioxide) da iska, ko iskar (Oxygen), ko ta hanyar amfani da bindiga mai shayayyen baki, wanda hakan bai kai wa zuwa ga mutuwa kafin a yanka su.

Na shida: Wajibi ne ga Musulman da suke rayuwa a ƙasashen da ban a Musulmai ba su bi dukan hanyoyin da doka ta amince da su wajen neman izinin samar wa kawunansu da mayanka (kwata/ abatuwa) da za ta yi daidai da tsarin Musulunci ba tare da an sumar da dabba ba.

Na bakwai: Ga Musulmai da suke kai ziya zuwa ƙasashen da ban a Musulmai ba, ko waɗanda suke zaune a ciki, za su iya cin yankar Ahlul kitabi idan sun yanka abin da yake halal ne a Musulunci, bayan sun tabbatar da cewa ba a cakuɗa su da abubuwan da aka haramta ba, sai dai idan sun sami tabbacin cewa ba yanka su ta hanyar da shari'a ta amince ba.

Na takwas: A asali yanka kaji ta kasancewa ne da hannun mai yanka, amma babu laifi idan aka yi amfani da inji wajen yanka kaji, muddin dai an cika sharuɗɗan yanka da Shari'a ta gindaya waɗanda aka ambace su a sakin layi (Na biyu), faɗin sunan Allah sau ɗaya ga tarin kajin da za a yanka a lokaci ɗaya ya isar, idan injin ya yanka su, sai a sake faɗin sunan Allah.

Na tara:

(a) Idan ana sayo naman ne daga ƙasashen da mafi yawan 'ya'yanta Ahlul kitabi ne, suna kuma yanka dabbobinsu ne a mayanka (kwata/ abatuwa) na zamani, suna kuma aiki da sharuɗɗan yanka da shari'a ta amince da su a sakin layi (Na biyu), to ya halatta a ci naman, saboda maganar da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi a inda yake cewa: **(Abincin waɗanda aka ba su littafi ya halatta a gare ku..)** [al-Ma'ida: 5].

(b) Haramun ne a ci naman da aka sayo daga ƙasashen da mafi yawan 'ya'yanta ba Ahlul kitabi ba ne.

(c) Idan an yanka naman da aka sayo daga ƙasashen da aka yi nuni zuwa gare su a (b) na wannan sakin layin yankar da Shari'a ta amince, kuma ƙarƙashin kulawar wata ƙungiya ko jam'iyya ta Musulunci, mai yankan kuma ya zama Musulmi ne, ko Ahlul kitabi, ya halatta a ci.

Cibiya tana yin wasizi da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Gwamnatocin Musulunci su tafi wurin 'yan uwansu gwamnatocin da ban a Musulunci ba, waɗanda Musulmai suke rayuwa a cikinsu, su nemi su samar masu

da hanyoyin da za su rinƙa yin yankar da shari'a ta amince masu da ita ba tare da sumar da dabba ba.

Na biyu: Saboda a kawo ƙarshen matsalolin da suke tattare da sayo nama daga ƙasashen da ban a Musulmai ba, ya kamata a lura da abubuwa masu zuwa:

(a) Aiki tuƙuru wajen haɓaka kiwon dabbobi a ƙasashen Musulmai, saboda a dogara da kai.

(b) Taƙaituwa da ƙasashen Musulmai wajen sayo nama gwargwadon iko.

(c) Sayo dabbobi masu rai a yanka su a ƙasashen Musulmai, saboda a tabbatar da cewa an bi sharuɗɗan yanka da Shari'a ta gindaya.

(d) Neman Ƙungiyar ƙasashen Musulmai ta zaɓi wata jiha ta Musulunci da za ta ɗaura mata alhakin sanya ido akan naman da ake sayowa daga ƙasashen waje, ta hanyar samar da cibiya da za ta yi aiki a wannan fage kai- tsaye, ta yanda zai kasance ba ta da wani aiki sai wannan, da kuma sanya dokoki da tsare-tsare akan sharuɗɗan yanka a Musulunci, su kuma tsara yanda sanya ido da kulawar za su kasance a wannan aikin. Su yi haka tare da taimakon ƙwararru a fannin hukunce- hukuncen shari'a, da kuma ƙwararru a fannin fawa, ya kuma zamana ana sanya karɓaɓɓiyar alama, da za a yi mata rijista ta duniya a hukumar da take lura da yin rijistar alamomin kasuwanci ta duniya.

(e) Yin aiki wajen taƙaita aiyyukan sanya idon ga hukumar da aka yi nuni a (d) na wannan sakin layin, da kuma cigaba da aiki na ganin cewa dukan ƙasashen Musulmai sun amince da ita a matsayin ita ce kawai suka amince da ta sanya ido akan haka.

(f) Zuwa lokacin da za a sami tabbatar da wasicin da aka bayyana a (d) na wannan sakin layin, za a nemi masu sayo nama daga ƙasashen wajen da su bayar da lamunin cewa lallai za su yi aiki da sharuɗɗan yanka da shari'a ta amince da su game da naman da suke

kai wa zuwa ƙasashen Musulmai, gudun kada Musulmai su auka cikin aikata haramun sakamakon rashin kula da naman da ake sayowa daga ƙasashen waje ba tare da sun tabbatar da cewa an bi sharuɗɗan yanka da shari'a ta gindaya ba.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 96 (4/10)([1])
GAME DA KATIN LAMUNI (CREDIT CARD)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na goma a Jidda (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 23 zuwa 28 ga watan Safar, 1418 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 28 ga watan Yuni zuwa 3 ga watan Yuli, 1997,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Katin lamuni (Credit card), ta kuma saurari tattaunawar da masana Fiḳihu da masana tattalin arziki suka gudanar akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

a. Ɗaura wa sakateriya alhakin bincike akan dukan tsare- tsare na sharuɗɗa da yarjejeniyoyin da ake yi akan wannan katin da bankuna suke bayarwa.

b. Kafa kwamitin da zai yi aikin nazari da bincike akan sigogin wannan katin saboda a san ayyukan da yake yi, da kuma bambance- bambancen da yake a cikinsu, da kuma iyakance yanda shari'a ta yi wa katin matsayi, wannan ɗin ya kasance bayan an samar da litattafai na Larabci da na sauran harsuna da suke magana akan nau'o'in wannan katin.

c. Shirya zama na musamman domin tattaunawa akan wannan maudhu'in daidai da shirye- shiryen da suka gabata, da kuma tsara cikakken sakamakon da aka cimma; saboda a gabatar a taron shekara- shekara mai zuwa.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta takwas, 2/571) da (Fitowa ta goma, 2/467)

Cibiyar tana bayar da wasici mai zuwa:

a- Wajibcin sake tsarin kalmomi na musamman a fannin tattalin arziki da suke da dangantaka da Shari'a a cikin abubuwan da suke da jiɓi da mu'amalolin da suka halatta da waɗanda suka haramta, ta yanda za su yi daidai da ma'anoninsu, su kuma bayyana haƙiƙaninsu.

Da fifita waɗanda suke da suna na musamman a shari'a akan waninsu, ta yanda za a tabbatar da lafazinsa da ma'anarsa, musamman waɗanda suke da tasiri na hukuncin shari'a, saboda a kawo gyara a cikin kalmomi na musamman a fannin tattalin arziki, su yi daidai da kalmomi na musamman a fannin Fiƙihu, a kuma fito da su daga litattafan da al'umma ta gada, tare da ma'anoninsu na shari'a.

b- Kira zuwa ga hukumomin da abin ya shaga a ƙasashen Musulmai kan su hana bankuna fitar da katin bayar da lamuni da yake da riba a ciki, saboda a kiyaye al'umma daga faɗawa cikin kwazazzabon riba da aka haramta, da kuma kiyaye tsarin tattalin arzikin ƙasa da kuɗaɗen ɗaiɗaikun mutane.

c- Samar da hukuma ta Musulunci da hada- hadar kuɗi da tattalin arziki, da za a ɗaura mata alhakin bai wa ɗaiɗaikun mutane kariya daga yin amfani da bankuna suke yi da su, da kuma kiyaye masu haƙƙoƙinsu; daidai da hukunce- hukuncen shari'a, da siyasar hada- hadar kuɗi wajen kiyaye tattalin arzikin ƙasa, da samar da tsararrun dokoki da ƙa'idoji domin bai wa al'umma da ɗaiɗaikun mutane kariya daga irin yanda bankuna suke amfani da su, saboda a kauce wa munanan sakamakon da hakan yake haifarwa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 97 (5/10)([1])
GAME DA SHA'ANIN GUDUMMUWAR MACE MUSULMA WAJEN AYYUKAN RAYA ƘASA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, a taronta na shekara - shekara, karo na goma a Jidda (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 23 zuwa 28 ga watan Safar, 1418 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 28 ga watan Yuni zuwa 3 ga watan Yuli, 1997,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Sha'anin gudummauwar mace Musulma wajen ayyukan raya ƙasa, bayan tattaunawar da aka gudanar akan maudhu'in, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

Ɗaura wa kwamiti alhakin duba maudhu'in da aka yi wasici da shi game da sha'anin gudummuwar mace Musulma wajen ayyukan raya ƙasa, sakateriyar cibiya ce za ta kafa kwamiti, za ku a gabatar da sakamakon ayyukanta a taron shekara- shekara mai zuwa in Allah Maɗaukakin Sarki ya yarda.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma, 3/435)

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA SHA ƊAYA NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

ALMANAMA (BAHRAIN)

25 - 30 GA WATAN RAJAB, 1419 H

14 - 19 GA WATAN NUWAMBA, 1998

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 98 (1/11)([1])
GAME DA HAƊIN KAI NA MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Haɗin kai na Musulunci. Tattaunawar da aka gudanar ta bayyana cewa lallai wannan maudhu'i ne mai muhimmancin da al'ummar Musulmai suke matuƙar buƙata a yau ta fuskokin hasashe da aiki; kuma yin aiki wajen haɗa kan al'ummar Musulmai a fagen tunani da dokoki da siyasa, da jawo su zuwa ga tsarkakakken tauhidi ɗaya ne daga cikin muhimman manufofin wannan cibiya ta ƙasa da ƙasa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Lallai haɗin kai tsakanin Musulmai wajibi ne da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar da umurnin a yi, ya kuma sanya shi ya zama sifa ce da take bin wannan al'umma a inda yake cewa: **(Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku kada ku kuskura ku rarraba..)** [Ali Imran: 103], da inda mai girma da buwaya yake cewa: **(Lallai wannan al'umma taku, al'umma ce guda ɗaya)** [al-

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 3/5)

Anbiya'i: 92], sunnar Annabi mai daraja kuma ta tabbatar da haka ta hanyar bayani da kuma a aikace, a inda Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Jinin Musulmai daidai suke da juna, dukansu hannu ɗaya ne akan wanda ba su ba, mafi ƙarancin cikinsu yana iya jagorantarsu..)**, lallai mai tsira da aminci ya tabbatar da wannan haɗin kan a aikace ta hanyar haɗa 'yan uwantaka tsakanin mutanen Makka da suka yi hijira (al- Muhajirun) da mutanen Madina (al- Ansar), ya tabbatar da haka a farkon yarjejeniyar zama a daular Musulunci ta garin Madinatul Munawwara, inda a ciki ya sifanta Musulmai da cewa (Al'umma ce guda ɗaya banda sauran mutane).

Lallai waɗannan ayoyi masu girma da Hadisai masu ɗaukaka da ma wasunsu da suke ɗauke da wannan ma'anar suna wajabta cewa dole ne muminai su zama a ƙarƙashin tutar Musulunci, su yi riƙo da Alƙur'ani da Hadisi, su kuma yi watsi da tsohuwar ƙiyayya da rikicin ƙabilanci da son zuciya, da suke wani abu da yake kai wa zuwa ga ta'assubanci. Lallai lokacin suka kasance a haka ne aka sami ƙarfin daular Musulunci a zamanin Annabi, da ma zamanin zaɓaɓɓu na farko, addinin Musulunci ya yaɗu, daularsa ta ƙara faɗaɗa a gabas da yamma, alumma ta jagoranci cigaban bil'adama mai matuƙar ban mamaki, sai da ta kai ga cewa ita ce mafi girman daula da ta ginu akan yi wa Allah bauta shi kaɗai, ta kuma tabbatar da adalci da 'yanci da daidaito.

Na biyu: Lallai haɗin kan Musulunci ya tattara ne akan tabbatar da yi wa Allah Maɗaukakin Sarki bauta, da jin hakan a zuciya, da kuma a aikace, da wurin Magana, daidai da shiryatarwar littafin Allah Maɗaukakin Sarki da sunnar Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da kuma kiyaye wannan addini da ya haɗa Musulmai akan daidaitacciyar kalma a dukan fagagen rayuwar tunani da na tattalin arziki da na zamantakewa da na siyasa. Lallai a lokacin da al'ummar Musulmai ta yi nesa da da dalilan da suka kai ta zuwa ga haɗin kanta aka sami rarrabuwar

kawuna suka kukkutsa cikinta, kuma wannan rabuwar ce ta yi ta ƙara zurfi sakamakon dalilai masu yawa, a cikinsu akwai ƙoƙarin 'yan mulkin mallaka da suka ɗaga taken (Ka rarraba su saboda shugabanci ya zama a hannunka), sai aka rarraba al'ummar Musulmai zuwa kashi- kashi kodai na ƙabila, ko kuma na dangi, aka kuma rana tsakanin Larabawa da sauran Musulmai, kuma mafi yawan ayyukan 'yan Mulkin mallaka ya tattara wajen ƙarfafa ayyukan masu bincikensu cikin mustashriƙun, inda suka yi ta nazari akan abubuwan da za su kawo rarrabuwar kawuna, suka kuma yaɗa su a tsakanin Musulmai.

Na uku: Lallai saɓanin fahimta a fagen ilimin Fiƙihu wanda ya ginu akan ijtihadi wajen fahimtar nassoshin Shari'a da ma'anoninsu, abu ne da ba shi da wata matsala akan kansa, lallai hakan ma ya bayar da gudummuwa wajen yalwa da faɗin Shari'ar Musulunci, wanda kuma hakan ne ya kai zuwa ga tabbatar da manufofin Shari'ar Musulunci da abubuwan da suke keɓantu da sun a sauƙi da ɗauke damuwa.

Na huɗu: Wajibi ne a kiyaye matsayi gami da darajar dukan sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su), a kuma kira malamai da su cigaba da bayyana daraja gami da falalar da suke da su wajen naƙalto shari'ar Musulunci zuwa ga al'umma, da kuma bayyana haƙƙoƙinsu, da kuma kira zuwa ga gwamnatoci da su fitar da dokoki da za su hukunta duk wanda yake suka, da kuma ƙasƙantar da darajarsu ta kowace irin hanya, saboda yin hakan kiyaye alfarmarsu ne (Allah ya ƙara yarda da su), da kuma tunɓuke ɗaya daga cikin dalilan da yake kai wa zuwa ga rarrabuwar kawuna tun daga tushe.

Na biyar: Wajibi ne a yi riƙo da Alƙur'ani da Sunna, da shiryatarwar magabatan wannan al'umma cikin sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su), da waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa, da kuma yin watsi da dukan ɓata, da nesantar duk wani abu da yake tayar da fitina a tsakanin Musulmai, yake kuma kai wa zuwa ga rarrabu a

tsakaninsu, da kuma yin aiki tuƙuru wajen yin amfani da dukan ƙoƙarin da ake yi wajen kira zuwa ga addinin Musulunci da yaɗa manufofi da ƙa'idojinsa a tsakankanin waɗanda ba Musulmai ba.

Wasici:

- Kowa ya san cewa wannan zamani namu zamani ne na ƙungiyoyi da suke da ayyukansu na tunai da na zamantakewa da na tattalin arziki, ƙarƙashin taken "al- Aulama" (Glibalisation) da "al- Almaniyya" (Secular), da zamananci "al- Hadatha" (Modernity), da kuma irin yanda harkar jarida da yaɗa labarai ya faɗaɗa ba tare da wata dole ko iyaka ba, abin da ya sanya ƙasashen Musulmai suka zama koda yaushe su ake hari saboda a kawar da dukan sifofinsu, duk wani ginshiƙi da jogo da suke da su a fagen cigaba na ruhi da tunani su narke, lallai ba zai yiwu al'ummarmu ta sami kariya ga barin waɗannan hatsarurruka ba, sai idan ta haɗa kanta, ta kuma kawar da dukan dalilan da suke kai wa zuwa ga rarrabuwar kawuna, musamman ma ganin cewa tabba sal'ummarmu tana mallakar abubuwa da yawa da za su ƙarfafi haɗin kanta, domin aƙidarsu ɗaya ce, rayuwarsu ta zamantakewa da na tattalin arziki da na dokoki da al'adu ma suna kusa da juna.

Saboda haka cibiya tana bayar da wasici da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Ƙara tattabar da ƙudurin cibiya mai lamba 48 (10/5) game da aiwatar da hukunce- hukuncen Musulunci, da abubuwan da suka biyo bayansa na wasici a wannan maudhu'I, da ƙudurin cibiya mai lamba 69 (7/7) game da yaƙin tunani a wasici na farko.

Na biyu: Ƙarfafa gwamnatocin Musulunci wajen bayar da gudummuwa ta tallafi ga ƙungiyar ƙasashen Musulmai da cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya a matsayinsu na manyan misalai wajen haɗin kan Musulmai a fagen siyasa da tunani.

Na uku: Kawar da kai ga barin tsofaffin rikice- rikice da aka gada, domin tayar da su ba zai tsinana wa al'umma komai ba sai tayar da gaba da ƙiyayya da kuma ƙara zurfafa rarrabuwar kawuna.

Na huɗu: Yin riƙo da kyautata zato, da kuma amincewa da juna tsakanin Musulmai a matsayinsu na ƙasashe da matsayinsu na al'umma, ta hanya fuskantar da kafafen yaɗa labarai zuwa ga yanda za su ƙarfafa soyayya, da yaɗa kyawawan ɗabi'u na tattaunawa da juna, da kuma juriya wajen ta'amuli da ra'ayoyin da suka samu ta hanyar ijtihadi.

Na biyar: Yin amfani da manyan mas'alolin da suka haɗa kan al'ummar Musulmai, musamman ƙadiyyar Ƙudus da Masajidul Aƙsa, alƙiblar Musulmai ta farko, wajen da Allah ya yi Isra'i da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), saboda a kawar da dukan hatsarurrukan da suke yi wa garin barazana akan zamanta ƙasa ta Musulmai, da kuma saurin ɗaukan matakan da suka dace, da suka haɗa da:

(a) Yin tir da Allah wadai da abin da yake faruwa akan ƙasar Falasxinu da mutanen cikinta na siyasar koro da gini a akan gidajensu da yahudantar da ƙasar, da kuma irin yanda 'yan ƙasar suke fuskantar zalunci da kama- karya da yanke masu duk wani abu na rayuwa, da kisa da tarwatsa su da kuma keta alfarma da haƙƙoƙinsu na 'yan Adam.

(b) Bai wa ƙasar Falasxinu da take jihadi a ƙasa mai albarka domin kare Masallacin da yake shi ne farkon alƙiblar Musulmai gudummuwa mara iyaka, a wannan yaƙi da take yin a neman 'yancin kai, inda al'ummar Falasxinawa suka tsaya tsayin daka wajen sadaukar da kai.

(c) Yin tir da Allah wadai da ƙungiyar Sahayuna da mulkin mallakar Isra'ila da ayyukan zalunci da azabtarwa da ta'addancin da suke yi wa al'ummar

Falasxinu da suke gwagwarmaya domin neman ‘yanci da kuma ƙwato wuraren bautarsu.

Na shida: Muhimmanta manya ayyukan da aka gabatar da cewa lallai su ne sukan kan gaba wajen tabbatar da haḍin kai tsakanin Musulmai a matakin farko, irinsu:

1) Samar da manhajojin karantarwa ƙarƙashin karantarwar Musulunci.
2) Samar da muhimman ginshiƙai na yaḍa labarai da aikin jarida na Musulunci
3) Kafa kasuwar haḍin gwiwa ta Musulunci.
4) Kafa kotun duniya ta Musulunci.

Na bakwai: sakateriya cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya ta kafa kwamiti da zai ƙunshi mambobin cibiyar da ƙwararrun da suke ciki saboda su samar da bincike da nazarin da za a iya zartar da su a aikace, kwamitin ya yi la’akari da halin da al’ummar Musulmai take ciki, su kuma taɓo fagagen al’adu da rayuwar zamantakewa da na tattalin arziki, su kuma samar da ƙa’idodjin da za su tabbatar da haḍin kai a waḍannan fagage tare da amfana da ƙoƙarin da aka riga aka yi su a aikace ƙarƙashin ƙungiyoyin Larabawa da na Musulunci, da kuma neman taimakon masana a dukan waḍannan fagage.

A ƙoƙarin samun tabbacin ayyukan wannan kwamiti, da kuma samun lamunin zartar da sakamakon da ya cimma, muna bayar da wasicin, cewa: Ƙungiyar ƙasashen Musulmai ta kafa wannan kwamitin, ta kuma bayyana ayyukansa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 99 (2/11)([1])
GAME DA ALMANIYYA (SECULAR)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Almaniyya (Secular), ƙarƙashin tattaunawar da ta mayar da hankali zuwa ga hatsarin wannan maudhu'i ga al'ummar Musulmai, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Lallai "Almaniyya" (wanda shi ne raba tsakanin addini da rayuwa) ya fara ne a matsayinsa na mayar da martani ga zalunci, gami da wuce iyaka da Coci ta aikata.

Na biyu: Almaniyya ta yaɗu a ƙasashen Musulmai ne da ƙarfin da 'yan mulkin mallaka da masu taimaka masu suka yi amfani da shi, da kuma tasirin yaɗuwar istishraƙ, hakan kuma ya kai zuwa ga rarraba kawunan al'ummar Musulmai, da sanya masu shakku akan ingantacciyatr aƙidarsu, da baƙanta tarihin al'ummarmu mai haske, da ruɗa al'umma masu tasowa da riya masu da cewa akwai

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 3/259)

tufka da warwara tsakanin hankali da nassoshin shari'a, sun kuma yi aiki wajen kwafe makwafin Shari'ar Musulunci da dokokin zamani, da kuma yaɗa baɗala, da gurɓatattun ɗabi'u, da rusa kyawawan ɗabi'u masu daraja.

Na uku: Almaniyya ce ta haifo mafi yawan tunane-tunanen da suke rusa al'umma waɗanda suka karaɗe ƙasashenmu da sunaye mabambanta irinsu wariya, da gurguzu, da sahayuna, masoniyya da sauransu, waɗanda suke suka yi sanadiyyar salwantar arzikin al'umma, da taɓarɓarewar tattalin arziki, suka kuma taimaka wajen mamayar da 'yan mulkin mallaka suka yi wa ƙasashenmu irinsu su Falasxinu da Ƙudus, abin da yake nuna gazawarta wajen samar da kowane irin alhairi ga wannan al'umma.

Na huɗu: Lallai Almaniyya tsari ne da ɗan Adam ya ƙirƙira wa kansa, ya kuma ginu akan Ilhadiyanci, ya yi hannun riga da Musulunci ta kowace hanya, ya haɗa zumunta da sahayuna na duniya da kuma kiraye- kirayen baɗala da suke rusa al'umma, saboda haka mazhaba ce ta Ilhadiyanci da Allah da Manzonsa da muminai ba sa sonsa.

Na biyar: Lallai addinin Musulunci addini ne mai haɗe da tsarin rayuwa, manhaji ne na cikakkiyar rayuwa, kuma ya yi daidai da kowane zamani da kuma kowane lokaci, bai yarda da a rabe tsakanin addini da rayuwa ba, hasali ma ya wajabta cewa dole ne dukan hukunce- hukunce su zo ne daga gare shi, ya kuma tsara rayuwar yau da kullum akan karantarwar Musulunci, shin a fage siyasa ne, ko tattalin arziki, ko zamantakewa, ko tarbiyya, da yaɗa labarai da aikin jarida da sauransu.

Wasiyyoyi:

An bayayar da wasiyya mai zuwa:

a- Dole ne shugabanni su yi aiki tuƙuru wajen hana dukan salo da hanyoyin da Almaniyya za ta sami wajen zama a cikin Musulmai da ƙasashen Musulmai,

su kuma ɗauki dukan matakan da suka dace a bai wa al'umma kariya ga barinta.

b- Dole ne malamai su ƙara himma wajen kira zuwa ga Allah, da tona asirin Almaniyya, da kuma yi wa mutane gargaɗi akanta.

c- Tsara wani shiri na tarbiyyar Musulunci da zai game dukan makarantu da jami'o'i, da cibiyoyin bincike, da kafafen bayanai na ilimi, saboda a samar da siga guda ɗaya, da bayanin tarbiyya guda ɗaya, kuma dole ne a yi aiki wajen raya saƙon da Masallaci yake isarwa, da mayar da hankali wajen huɗuba da wa'azi da shiryatarwa, da bayar da horo na musamman ga masu yinsu, ta yanda za su yi daidai da buƙatun zamani, da mayar da martani akan shubuhohi, da kuma kiyaye manufofin shari'ar Musulunci masu haske,

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 100 (3/11)([1])
GAME DA FUSKOKIN DA MUSULUNCI YAKE YAƘAR ZAMANANCI (MODERNITY)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Fuskokin da Musulunci yake yaƙar zamananci (modernity), ƙarƙashin tattaunawar da ta mayar da hankali zuwa ga hatsarin wannan maudhu'i ga al'ummar Musulmai, ta kuma yaye kallabi game da haƙiƙanin zamananci cewa sabuwar mazhaba ce ta tunani, wadda ta ginu akan allantar da hankali, da kuma yin watsi da gaibi, da inkarin wahayi, da rusa duk wani abu da aka gada na imani da kyawawan ɗabi'u,

Kuma lallai muhimman abubuwan da suke bambance ta da saura a wurin masu binta su ne:

- Dogaro kacaukan akan hankali, da taƙaita akan abin da ilimi na gwaji ya bayar ba tare da kowane irin la'akari da ingatacciyar aƙidar Musulunci ba.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 3/467)

- Cikakken rarrabe tsakanin addini da sauran hukumomin al'adu da na zamantakewa da na tattalin arziki da na siyasa da na ayyukan jinƙai, da haka ne suka haɗa ƙawance da Almaniyya,

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Zamananci da ma'anar da aka yi bayani mazhaba ce da Ilhadiyanci, wadda Allah, da Manzonsa, da sauran muminai ba su yarda da ita ba, saboda ta yi hannun riga da Musulunci da usul ɗinsa gami da ƙa'idojinsa, koda kuwa wane irin bargo na kishin Musulunci da ƙoƙarin kawo tajdidi a cikinsa ta yafa wa kanta.

Na biyu: Lallai a cikin ƙa'idojin Musulunci da abubuwan da suka bambance shari'arsa da saura akwai abubuwan da za su biya buƙatun ɗan Adam a dukan zamani da lokaci, saboda ta ginu ne akan wasu tabbatattun ƙa'idoji da ba sa sauyawa, waɗanda rayuwar ɗan Adam ba za ta yiwu ba sai idan akwai su a koda yaushe, akwai kuma wasu abubuwa da suke sauyawa da suke suka riƙe sashen cigaba da sababbin abubuwa da suke faruwa, suke kuma yin maraba da duk wani sabon abu mai kyau da nagarta, ta hanyar yin ijtihadin da ya ginu akan madogararorin Shari'a da suke da yawa da yalwa.

Wasiyyoyi:

Cibiya ta yi wasici da abubuwa masu zuwa:

a. Ƙungiyar ƙasashen Musulmai ta muhimmanta kafa kwamitin da zai ƙunshi malamai masu tunani da hangen nesa cikin Musulmai saboda bibiya da sanin duk wani motsi da wannan mazhaba ta zamananci take yi, da bibiyan sakamakon da take bari, da kuma nazartarta a ilmance domin a bayyana ƙarerayin da ƙunsa, saboda a kare 'ya'yan Musulmai daga hatsarurrukanta.

b. Dole ne shugabanni su yi aiki tuƙuru wajen hana dukan salo da hanyoyin da mazhabar zamananci za ta sami wajen zama a cikin Musulmai da ƙasashen

Musulmai, su kuma ɗauki dukan matakan da suka dace a bai wa al'umma kariya ga barinta.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 101 (4/11)([1])
GAME DA SAYAR DA BASHI, DA SAYAR DA TAKARDUN BASHI, DA ABIN DA YAKE KWAFE MAKWAFINSU NA SHARI'AR MUSULUNCI A FAGAGEN KAMFANONIN GWAMNATI DA MASU ZAMAN KANSU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: (Sayar da bashi, da sayar da takardun bashi, da abin da yake kwafe makwafinsu na shari'ar Musulunci a fagagen kamfanonin gwamnati da masu zaman kansu), a ƙarƙashin tattaunawar da aka gudanar, wadda ta jawo hankali zuwa ga cewa: lallai wannan maudhu'i ne mai matuƙar muhimman da ake yin su a fagen mu'amalolin kuɗi na wannan zamanin, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Lallai bai halatta a sayar da bashin da lokacin biyansa bai yi ba daga wanin wanda ake bi bashi, da kuɗi jinsinsa nan take, ko da kuɗin da ba daga jinsin bashin ba,

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 1/53)

saboda hakan yana kai wa zuwa ga riba, haka ma bai halatta a sayar da shi da kuɗi bashi na jinsinsa, ko wanin jinsinsa ba, saboda hakan yana kai wa zuwa ga sayar da bashi da bashi da shari'a ta hana. Kuma babu wani bambanci tsakanin bashin da asalinsa rance ne, da bashin da asalinsa kasuwanci ne.

Na biyu: Ƙara tabbatar da ƙudurin cibiya mai lamba 60 (11/6) game da takardun shaida na kuɗi a taron shekara – shekara karo na shida, da aka yi a ƙasar Saudiyya a ranakun 17 -23 ga watan Sha'aban, 1410 H waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 – 20 ga ga watan Maris, 1990. Da sakin layi (Na biyu) na ƙudurin cibiya mai lamba 64 (2/7) game da zamiyen takardun kasuwanci, a taronta na shekara- shekara karo na bakwai da aka yi a ƙasar Saudiyya a ranakun 7 – 12 ga watan Zul Ƙida, 1412 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 9 – 14 ga watan Mayu, 1992.

Na uku: Cibiyar ta bijiro da wasu surorin na sayen bashi, tana kuma ganin a jinkitar fitar da maganar ƙarshe game da su saboda a ƙara bincike, a kuma nemi sakateriya ta kafa kwamitin nazari da bincike domin nazartar waɗannan surori da kawo makwafin sayar da bashi da shari'a ta halatta, saboda a sake gabatar da su a taron cibiyar na shekara- shekara mai zuwa.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 102 (5/11)([1])
GAME DA KASUWANCI DA TAKARDUN KUƊAƊE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Kasuwanci da takardun kuɗaɗe, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ƙara tabbatar da ƙudurin cibiya mai lamba 21 (9/3) game da takardun kuɗaɗe da kuma sauyawar darajar takardar kuɗi, da kuma ƙuduri mai lamba 63 (1/7) game da kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe, sakin layi (Na uku: Yanda ake ta'amuli da haja da takardun kuɗaɗe da kuma manunai a kasuwannan da aka tsara lamba (2) ta'amuli da takardun kuɗaɗe), da mai lamba 53 (4/6) game da amsar kuɗaɗe, sakin layi (Na biyu: (1 – d).

Na biyu: Shari'a ba ta halatta kasuwancin bashi a cikin takardun kuɗaɗe ba, bai kuma halatta a yi alƙawari akan

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 1/431)

canji a cikin kasuwancin ba, wannan ya haramta ne ta hanyar ma'anonin da Alƙur'ani mai girma da Hadisai da ijma'in al'umma suka yi nuni akansu.

Na uku: Lallai riba da yin kasuwancin takardun kuɗaɗe, da canji ba tare da bin hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci ba, babban dalili ne na kawo matsaloli da sauye- sauye a tsarin tattalin arziki, wanda hakan ne yake durƙusar da tattalin arzikin wasu ƙasashen.

Wasici:

Cibiya tana bayar da wasici mai zuwa:

- Wajibi ne a sanya ido –da shari'a ta yarda da shi- a kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe, a kuma samar da tsarin yanda za su gudanar da ayyukansu daidai da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci a kuɗaɗe da wasunsu, saboda waɗannan hukunce- hukuncen su ne suke hana faruwar bala'o'in tattalin arziki da suke bijirowa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 103 (6/11)([1])
GAME DA YARJEJENIYAR GYARA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Yarjejeniyar gyara, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Yarjejeniyar gyara, sabuwar yarjejeniya da babu ita a da, ana kuma aiki da hukunce- hukunce na bai ɗaya ne a wannan yarjejeniya. Hukuncinta yana sha bamban daidai da irin surar da ta zo da ita, a haƙiƙani wannan yarjejeniya ce ta tsakanin ɓangarori biyu, wanda ɓangare ɗaya zai zama wajibinsa shi ne ya duba, ya kuma gyara abubuwan da suke buƙatar a gyara a cikin wani inji, ko kuma duk wani abu da yake buƙatar gyara duk bayan

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 2/5)

wucewar wani lokaci, ko kuma wanda ya faɗo bagtatan zuwa wani lokaci, shi kuma ɗaya ɓangaren ya biya da sanannen lada, ta yiwu ɓangaren mai gyarar ya zama aiki ne kaɗai yake a kansa, ko kuma aiki tare da kayan da za a sanya a gyara.

Na biyu: Yarjejeniyar gyara yana da surori da yawa, a cikinsu akwai waɗanda hukuncinta ya bayyana, waɗanda su ne:

1) Yarjejeniyar gyarar da ba a haɗa ta da wata cinikayya ba, aikin mai gyaran kawai shi ne ya gabatar da aiki, ko ya haɗa da gabatar da kayan aikin da ba mai yaw aba, wanda a al'adance dukan ɓangarorin yarjejeniyar ba sa kallonsu a wani abu na a zo a gani.

Irin wannan yarjejeniya ana ɗaukanta a matsayin jingar gabatar da aiki, wannan kuma halal ne a Shari'ar Musulunci, sharaɗinsa shi ne aikin ya zama sananne ne, haka ma ladan shi yay a zama sananne.

2) Yarjejeniyar gyarar da ba a haɗa ta da wata cinikayya ba, aikin mai gyarar kawai shi ne ya gabatar da aiki, shi kuma mai neman gyarar zai kawo kayan aiki.

Ita ma wannan sura daidai take da sura ta farko.

3) Gyarar da ake sanya ta cikin yarjejeniyar saye akan mai sayarwa har zuwa wani lokaci sananne.

A nan wannan cinikayya ta haɗa tsakanin cinikayya da sharaɗi, ita ma ta halatta, sawa'un gyarar ne kawai ba tare da kawo kayan aiki ba, ko kuma tare da kawo kayan aikin duka.

4) Gyarar da ake sharanɗa ta a cikin yarjejeniyar haya akan mai bayar da haya, ko ɗan haya.

Wannan yarjejeniya ce da ta haɗa tsakanin haya da sharaɗi, hukuncin wannan sura kuwa shi ne: lallai idan gyarar tana cikin irin nau'in da sai an yi ta za a iya amfana da abin hayar, to a nan wajibin mai bayar da hayar ne kai tsaye ba tare da ma wani sharaɗi ba, sam bai halatta a sharɗanta haka akan ɗan haya ba, amma idan rashin yin gyarar ba zai hana amfana da abin hayar ba, to a nan ya

halatta a shardanta yin gyarar akan ko mai bayar da hayar, ko dan hayar, idan har an bayyana ta yanda za a kawar da dukan jahilci da shakku.

Akwai kuma wadansu surorin da cibiya take ganin a jinkirta su saboda a kara bincike da nazari.

Na uku: Sharadi ne a cikin dukan surorin a bayyana irin gyarar da ake bukata ta yanda kowa zai sani, a kawar da kowane irin jahilcin da zai iya kai wa zuwa ga rikici, haka ma a bayyana al'amarin kayayyakin gyara idan suna kan mai gyarar ne, haka sharadi ne a bayyana ladansa a dukan surorin.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 104 (7/11)([1])
GAME DA HANYOYIN AMFANA DA FATAWOWI AKAN SABABBIN ABUBUWA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in: Hanyoyin amfana da fatawowi akan sababbin abubuwa, ta kuma saurari tattaunawar da aka gudanar akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

(1) Yin amfani da nau'o'in tsofaffin fatawowi na Fiḳihu waɗanda a lokacinsu sababbi ne, saboda a samar da mafita ga sababbin abubuwa na zamani da suka faru, sawa'un a fagen manhajojin fatawa ne ƙarƙashin ƙa'idojin ijtihadi da fitar da hukunci da nassi, ko kuma takhriji (wanda shi ne fitar da hukunci daga hukunci) da kuma ƙa'idojin ilimin Fiḳihu, ko kuma wanda yake a fagen rassa na fiḳihu da tuni malaman

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 2/281)

Fiƙihu sun riga sun samar da mafita a ire- irensu a cikin ayyukan da aka gudanar da su a aikace a zamaninsu.

(2) Tahƙiƙin muhimman litattafan fatawowi, da kuma raya litattafan Fiƙihu da suke taimaka wa fatawa ire-iren littafi (al- Tanbihat alal Mudawwana) na Alƙali Iyadh, da (Barnamij) na Sheikh Azzum, da (Fatawa) na Imamul Ghazaliy, da (Taƙwimun Nazar) na Ibn Alduhhan, da litattafan da ake aiki da su a mazhabar Malikiyya da manyan garuruwan ilimin malikiyya Kaman garin Fas da al- Ƙairawan, da Ƙurɗuba, da (Ma'arudhat) na Ibn Su'ud da sauransu cikin litattafan da suke hanyoyi ne na ƙara fito da nishaɗi da muhimmancin ilimin Fiƙihu.

(3) Samar da littafi da zai yi bayani dalla- dalla akan Usulun ilimin fatawa, da manhajojin masu bayar da fatawa, da kalmomin mazhabobi mabambanta na musamman "al- Musɗalahat", da hanyoyin rinjayar da fahimta, da fitar da hukunci daga cikin hukunci da yake a tabbace a cikin dukan mazhabobi, tare da tattara abubuwan da ake yin aiki da su a mazhabar Malikiyya da sauransu, da kuma yaɗa littafin (al-Madkhal ila fiƙhin Nawazil) da shugaban wannan cibiya.

(4) Shigar da sauran litattafan Fatawa a cikin tsarin Kundin ƙa'idojin Fiƙihu domin isa zuwa ga ƙa'idodjin da ake gina fatawa akansu, waɗanda babu su a cikin Mudawwanonin Fiƙihu.

Majalisar cibiya tana bayar da wasici mai zuwa:

1. Kiyayar fatawowin da ba su da tushe na Shari'a, waɗanda ba su dogara da wani dalili ko hujja da shari'a take la'akari da ita ba, kawai sun dogara ne da maslahar da riyata kawai aka yi, wadda tuni shari'a ta yi watsi da ita, wadda asalinta ta fito ne daga son zuciya, ta kuma tasirantu da yanayi da

halin da ake cikin waɗanda sun saɓa da hukunce-hukuncen Shari'ar Musulunci da manufofinta.

2. Kira zuwa ga masu ruwa da tsaki akan al'amurran bayar da fatawa da suka haɗa da malamai da hukumomi da kwamitocin bayar da fatawa akan su yi amfani da ƙudurori da wasicin da suka fito daga cibiyoyin Fiƙihun Musulunci da ake la'akari da su, saboda a samu a saita harkar bayar da fatawa, da kuma tuntuɓar juna da haɗin kai a ƙasashen Musulunci.
3. A miƙa batub bayar da fatawa ga waɗanda akan cewa su malamai ne masu tsantseni da kuma tsoron Allah mai girma da buwaya.
4. Dole ne masu bayar da fatawa su yi la'akari da ƙa'idojin bayar da fatawa da malamai suka bayyana, musamman waɗannan masu zuwa:
   a. Riƙo da hujjojin Shari'a da suka haɗa da Alƙur'ani da Hadisi da Ijma'i da Ƙiyasi da sauran hujjoji na Shari'a, da kuma yin riƙo da ƙa'idojin kafa hujja da kuma fitar da hukunci.
   b. Muhimmanta jera abubuwan da suka fi muhimmanci wajen samar da maslaha da kuma tunkuɗe ɓarna.
   c. Lura da waƙi'i da al'adu da kuma sauye-sauyen yanayi na lokaci, waɗanda ba su ci karo da wani asali daga cikin asalin Shari'a ba.
   d. Daidaita al'amurra da cigaban da zai haɗa tsakanin maslahar da Shari'a take la'akari da ita, da riƙo da hukunce- hukuncen Shari'ar Musulunci.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 105 (8/11)([1])
GAME DA AL'AMARIN GADO (GENETICS) ILIMIN KIMIYYAR TSARIN GADO

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa majalisar game da maudhu'in da aka ambata a sama, da kuma duba ƙudurori da wasicin da taron ƙara wa juna sani da aka gudanar taron likitanci da Fiƙihu karo na goma sha shida, wanda aka gudanar da haɗin gwiwa tsakanin Majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci da take Jidda, da Ƙungiyar Musulunci mai lura da ilmomin likitanci da take Kuwait, da Ofishin Hukumar lafiya ta duniya na yanki da yake Aleɗanderia, da Ƙungiyar Musulunci mai lura da tarbiyya da ilmomi da al'adu a tsakankanin ranakun 23 zuwa 25 ga watan Jumada al- Akhir, 1419, waɗanda suka yi daidai da

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha ɗaya, 3/533)

ranakun 13 zuwa 15 ga watan Oktoba, 1998 a ƙasar Kuwait, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta fitar da ƙuduri akan al'amarin gado (genetics) ilimin kimiyyar tsarin gado saboda a ƙara bincike da nazari.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 106 (9/11)
GAME DA TARON ƘWARARRU AKAN RAWAR DA MACE TAKE TAKAWA WAJEN CIGABAN AL'UMMAR MUSULMAI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha ɗaya a Almanama (Bahrain), wanda ya gudana daga ranar 25 zuwa 30 ga watan Rajab, 1419 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 14 zuwa 3 ga watan Nuwamba, 1998,

Bayan an tattauna akan wannan maudhu'in, an kuma sami matsaya akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta duba fitar da ƙuduri akan maudhu'in (Taron ƙwararru akan rawar da mace take takawa wajen cigaban al'ummar Musulmai) saboda a ƙara nazari, an kuma kafa kwamiti saboda wannan dalilin, wanda ya haɗa da: mai girma Sheikh Dr. Bakar Bn Abdullahi Abuzaid, shugaban majalisar cibiyar, da mai girma Sheikh Aliyu al- Taskhiriy, da mai girma Sheikh Muhammad Taƙiy al- Usmaniy, da sharaɗin su gabatar da rahotonsu a taron da cibiya take gudanarwa na shekara – shekara mai zuwa.

Allah ya sa mu dace;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA SHA BIYU NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

ALRIYADH (SAUDIYYA)
25 GA WATAN JIMADA AL'AKHIR - ZUWA 1 GA WATAN RAJAB, 1421
23 - 28 GA WATAN SATUMBA, 2000

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 107 (1/12)([1])
GAME DA YARJEJENIYAR KAWO KAYA DA KUMA KWANGILA Tanda

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha biyu a Al-Riyadh (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 25 ga watan Jimada al- Akhir, zuwa 1 ga watan Rajab, 1421, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 28 ga watan Satumba, 2000,

Bayan ta duba bincike- binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Yarjejeniyar kawo kaya, da kuma Kwangila Tanda. Bayan ta saurari tattaunawar da ta gudana tsakanin mambobin cibiya da ƙwararrunta da kuma adadin malamai masana Fiƙihu akan wannan maudhu'in, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1. **Yarjejeniyar kawo kaya:**

Na farko: Yarjejeniyar kawo kaya itace: Yarjejeniyar da ɗaya daga cikin ɓangarorinsa yake ɗaukan alƙawarin bayar da sananniyar haja a nan gaba, a duk wucewar wani lokaci na kuma tsawon wani sanannen lokaci ga ɓangare na biyu,

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 2/391)

shi kuma za a ba shi wani sanannen adadi na kuɗi da za a jinkirta bayar da shi dukansa, ko wani sashe nasa.

Na biyu: Idan kayan da aka ƙulla wannan yarjejeniya na kawo shi haja ce ta ke buƙatar a sana'anta ta, to wannan yarjejeniya jingar sana'antawa kenan, kuma duk hukunce-hukuncenta ne za a yi amfani da su a nan. Kuma cibiya ta riga ta fitar da ƙuduri game da jingar sana'antawa mai lamba 65 (3/7).

Na uku: Idan kayan da aka ƙulla wannan yarjejeniya na kawo shi haja ce da ba sana'anta ta ake yi ba, kawai da an sifanta ta ne akan sharaɗin wannan sifar ce take akansa wadda ya zama dole ya gabatar idan lokacin ya yi, wannan kuma yana samuwa ne ta ɗayan hanyoyi biyu:

a. Wanda ya buƙaci kawo hajar ya gabatar da dukan kuɗin a lokacin ƙulla yarjejeniyar, shi irin wannan yarjejeniya yana ɗaukan hukuncin cinikayyar salam ne, saboda haka ya halatta idan an yi la'akari da sharuɗɗan da shari'a ta gindaya akan wannan cinikayya, waɗanda aka bayyana su a ƙudurin cibiya mai lamba 85 (2/9).

b. Idan wanda ya buƙaci a kawo masa hajar bai gaggauta gabatar da dukan kuɗinta a lokacin ƙulla yarjejeniyar ba, to wannan bai halatta ba saboda an gina shi akan alƙawarin da ya zama wajibi ga dukan ɓangarori biyun su zartar da shi. Lallai cibiya ta riga ta fitar na 40 da 41 wanda ya ƙunshi cewa lallai alƙawarin da ya zama dole a cika shi ya yi kama da ita kanta yarjejeniyar, a nan sai kasuwancin ya zama yana cikin cinikayyar bashi da bashi. Amma idan yarjejeniyar ba ya zama dole akan ɗaya daga cikin ɓangarorinsa, ko dukan ɓangarorin ba, to a nan ya halatta, da sharaɗin a cika kasuwancin da wata sabuwar yarjejeniya, ko ta hanyar miƙawa.

2. Yarjejeniyar Kwangila Tanda:

Na farko: Kwangila Tanda ita ce: Neman isa zuwa ga farashi mafi arha wajen sayen wata haja, ko gabatar da

wani aiki, inda masu neman wannan abu za su gayyaci masu sha'awar yin aikin da su gabatar da tayinsu, daidai da wasu sharuɗɗa, da wasu ƙididdigaggun sifofi.

Na biyu: Kwangila abu ne da ta halatta a Shari'ar Musulunci, daidai take da kaɗa ƙararrawa, saboda haka hukunce- hukuncen kaɗa ƙararrawa take ɗauka, sawa'un kwangilar ta gama gari ne, ko kuwa mai iyaka, ko ta cikin-gida, ko ta waje, ta bayyane ce ko kuwa ta sirri, cibiya ta riga ta fitar da ƙuduri mai lamba 73 (4/8) akan kaɗa ƙararrawa a taronta na shekara – shekara karo na takwas.

Na uku: Ya halatta a taƙaita shiga cikin tayin kwangila akan waɗanda aka bayyana su a hukumance, ko waɗanda suke da lasisi, waɗanda hukuma ta amince masu, sai dai dole ne ya zama an yi hakan ne akan wasu dokoki da sharuɗɗa na adalci.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 108 (2/12)([1])
GAME DA KATIN LAMUNI DA BA A SAKA MASA KUƊI BA (CREDIT CARD)

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha biyu a Al-Riyadh (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 25 ga watan Jimada al- Akhir, zuwa 1 ga watan Rajab, 1421, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 28 ga watan Satumba, 2000.

Lura da ƙudurin majalisa mai lamba 63 (1/7) game da maudhu'in: Kasuwannin hada- hadar kuɗaɗe akan katin lamuni da ba a saka masa kuɗi ba (credit card), inda aka ɗauki matakin jinkirta bayyana matsayin shari'a, da hukuncinta game da wannan katin zuwa taron shekara-shekata ta gaba.

Da nuni zuwa ga ƙudurin majalisa a taronta na shekara – shekara karo na goma mai lamba 96 (4/10), bayan ta duba bincike- binciken da aka gabatar mata game da maudhu'in: katin lamuni da ba a saka masa kuɗi ba (credit card), bayan ta saurari tattaunawar da malaman Fiḳihu da masana tattalin arzki suka gudanar akansa, ta kuma koma zuwa ga

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 2/391)

ma'anar credit card da ya zo a ƙudurinta mai lamba 63 (1/7), wanda aka fahimci ma'anar katin lamuni da ba a saka masa kuɗi ba (credit card) da cewa shi ne:

(Wata madogara ce da mai bayar da ita (Banki) yake bayarwa ga mutum na ɗabi'a, ko na ma'ana (wanda yake ɗauke da ita) sakamakon yarjejeniya da yake a tsakaninsu, inda shi wannan katin zai iya ba shi daman sayen kayayyaki, ko neman a gabatar masa da wata hidima, daga wanda madogarar (Banki) ta amince da shi (ɗan kasuwa) ba tare da ya biya kuɗin a nan take ba, saboda yana ƙunshe da wajibcin cewa wanda ya bayar da wannan madogarar (Banki) shi zai biya, za kuma a biya ne daga asusun jahar da ta bayar da madogarar (Banki), sannan su dawo kan wanda yake ɗauke da madogarar a lokacin da aka ajiye mai kewayowa, wasu daga ciki sukan sanya ƙarin na kuɗin ruwa (riba) akan jimillar kuɗin da ba a biya ba bayan wucewar wani lokaci daga lokacin da ya kamata a biya, wasu kuma ba sa wajabta biya kuɗin ruwa), an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Bai halatta a bayar da katin lamuni da ba a saka masa kuɗi ba (credit card), bai kuma halatta a yi ta'amuli da shi ba, muddin akwai sharaɗin bayar da kuɗin ruwa (riba), koda kuwa wanda yake ɗauke da katin ya yi niyyar biya a cikin lokacin da aka amince masa ya biya a kyauta.

Na biyu: Ya halatta a bayar da katin lamuni da ba a saka masa kuɗi ba (credit card) idan ba ya ƙunshe da wani sharaɗi na bayar da kuɗin ruwa (riba) akan asalin bashin.

Da haka zai zama ya karkasu zuwa:

a) Ya halatta ɓangaren da yake bayar da wannan katin (Banki) ya amshi lada daga hannun abokin huldarsa a lokacin da za a yi wannan katin, ko a lokacin da za a ƙara sabunta, amma dole ne ladan ya zama ya yi daidai da hidimar da aka gabatar.
b) Ya halatta bankin ya amshi kamaso akan kayayyakin da abokin huldar ya saya daga hannun ɗan kasuwan,

da sharaɗin kuɗin da ɗan kasuwan ya sayarwa mai ɗauke da katin shi ne dai kuɗin da yake sayarwa wanda ya zo da kuɗi hannu.

Na uku: Cire tsabar kuɗi da mai ɗauke da katin zai yi daidai yake da amsar bashi daga wanda ya ba shi katin (Banki), wannan abu ne da babu wata damuwa ta shari'a akansa, matuƙar babu wani ƙarin kuɗin ruwa (riba) a ciki. Ba kuma za a ɗauki hakan a matsayin kuɗin da aka cire wanda ba shi da wata dangantaka da kuɗin bashin, ko lokacin biyansa a matsayin ladan hidima ba. duk wani ƙari akan haƙiƙanin hidimar da aka gabatar haramun ne; domin yana cikin kuɗin ruwa da Shari'a ta haramta, kaman yanda ƙuduri cibiya mai lamba 10 (10/2), da 13 (1/3) suka bayyana.

Na huɗu: Bai halatta a sayi zinare da azurfa, haka ma da takardun kuɗaɗe ta hanyar katin lamunin da ba a saka masa kuɗi ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 109 (3/12)([1])
GAME DA SHARAƊI NA HUKUNCI (PENALTY CLAUSE)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha biyu a Al-Riyadh (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 25 ga watan Jimada al- Akhir, zuwa 1 ga watan Rajab, 1421, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 28 ga watan Satumba, 2000.

Bayan ta duba baincike- binciken da aka gabatar da cibiya akan maudhu'in: Sharaɗi na Hukunci (Penalty Clause), bayan kuma ta saurari tattaunawar da mambobin cibiya, da ƙwararrunta, da wasu daga cikin malaman Fiƙihu suka gudanar akan wannan maudhu'in, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ma'anar Sharaɗi na Hukunci (Penalty Clause) a wurin masana dokoki ita ce: Yarjejeniya tsakanin abokan hulɗa akan kimanta asarar da za ta hau ɓangaren da ya cutu idan ɗaya ɓangaren bai zartar da yarjejeniyar ba, ko kuma ya yi jinkiri wajen zartarwa.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 2/91)

Na biyu: Majalisa tana ƙara tabbatar da ƙudurorinta game da Sharaɗi na hukunci (Penalty Clause) da suka gabata, waɗanda suke zo a ƙudurinta game da Salam mai lamba 85 (2/9), wanda ya bayyana cewa: (Bai halatta a gindaya sharaɗin uƙuba sakamakon jinkiri gabatar da abin da aka yi cinikayyar salam akansa ba, saboda shi ɗin bashi ne, bai kuma halatta a sanya sharaɗin ƙari a cikin bashi a lokacin da aka yi jinkiri ba), da ƙudurinta akan jingar sana'antawa mai lamba 65 (3/7), wanda ya bayyana cewa: (Ya halatta mai bayar da jingar da wanda aka bai wa jingar su samar da wani sharaɗi na hukunci ga wanda bai cika abin da aka yi yarjejeniya akansa ba, matuƙar dai ba wani abu ne da ya wuce ƙarfinsu ya shigo ba), da ƙudurinta akan cinikayyar da aka rarraba lokacin biyan kuɗinta mai lamba 51 (2/6) wanda ya bayyana cewa: (Idan mai sayen da ake bi bashi ya yi jinkiri wajen biyan kason da aka rarraba a lokacin da aka iyakance, sam bai halatta a tilasta masa biyan wani ƙari akan bashin da yake a kansa sakamakon wani sharaɗi da ya gabata, ko kuma ba ma da sharaɗi ba; saboda hakan riba ne da Allah ya haramta).

Na uku: Ya halatta Sharaɗi na hukunci ya zama yana cikin yarjejeniyar farko, Kaman yanda ya halatta ya zo a wata sabuwar yarjejeniya kafin faruwar cutarwar.

Na huɗu: Ya halatta sharaɗi na hukunci ya zo a cikin dukan yarjejeniyar cinikayya na kuɗi, matuƙar asalin cinikayyar da ta wajaba a zartar ba bashi ba ne; saboda yin haka cin kuɗin ruwa ne (riba) ƙarara.

Saboda haka wannan sharaɗin –alal misali- ya halatta a yarjejeniyar kwangila akan ɗan kwangila, da yarjejeniyar kawo haja, ko kayayyaki akan mai kawo hajar ko kayayyakin, da yarjejeniyar jingar sana'antawa akan mai sana'antawar idan ba su zartar da abin da ya wajaba akansu ba, ko idan suka yi jinkiri wajen zartar da shi.

Bai kuma halatta ba -alal misali- a cikin cinikayyar da aka rarraba lokutan biyan kuɗinta sakamakon jinkirin da wanda ake bi bashin ya yi wajen biyan kason da ya rage

ba, sawa'un hakan ya faru sakamakon rashinne da ya faɗa masa, ko kuma sakamakon taurin bashi, bai kuma halatta a cikin yarjejeniya jingar sana'antawa akan wanda za a sana'anta w aba, idan ya yi jinkiri wajen gabatar da abin da yah au kansa.

Na biyar: Cutuwar da ya halatta a biya ta ƙunshi cutuwa na kuɗi da ta faru, da asara ta haƙiƙa da ta sami wanda ya cutu, da kuma samun da yake da tabbacinsa idan ya kuɓuce masa, amma bai shafi cutuwa ta ma'ana, ko ta daraja ba.

Na shida: Ba za a yi aiki da sharaɗi na hukunci ba, idan wanda aka shardantawa ya tabbatar da cewa dalilin rashin sauke nauyinsa wani abu ne da ya fi ƙarfinsa, ko ya tabbatar da cewa babu wata cutuwa da ta sami wanda ya sanya sharaɗin sakamakon rashin sauke nauyin da bai yi ba.

Na bakwai: Ya halatta alƙali ya sauya ƙimar abin da za a biya idan ɗaya daga cikin ɓangarorin ya nema, idan dai har ya ga abin da zai sanya ya yi haka, ko kuma idan an wuce iyaka wajen wannan sharaɗin.

Cibiya tana bayar da wasici mai zuwa:

- Shirya taro na musamman domin gudanar da bincike akan sharuɗɗa da matakan da bankunan Musulunci suke ɗauka wajen samun lamuni akan basussukan da suke bayarwa.

Allah shi ne masani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 110 (4/12)([1])
GAME DA HAYAR DA TAKE ƘAREWA DA MALLAKA, DA KASHE- KASHEN KUƊIN HAYA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha biyu a Al-Riyadh (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 25 ga watan Jimada al- Akhir, zuwa 1 ga watan Rajab, 1421, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 28 ga watan Satumba, 2000.

Bayan ta duba bincike- binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in: (Hayar da take ƙarewa da mallaka, da kashe- kashen kuɗin haya). Bayan ta saurari tattaunawar da mambobin cibiya da ƙwararrunta da wasu daga cikin masana Fiḳihu suka gabatar, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

- **Hayar da take ƙarewa da mallaka:**

Na farko: Ƙa'idar surar da ta halatta da kuma wanda aka hana kamar haka:

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 1/313)

a. **Ƙa'idar hanawa:** Idan aka samu cinikayya biyu daban-daban, a lokaci ɗaya, akan abu ɗaya, kuma a zamani ɗaya.
b. **Ƙa'idar halacci:**
    1. Samun cinikayya guda biyu daban- daban, kowane ya dogara da kansa, kuma lokacin ma daban- daban, ta yadda zai zamana an fara ƙulla cinikin sayarwa ne bayan an ƙulla yarjejeniyar haya, ko kuma an samar da alƙawarin mallaka bayan lokacin haya ya ƙare, a nan zaɓi daidai yake da alƙawari a wurin yin hukunci.
    2. Hayar ta kasance ta gaskiya, ba wai an saya sayarwa ba ne.
c. Lamunin abin da ake hayar ya zama yana kan mai kayan ne, ba akan mai haya ba, da haka mai mallaka shi ne zai ɗauki duk wani ƙaddara da za ta faɗa wa abin da ake hayar, in dai ba mai hayar ya yi ganganci, ko sakaci ba ne, kuma babu komai akan mai haya idan bai amfana da shi ba.
d. Idan cinikayyar ta ƙunshi inshora akan abin da ake hayar, ya zama dole inshorar ta zama taimakekeniya ce ta Musulunci, ba ta kasuwanci ba, kuma mai mallaka ne zai ɗauki nauyi ba mai haya ba.
e. Ya wajaba a zartar da dukkan hukunce – hukunce hayar da take ƙarewa da mallaka a tsawon lokacin hayar gaba ɗaya, sannan a zartar da hukunce – hukuncen sayarwa lokacin da za a mallaka.
f. Kuɗaɗen gyara yana kan mai mallaka, ba akan ɗan haya ba, har a gama haya, in banda gyarar kayan amfanin yau da kullum.

Na biyu: Cikin surorin cinikayyar da aka hana:

a. Ƙulla yarjejeniyar hayar da za ta ƙare da mallakar abin da ake haya, a maimakon abin da mai haya ya biya na haya a tsawon lokacin da aka iyakance, ba tare da an fara ƙulla sabon ciniki ba, ta yadda a ƙarshe hayar za ta zama sayarwa da zaran lokaci ya cika.

b. A bayar da haya ga wani akan wani sanannen kuɗi, zuwa lokaci sananne, tare da ƙulla cinikin sayarwa da sharaɗin biyan duka kuɗin hayar da aka yi yarjejeniya a kai a lokacin da aka sanya, ko kuma zuwa wani lokaci a gaba.

c. A ƙulla yarjejeniyar haya ta gaskiya, amma a haɗa shi da cinikin sayarwa da sharaɗin zaɓi ta yadda mai mallakar ne zai amfana, kuma ya kasance an ɗaga lokacin zuwa wani Lokaci mai tsawo da aka yanke (wanda shi ne ƙarshen lokacin haya).

Wannan shi ne abin da fatawoyi da ƙudurorin da suka zo da ga cibiyoyi na ilimi, ciki har da majalisar manyan malamai ta ƙasar saudiyya.

Na uku: Daga cikin surorin cinikayyar da aka halatta:

a) A ƙulla yarjejeniyar haya ta yadda mai haya zai amfana da abin da ya amsa haya, akan wani kuɗi sananne, da kuma lokaci sananne, sannan a haɗa shi da yarjejeniyar kyauta da abin da ake hayar ga mai hayar, a sanya sharaɗin zai biya duka kuɗin hayar, amma da sabuwar yarjejeniya, ko kuma a yi masa alƙawari za ba shi kyauta bayan ya gama biya, wannan daidai da ƙudirin cibiya akan abin da ya shafi kyauta mai lamba 13 (1/3).

b) Ƙulla yarjejeniyar haya, tare da bayar da zaɓi ga mai haya, bayan ya gama biyan kuɗin hayar da yake kansa a tsawon lokacin hayar nay a sayi abin da yake hayar da farashinsa na kasuwa a lokacin da hayar ya zo ƙarshe, wannan daidai da ƙudirin cibiyar mai lamba 44 (5/6).

c) A ƙulla yarjejeniyar haya da mai hayar zai yi amfani da abin da ya haya, akan wani kuɗi sananne, zuwa lokacin da aka sani, sannan a haɗa da alƙawarin sayar masa da abin da yake hayar idan ya biya dukan kuɗin akan wani kuɗi da ɓangarori biyun suka amince a tsakaninsu.

d) A ƙulla yarjejeniyar haya da mai haya zai yi amfani da abin da ya haya, akan wani kuɗi sananne, zuwa wani lokaci sananne, sai kuma mai mallakar ya ba mai haya zaɓin mallakar abin ake hayar a duk lokacin da ya so, da sharaɗin a yi sabon ciniki a wannan lokacin akan farashin kasuwa, wannan daidai da ƙudirin cibiya da ya gabata, mai lamba 44 (5/6), ko kuma dai yadda suka daidaita.

Na huɗu: Akwai wasu surori na hayar da take ƙarewa da mallaka, waɗanda malamai suka yi saɓani a kansu, waɗanda suna buƙatar bincike, za a kawo su a taron shekara- shekara gaba da ikon Allah Maɗaukakin Sarki.

- **Kason kuɗin haya:**

Cibiyar ta yanke hukuncin a jinkirta magana akan kason kuɗin haya, saboda a ƙara bincike, a gabatar a taron shekara- shekara na gaba.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 111 (5/12)([1])

GAME DA KASUWANCI DA RIBAR WAƘAFI (HUBUSI)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taronta na shekara - shekara, karo na goma sha biyu a Al-Riyadh (Saudiyya), wanda ya gudana daga ranar 25 ga watan Jimada al- Akhir, zuwa 1 ga watan Rajab, 1421, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 zuwa 28 ga watan Satumba, 2000.

Bayan ta yi nazari akan binciken da a ka ƙaddamar wa cibiyar akan maudhu'in (Kasuwanci da ribar waƙafi - Hubusi-), bayan ta saurari tattaunawar da mambobinta tare da ƙwararru da masana da ma wasu daga cikin masana Fiƙihu suka gabatar,

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta fitar da ƙuduri akan maudhu'in: Kasuwanci da ribar waƙafi (Husubi) saboda a ƙara bincike da nazari akansa, musamman akan maudhu'ai masu zuwa:

1. Kasuwanci da waƙafi
2. Waƙafin kuɗaɗe.

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 1/39)

3. Canji da canjarwa
4. Cakuɗa waƙafi
5. Bambanci tsakanin waƙafi da killace wata dukiya daga cikin Baitul Mali domin amfanin wasu ayyanannun mutane kaman malamai ko ladanai da sauransu. (Trust).

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 112 : (6/12)([1])
GAME DA TABBATARWA TA HANYAR ƘARINA KO ALAMU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta yi nazari akan binciken da a ka ƙaddamar wa cibiyar akan maudhu'in (Tabbatarwa ta hanyar ƙarina ko alamu),

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta fitar da ƙuduri akan maudhu'in (Tabbatarwa ta hanyar ƙarina ko alamu) saboda an taƙaita bincikensa kawai akan sababbin abubuwa, da ƙididdige su da bayanin hukunce – hukuncensa.

Allah ya sa mu dace;;

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 3/5)

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 113 (7/12)([1])
GAME DA HAƘƘOƘIN ƘANANAN YARA DA TSOFAFFI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta yi nazari akan binciken da a ka ƙaddamar wa cibiyar game da maudhu'in (Haƙƙoƙin ƙananan yara da tsofaffi), da kuma wasicin da ya zo daga taron ƙarawa juna sani na likitoci da malamai masana Fiḳihu, wanda aka yi a ƙasar Kuwait ta hanyar taimakekeniya da Cibiyar fiḳihun Musulunci ta duniya, da ƙungiyar Musulunci ta ilmomin likitanci da aka gudanar a ranakun 9 zuwa 12 Rajab 1420 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 18 zuwa 21 Oktoba 1999, akan (Haƙƙoƙin tsofaffi), da kuma sauraron tattaunawar da aka yi akan maudhu'in tare da mambobinta, da kuma masana, da kuma wasu daga cikin malaman fiḳihu, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Haƙƙoƙin ƙananan yara a Musulunci:

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 4/293)

Yaranta mai girma shi ne harsashin gina daidaitacciyar al'umma, kuma lallai Musulunci ya ba ta muhimmanci matuƙa, ya kwaɗaitar da auratayya, da kyautata zaɓin juna ga ma'aurata, saboda hakan yana da tasiri wajen kyautata zamantakewa da kuma tasowar ƙananan yara su zama na gari.

Saboda haka, cibiyar ta tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1. Kare jaririn da yake cikin mahaifiyarsa daga dukan abubuwan da za su cutar da shi, ko su cutar da mahaifiyarsa, irinsu: kayan sanya maye, da masu bugarwa, wajibi ne a shariar Musulunci.
2. Jariri yana da haƙƙi ya rayu, tun daga lokacin da aka fara halittarsa, ba a yarda a yi masa ta'adin da zai kais hi zuwa ga zubewa, ko a cutar da shi ta kowace irin hanya da za ta yi wa halittarsa dameji ba.
3. Kowane yaro -bayan an haife shi- yana da haƙƙoƙi da ake iya riska, da kuma waɗanda haƙƙoƙi ne na ma'ana, a cikin haƙƙoƙin da ake iya riska, akwai: haƙƙin mallaka, da gado, da wasiyya, da kyauta, da waƙafi, a cikin haƙƙoƙin ma'ana kuma akwai: zaɓa masa suna mai kyau, da samar masa da nagartacciyar nasaba, da addini, da kuma ƙasar da yake.
4. Ƙananan yara marayu, da yaran tsintuwa, da waɗanda yaƙi ya kashe iyayensu, da sauran waɗanda ba su da masu ɗaukar nauyi da ɗawainiyarsu, suna da dukan haƙƙoƙin da ƙananan yara suke da su, nauyinsu yana kan ɗaukacin al'umma da gwamnati.
5. Kiyaye haƙƙin ƙaramin yaro na samun shayarwa har zuwa shekara biyu cikakku.
6. Ƙaramin yaro yana da haƙƙin kulawa da raino a yanayi mai kyau da tsafta, kuma uwa wadda ta cancanta ita ce ta fi dacewa da wannan aikin akan waninta, sannan sauran 'yan uwansa a jere kamar yadda aka sani a Shari'ar Musulunci.

7. Walittaka ga ƙaramin yaro –ta hanyar iyayensa, ko ta hanyar kotu, akan kansa da dukiyarsa saboda a ba su kariya- haƙƙi ne daga cikin haƙƙoƙinsa da sam bai halatta a yi sakaci da su ba, bayan ya balaga, ya yi hankali sai ya wakilci kansa.
8. Tarbiyya madaidaiciya, da kuma tashi da ɗabi'u masu kyau, da ilmantarwa, da horasawa, da kuma samun ƙwarewa da gwanancewa, da samun sana'ar da ta halatta a shari'a, wadda za ta sanya yaro ya dogara da kansa, ya kuma nema arzikinsa bayan ya balaga, suna cikin mafi muhimmancin haƙƙoƙin da ya kamata a kula da su, tare da keɓance 'yan baiwar cikinsu, da ba su kulawa ta musamman; saboda haɓaka ƙoƙarinsu, duk wannan a cikin da'irar shari'ar Musulunci.
9. Musulunci ya haramta wa iyaye biyu da ma wasunsu yin watsi da bai wa ƙananan yara kulawar da ta dace, gudun kada su bi duniya su salwanta, haka ma ya haramta yin amfani da su saboda biyan buƙatun kai, da ɗaura masu nauyi da ayyukansu da za su yi mummunan tasiri a jikkkuna da hankali da zukatansu.
10. Lallai zaluntar ƙananan yara a aƙidarsu, ko a kawunansu, ko a mutuncinsu, ko a dukiyoyinsu, ko a hankalinsu laifi ne babba.

Na biyu haƙƙoƙin tsofaffi:

Addinin Musulunci ya bai wa ɗan Adam kulawa a dukan matakan rayuwarsa, ƙarƙashin karramawar da Musulunci ya yi wa duk wani bani Adama, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai mun riga mun karrama ɗan Adam..)** [al- Isra'i: 70], Allah mai girma da buwaya yana cewa: **(Lallai Ubangijinka ya riga ya hukunta cewa kada a bauta wa kowa sai shi, su kuma iyaye a kyautata masu..)** [al- Isra'i: 23]. Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Babu wani matashin da zai girmama tsoho saboda yawan**

shekarunsa, face Allah ya samar masa da wanda zai girmama shi a lokacin da ya tsufa) [al- Tirmiziy], haka ma yana cewa: **(Wanda duk bai ji tausayin ƙaramin cikinmu ba, bai kuma san daraja da girman babban cikinmu ba, to lallai ba shi daga cikinmu)** [al- Tirmiziy, da Ahmad a cikin Musnad]; saboda haka cibiyar ta tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

1- Wayar da kan tsofaffi akan abin da zai taimaka masu wajen kiyaye lafiyar jikkunansu da na ruhi da na zamantakewa, da kuma cigaba da sanar da su hukunce- hukuncen addini da suke buƙata wajen gudanar da ibada da mu'amala da halayensu, da kuma ƙarfafa su wajen kyautata dangantaka da Ubangijinsu, da kyautata masa zato wajen samun afuwarsa da gafararsa.

2- Ƙara tabbatar da muhimmancin zamantowar tsofaffi mambobi a cikin al'umma, da kuma irin yanda suke da cikakkun haƙƙoƙin ɗan Adam a ciki.

3- Gidajensu cikin iyalansu su ne asalin wurin da ya kamata su rayu, saboda su ji daɗin rayuwa a cikin iyalai, 'ya'yansu da jikokinsu suna yi masu biyayya, suna kuma jin daɗin sada zumunci da makusantansu da abokansu da maƙwabtansu, idan ba su da iyalai, to lallai ya kamata a samar masu da wani yanayi irin na iyalai a gidan kulawa da tsofaffi.

4- Wayar da kan al'umma game da muhimmancin tsofaffi, da kuma haƙƙoƙinsu ta hanyar manhajojin karantarwa, da shirye- shirye aikin jarida, a kuma muhimmanya biyayyar 'ya'ya ga iyayensu.

5- Samar da gidajen kulawa da tsofaffi ga waɗanda ba su da waɗanda za su kula da su, ko waɗanda iyalansu sun gaza yi masu haka.

6- Muhimmanta harkar likitancin tsofaffi a tsangayoyin likitanci da cibiyoyin lafiya, da bai wa wasu daga cikin likitoci horo akan gano cutar tsufa, da kuma yi

wa tsofaffi magani, da samar da sassa na musamman domin magance matsalolin tsufa a asibitoci.

7- Samar da gujeru ga tsofaffi a hanyoyin sufuri da zirga- zirga, da wuraren shaƙatawa da al'umma, da tashohin motoci da sauransu, domin kula da su.

8- Aiki da sanarwar Kuwait game da haƙƙoƙin tsofaffi.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 114 (8/12)
BAYANIN MUSULUNCI GAME DA RAWAR DA MACE ZA TA TAKA WAJEN CIGABA DA HAƁAKA AL'UMMAR MUSULMAI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta duba wasicin taron ƙwararru game da rawar da mace take takawa wajen cigaba da haɓaka al'ummar Musulmai da aka gudanar a Tehran na Jamhoriyar Musulunci ta Iran a ranakun 17 zuwa 19 ga watan Zulƙida, 1415 H, waɗanda suka yi daidai da 17 zuwa 19 ga watan Afrilu, 1995, daidai da ƙuduri mai lamba 10/7- S (Ƙ. A) da ya zo daga taron ƙolin ƙasashen Musulmai, wannan dai wasicin da aka yi wa gyara a sashen bayar da fatawa a taron cibiyar na tara da na goma,

Da ƙara tabbatar da babban matsayin da Musulunci ya kewaye mace da shi, waɗanda tarurrukan duniya da aka yi akan mace da suka ci karo da shi, musamman taron Alƙahira da na Beijing, da waɗanda suka biyo bayansu, ƙarƙashin bayanan Musulunci da suka zo domin

ƙalubalantar waɗannan munanan yunƙuri, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Lallai a cikin manufofin addinin Musulunci akwai gina al'umma ta yanda kowane namiji da kowace mace za su taka cikakkiyar rawar da ya kamace su wajen gina al'umma da samar da ayyukan raya ƙasa, lallai Musulunci ya bai wa mace cikakkun haƙƙoƙinta da suka yi daidai da irin yanda Allah ya halicce ta, da kuma irin iko da ƙarfi, da kuma ɗabi'ar da take da su da za su ba ta daman gabatar da muhimmiyar gudummuwarta a rayuwa. A mahangar addinin Musulunci, ana gina al'umma da rayuwar zamantakewar ne akan wani abu da yake a haɗe, ta yanda namiji da mace za su yi taimakekeniya a dukan fagage, Alƙur'ani mai girma da Hadisan Annabi sun tabbatar da haɗin kan al'ummar Musulmai a matsayinsu na abu guda ɗaya, da yake da sassa masu matuƙar muhimmanci, saboda haka, kowanne daga cikin mace da namiji suna da sifofinsu, da kuma matsayinsu a cikin al'ummar Musulmai.

Na biyu: Iyalin da aka gina samuwarsa akan halataccen aure da Shari'a ta amince da shi, shi ne tobalin gina nagartacciyar rayuwar zamantakewa, saboda haka Musulunci bai amince da duk wata hanya da ake riya cewa tana samar da iyali ba wadda ba aure ba, da ma duk wata alaƙa wadda ba wannan ba, wadda ta saɓa da shari'. Lallai mace –a matsayinta na uwa, da kuma wasu sifofi da ta keɓanta da su- tana da babbar gudummuwa da za ta bayar wajen samar da kwanciyar hankali da arzikin wannan gini na rayuwar iyali.

Na uku: Lallai zama uwa, ɗaya ne daga cikin muhimman ayyukan mace a rayuwa, ba kuma za ta taɓa iya gabatar da wannan muhimmin saƙo mai daraja Kaman yanda ya kamata, ta kuma gina al'umma mai tasowa ba, sai idan ta sami dukan haƙƙoƙinta na Musulunci, saboda ta gabatar da ayyukanta a fagagen rayuwa da ta keɓantu da su.

Na huɗu: Mace da namiji daidai suke da juna a wajen karamar ɗan Adam, kaman yanda mace take da haƙƙoƙi, akwai kuma wajibai da suke akanta waɗanda suka yi daidai da halittar da Allah ya yi mata, daidai da iko da halittarta, haka ma dukan namiji da macen suna da sifofi na ɗabi'a da suke da bambanci da juna, amma dukansu a haɗe suna cika juna ne wajen ɗaukan alhaki da Allah ya ɗaura wa kowannensu a Shari'ar Musulunci.

Na biyar: Kira zuwa ga mutunta mace a dukan fagage, da kuma rashin amincewa da zaluncin da har yanzu take fuskanta a wasu garuruwa, ciki har da zaluncin da ke yi mata a cikin gida, da yin amfani da su domin biyan buƙatu na jinsi, ko ɗaukan hotunan tsaraicinsu, ko karuwanci, da yin yi fasa- gwafrinsu, da tirsasa masu wajen alaƙa kaman yanda ake gani a wasu al'umma da aka sansu da wulaƙanta ce, da tozarta karamarsu, da inkarin haƙƙoƙinsu da shari'ar Musulunci ta ba su, duka waɗannan abubuwa ne aka cusa su da ƙarfin tsiya babu ruwan Musulunci da su.

Na shida: Hanyoyin sadarwa da kafafen yaɗa labarai su ƙarfafa da bayyana gudummuwa mai amfani da mace za ta bayar, da kuma rashin amincewa da dukan hanyoyin yin amfani da mace da ake yi wajen tallace- tallace, da kuma farfaganda masu muni da suke kai wa zuwa ga lalata kyawawan ɗabi'u, waɗanda dukansu a ƙarshe cin mutunci da ƙasƙantar da darajar mace ne.

Na bakwai: Ya kamata a gabatar dukan ƙoƙarin da ya dace wajen rage wa mata raɗaɗin da suke fuskanta, musamma masu rauni daga cikinsu, musamman mata Musulmai da har yanzu su ne waɗanda rikice- rikice da yaƙe- yaƙe, da mulkin mallaka da talauci da matsin rayuwa na tattalin arzikin da suka zo daga ƙasashen ƙetare suka ritsa da su.

Na takwas: Lallai samar da cikakkun ayyukan raya ƙasa kuma masu ɗaurewa abu ne da ba zai yiwu ba sai idan an gina su ne akan ƙa'idojin addini da na kyawawan ɗabi'u,

wannan yana nufin cewa dole ne a yi watsi da duk wani yunƙuri na wajabta wasu ma'anoni na baƙin al'adu da rayuwar zamantakewa da ta saɓa da tamu, a kuma yi tir da Allah wadai da wannan hari da wasu suke yi wa ma'anoni da hukunce- hukuncen Musulunci da suke shafi mata.

Na tara: Nuna rashin amince da salon da wasu gwamnatoci suke bi na hana mace Musulma bin addininta da kuma gabatar da ayyukan ibada da Allah ya farlanta mata, kaman kunya da sanya hijabi.

Na goma: Aiki tuƙuru wajen samar da cibiyoyin ilimi na mata a dukan matakai da za su zamo an raba su da cibiyoyin ilimi na maza, saboda a bai wa mata cikakkun haƙƙoƙinsu da shari'a ta ba su, wanda kuma yin hakan ne aiki da Shari'ar Musulunci.

Na goma sha ɗaya: Lallai Shari'ar Musulunci –ta hanyar manya asalinta- ita ce za a koma zuwa gare ta domin fassara, ko ƙarin haske akan dukan dokokin da suke cikin wannan bayanin.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 115 (9/12)([1])
GAME DA HAUHAWAR FARASHIN KAYAN BUƘATU (INFLATION) DA SAUYI DARAJAR TAKARDAR KUƊI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta duba bayanin bayan taron ƙara wa juna na Fiḳihun tattalin arziki domin nazari akan mas'alolin hauhawar farashin kayayyakin buƙatu (da aka gudanar hau sau uku: Jidda, da Kuala Lampur, da al- Manama), da wasicinsu, gami da shawarwarin da suka bayar, bayan kuma ta saurari tattaunawar da ta gudana tsakanin mambobi da ƙwararru, da kuma wasu daga cikin masana Fiḳihu akan wannan maudhu'i, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Tabbatar da cigaba da aiki da ƙudurin da ya gabata mai lamba 42 (4/5), wanda ya bayyana cewa:

(Abin da za a yi la'akari da shi wajen biyan basussukan da suka tabbata da wani nau'i na takardun kudi shi ne kwatankwacinsa ba ƙimarsa ba, saboda shi bashi ana biyansa ne da kwatankwacinsa, bai halatta a haɗa

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha biyu, 4/10, da fitowa ta biyar, 3/1609).

basussukan da suka hau kan zimma da darajar farashi ba, ko mene ne kuwa ya kai zuwa ga bashin).

Na biyu: Zai yiwu a kula, a kuma ɗauki matakai a lokacin da za a ƙulla yarjejeniyar bayar da bashi ba da takardar kuɗin da ake tunanin farashinta zai faɗi ba, a ƙulla yarjejeniyar bashin da abubuwa masu zuwa:

a. Zinare ko azurfa
b. Hajar da take da kwantankwaci
c. Jerin wasu hajojin da suke da kwatankwaci
d. Wata takardar kuɗin da ta fi tabbas
e. Jerin wasu takardun kuɗi da suka fi tabbas

Dole ne abin da za a biya bashin da shi a surorin da suka gabata ya zama irin abin da aka basa ne, domin babu abin da yake akan wanda ya yi bashi sai abin da ya basa a haƙiƙa.

Wannan yanayin ya saɓa da yanayin da aka hana, wanda masu ƙulla yarjejeniyar bashi na nan take da wani takardar kuɗi, tare da sanya sharaɗin cewa za a biya ne da wata takardar kuɗi ta daban (a haɗe ta da wannan takardar kuɗin), ko da jerin wasu takardun kuɗi da suka fi tabbas, lallai an hana irin wannan sura da ƙudurin cibiya mai lamba 75 (6/8) na huɗu.

Na uku: A shari'a sam bai halatta a haɗe tsakanin bashin nan take da ɗaya daga cikin abubuwa masu zuwa a lokacin ƙulla yarjejeniyar bashi ba:

a) Ɗaure shi da takardar kuɗi na lissafi (artificial currency).
b) Ɗaure shi da alƙalumman wahalhalun rayuwa, ko waninsa na alƙalumma da hasashe.
c) Ɗaure shi da zinare ko azurfa.
d) Ɗaure shi da farashin wata ayyananniyar haja
e) Ɗaure shi da hauhawar tattalin arzikin ƙasa
f) Ɗaure shi da wata takardar kuɗi ta daban
g) Ɗaure shi da hauhawar farashin wasu jerin kayayyaki

Saboda irin wannan hadin cike yake da rudu, da kuma mummunar jahiltar abin da zai faru, ta yanda babu wane sashe da ya san abin da yake akansa da kuma hakkinsa, daga nan sharadin sani ya sami tangarda kenan, haka nan idan wadannan abubuwa da aka hade suna kara hauhawa, hakan zai kai ga rashin samun daidaito tsakanin abin da yake akan wanda ya yi bashi, da abin da zai biya, kuma an shardanta a wurin kulla yarjejeniya, da haka ya zama riba kenan.

Na huɗu: Hade albashi da kudin haya da kimar kudi([1]):

a- Kara tabbatar da yin aiki da kudurin majalisar cibiya mai lamba 75 (6/8) sakin layi na: Na Farko Ya halatta a "daure albashi da kima", daidai da sauye- sauyen da aka samu a farashi.

b- Ya halatta a haya mai dogon zango na wasu abubuwa, inda za a bayyana kudin hayar zuwa wani lokaci na farko, da kuma bayyana cewa za a daure kudin hayar da wani alkalami a lokuta masu biyowa, da sharadin sanin gwargwadon kudin hayar a farkon kowane lokaci.

Cibiyar tana bayar da wasici mai zuwa:

1. Ganin cewa babban dalilin hauhawar farashin kayayyakin bukatu shi ne kara yawan takardun kudade da hukumomin gwamnati da abin ya shafa suke yi saboda dalilai masu yawa kuma sanannu, muna kira zuwa ga wadannan hukumomi da su yi

([1]) Ma'anarsa ita ce: Cikon da ake gabatarwa a albashi ko kudin haya a duk sanda farashin kudi ya fadi, ana kuma yin haka ne saboda a bai wa kimar albashi, ko fansho, ko kudin haya, ko haraji kariya, misalign haka shi ne: Idan dan kwadugo, ko ma'aikaci ya kulla yarjejeniya akan aiki na tsawon shekaru biyu, akan cewa duk wata za a ba shi Naira dubu dari, sai akan sami fadin darajar kudi bayan ya yi shekara yana wannan aiki, inda abin da yake saye da Naira dubu dari yanzu ba zai samu ba sai ya biya Naira dubu dari da talali misali, anan kimar kudin ya fadi da kaso 30% kenan, to a irin wannan yanayi ba Naira dubu dari za a cigaba da ba shi a duk wata ba, maimakon haka albashinsa na wata zai koma Naira dubu dari da talatin ne har tsawon wannan shekarar, da sharadin ba a sake samun matsalar faduwar darajar kudi sama da yanda yake a baya ba.

aiki tuƙuru wajen kawar da waɗannan dalilai da suka kawo hauhawar farashin kayayyakin buƙatu, waɗanda suke matuƙar cutar da al'umma, su kuma nesanci sanya tallafi, shin a wajen da kasafin kuɗi ya gaza ne, ko kuwa a cikin manyan ayyukan raya ƙasa. A kuma daidai wannan lokacin muna yi wa al'ummar Musulmai nasihar yin riƙo da ɗabi'un Musulunci wajen kashe kuɗaɗen buƙatu na yau da kullum, saboda mu nesanta al'ummarmu ta Musulmai daga dukan nau'o'in almubazzaranci da ɓarna, waɗanda suke a matsayin misalan da suke haifar da hauhawar farashin kayayyakin buƙatu.

2. Ƙara taimakekeniya na tattalin arziki tsakanin ƙasashen Musulmai, musamman a fagen kasuwancin ƙasashen waje, da kuma yin aiki tuƙuru wajen mayar da kamfanonin waɗannan ƙasashe su kwafe makwafin kamfanonin da suke shigo da kayayyaki daga ƙasashen ƙetare masu manyan masana'antu, da kuma ƙarfafa matsayarsu wajen tattaunawa da daman yin gogayya a ƙasashe masu ƙarfin masana'antu.
3. Bankunan Musulunci su gudanar da bincike da nazari domin sanin abubuwan da hauhawar farashin kayayyaki yake bari a cikin kayayyakin da suka mallaka, su kuma kawo shawarwari game da hanyoyin da suka dace a yi amfani da su wajen kiyaye kawunansu, da kiyaye masu ajiya da masu kasuwanci a wurinsu daga waɗannan tasiri. Haka ma da nazari gami da sabunta ƙa'idojin bibiya da lissafi yanayin hauhawar farashin kayayyakin buƙata a manyan cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci.
4. Gudanar da nazari akan faɗaɗa amfani da hanyoyin bayar da tallafi da na kasuwancin Musulunci akan hauhawar farashin kayayyaki, da tasirin da zai yiwu su kawo sauyi a hukuncin Shari'a.

5. Gudanar da nazari akan amfani da yiwuwar dawowa ɗaya daga cikin halin da ake ciki na ɗaure tsakanin takardun kuɗaɗe da zinare, a matsayin salon nesantar hauhawar farashin kayayyaki.
6. Gane cewa ayyukan raya ƙasa ta hanyar sana'anta abubuwan buƙata, da ƙara ƙarfafar kamfanoni a aikace ɗaya ne daga cikin muhimman dalilan da suke yaƙi da hauhawar farashin kayayyaki a matsaki matsakaicin zango da dogon zango, saboda haka ya kamata a yi aiki tuƙuru wajen ƙara yawan abubuwan da ake sana'antawa a cikin gida, da kuma ƙara inganta da su a ƙasashen Musulmai, za a yi hakan ne ta hanyar samar da tsare- tsare, da ɗaukan matakan da za su bayar da ƙarfin gwiwar samar da adana, da kuma kasuwanci, ta yanda zai yiwu a samar da ayyukan raya ƙasa masu ɗaurewa.
7. Kira zuwa ga hukumomin ƙasashen Musulmai na su yi aiki tuƙuru wajen samun daidaito a kasasfin kuɗaɗensu na bai ɗaya (da suka haɗa da dukan kasafin shekara- shekara, da na ayyukan raya ƙasa masu haɓaka, da masu zaman kansu waɗanda suke dogara da asusun gwamnati wajen ɗaukan nauyinsu), ta hanyar matse bakin aljihu wajen kashe kuɗaɗe, da kuma fuskantar da kuɗaɗen a wurarem da addinin Musulunci ya amince.

   Idan har kasafin ko asusun yana buƙatar a tallafa masa, to mafita ita ce: yin riƙo da hanyoyin da addinin Musulunci ya amince da su, waɗanda suka dogara akan tarayya, da siye da sayarwa da haya, kuma dole ne a nesanci bayar da bashi da ruwa (riba), sawa'un a bankuna da cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe ne, ko kuma ta hanyar samar da shahadun bayar da bashi.
8. Bayar da kulawa ta musamma ga ƙa'idojin shari'a a lokacin da za a yi amfani da hanyoyin siyasar kuɗaɗi, sawa'un waɗanda suke da jiɓi da sauya hanyoyin

shigar kuɗaɗe ne, ku kuma waɗanda suke da jiɓi da hanyoyin kashe kuɗaɗen ga al'umma, za a yi haka ne ta hanyar samar da waɗannan siyasar akan ƙa'idojin adalci da masalahar al'umma ta bai ɗaya domin amfanar ɗaukacin al'umma, da bai wa talakawa kulawa ta musamman, da ɗauke wa ɗaiɗaikun mutane nauyi da wahalhalun samar da kuɗaɗen shiga, kowa daidai da gwargwadon samunsa, da suka haɗa da abin da yake shigo masa, da abin da yake da shi.

9. Wajibcin yin amfani da dukan hanyoyin da shari'a ta amince da su wajen samar da sisayar kuɗi, da hanyoyin gamsarwa ta hujja, da sisayas tattalin arziki da na gudanarwa, saboda a yi aiki wajen tsarkake al'ummar Musulmai daga cututtukan da hauhawar farashi take haifarwa, ta yanda waɗannan siyasar za su mayar da hankali wajen cimma manufar rage hauhawar farashi zuwa mafi ƙarancin abin da za a iya.

10. Samar da lamuni da zai bai wa ƙudurorin babban banki cikakken dama da cin gashin kai wajen gudanar da al'amurran hada- hadar kuɗaɗe, ya kuma zama ya ɗauki aniyar samar da tabbas a harkar hada-hadar kuɗi, da yake da faɗuwar darajar kuɗaɗe, tare da la'akari da tuntuɓar juna tsakanin babban bankin ƙasa da hukumomin tattalin arziki, saboda a samar da manufofin ayyukan raya ƙasa na tattalin arziki da samun tabbas a siyasar tsumi da tanadi, da na kuɗaɗe, da kuma yaƙi da zaman- banza.

11. Nazari da kuma tantance manyan ayyuka, da ma hukumomin gwamnati idan har ba su samar da amfanin tattalin arziki da shi ne manufar samar da su ba, da kuma duba yiwuwar sauya su zuwa kamfanoni masu zaman kansu, da sanya su a kasuwa daidai da manhajin Musulunci, ganin cewa hakan yana da muhimmin tasiri wajen kyautata ayyukansu

da inganta su, da kuma rage nauyin kuɗaɗen da suke ja daga kasafin kuɗaɗe, abin da hakan zai bayar da gudummuwa mai kyau wajen rage hauhawar farashi da faɗuwar ƙima da darajar kuɗin ƙasa.

12. Kira zuwa ga ɗaiɗaikun Musulmai da hukumomi zuwa ga yin riƙo da tsarin Shari'ar Musulunci, da ƙa'idojinsa na tattalin arziki da tarbiyya, da na kyawawan ɗabi'u da na zamantakewa.

Wasiyya game da mafita game da hauhawar farashi da faɗuwar darajar kuɗi:

Cibiyar tana ganin a jinkirta bayani game da shawarwari da mafita da aka kawo game da hauhawar farashin da faɗuwar darajar kuɗi zuwa taron shekara- shekara mai zuwa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 116 (10/12)
GAME DA TARJAMAR ALƘUR'ANI MAI GIRMA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta duba takardar ajandar taro wanda ya ƙunshi (Tarjamar Ma'anonin Alƙur'ani mai girma), wanda babban sakateriya ta gabatar a taron ministocin Auƙaf da al'amurran Musulunci, wanda Cibiyar Sarki Fahad mai buga Alƙur'ani mai girma ta ƙaddamar game da ƙa'idoji da sharuɗɗa na musamman, da matakan da za a bi wajen tarjamar ma'anonin Alƙur'ani mai girma,

Bayan cikakken nazari, da sauraron tattaunawar da aka gabatar game da wannan maudhu'in, inda mambobin cibiya da ƙwararrunta da wasu daga cikin masana ilmin Fiḳihu suka gudanar, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Tabbatawa gami da amincewa da duka dokokin da ƙa'idoji da wannan takardar bincike game da tarjamar ma'anonin Alƙur'ani mai girma ta ƙunsa,

Cibiya tana bayar da shawarar:

- Kafa Hukumar da za ta kula da Tafsirin Alƙur'ani mai girma da ilmominsa, wadda za ta zama tana da

dangantaka da Cibiyar Sarki Fahad mai buga Alkur'ani mai girma.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 117 (11/12)
GAME DA KAFA HUKUMAR MUSULUNCI MAI LURA DA AL'AMURRAN ALƘUR'ANI MAI GIRMA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na ƙasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan nazari game da takardar ajandar taro, wanda ya ƙunshi (Kafa hukumar Musulunci mai lura da al'amurran Alƙur'ani mai girma a duniya), wanda ma'aitakar Auƙaf da al'amurran Musulunci, ta ƙasar Ƙatar ta gabatar, bayan tattaunawa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

A samar da taimakekeniya gami da aikin tarayya da tuntuɓar juna tsakanin Ma'aikatar Auƙaf da al'amurran Musulunci ta ƙasar Ƙatar, da Ma'aikatar Auƙaf da al'amurran Musulunci ta ƙasar Saudiyya, da Cibiyar Sarki Fahad mai buga Alƙur'ani mai gir da take Madina game da wannan al'amari.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki daya.

KUDURI MAI LAMBA 118 (12/12)
GAME DA AL KUDUS MAI DARAJA

Lallai majalisar cibiyar Fikihun Musulunci na duniya, da take karkashin kungiyar kasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyu, da ya gudana a garin Alriyadh na kasar Saudiyya a ranakun 25 jumada Akhir zuwa 1 ga watan Rajab, 1421 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 23 – 28 ga watan Satumba 2000.

Bayan ta duba bayanai na zalunci da shawarwarin keta da wasu jagororin Yahudawa suka yi game da Garin Kudus, an tabbatar da kuduri mai zuwa:

1- Lallai garin Kudus tana nan a matsayin wani sashe ne na akidar daukacin Musulmai a duk fadin duniya, saboda a wannan garin ne mu'ujizar Isra'i da Mi'iraji da suka zo a cikin Alkur'ani mai girma suka faru.

2- Lallai kasancewar wannan gari da ma Masallacinsa mai albarka su zama hakki ne na Musulmai daidai da Nassin Alkur'ani da bai zai lamunci kowane irin warwara ko sauyi, ko wata kwaskwarima yana nan daram, babu wani fage na samar da mafita na tsaka-tsaki game da wannan gari.

3- Lallai Masjidul Aksa mai albarka mallaka Musulmai ne su kadai, ba shi da wata dangantaka da Yahudawa, kuma dole a yi gargadi duk wanda yake son yak eta alfarmar wannan Masallaci, da daura alhakin duk wani ta'addanci da zai fuskan akan jagororin Yahudawa 'yan kama- wuri zauna. Sam bai

halatta a shiga tattaunawa da kowa akan wannan Masallacin ba, daraja da ƙimarsa ya wuce haka nesa ba kusa ba.

4- Ba zai yiwu sa sami zaman lafiya mai cike da adalci, da kuma kwanciyar hankali a yankin gabas ta tsakiya ba, sai idan an kawo ƙarshen mulkin mallakar da Yahudawa suke yi wa garin Ƙudus da Masallacinsa mai albarka, da kuma mayar da Falasɗinu zuwa ga ‘ya’yanta Falasɗinawa.

Cibiyar tana bayar da wasici da abu mai zuwa:

Kira zuwa ga shugabanni da al’ummomi a ƙasashen Larabawa da na Musulmai da su tashi haiƙan wajen bai wa wannan gari da aka ƙwata da ƙarfin tsiya, da Masallacinsa mai albarka kariya, su cigaba da tsayawa tare da ‘yan uwansu da suke zaman dako domin hana yahudantar da wannan gari, ko mayar da mas’alar garin ya zama an sanya shi a ƙarƙashin kulawar ƙasa da ƙasa, lallai duk wani yunƙuri na yahudantar da garin, ko mayar da shi ƙarƙashin kulawar ƙasa da ƙasa abu ne da ba za mu taɓa lamunta ba a cikin kowane irin yanayi.

Allah ya sa mu dace;;

KUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA SHA UKU NA MAJALISAR CIBIYAR FIKIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

KUWAIT

7 – 12 GA WATAN SHAWWAL, 1422

22 - 27 GA WATAN DISAMBA, 2001

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 119 (1/13)([1])

GAME DA KASUWANCI DA WAƘAFI DA ABUBUWAN DA YA MALLAKA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Kasuwanci da waƙafi da abubuwan da ya mallaka), wanda aka gabatar a taron cibiyar na shekara-shekara, karo na goma sha uku, bayan ta duba ƙudurin cibiyar game da waƙafi a taronta na shekara- shekara karo na hudu, bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Jinkirta duba wannan maudhu'i na (Kasuwanci da waƙafi da abubuwan da ya mallaka) saboda a fitar masa da Ƙuduri Mai Lamba musamman a taron shekara- shekara

([1]) Mujallar Cibiya, (Fitowa ta goma sha uku).

mai zuwa, saboda a sami daman gudanar da ƙarin nazari da bincike.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 120 (2/13)

GAME DA ZAKKAR KAYAN NOMA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Zakkar kayan noma), bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ba a lissafa kuɗaɗen da aka kashe wajen ban- ruwa a cikin kuɗin da za a fitar wa da zakka; saboda shari'a ta bai wa kuɗaɗen da aka kashe wajen ban- ruwa wani matsayi na musamman, a cikin gwargwadon abin da ya kai nisabin zakka.

Na biyu: Ba a lissafa kuɗaɗen da aka kashe wajen gyara ƙasa, da haƙa magudan ruwa, da ɗauko ƙasar noma a cikin nisabin zakkar noma.

Na uku: Ba a lissafa kuɗaɗen da aka sayi iri, da taki, da magungunan ƙwari, saboda a bai wa tsiro kariya da ma makamantan haka da suke faruwa a lokacin noma, idan kuɗin da manomin ya yi amfani da su nasa ne na kansa, amma idan tilas ce ta sanya ya yi ba shi saboda ba shi da shi, to ana lissafa su cikin nisabin zakka. Dalili kuwa shi ne Hadisan da suka zo daga wasu daga cikin Sahabbai, irinsu Ibn Umar da Ibn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su), wanda shi ne manomi zai fitar da abin da ya basa daga cikin amfanin gonarsa, sannan ya fitar da zakka a cikin abin da ya rage.

Na huɗu: A zakkar noma ake cire kuɗaɗen da aka yi amfani da su wajen isar da zakkar ga waɗanda suka cancanta.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 121 (3/13)

GAME DA ZAKKAR HANNAYEN JARIN DA AKA SAYA SABODA A AMFANA DA RIBAR DA SUKE SAMARWA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Zakkar Hannayen jarin da aka saya saboda a amfana da ribar da suke samarwa), bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta,

Bayan ta duba ƙudurin cibiya mai lamba 28 (3/4) game da zakkar hannayen jari a kamfanoni da ya zo a sakin layi na (Na uku), da yake cewa: (Idan kamfanin bai fitar wa dukiyarsa zakka ba saboda kowane irin dalili, to abin da ya wajaba akan masu hannayen- jari shi ne kowa ya fitar da zakka akan adadin hannayen- jarin da yake mallaka, idan ya sami daman sanin jimillar dukiyar kamfanin da zakka ya hau kan hannayen- jarin gaba ɗaya, idan ya fitar da zakkar daidai da tsarin da muka faɗi, a nan sai ya yi wa nasa hannayen- jarin zakka ta wannan fuska; saboda yin haka shi ne asali wajen fitar da zakkar hannayen- jari.

Idan kuma mai hannayen- jarin bai sami daman sanin haka ba:

To idan da ma ya saka hannun- jarinsa a kamfanin da niyyar ya amfana da ribar da hannayen- jarin za su kawo masa ne a shekara- shekara, ba wai da niyyar kasuwanci ba, to a nan zai fitar da zakka ne irin ta wanda ya sami galla, a nan kaman yanda ƙudurin da Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta duniya ta bayyana a taronta na shekara-shekara karo na biyu game da zakkar tabbatattun abubuwa da filayen haya da ba a noma ba, babu zakka akan wanda ya mallaki irin wannan hannayen- jari a asalin hannayen jarinsa; tana dai wajaba ne akan ribar da hannayen- jarin suka haifar, wato "rubu'in ushiri" bayan kewayowar shekara daga ranar da aka amshi wannan ribar, idan sharuɗɗan zakka sun cika, ba kuma a sami wani abu cikin abubuwan da suke hana yin zakka ba), an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Idan kamfunoni suna da kuɗin da zakka ta hau kansu, kaman tsabar kuɗaɗe, da kayayyakin kasuwanci da aka baje a kasuwa, da basussukan da suke akan wasu da ba a fitar masu da zakka ba, shi kuma mai hannun jarin bai san nawa ne rabonsa a cikin asusun kamfanin cikin abubuwan da za a fitar masu da zakka ba, to a nan wajibi ne ya bincika gwargwadon iko, ya fitar da zakka a asalin yawan hannayen da yake mallaka a cikin hannayen da za a fitar masu da zakka. Wannan idan kamfanin ba yana cikin wani hali na gajiyawa ba kenan, ta inda bashin da ake binsa kawai ya fi ƙarfin abubuwan da yake mallaka ba.

Amma idan kamfanonin ba su da dukiyar da zakka ta hau kansu, to a nan abin da ya zo a ƙuduri mai lamba 28 (3/4) yake akansu, ma'ana zai fitar da zakka ne daga cikin ribar da aka samu kawai, ba daga asalin hannun jarin ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 122 (4/13)

GAME DA TARAYYA MAI WARWARA([1]) A ƘARƘASHIN SABABBIN YARJENIYOYIN KASUWANCI NA ZAMANI

Lallai majalisar cibiyar Fikihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Tarayya mai warwara a ƙarƙashin sababbin yarjeniyoyin kasuwanci na zamani), bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

An jinkirta duba maudhu'in (Tarayya mai warwara a ƙarƙashin sababbin yarjeniyoyin kasuwanci na zamani), saboda a fitar masa da ƙuduri mai lamba musamman, har

([1]) Ma'anar tarayya mai warwara ita ce: Tarayyar da banki yake bai wa abokin tarayyarsa haƙƙin sayen rabonsa a cikin haɗakarsu sannu a hankali kason bankin yana raguwa, shi kuma kason abokin hulɗar yana ƙaruwa, inda a ƙarshe duka shirin zai zama mallaka na abokin tarayyar shi kaɗai.

zuwa taron shekara- shekara mai zuwa saboda a ƙara gudanar da nazari da bincike.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 123 (5/13)

GAME DA BAYAR DA BASHI KO MUDARABA HAƊIN GWIWA A CIBIYOYIN HADA- HADAR KUƊAƊE (ASUSUN KASUWANCI) (INVESTMENT ACCOUNTS)

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in: Bayar da bashi ko Mudarabar haɗin gwiwa a Cibiyoyin hada- hadar Kuɗaɗe (Asusun kasuwanci- inɓestment accounts), bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: ma'anar mudarabar haɗin gwiwa:

Mudarabar haɗin gwiwa ita ce mudarabar da masu sanya kuɗinsu saboda kasuwanci waɗanda suke da yawa – waɗanda sukansu ko ɗaya bayan ɗaya- suke miƙa wa wani mutum na ɗabi'a, ko mutum na ma'ana (kamfani) dukiyoyinsu domin ya yi kasuwanci da su. Sau da yawa akan miƙa masa daman yin kasuwanci a cikin duk abin da yake ganin cewa shi ne ya fi zama masalaha, zai kuma

yiwu a iyakance shi da wani nau'i na kasuwanci, tare da ba shi izini a fili ko a ƙunshe nay a haɗa dukiyoyinsu da juna, ko da dukiyarsa, shi kuma a wasu lokaci ya amince da yiwuwar su janye dukiyoyin nasu gaba ɗaya, ko wani sashe daga ciki idan buƙatar hakan ta taso ƙarƙashin wasu sanannun sharuɗɗa.

Na biyu: Halaccin yin mudarabar haɗin gwiwa:

Wannan mudaraba ta haɗin gwiwa ta ginu ne akan abin da malamai masana Fiƙihu suka tabbatar da halaccin yawaitar masu mallakar uwar kuɗi (jari), da halaccin shi ma mai kasuwancin ya yi tarayya da su a cikin uwar kuɗi (jari), lallai ba ta fita daga cikin surorin mudarabar da suka halatta ba idan har an kiyaye sharuɗɗa da ƙa'idojin da shari'a ta shimfiɗa game da mudaraba, tare kuma da la'akari da abubuwan da tarayyar a cikinta suke buƙata, gudun kada ta sauka akan gwadaben Shari'a.

Na uku: Ɓangarorin mudaraba:

Masu bayar da kuɗaɗensu dukansu su ne masu mallakar jari, dangantakar da take tsakaninsu –duk da mai kasuwanci idan ya haɗa da dukiyarsa- ita ce tarayya. Wanda aka damƙa masa alhakin yin kasuwanci da dukiyar shi ne mai mudaraba, sawa'un shi ɗin mutum ne na ɗabi'a, ko mutum na ma'ana, kaman kamfanoni da hukumomin hada- hadar kuɗaɗe. Dagantakar da take tsakaninsa da su ita ce mudaraba, wato bayar da kuɗi, saboda shi ne yake da alhakin ɗaukan mataki da ƙudurin gudanar da kasuwanci da kuma tsare- tsaren yanda za a yi. Idan shi mai mudarabar ya bai wa wani ɓangare na uku alhakin yin kasuwancin, a nan an shiga lissafin mudaraba ta biyu kenan, tsakanin mai mudaraba ta farko, da wanda aka miƙa masa alhakin yin kasuwanci, ba wai shiga tsakani ya yi tsakaninsa da masu dukiya ba (wato waɗanda suka miƙa dukiyoyinsu domin a yi kasuwanci da su).

Na huɗu: Haɗa dukiyoyi a mudarabar haɗin gwiwa:

Babu laifi a haɗa dukiyoyin masu mallakar jari da junansu a wuri ɗaya, ko ma da dukiyar mai mudaraba,

saboda hakan yana faruwa ne da yardarsu ko dai a rubuce, ko kuma a ƙunshe, haka ma idan wanda zai yi mudarabar mutum ne na ma'ana (kamfani ko hukumomin hada-hadar kuɗi- ya yi mudarabar, ya tsattsara yanda zai yi kasuwanci babu tsoron wani daga cikinsu ya cutu, ko ya cutar, saboda an san rabo ko kason kowanne daga cikin su a cikin uwar kuɗin (jari), kuma wannan haɗawar yana ƙara ƙarfin jarin ne saboda ya ƙara faɗin kasuwancinsa, a kuma sami ƙarin yawan riba.

Na biyar: Iyakance mudaraba da wani lokaci:

A asali mudaraba ba yarjejeniya ce da ta zama tilas ba, ya halatta ga kowa daga cikin ɓangarorinta ya rusata. Amma akwai hali ko yanayi guda biyu da wannan haƙƙi na rusa mudaraba yakan kau, waɗannan halaye ko yanayi su ne (1) Idan mai mudaraba ya fara gudanar da aiki, inda anan wannan mudarabar za ta zama tilas ne ta cigaba har zuwa lokacin kayan za su zama kuɗi da za a iya cire wa kowa haƙƙinsa a haƙiƙa ko a shari'ance ta hanyar kotu, (2) idan masu mallakar dukiyoyi, ko mai mudarabar ya ɗauki alƙawarin rashin rusata a tsawon wani lokaci, to ya kamata a cika wannan alƙawari, saboda saɓa wannan alƙawarin zai gurgunta harkar kasuwancin a cikin wannan lokacin.

Na shida: Yi wa mudaraba lokaci:

A shari'a babu laifi a yi wa mudaraba lokaci ta hanyar yin ittafaƙi tsakanin ɓangarori biyu, ta yanda za ta ƙare idan lokacin ya yi, ba tare da buƙatar wani sashe ya nei a warware ta ba, tasirin wannan sanya lokacin yana taƙaita ne akan hana shiga wani sabon kasuwanci bayan lokacin ya ƙare, amma hakan ba zai hana a ƙara lokaci har a sauran kayan kasuwancin da ake yi ya ƙare ba.

Na bakwai: Raba riba ta hanyar (Nimar)([1]) a mudarabar haɗin gwiwa:

([1]) Rabon ribar mudaraba ta hanyar Nimar yana nufin: yin amfani da hanyoyi biyu wajen sanin kason kowanne daga cikin waɗanda suka saka dukiyoyinsu a cikin mudaraba, ciki har da mai gudanar da kasuwanci idan shi ma ya sanya dukiyarsa a ciki, hanyoyin kuwa su ne: yawan dukiyar da

Shari'a ba ta hana a yi amfani da hanyar Nimar wajen raba rib aba, hanyar da take la'akari da yawan dukiyar da kowanne ya zuba, fa kuma tsawon lokacin da dukiyar ta yi a cikin kasuwancin, saboda duka dukiyoyin masu zuba jarin a haɗe ne suka bayar da gudummuwa wajen samar da ribar, daidai ya yawansu, da kuma tsawon lokacin da suka ɗauka, saboda haka dukiya da lokacin su sami wani kaso shi ne abin da ya fi zama adalci wajen isar fa dukiyoyinsu zuwa gare su, kuma lallai samun masu zuba jarin su shiga cikin wannan kasuwanci na mudarabar haɗin gwiwa kawai yana nufin sun yafe wa juna abubuwan da zai yi wahala a iya cimma su, haka ma a cikin ɗabi'ar mudaraba dole ne abokin tarayya ya amfana da ribar dukiyar abokin tarayyarsa, a wannan hanya babu abin da yake yanke yin tarayya a wajen riba, hasali ma an riga an yarda da ribar ta zama tasu ce su duka.

Na takwas: Kafa kwamitin sa- kai domin kiyaye haƙƙoƙin masu uwar kuɗi (Kwamitin masu zuba jari):

Ganin cewa masu zuba jari suna da haƙƙoƙi akan mai kasuwancin waɗanda suke ƙunshe a cikin sharuɗɗan da ya sanar, suka kuma amince da su, waɗanda akansu ne suka shiga cikin wannan mudaraba ta haɗin gwiwa, to lallai babu laifi idan suka zaɓi wasu daga cikinsu suka kafa su a matsayin kwamitin sa- kai da za su yi aiki domin kiyaye waɗannan haƙƙoƙin, da sanya ido wajen zatar da sharuɗɗan mudaraba da aka yi ittifaƙi akansu, ba tare da sun yi katsalandan a cikin matakan da yake ɗaukan na gudanar da kasuwanci ba, sai dai ta hanyar bayar da shawara, wadda ita ma a dole ne mai kasuwancin ya yi aiki da ita ba.

Na tara: Sakataren kasuwanci:

Abin da ake nufi da sakataren kasuwanci shi ne: banki ko cibiyar hada- hadar kuɗaɗe da take babban matsayi a

ya sanya, da kuma tsawon lokacin da dukiyar ta yi a cikin kasuwancin mudarabar.

wajen jerin bankuna ko cibiyoyin kuɗaɗe, take kuma da ƙwarewa da ƙarfin jari, wanda ake sallama masa dukiya da takardun abubuwan da ake da su, saboda ya zama lamuni kuma amintacce akansu, saboda a hana mai yin kasuwanci yin gaban- kansa ta yanda zai saɓa wa sharuɗɗan da aka shimfiɗa wajen yin kasuwancin mudaraba. Lallai shari'a ba ta hana yin haka ba, da sharaɗin hakan ya zama yana nan a rubuce a tsarin gudanar da cibiyar, da na mai kasuwancin, saboda masu zuba jarin su zama suna sane da haka, shi ma da sharaɗin cewa sakataren kasuwancin ba zai yi katsalanda a ciki matakan da mai kasuwancin yake ɗauka wajen gudanar da kasuwancinsa ba, aikinsa kawai zai taƙaita ne akan kiyayewa, da kuma tabbatar da an yi aki da sharuɗɗan kasuwancin na shari'a da na gudanar da aiki.

Na goma: Sanya ribar da aka hasashe a mudaraba da ƙarfafa gwiwar mai kasuwanci:

Shari'a ba ta hana a samar da hasashe akan ribar da ake tunanin samu ba, a kuma rubuta shi a rubuce akan cewa idan ya wuce haka mai kasuwancin yana da wani ƙarin kaso akan wannan ƙarin. Wannan ana yinsa ne bayan an iyakance ribar kowane ɓangare a cikin wannan ribar.

Na goma sha ɗaya: bayyana wanda yake kasuwancin idan mutum na ma'ana (banki ko kamfanin hada- hadar kuɗaɗe) ne yake gudanar da mudarabar:

Idan gudanar da kasuwancin mudaraba yana hannun mutum ne na ma'ana, kaman bankuna, ko kamfanonin hada- hadar kuɗaɗe, to mai kasuwancin anan shi ne mutum na ma'ana, ba tare da la'akari da kowane sauyi a cikin babban zaurensa, ko majalisar gudanarwa, ko majalisarsa ta zartarwa ba, babu wani tasirin da zai shafi masu zuba jari a mudaraba idan an sami sauyi a cikinsu, matuƙar dai sun yi daidai da tsarin da aka sanar, wanda akansa ne suka amsa suka shiga cikin wannan mudaraba ta haɗin gwiwa, haka ma mudaraba ba za ta tasirantu da haɗewar mutum na ma'ana da yake gudanar da ita, da

wani mutum na ma'anan idan suka zama abu ɗaya ba. idan ɗaya daga cikin sassan mutum na ma'ana ya koma cin – gashin- kansa, ya zama shi ma yana da nasa sifar ta mutuntaka ta ma'ana da ta saɓa da ta farko, to a nan ya halatta masu zuba jari su fita daga cikin wannan mudarabar, koda kuwa lokacin da aka ɗiba masa bai yi ba.

Ganin cewa shi mutum na ma'ana yana gudanar da mudaraba ne ta hanyar ma'aikatansa, to shi ne zai ɗauki alhakin haƙƙoƙinsu, kaman yanda shi ne zai ɗauki dukan kuɗaɗen da aka kashe ba a kai tsaye ba, domin zai kwafe makwafinsu ta hanyar rabonsa da zai samu a cikin riba. Babu abin da mudaraba za ta ɗauka sai kuɗaɗen da aka yi amfani da su kai- tsaye, da kuma kuɗaɗen abubuwan da ba su zama dole akan mai kasuwanci ya yi su ba, irin waɗanda zai nemi taimakonsu waɗanda ba su cikin ma'aikatansa.

Na goma sha biyu: Lamuni a mudaraba, da hukuncin lamunin mai mudaraba:

Mai kasuwanci a mudaraba amini ne, ba ya lamuntar hasara, ko lalacewar da za su faru, sai dai idan da gangar ya yi haka, ko kuma ya ƙi ɗaukan matakin da ya kamata, ko ya saɓa wa sharuɗɗan shari'a, ko na kasuwanci da aka shimfiɗa, waɗanda akansu ne akan shiga cikin wannan kasuwanci na mudaraba. A wannan hukuncin babu bambanci tsakanin mudaraba ta mutum ɗaya, da mudarabar haɗin gwiwa. Ba kuma za ta sauya ba koda an yi da'awar yin ƙiyasinta akan hayar haɗin gwiwa, ko ta hanyar sanya sharaɗi, ko lizimtawa. Babu laifi idan aka ɗaura lamuni akan ɓangare na uku daidai da yanda ya zo a ƙudurin cibiya mai lamba 30 (5/4) sakin layi na 9.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 124 (6/13)

GAME DA INSHORAR LAFIYA DA AMFANI DA KATIN ASIBITI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Bayan ta duba binciken da aka gabatar wa cibiyar game da maudhu'in (Inshorar lafiya da amfani da katin asibiti), bayan ta saurari tattaunawar da aka gudanar akan maudu'in daga mambobin cibiya da ƙwararrunta, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

An jinkirta duba maudhu'in (Inshorar lafiya da amfani da katin asibiti), saboda a fitar masa da ƘUDURI MAI LAMBA musamman, har zuwa taron shekara- shekara mai zuwa saboda a ƙara gudanar da nazari da bincike, musamman samar da sigogi da sharuɗɗa.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 125 (7/13)

GAME DA HALIN DA AKE CIKI A FALASƊINU DA MA WASU ƘASASHE

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001, tana bibiyar hali da yanayin da al'ummar Musulmai suke fuskantan a wannan zamani, sun kuma gano ƙiyayya da zaluncin da ake yi wa Musulunci da Musulmai waɗanda suke nufin isa zuwa ga manufofi guda biyu:

- Baƙanta haƙiƙanin Musulunci ta hanyar sukar aƙidar Musulmai, da jefa shakku a cikin hukunce- hukuncen shari'arsa.
- Keta alfarmar Musulmai, da ƙwace garuruwansu, da zubar da jininsu, da kuma mamaye arzikin ƙasashensu, da rusa tattalin arzikinsu.

Lallai wajibi na shari'a ya ɗaura wa masana Fiƙihun Cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya alhakin bayyana hukunce- hukuncen Shari'a da suke da jiɓi da yanayin da

Musulmai suke ciki, kuma kada malamanta su ɓoye shaidar abin da suka sani, wanda wajibi ne a bayyana shi, wannan shi ne alƙawarin da Allah ya ɗauka da malamai wajen wajibcin bayyana gaskiya da hukuncin shari'a, ya kuma haramta ɓoyeta, ya yi alƙawarin yin azaba akan haka, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Wane ne ya kai mutumin da yake ɓoye gaskiyar da ya sani a cikin littafin sa zalunci?! Da sannu Allah zai saka maku akan jayayyar da kuke kutsawa akan ɓata, lallai Allah ba mai rafkana akan abin da kuke aikatawa ba ne)** [al- Baƙra: 140]. Lallai malaman Bani Isra'ila sun cancanci la'anta da koro daga rahamar Allah ne sakamakon irin yanda suka ɓoye ilimi, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Su waɗancan da suka yi maku inkarin al'amarin addinin ku, jama'a ne guda biyu: jama'a ta Ahlul-Kitabi, waɗanda sun san gaskiya, amma suke ɓoye ta, suna sane domin taurin-kai, da kuma jama'a ta mushrikai, waɗanda zukatan su suka makance ga barin gaskiya, suka kuma riƙi gumaka a matsayin alloli koma bayan Allah. Su kuwa Ahlul-Kitabi waɗanda suka san hujjojin da suke bayyanar da gaskiyarka, sun gane cewa gaskiya tana cikin addinin ka, sannan kuma suka ɓoye waɗannan hujjojin ga barin mutane, waɗannan su ne waɗanda Allah ya kwarara masu fushinsa, ya kuma nesantar da su ga barin rahamarsa, masu addu'a ma daga cikin mala'iku da muminan mutane da aljannu suke yin addu'a akan su kan Allah ya nesanta su da rahamar sa)** [al- Baƙra: 159]. Lallai hukuncin da wannan aya ta zo da shi ya game duk wani wanda ya ɓoye abin da ya zama wajibi ya bayyana, Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Babu wani mutum da zai kiyaye ilimi, sannan ya ɓoye shi, face ya an zo da shi ranar alƙiyama da linzamin wuta)** [Ibn Majah, da ingantaccen isnadi].

Haka ma sam bai halatta a jinkirta gabatar da bayani a lokacin da ake matuƙar buƙtarsa ba, lallai a cikin mas'alolin al'umma da suke matuƙar buƙatar a yi bayani

akansu akwai mas'alar Falasdinawa, da mas'alolin da suka yi kama da haka da suke gudana a wasu daga cikin ƙasashen Musulmai.

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Lallai ƙasar Falasdinu ita ce ƙasar Masjidul Aƙsa, alƙiblar Musulmai ta farko, Masallacin Musulmai mai daraja ta uku, waɗanda ba a niƙar gari zuwa ko'ina sai wurinsu, daga nan ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi mi'iraji, ƙasa ce ta Annabawa, wannan ƙasa haƙƙi ne na ɗaukacin Musulmai. Wannan haƙƙin a gefe ɗaya kuma dole ne kuma wajibi ne Musulmai su tsaya tsayin daka wajen taimakonsa ta dukan hanyoyin da suke kamata suka kuma dace gwargwadon iko, koda kuwa 'yan yama- ɗidi da terere sun bayar da mu, koda kuwa 'yan a ci bulus sun miƙa wuya; a kowane lokaci hujja tana tare da gaskiya da ma'abota gaskiya, tana kuma fi ƙarfin zalunci da azzalumai.

Lallai malamai masana fihiƙu sun yi ijma'i akan haramci goyon bayan maƙiyin da ya ƙwace kowane irin sashe daga cikin sassan ƙasar Musulmai; saboda yin hakan tabbatar da azzalumi ɗan ta'adda ne akan zalunci da ƙwacen da ya yi, da kuma bai wa maƙiyi dagan cigaba da zaluncin da yake yi, lallai Musulunci ya wajabta wa wanda ake zalunta ya tashi tsaye ya yi gwagwarmaya ya yaƙi azzalumin da ya ƙwace masa ƙasa, har sai ya fitar da shi cikin ƙaskanci.

Na biyu: Wajibi ne gwamnatoci da al'ummar Musulmai su yi aiki tuƙuru wajen ƙwato ƙasar Musulmai da dawo da ita zuwa ga hannun masu ita, su kuma bai wa Masjidul Aƙsa kariya ga barin daudar Yahudawa da suke mamaye shi, waɗanda suke tsananin ƙin Musulunci da Musulmai tun farkon bayyanar Musulunci, kuma har zuwa wannan lokacin ba su daina yi masa makirci da maƙarƙashiya ba, musamman ganin cewa yanzu suna da ƙarfi da faɗa a ji.

Na uku: Wajibi ne akan ɗaukacin Musulmai –kowa gwargwadon yanda zai iya- su taimaka wa al'ummar Falasdinawa da rayukansu da dukiyoyinsu saboda su kare

ƙasarsu da alfarmar ƙasar, su yi gwagwarmaya da zaluncin Yahudawan sahayina, waɗanda suke kwararar da jininsu, suke kasha waɗanda ba su ji ba ba su gani ba cikin ƙananan yara da mata, da rushe gida, ta hanyar amfani da makaman yaƙi masu muni da suka haɗa da bama- bamai da roket- roket da igwa- igwa, da jiragen- saman yaƙi, a gefe ɗaya kuma ga yaƙin tattalin arziki na lalata ƙasar noma, da tunɓuke bishiyoyi, da hana shigar da kayayyakin amfani zuwa ga ƙasar Falasdinu bayan sun mata ƙawanya.

Wannan wajibcin taimakon yana kan ɗaukacin al'ummar Musulmai a matsayinsu na al'umma da gwamnatoci, lallai su Musulmai abu ne guda ɗaya, ƙaraminsu sai ya jagorance su, kalmarsu a haɗe take wajen ƙalubalantar wanda ba su ba, mumini da mumini tamkar gini ne guda ɗaya da yake ƙarfafa junansa.

Na huɗu: Wajibi ne dukan gwamnatocin ƙasashen Musulmai su yi duk abin da ya kamata a ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa, da dangantaka ta siyasa da ta tattalin arziki da sauransu, wajen daƙile duk wani goyon baya da taimakon siyasa da na soji da maƙiya suke samu.

Na biyar: Lallai kafa daula mai zaman kanta a dukan faɗin ƙasar Falasdinu, babban birninta Ƙudus haƙƙi ne na Falasdinawa, haƙƙinsu ne su kare kansu, ya kuma yaƙi maƙiyansu da dukan hanyoyin da suka dace da dokokin ƙasa da ƙasa, suka kuma yi daidai da sharafi gami da darajar Musulmi, abin alfahari Musulmi yam utu ta hanyar shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah.

Cibiyar tana wa ɗaukacin al'ummar Musulmai, gwamnatoci da 'yan ƙasa wasici da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Riƙo da Aƙida gami da Shari'aaddinin Musulunci:

Lallai wahalhalu da bala'o'in da matsaloli da yaƙe-yaƙen da suka faru da Musulmai babban dalilin faruwarsu shi ne nesantar aƙida da Shari'ar Musulunci da suka yi, kuma su ne shiriyar Allah da ambatonsa, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Wanda kuma duk ya kawar da**

kai ga barin shiriyar Allah da yi masa biyayya, to kuwa lallai zai rayu ne rayuwa mara jin daɗi, ba zai gamsu da abin da Allah ya raba ya ba shi ba, ba kuma zai sallama wa hukuncin Allah da ƙaddararsa ba..) [Taha: 124]. Lallai tsawon lokacin da aka ɗauka ana nesantar shari'ar Musulunci shi ne yake ƙara samar da tazara gami da ɓaraka tsakanin gwamnatoci da al'ummarsu, yake kuma ƙara yawan ijtihadin da ake yi akan kuskure, shi ne kuma yake da alhakin ɓatar da ɗaiɗaikun mutane gami da al'umma suke yawan yi a wurin tunani da rayuwa.

Lallai cibiyar tana ƙara ƙarfafa wasiyyar da ta yi a taron ta na shekara- shekara karo na bakwai, inda take kiran gwamnatoci a ƙasashen Musulmai da su yi aiki tuƙuru wajen bai wa aƙida da shari'ar Musulunci kariya, da kuma bai wa tsaftatacciyar shari'a daman yin aiki a cikin rayuwar al'umma, da kuma yin gargaɗi akan duk wani abu da zai kai zuwa ga rushe ta, ko ya sanya shakku a asalinta, ya kuma kai zuwa ga rarrabuwar kawunan Musulmai ta yanda za su zama masu gaba da ƙiyayyar juna.

Haka ma cibiyar tana ƙara tabbatar da abin da ya zo a cikin wannan wasiyya na kiran gwamnatoci ƙasashen Musulmai zuwa ga: (Aiki tuƙuru wajen aiwatar da Shari'ar Musulunci, su kuma yi aiki da ita wajen shata manhajin dangantakarsu ta siyasar cikin gida da na ƙasashen waje).

Na biyu: Taimakon Musulmai:

Musulmai a duk inda suke al'umma ce guda ɗaya, aƙidar kaɗaita Allah ta haɗa su, shari'ar Musulunci kuma ta kusanta su da juna, alƙiblarsu ɗaya ce, su ɗin kaman gangan jiki ɗaya ne da idan wani sashe ya koka, dukan jikin zai koka, kaman yanda bayanin hakan ya zo daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), saboda haka taimakon junansu wajibi a kowane wuri da aka zalunci wasunsu, ko aka keta alfarmar ƙasarsu, ko wani bala'i ya auka masu, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **(Muminai maza da mata dukansu masoyan juna ne,**

kuma masu taimakon juna; sakamakon imanin da suka yi, suna bayar da umurnin aikata abin da addininsu na gaskiya ya bayar da umurni, suna kuma hana aikata abubuwan da addini bai yarda a aikata ba) [al- Tauba: 71], haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba ya zaluntarsa, ba kuma ya bayar da shi, duk wanda ya tsaya wajen biyan buƙatar ɗan uwansa, Allah zai tsaya masa wajen biyan buƙatarsa, duk wanda ya yaye wa Musulmi baƙin ciki, Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙin cikin ranar alƙiyama)** [Muslim: 1830].

Taimako ana yinsa ne da rai da dukiya, da kuma ƙarfafawa da goyon baya na ma'ana da na siyasa da sauransu, daidai da dama da yanayin da aka sami kai a ciki, shi kuma yanaya abu ne da ya sassauyawa.

Cibiyar tana ƙara tabbatar da wasiyyar da ta yi a taron shekara- shekara karo na bakwai, inda ta roƙi ƙasashen Larabawa da na Musulunci su taimaka wa Musulman da suke fuskantar zalunci da kama- karya a ko'ina a faɗin duniya, su goya masu baya, su tunkuɗe masu zaluncin da aka yi masu da dukan hanyoyin da za su iya.

Na uku: Haramta zalunci a Musulunci:

Lallai Musulunci ya haramta zalunci ba tare da haƙƙi ba, irinsu razana waɗanda ba su ji ba ba su gani ba, mutanen da shari'a ta haramta zubar da jininsu, kowane irin zaluncin da yake wannan babin nau'i ɗaya daga cikin nau'o'in ta'addanci da shari'a ta haramta

Lallai tattalar kayan aiki na kare kai da ƙara wa kai ƙarfi da zai sanya maƙiyi ya shiga taitayinsa abu ne da shari'a ta nema mu yi, wannan umurnin ya zo a maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **(Ya ku Musulmai, ku tattali duk abubuwan da za ku iya, na makaman yaƙi, da kayan faɗa, da dakon maƙiya a dukan kafafe, da ƙofofin gari, wajen fuskantar maƙiyanku, inda wannan tattali da dakon za su tsoratar da maƙiya Allah, da maƙiyanku cikin kafiran da suke jiran kowace irin dama domin su**

auka maku, ku ma tsoratar da wasu mutanen da ku ba ku sansu ba a yanzu, amma Allah ya sansu, saboda babu wani abu da yake iya ɓuya masa) [al- Anfal: 60].

Babu shakka duk wanda yake bai wa ƙasarsa da aka ƙwace kariya da duk abin da yake da shin a kayan ƙarfi da kare kai, to lallai yana yi halattaccen aiki ne da kuma ya zama wajibi, wannan shi ne halin gwagwarmayar da Falasɗinawa suke wajen yaƙar sahayina da suka mamaye masu ƙasa, suke kuma keta masu dukan haƙƙoƙi.

Lallai siyasar ya mowa da 'yar bora da wasu daga cikin manyan ƙasashe suke yi game da ƙadiyyar Falasɗinawa zalunci ne da yake da ƙuna, inda suke ɗauka mai haƙƙi a ƙasa, wanda yake kare kansa da ƙasarsa da mutuncinsa a matsayin ɗan ta'adda, shi kuma azzalumi maƙetaci da yake keta dukan alfarmar mutuntaka, bayan amfani da makaman ƙare- dangi da yake, da halatta zubar da jini, ya kuma yi watsi da dukan dokoki da al'adun ƙasa da ƙasa, suke ɗaukansa a matsayin mai kare kansa da ba shi da na yi!.

Haka ma zalunci ne mai matuƙar muni a sifanta Musulunci da ta'addanci, hasali ma shi addini ne na daidaito da wasaɗiyya. Haka ma zalunci ne a yaƙi wasu daga cikin ƙungiyoyin kira zuwa ga Allah da masu bayar da tallafi, da cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci a sifanta su da ta'addanci ba tare da wata hujja ko dalili akan haka ba.

Na huɗu: Kyawawan ɗabi'un Musulunci:

Lallai duniya a wannan zamanin tana matuƙar buƙatar kyawawan ɗabi'un Musulunci a halin zaman lafiya da halin yaƙi, saboda ma'aunin adalci da ta dalilinsa ne sama da ƙasa suke a tsaye a yanda suke ya mamaye ko'ina, a kuma samu a yi watsi da halin da ya zama ruwan- dare a wannan zamanin na zalunci da girman kai da ɓarna, domin babban dalilin arziki da fitintunu da ruba duniya ta zama hawa- hawa, suka kuma sanya wasu ƙasashen suka kwashe arziki da ƙarfi da ilimi, wanda Allah ya wajabta

nemansa, ya kuma aiko mazanninsa da shi, ya saukar da litattafansa saboda shi, saboda mutane su yi aiki da gaskiya da adalci a tsakaninsu, Allah Maɗaukakin sarki ya ce: **(Lallai mun aiko da manzanninmu da muka zaɓe su, muka kuma ba su wasu ḳarfafan mu'ujizozi, mun kuma saukar masu da littattafai waɗanda suke ḳunshe da hukunce-hukunce da shari'o'in addini, da ma'aunin da zai tabbatar da adalci wajen mu'amala; domin mutane su yi ta'amuli da adalci a tsakaninsu..)** [al- Hadid: 25].

Na biyar:

Lallai cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya tana jinjina ga mai girma babban sakatare ḳungiyar ḳasashen Musulmai saboda jawabinsa na tarbar baḳi mai muhimmanci da mai girma mataimakin babban sakatare mai lura da al'amurran siyasa da inda Musulmai suke a matsayin tsiraru ya gabatar, inda ya ce: (Lallai wannan taro naku na shekara- shekara mai matuḳar daraja ana yinsa a wani lokaci mai matuḳar muhimmanci, lokaci ne da ḳalubalen samuwarmu ya fi bayyana akan dukan lokutan da suka gabata, ganin cewa zaluncin da ake yi mana a yau yana barazana ne game da makomarmu, yana tura mu zuwa ga wani baḳin ḳarshe mai cike da duhu, wannan kawai ya isa ya sanya mu tsaya a sahu ɗaya a jere, mun ɗaura ɗammarar yaḳi domin bai wa wuraren ibadunmu masu tsarki kariya, mu bai wa ḳasashenmu da al'ummominmu kariya.

Lallai ga shi nan kuna ganin iya rashin ta- ido, da ruɗin da maḳiyanmu Yahudawa sahayina suke yi, da irin yanda sha'awarsu ta su zalunce mu ya kai matuḳar hauka da rashin hankali, waɗannan maḳiyan da suka sanya yankin gabas ta tsakiya gaba ɗayansa a gefen wani rami na wutar yaḳi, kuma hakan ya sanya yankin yana daf da fashewa, ga kuma irin yanda suke yaḳar Falasɗinawa yaḳi irin na ḳare – dangi, cikin wani yanayi na zalunci, da yake nuna irin yanda suke cin karensu babu babbaka, tare kuma da goyon

bayan soji da tattalin arziki da siyasa da suke samu daga wasu ƙasashe ba tare da wasu sharuɗɗa ba.

Bayan Falasɗinu haka aka kara mummunan yaƙi da wasu ƙudundunannun manufofi a ƙasar Musulmai ta Afganistan da aka sanya ta cikin ƙaƙanikayi, inda waɗanda ba su ji ba ba su gani ba cikin tsofaffi da mata da ƙananan yara suka ɗanɗana kuɗarsu.

Saboda haka, lallai bai wa al'ummar Musulmai kariya ga barin makirce- makircen da suke zuwa daga waje, sakamakon sauye- sauyen siyasar ƙasa da ƙasa yana cikin ainihin ayyukan da za ku yi a ilmance, ganin irin muhimmanci da hakan yake da shi wajen gina fahimtar al'umma, da samar da tunani da kuma ƙarfafa kishin cigaban Musulunci na asali, wanda babu yanda za a iya cire shit un daga asalinsa komin zafin duka, saboda shiryatar da ɗan Adam a fagen imani da ilimi shi ne muhimmiyar ƙadiyyar da take sama da komai, saboda hakan yana ɗamfare ne da makomar al'umma, ta wannan fuska ne muke ganin cewa wannan ƙadiyyar ta cancanci a ba ta kulawa ta musamman, a fitar da ita a matsayin aiki na musamman mai matuƙar muhimmanci, wanda akansa ake cikin cigaban al'ummar Musulmai).

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 126 (8/13)

GAME DA HAƘƘOƘIN BIL'ADAMA A MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha uku, da ya gudana a ƙasar Kuwait a ranakun 7 - 12 ga watan Shawwal, 1422 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 27 ga watan Disamba 2001.

Imanin da cibiya ta yi da cewa lallai Allah Mahalicci mai girma da buwaya shi ne ya karrama ɗan Adam, wanda wannan karramawar ce tushen duk wasu haƙƙoƙi da wajibai, ya wajabta wa ɗan Adam wasu haƙƙoƙi na Ubanginsa, wasu kuma haƙƙoƙinsa shi kansa, wasu kuma haƙƙoƙi ne na 'yan uwansa mutanen da yake rayuwa da su, wasu kuma haƙƙoƙi ne na yanayi da yake zagaye da shi, lallai kallo ɗaya na adalci ga Shari'ar Musulunci zai sanya mutum ya sami tabbacin cewa lallai addini ne da ya yi daidai da rayuwar zamantakewar al'aumma, ya kuma yi daidai da ɗabi'ar ɗan Adam da rayuwar duniya, wannan ne ya sanya ake kiran addinin Musulunci da addinin fiɗira, ana kuma kafa hujja akan haka da maganar Allah

Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **(Ka tsaya da kyau a cikin wannan addini mai daraja, fiḍ̈ra ce ta Allah da ya halicci mutane akanta..)** [al- Rum: 30]. Haḳḳoḳin bil'adama a Musulunci suna nufi wasu kyaututtuka da aka yi masa da suka samo asali da karramawar da Allah ya yi masa, ya kuma wajabta wa kowa da kowa ya mutunta su daidai da ƙa'idoji da sharuɗɗan shari'a.

Imanin da muka da abin da ɗaukacin al'ummar Musulmai suka haɗu akansa na cewa lallai Shari'ar Musulunci shari'a ce da ta yi daidai da kowane zamani da kuma kowane wuri, da kuma imanin da muka yin da haḳḳin kowace al'umma ce ta kiyaye sifofinta na al'adu da na addini da ta bambanta da saura akansu, da haḳḳin kowace al'umma na su yi hukunci da tsari ko shari'ar da suka gay a dace da su, lura da dukan abubuwan da suka gabata, lallai cibiya tana ƙara tabbatar da abubuwan da sanarwar Alḳahira game da haḳḳoḳin bil'adama a Musulunci ta ƙunsa, wadda minisitocin harkokin wajen ƙasashen Musulmai su fitar a taron ranar 14 ga watan Almuharram, 1411 H, wadda ta yi daidai da 5 ga watan Ogusta, 1990, da bayanin da ya fito daga taron ƙara wa juna sani game da haḳḳoḳin bil'adama, wanda cibiyar Fiḳihun Musulunci ta duniya ta yi a Jidda a ranakun 8 – 10 ga watan Almuharram, 1418 H, waɗ̈nda suka yi daidai da 25 – 27 ga watan Mayu, 1996.

Ganin cewa al'ummar Musulmai suna riḳo da tsare-tsaren Musulunci da shari'o'insa da son kansu, a cikin al'amurran rayuwar aure da zamantakewa, da sha'anin mata da dangantakar iyali da sauran fagagen zamantakewa da tattalin arziki. Wanda lallai sanarwar duniya game da haḳḳoḳin bil'ama da babban zauren majalisar ɗ̈inkin duniya ta fitar a shekarar 1948 sun yi daidai a mafi yawan abubuwan da suke ciki da shari'ar Musulunci, sun yi daidai a wasu daga cikin abubuwan da suka ƙunsa, da wasu daga cikin manufofi, sun kuma saɓa da juna a wasu sassa da fagage, waɗ̈anda dukansu suna

komawa ne zuwa ga kyawawan ɗabi'u da tsarin rayuwar al'umma ta suka ginu akan addinin Musulunci.

Ganin cewa Shari'ar Musulunci ta tabbatar da wasu hukunce- hukunce waɗanda suke ƙunshe da kiyaye manufofinta akan halitta, wanda muhimmai daga cikinsu ne aka fi sani da manyan manufofin Shari'a guda biyar, da haka sai ta tabbatar da jiga- jigan haƙƙoƙin bil'adama a cikin ransa, da addininsa da dukiyarsa da mutuncinsa da hankalinsa. Kaman yanda Shari'ar Musulunci ta magance nau'o'in ɓata da karkacewa masu yawa, ta hanyar ɗaukan matakan riga kafi, da na horo da nufin kiyaye rayuwar zamantakewa, da kuma kawo gyara a inda aka sami tangarɗa, duk kuwa da cewa akwai matakan riga kafi da horo a kowace shari'a, a kuma kowane zamani da wuri. Kuma hukumomi da tarurrukan na ƙasa da ƙasa masu yawa sun tabbatar da nagartar shari'ar Musulunci wajen warware matsalolin bil'adama, abin da ya sanya masu hankali su mutunta ta, su kuma fa'idanta da ita.

Ganin cewa dokokin kafa majalisar ɗinkin duniya ya bayyana cewa kowace ƙasa tana da haƙƙin shugabanci a faɗin ƙasarta na jogurafi, da hana yi mata katsalandan a cikin al'amurranta na cikin gida. Kuma lallai dokokin da suke shafi cikin gida a ƙasashe masu cikakken iko ba su a ƙasan tsare- tsare da dokokin ƙasashen ƙetare.

An tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Dole ne ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa masu aikin kare haƙƙoƙin bil'adama –duk da bambancin dokoki da tsare- tsarensu- su nesanci yin katsalandan a fagagen da shari'ar Musulunci ta tsara yanda rayuwar Musulmai za ta kasance, ba su da haƙƙin tilasta wa Musulmai yin aiki da tsare- tsarensu, ko dokokinsu da suka saɓa da shari'arsu da dokokinsu, kuma bai bai halatta sun hukunta su saboda sun saɓa da dokokin da tun asali ba su yarda da su zama dokoki a gare su ba.

Na biyu: Kafa cibiyar haƙƙoƙin bil'adama nata na kanta, an kuma ɗauki dukan matakan kafa ta da samar mata tsare- tsarenta na musamman.

Ciniyar tana wasiyya da abubuwa masu zuwa:

Na farko: Tana kira ga dukan ƙasashe, da ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa da na jinƙai da su mutunta haƙƙoƙin Musulmai a inda suke 'yan tsirari a ƙasashen duniya, da yi masu adalci, musamman a wannan lokacin da yin adalci da bai wa masu haƙƙi haƙƙinsu yake da tsananin wahala.

Na biyu: Cibiya tana bayyana cewa a shirye take ta tuntuɓi masana dokoki da ƙungiyoyi da cibiyoyin ilimi na duniya da na ƙasashe da na al'umma da dukan fahimtoci a duk inda suke; saboda a yi nazari da bincike akan hanyoyin fahimtar juna da taimakekeniya a dukan fagagen haƙƙoƙin bil'adama, akan abubuwan da za su kiyaye tsaro da adalci da arziki da ingatacciyar rayuwa, da kuma daƙile dukan ɓarna, da samar da rayuwar tare tsakanin mutane, daidai da ginshiƙan da aka ambata a sama. Takenmu a koda yaushe shi ne maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **(Lallai Allah yana umurtan bayinsa da su yi adalci a cikin maganganunsu da ayyukansu, su kuma rinƙa nufan abubuwa masu kyau a cikin dukan al'amurra, su fifita shi akan waninsa, haka ma yana ba su umurnin bai wa makusanta abubuwan da suke buƙata saboda ƙarfafa dangantaka ta soyayya tsakanin iyali, yana kuma hana aikata kowane irin laifi, musamman zunubai ma suke wuce gona da iri wajen muni, da duk wani abu da shari'o'i da lafiyayyun hankula ba su yi na'am da shi ba, haka ma yana hana zaluntar wani, da wannan Allah Maɗaukakin Sarki yana tunatar da ku ne, kuma ya kiranku zuwa ga nagartattun al'amurra a cikin al'amurranku, ko za ku tuna falalarsa wajen sanya ku a mafi kyawon haka, ku yi aiki da maganarsa)** [an- Nahli: 90]. Da maganar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da yake cewa: **(Lallai keta alfarmar jininku da dukiyoyinku da mutuncinku haramun ne akanku,**

kaman dai haramcin keta alfarmar wannan ranar, a cikin wannan watan, a kuma cikin wannan garin).

Allah ya sa mu dace;;

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA SHA HUƊU NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

DOHA (ƘATAR)

8 – 13 GA WATAN ZUL ƘIDA, 1423

11 - 16 GA WATAN JUNAIRU, 2003

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 127 (1/14)

GAME DA KATIN MUSABAƘA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: Katin musabaƙa, bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

Na farko: Ma'anar musabaƙa:

Musabaƙa wata mu'amala ce da ake yi tsakanin masu takara biyu ko sama da biyu wajen tabbatar da wani abu, ko gabatar da shi domin samun kyauta (lambar yabo), ko kuma ba tare da nufin samun kyauta (lambar yabo) ba.

Na biyu: Halaccin musabaƙa:

(1) Musabaƙa ba tare da bayar da kyauta (lambar yabo) ba, abu ne da ya halatta a cikin komai, muddin ba wani nassi ne ya zo ya haramta shi ba, kuma bai kai

zuwa ga barin abin da ya wajaba a aikata, ko aikata abin da ya haramta ba.

(2) Musabaƙa tare da bayar da kyauta ya halatta idan sharuɗɗa da ƙa'idoji masu zuwa suka samu:

(a) Manufofin musabaƙar da hanyoyin da ake bi wajen gudanar da ita da fagagen yenta su zama halattattu.

(b) Kada kyautar (lambar yabo) ta zama an samar da ita ne daga dukan masu musabaƙar.

(c) Musabaƙar ta cimma wata manufa daga cikin manufofin da shari'a take la'akari da su.

(d) Kada sanadiyyar musabaƙar a bar wani abu da ya wajaba a aikata, ko a aikata abin da ya haramta.

Na uku: Bai halatta katin musabaƙar da ƙimarsu, ko wani sashe na ƙimarsu yake shiga cikin jimillar kyaututtuka ba; saboda haka ɗaya ne daga cikin nau'o'in caca.

Na huɗu: Saye tsakanin ɓangarori biyu, ko sama da biyu akan sakamakon aikim wani a cikin wani abu da za a iya tasarrufi akansa, ko na ma'ana haramun ne; saboda ayoyi da Hadisan da suka haramta caca.

Na biyar: Biyan kuɗi akan kiran waya saboda shiga cikin musabaƙa bai halatta ba a shari'a, idan wannan kuɗin, ko wani sashe nasa yana cikin ƙimar kyaututtuka, an haramta wannan ne saboda a hana cin dukiyoyin mutane ta hanyar ɓarna.

Na shida: Ba a hana mai gabatar da kyaututtukan musabaƙa ya amfana ta hanyar tallata kayayyakinsa kawai ba –banda amfana ta kuɗi- ta hanyar halatacciyar musabaƙa, da sharaɗin kada ƙimar kyaututtukan, ko wani sashe daga ciki ya zama an amshe su ne daga masu musabaƙar; kuma kada wannan tallar ta zama yaɗa algushi da yaudara, ko ha'intar masu saye.

Na bakwai: Tashin ƙimar kyautar, ko faɗuwar na sakamakon asarar da ta biyu bayan cinye musabaƙar abu ne da bai halatta ba.

Na takwas: Katunan hotel da na kamfunan sufurin jiragen sama da ƙungiyoyi da suke bayar da points ɗin da suke samar da halattaccen amfani abu ne da ya halatta idan kyauta bayarwa ba saye ba, amma idan saye ake yi bai halatta, saboda ruɗin da yake ciki.

Wasiyya:

Cibiyar tana yi wa ɗaukacin Musulmai wasiyyar neman halal a cikin dukan mu'amalolinsu da nishaɗinsu na tunani da na talla, da kuma nesantar ɓarna da almubazzaranci.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 128 (2/14)

GAME DA HAƘƘOƘIN BIL'ADAMA DA AIKI DA ƘARFI NA ƘASA DA ƘASA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: Haƙƙoƙin bil'adama da aiki da ƙarfi na ƙasa da ƙasa, bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

(1) Musulunci ya karrama ɗan Adam a matsayinsa na ɗan Adam, ya muhimmanta tabbatar da haƙƙoƙinsa, da kiyaye alfarmarsa. Fiƙihun Musulunci shi ne fiƙihu na farko a duniya da ya gabatar da dokoki na cikin gida da na ƙasashen ƙetare da suka shafi dangantaka ta mutum da mutum a halin zaman lafiya da halin yaƙi.

(2) Ta'addanci: Shi ne zalunci da tsoratarwa da barazana na a aikace ƙiri- ƙiri ko na ma'ana da ƙasashe, ko

ƙungiyoyi, ko ɗaiɗaikun mutane suke yi waɗ an Adam a addininsa ko ransa, ko mutuncinsa, ko hankalinsa, ko dukiyarsa ba tare da wani haƙƙi ba, kuma ta dukan surorin ɓarna a bayan ƙasa.

(3) Cibiya tana ƙara tabbatar da cewa: lallai jahadi, da neman samun shahada saboda yaɗa aƙidar Musulunci da ba ta kariya, da kiyaye ƙasa ba ta'addanci ba ne, hasali ma kare muhimman haƙƙoƙi ne, saboda haka haƙƙin kowace al'umma ce da ake zaluntarta, wadda take ƙarƙashin 'yan mulkin mallaka ta yi duk abin da za ta iya wajen samun 'yancin kanta ta dukan hanyoyin da take da su.

(4) Lallai bayyana ma'anonin kalmomi na musamman irinsu: kahadi da ta'addanci da aiki da ƙarfi waɗanda ake yawan amfani da su a kafafen yaɗa labarai mabambanta kalmomi ne na ilimi na musamman, sam bai halatta a yi amfani da kowace kalma ta musamman ba a abin da take nufi ba.

(5) Game da hukunci ƙunar- baƙin- wake (auka wa maƙiya duk a mutu) kuwa, majalisa tana ganin a jinkirta wannan batu zuwa taron shekara – shekara mai zuwa saboda a gudanar da bincike na musamman.

Wasiyya:

1. Cibiya tana yin wasiyya da wajibcin rubuta Babban kundin Musulunci a fannin dokokin ƙasa da ƙasa na jinƙai, irin manyan kundayen dokoki da aka saba da su, sannan a tarjama wannan kundin zuwa harsunan duniya mabambanta, a kuma sanya su a ɗakunan karatu na jami'o'i da cibiyoyi da na majalisar ɗinkin duniya, wannan shi ne abin da ya fi amfani sama da yawan maimaita cewa addinin Musulunci ba ta'addanci ba ne da muke yawan yi, kuma saboda waɗanda ba Musulmai ba su san matsayar Musulunci a fili ba tare da wani ƙudundune- ƙudundune ba.

2. Cibiya tana yin wasiyya da a kafa kwamiti na masana domin samar da yarjejeniya ta Musulunci da za ta bayyana tsarin da Musulunci ya shimfiɗa wajen yin dangantaka da waɗanda ba Musulmai ba, a kuma tarjama wannan yarjejeniyar zuwa harsunan duniya, a kuma yaɗa ta mabambanta kafafen yaɗa labarai na zamani, wannan shi ne hanyar da za a yaƙi ƙare- rayi masu tarin yawa, ta kuma bayyana haƙiƙanin Musulunci ga waɗanda ba Musulmai ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 129 (3/14)

GAME DA ƘULLA KWANGILA DA GINE- GINE: HAƘIƘANINSA, DA YANDA YAKE, DA SURORINSA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: Ƙulla kwangila da gine- gine: Haƙiƙaninsa, da yanda yake, da surorinsa, bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, tare da la'akari da hujjojin shari'a da ƙa'idojinta da manufofinta, da kuma kiyaye maslahohin al'umma a cikin ƙulla yarjejeniyoyi da ayyuka,

Lura da muhimmancin ƙulla kwangila da gudummuwarsa mai girma wajen farfaɗo da kasuwanci da masana'antu, da buɗe fagage zuba jari mai yawa, da haɓaka tattalin arzikin ƙasashen Musulmai, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

1. **Ƙulla yarjejeniyar kwangila:** Yarjejeniya ce da ɗaya daga cikin ɓangarorinta yake ɗaukan alƙawarin

sana'anta wani abu, ko aiwatar da wani aiki akan ɗayan ɓangaren kuma zai biya shi, wannan yarjejeniya ta halatta, sawa'un ɗan kwangilan ya aiwatar da aiki bayan ya samar da kayan aikin ne a tare a lokaci ɗaya, wanda shi ne malaman Fiƙihu suke kira da "al- Istisna'u", ko kuma ya aiwatar da aikin ne kawai ba tare da shi ne ya samar da kayan aikin ba, wanda shi ne malaman Fiƙihu suke kira da "al-Ijara".

2. Idan ɗan kwangila ne ya samar da kayan aiki ya kuma aiwatar da aikin, to za a yi amfani da ƙudurin cibiya mai lamba 65 (3/7) game da sana'antawa "al-Istisna'u".

3. Idan ɗan kwangilan aiki kawai ya aiwatar, to dole ne ladansa ya zama sananne.

4. Ya halatta a yi ittifaƙi wajen bayyana kuɗaɗen kwangila ta ɗaya daga cikin hanyoyi masu zuwa:

a. Ittifaƙi akan jimillar kuɗin akan takardun da aka gabatar na shirye- shiryen aiki da sifofinsa da aka bayyana dalla- dalla.

b. Ittifaƙi akan iyakance kuɗin akan kuɗin kowane sashe da aka ƙiyasta, da yawan sassan da ake da su, daidai da zanen aikin da taswiyarsa da aka gabatar da yarjejeniya akansa.

c. Ittifaƙi akan iyakace kuɗin akan kuɗin da aka sayi kayayyakin aiki na haƙiƙa, da kuma ƙarin riba a kai. A wannan halin dole ne ɗan kwangila ya gabatar da jerin kuɗaɗen kayayyakin da kyau Kaman yanda suke, dalla- dalla da sifofinsu da kukaɗensu, zai gabatar was ashen da abin ya shafa da alhakinsa ne ƙulla yarjejeniyar, inda zai zama ya cancanci a biya shi kuɗaɗen kayayyaki, a kuma ƙara masa adadin ribarsa da aka yi ittifaƙi akai.

5. Ya halatta yarjejeniyar ƙulla kwangila ta ƙunshi sharaɗin horo a cikin yarjejeniyar kwangila, daidai da yanda ɓangarorin biyu suka yi itttifaƙi, matuƙar dai

ba wani abu ne ya faru da babu yanda za a iya hana faruwarsa ba. A irin wannan yanayi za a yi aiki ne da ƙudurin cibiya da yake Magana akan sharaɗin horo mai lamba 109 (3/12).

6. Ya halatta a a jinkirta kuɗin kwangila dukansa, ko a rarraba shi ta yanda za a biya a wasu sanannun lokuta, daidai da matakan ayyukan da aka aiwatar wanda aka yi ittifaƙi akai.
7. Ya halatta a yi ittifaƙi akan shiga da wasu gyare-gyare, ko ƙare- ƙare a cikin yarjejeniyar kwangila.
8. Idan ɗan kwangila ya yi wasu 'yan gyare- gyare, ko ƙare- ƙare da izinin mai bayar da kwangila ba kuma tare da sun yi ittifaƙi akan kuɗin hakan ba, to za a bai wa ɗan kwangilar ƙimar wannan gyara, ko ƙari da ya yi.
9. Idan ɗan kwangila ya yi wasu 'yan gyare- gyare, ko ƙare- ƙare ba tare da an yi ittifaƙi akansu ba, to bai cancanci a yi masa ƙari akan abin da aka ambata ba, bai cancanci a bas hi makwafin wannan gyare- gyare, ko ƙare- ƙare da ya yi ba
10. Dan kwagila ne zai lamunci duk wani zalunci, ko wuce gona da iri, ko saɓa sharuɗɗan yarjejeniya, haka ma shi ne zai lamunci duk wani aiki ko kuskure da shi ne sanadin faruwarsa. Amma ba zai lamunci wanda mai bayar da kwangila ne ya yi sanadiyyar faruwarsa, ko kuma wanda ya faru ta wani dalili da babu mai hannu wajen zuwansa ba.
11. Idan mai bayar da kwangila ya sharɗanta wa ɗan kwangila cewa shi da kansa ne gabatar da aiki, to sam bai halatta ɗan kwangilan ya yi yarjejeniya da wani a ɓoye akan shi ne zai gabatar da aikin a maimakonsa ba.
12. Idan mai bayar da kwangila bai sharɗanta wa ɗan kwangila cewa shi da kansa ne gabatar da aiki, to ya halatta ɗan kwangilan ya yi yarjejeniya da wani a ɓoye akan ya gabatar da aikin a maimakonsa,

matuƙar manufar aikin bai wajabta shi da kansa ɗan kwangilan ne ake so ya gabatar da shi, sakamakon wani fifiko da aikinsa yake da shi akan ayyukan sauran mutane ba.

13. Dan kwangila shi ne zai ɗauki duk wani alhaki 'yan kwangilar da ya yi yarjejeniya da su a ɓoye, babu abin da zai sauya cikin alhakin da yake akansa wanda ya ɗauka tsakaninsa da mai bayar da kwangila daidai da yadda yarjejeniyar kwangila ta bayyana.

14. A yarjejeniyar kwangila sam ba za a amince da sharaɗin da zai ɗauke lamuni akan ɗan kwangila ba.

15. Ya halatta a shardanta lamuni na wani iyakantaccen lokaci.

16. Sam bai halatta a shardanta ɗauke alhakin aibobi a tsawon lokacin lamuni a yarjejeniyar kwangila ba.

Wasiyya:

Cibiyar tana yin wasiyyar gabatar da nazari akan yarjeniyoyin kwangila irin wanda ake kira da (B. O. T), wato ginawa da mallaka da gudanarwa, da kuma tashin mallaka.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 130 (4/14)

GAME DA KAMFANONIN ZAMANI: KAMFANONIN BABA- KERE DA IRE- IRENSU DA HUKUNCE – HUKUNCENSU A SHARI'A

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: (Kamfanonin zamani: kamfanonin baba- kere da ire- irensu da hukunce- hukuncensu a Shari'a), bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

Na farko: Ma'anar kamfanonin zamani:

(1) Kamfanonin dukiyoyi: Su ne kamfanonin da aka dogara da kuɗaɗen abokan tarayya wajen kafa su, ba tare da la'akari da sifofin mutanen da suka sanya jarinsu a ciki, inda inda hannayen jarinsu za su rinƙa jujjuyawa a harkoki da hada – hada. Su ma sun kasu zuwa:

(a) **Kamfanin bayar da kaso:** Shi ne kamfanin da aka rarraba jarinsa zuwa kaso- kaso da suke daidai wadaidai da juna, waɗanda ake harkoki da hada-hada da su, inda kowane abokin tarayya zai zama shi ne yake ɗaukan alhakin kasonsa da yake a cikin jarin.

(b) **Kamfanin wasici da hannayen jari:** shi ne kamfanin da jarinsa ya haɗu da hannayen jari da za a iya yin hada- hada da hulɗa da su, inda abokan tarayya a cikin suka kasu zuwa kaso biyu: abokan tarayya da suke ɗaukan cikakken lamuni da alhakin basussukan da suka kan kamfanin, da kuma abokan tarayya da suke ɗaukan alhakin kowa gwargwadon rabonsa a ciki.

(c) **Kamfanin da yake ɗaukan taƙaitaccen alhaki:** shi ne kamfanin da jarinsa mallaka ne na wasu daga cikin abokan tarayyarsa, waɗanda ba su wuce wani sanannen adadi ba (ana samun bambanci a haka daidai da bambancin dokoki), ana kuma iyakancen alhakin abokan tarayya a ciki ne kowa daidai da rabonsa a cikin jarin, kuma ba a yin hada- hada da hulɗar kuɗaɗe a hannayen jarinsa.

(2) **Kamfunonin mutane:** su ne kamfanonin da suka ginu akan ƙadarin waɗanda suka yi tarayya a cikinsu, inda za a riƙa la'akari da sifofin mutane, kuma ya zama sun san junansu, kuma dukansu sun amince da juna. Irin wannan kamfanin ya kasu zuwa:

a. **Kamfanin lamuni:** shi ne wanda mutane biyu ko sama da haka suke haɗuwa su kafa shi da niyyar yin kasuwanci, akan su raba hadɗa jarin a tsakaninsu, inda za kuma su haɗu a tare ɗauki cikakken alhakin akan dukan dukiyoyin kamfanin, musamman a gaban waɗanda suke bin kamfanin bashi, shi irin wannan kacaukan ya ginu ne akan sanayyar da take tsakanin abokan tarayyar cikinsa.

b. **Kamfanin wasici mai sauƙi:** shi ne kamfanin da aka kafa shi tsakanin abokin tarayya ɗaya, ko sama da ɗaya da za su zama suna ɗaukan cikakken alhaki, da kuwa wani abokin tarayyar guda ɗaya, ko sama da ɗaya da ba su cikin masu gudanarwa, ana kiransu da masu wasici, alhakin da suke ɗauka yana da iyaka, kowa gwargwadon rabonsa a cikin jarin.
c. **Kamfanin kaso:** kamfani ne da ake yinsa a asirce, shi wannan kamfanin bas hi da shakhasiyya ta doka, ana kafa shi ne tsakanin mutane biyu, ko sama da haka, kowanne daga cikin yana da sanannen kaso a cikin jari, suna yi yarjejeniya akan hanyar da za a bi wajen raba riba, ko asarar da aka samu sakamakon kasuwanci da ta yiwu ɗaya daga cikinsu ne yake gudanarwa, ta kuma yiwu sama da mutum ɗaya daga cikinsu ne yake gudanarwa da sunana, inda zai zama yana ɗaukan iyakantaccen alhaki a gaban wanda yake gudanar da aiki a ciki.

(3) Kamfanin da yake ƙasashe masu yawa: gamayya ne na kamfuna da suke a matsayin rassa da suke da hedikwata a ɗaya daga cikin ƙasashe, a daidai lokacin da sauran kamfunan da suke binsa kuma suke a ƙasashe mabambanta, suke kuma ɗaukan izinin zama ‘yan waɗannan ƙasashen. Babban cibiyar da sauran rassanta suna haɗuwa ne ta hanyar samar da cikakkiyar siyasar tattalin arziki ta bai ɗaya, wadda manufarta shi ne gudanar da kasuwanci akan wani sanannen abu.

Na biyu: Asali akan samar da kamfanoni shi ne halacci idan babu wani abu da aka haramta da ya shigo ciki, ko wani abu da shari’a ba a hana yin kasuwanci akansa ba, amma idan tun asali kamfanin zai yi kasuwanci ne da shari’a ta haramta kaman bankuna da suke ta’amuli da riba, ko kamfanonin da suke ta’amuli da abubuwan da aka

haramta Kaman kasuwancin kayayyakin maye da barasa, ko suke kasuwanci da mutunci, ko suke sayar da aladu, sawa'un a dukan mu'amalansu ne, ko a wani sashe na mu'amalansu, to waɗannan nau'o'i na kamfanoni ne da shari'a ta haramta yin mu'amala da su, bai halatta a mallaki hannayen jari a cikinsu ba, ba kuma halatta a yi kasuwanci da su ba. Haka ma dole ya zama sun wofinta ga barin ruɗi ko jahilci da rashin sani da suke kai wa zuwa ga haddasa rikici, da ma dukan saura dalilan da suke kai wa zuwa ga rusa kamfani, ko ɓarna a cikin shari'a.

Na uku: Haramun ne kamfani ya fitar da wasu hannayen jari na musamman, da suke da wani tagomashi, ko suke da wata dama na bayar da bashi.

Na huɗu: Idan asara ta auka wa jari, to dole ne kowanne daga cikin abokan tarayya ya ɗauki asari daidai da rabon da ya saka a cikin jarin.

Na biyar: Lallai wannan ya sanya wani kaso a cikin kamfani yana mallaka rabo ne na tarayya a cikin kayayyakin kamfani, gwargwadon abin da yake mallaka na hannayen jari. Zai kuma cigaba da mallakar asali, har zuwa lokacin da mallakar za ta tashin zuwa ga wani ta kowane irin dalili daga cikin dalilan yin haka, da suka haɗa da fita daga kamfanin, ko wanin haka.

Na shida: Game da abin da ya shafi fitar da zakka akan hannayen jari a kamfanonin baba- kere, da kamfanonin da suke a ƙasashe masu yawa, za a iya komawa zuwa ga ƙuduri mai lamba 28 (3/4) a taron shekara- shekara karo na huɗu, da mai lamba 121 (3/13) a taron shekara – shekara karo na goma sha uku.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 131 (5/14)

GAME DA ALHAKIN DA YAKE AKAN DIREBAR ABABEN SUFURI NA AL'UMMA GAME DA KISAN KUSKURE DA KUMA YAWAITAR KAFFARA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: (Alhakin da yake akan direban ababen sufuri na al'umma game da kisan kuskure da yawaitar kaffara), bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

- Jinkirta wannan maudhu'in zuwa a yi nazari akan mas'alolin shari'a masu zuwa, da kuma samar da bincike masu zaman kansu akan kowace mas'ala da suka haɗa da:

(1) Yawaitar kaffara daidai da yawaitar kisa.

(2) Abubuwan da za su iyake kwafewa makwafin dangi idan an rasa dangi da za su haɗu wajen biyan diyya, ko idan sun gaza biya.

(3) Haramta gado ga wanda ya yi kisa da kuskure.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 132 (6/14)

GAME DA KASUWANCIN MIƘA WUYA

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: (Kasuwancin miƙa wuya), bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

1. Kasuwancin miƙa wuya kalma ce sabuwa ta musamman a fannin dokokin ƙasashen yamma, ana kuma kiran duka wata yarjejeniya da take ɗauke da sifofi masu zuwa ne da ita:
   (a) Yarjejeniyar ta zama akan wata haja, ko amfanin da ɗaukacin mutane suke matuƙar buƙata, wadda ba za su iya wadata ga barinta ba, kaman ruwan sha, da wutar lantarki, da iskar gas, da waya, da gida waya, da sufuri da sauransu.

(b) Doka, ko kuma a aikace a taƙaita samar da waɗannan kayayyaki, ko amfani, ko hukumomin ga wasu mutane ko kamfanoni kaɗan, ta yanda za su riƙa yin gasa ne a junansu kaɗai

(c) Mai samarwar ya zama shi ne yake shata yarjejeniya da sharuɗɗan da ta ƙunsa, ba tare da ɗayan ɓangare na mai amfana da kayayyaki, ko hidimar yana da haƙƙin ya tattauna akansu, ko ya cire wani sharaɗi, ko kuma ya kawo gyara a cikin yarjejeniyar ba.

(d) Tattala hajar ga ɗaukacin al'umma, a wani tsari na bai ɗaya wajen bayaninta, da sharuɗɗanta a tsawo lokaci ba tare da janyewa ba.

2. Ana ƙulla yarjejeniyar miƙa wuya ne da zaran an sami haɗuwa tsakanin gabatarwa da amsa (da ake ƙaddarawa), wanda su ne duk wani abu da yake nuna yardarm ɓangarorin guda biyu akan samar da wata dangantaka ta kasuwanci a tsakaninsu daidai da sharuɗɗa da bayanai da aka gabatar a wajen ƙulla wannan yarjejeniya, ba tare da shardanta yin lafazi ko rubutu, ko wani ayyanannen sifa ba.

3. Ganin cewa akwai yiwuwa a sami ɓangaren da yake da ƙarfin sanya farashi da sharuɗɗa a wannan yarjejeniya ta miƙa wuya ya yi amfani da wannan dama ya wuce gona- da irin da zai iya cutar da sauran mutane, shi ya sanya shari'a ta tilasta cewa dole ne a ya zama yana ƙarƙashin sanya ido da kulawar gwamnati (tun kafin ma ya kai zuwa ga samun ƙarfin gudanar da kasuwancinsa), saboda a tabbatar da abin da yake shi ne adalci, daidai da irin adalcin da shari'a ta tabbatar.

4. Kasuwanci ko yarjejeniyar miƙa wuya –a ilimin Fiƙihu- ya kasu gida biyu:

Na farko: Wanda akwai adalci a farashinsa, bai ɗauke da sharuɗɗan da za su zalunci ɗayan ɓangaren da dolensa ya shiga cikin wannan kasuwanci ko yarjejeniya, wannan abu

ne da ya inganta a shari'a, ko dole ne ɓangarori biyun su zartar da shi, gwamnati ko sashen shari'a ba su da daman yin katsalanda a cikinsa ta hanyar watsi da shi, ko yin masa gyara, saboda babu dalilin da zai sanya su yi hakan a shari'ance, ganin cewa ɓangaren da yake da faɗa a ji a cikinsa ya gabatar da hajarsa, ko aikin da ya kamata a matsayin hidima ga al'umma, bai kuma ƙi sayar da su ga wanda duk yake da buƙata da farashin mai rahusa da kyau ba, wanda shi ne kuɗin da ya yi daidai da haja, ko aikin da aka gabatar (ko da riba kaɗan, wanda shari'a ba ta hana ba, ko wanda ba za a taɓa iya kauce mas aba a duk wata cinikayya da ake gudanarwa, kuma mutane sun saba yi wa juna rangwame akansa), saboda cinikayya da wanda yake da tsananin buƙata da farashi mai sauƙi abu ne da ya halatta a wurin malamai masana.

Na biyu: Wanda yake ƙunshe da zaluntar ɗayan ɓangaren da dolensa ya shiga cikin wannan kasuwanci ko yarjejeniya, ganin cewa an sanya masa farashin da babu adalci a ciki (ma'ana ya yi muni kwarai), ko kuma ya zama yana ƙunshe da sharuɗɗan da suke cutar da shi. A nan dole ne gwamnati ta shiga cikin wannan al'amari tun farko (kafin ma a fara gudanar da shi) domin sanya farashi na adalci da dole ne a yi aiki da shi, wanda shi ne zai kawar da zalunci da cutar da mutanen da suke da tsakanin buƙatar wannan haja, ko aiki za su fuskanta, inda za ta rage farashin da aka sanya wanda aka wuce iyaka akansa, ta dawo da shi zuwa ga farashi adalci adalci mai sauƙi, ko kuma ta gyara sharuɗɗa da suke wuce ƙima, ta yanda za su yi daidai da adalci ga dukan ɓangarori biyun, ganin cewa:

a. Shari'a ta sanya dole ne gwamnati (shugaba) ta yaƙi duk wani ihtikari([1]), sawa'un mutane ɗaidaiku ne suka yi, ko kamfanoni, dole ne idan suka ɓoye wata haja, ko suka ƙaurace wa duk wani aikin da al'umma

([1]) Ihtikari shi ne: Voye kayan amfanin al'umma da nufin su yi qaranci a kasuwa, sannan a fito da su a sayar masu da tsada.

take tsananin bukatarsa, ko suka ki sayar da su da farashin na adalci, ta shiga domin yi wa kayan ko bukatar farashi na adalci, da zai kiyaye hakkokin bangarori biyun duka: hakkin mutanen gari na kar su cutu sakamakon zaluncin da mai ihtikarin ya yi a wajen sanya farashi, ko shimfida sharuddа, da kuma hakki shi mai ihtikarin na a ba shi kudinsa daidai da hajarsa, ko aikin da ya yi.

b. A sanya wannan farashi an gabatar da maslahar daukacin al'umma –wanda ita ce tsananin bukatar da mutane suke yi wa hajar, ko amfanin na su saya da farashin mai sauki na adalci- akan kebantacciyar maslaha, wadda ita ce maslahar mai yin ihtikarin ta zalunci, sakamakon kin sayar masu da ya yi sai da kazamiyar riba, ko da sharuddan zalunci, an riga an sani cewa a cikin tabbatattun ka'idojin Fikihu akwai ka'idar da take cewa: (Ana gabatar da maslahar al'umma akan kebantacciyar maslaha), kuma (Ana jure wa kebantacciyar cutarwa saboda a hana gamammiyar cutarwa).

5. A tsarin wakilcin da ake takaita shi a wasu mutane na su shigo da kayayyaki, akan bambance yanayi guda uku:

Na farko: Ya zama babu wata bukata ko wajibci nag aba daya, ko na daidaiku da ya kebanta da wasu gungu na mutane na a samar da kayan da aka daure takaitaccen wakilcin da shi, ganin cewa yana cikin kayayyaki, ko amfanin nishadi da debe kewa, wadanda zai yiwu a rayu babu su, ko kuma ya zama akwai lalura ko bukatarsa wadda ba a ayyana ba, saboda akwai wani abin da zai iya kwafe makwafinsa a kasuwa da kuma farashi mai rahusa, to a nan hakkin wakilin da yake kawo kayan ne ya sayar da ita da farashin da suka daidaita tare da mai saye, gwamnati ko sashen shari'a ba su da hakkin yin katsalandar wajen sanya masa farashin da zai sayar da kayan, domin yarda it ace asali wajen ingacin kulla kowace

cinikayya, ta kuma ginu ne akan abin da masu ƙulla cinikayyar su biyu suka wajabta wa kansu, domin keɓance mai wakilcin da ya kawo wani kaya, a kuma hana kowa ya kawo irinsa abu ne da ya halatta a shari'a, saboda haƙƙinsa ne ya sayar da abin da yake mallaka da farashin da ya aminta da shi, matuƙar da ba ya ƙunshe da zalunci ko cutar da mutane, bai halatta a sanya masa farashin dole ba.

Na biyu: Ya zama akwai lalura ko buƙata na ɗaukacin al'umma, ko ta ɗaiɗaikun mutane da aka ayyana ta da take ɗamfare da taƙaitaccen wakilci, ya kuma zama shi mai wakilcin ya yi wa kayan farashi na adalci, babu neman ƙazamiyar riba, babu kuma baba- kere na zalunci, a irin wannan yanayi bai halatta gwamnati ta shiga domin ta sanya masa farashi ba, domin keɓantuwarsa da kuma irin yanda shi kaɗai ne yake da wannan kayan abu ne da ya halatta, ya yi tasarrufi ne a cikin abin da yake mallaka ne, babu zalunci a ciki, babu kuma cutar da mutanen da suke buƙatar kaya, saboda haka ba za a yi masa katsaladan ba.

Na uku: Ya zama akwai lalura ko buƙata na ɗaukacin al'umma, ko ta ɗaiɗaikun mutane da aka ayyana ta da take ɗamfare da taƙaitaccen wakilci, amma mai wakilci ya ƙi ya sayar wa mutane sai ya sanya masu ƙazamiyar riba, ko sai dole sun yarda da sharuɗɗansa na zalunci, to a irin wannan yanayi dole ne gwamnati ta yi katsalanda a ciki al'amarin domin da ɗauke zalunci da ake yi wa masu buƙatar kayan, ta hanyar tilasta farashi akan mai wakilcin.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA 133 (7/14)

GAME DA MATSALAR BASUSSUKAN DA SUKA YI KWANTAI A CIBIYOYIN HADA- HADAR KUƊAƊE NA MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar mata game da maudhu'in: (Matsalar basussukan da suka yi kwantai a cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci), bayan ta saurari tattaunawar da aka yi akansa, **an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:**

Na farko: Lallai salon da ake magance matsalar basussukan da cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci suke fuskanta ya bambanta da salon da bankunan da aka sani suke amfani da shi, inda bankuna suna ta'amuli da fa'idar da aka haramta ne, saboda haka ya kamat a ƙara tabbatar da haramcin duk wata fa'ida ta banki a ƙarƙashin abubuwa masu zuwa:

(a) Ayyukan bankunan da aka saba da su:

Lallai dokokin da suka tsattsara aikin bankuna sun hana su yin aiki a fagagen kasuwanci a cikin abubuwan da suke ɗaukan riba da asara. Suna amsa ajiye- ajiye ne daga al'umma a matsayin basussuka, suna kuma taƙaita ayyukansu –kaman yanda masana dokoki da masana tattalin arziki suke faɗi- a fagen amsar basussuka, da kuma bayar da bashi da fa'ida, inda suke samar da lamunin wannan basussuka da suke bayarwa ta hanyar ajiye- ajiye da fa'ida.

(b) Dangantaka tsakanin bankunan da aka saba da su da masu ajiya:

Lallai sifar danganka tsakanin masu ajiya da bankuna a wurin shari'a, da ma a wurin dokokin zamani it ace: bayar da bashi, ba wakilci ba, wannan shi ne abin da dokokin zamani da tsare- tsaren bankuna suke tabbatarwa, saboda tsarin wakilci a kasuwa yana nufin wata yarjejeniya ce da take bai wa wani mutum daman yin kasuwanci da wata dukiya mallakar wanda ake wakilta, akan za a biya shi da wani sanannen lada, ko wani kaso daga cikin ribar da aka samu a kasuwancin, lallai malamai sun yi ijma'i akan cewa kuɗin kasuwancin mallaka ne na wanda ake wakilta, ribar kasuwancin tasa ce, kaman yanda asarar da aka fuskanta ma tasa ce, shi wakili yana da ladan da aka bayyana a yarjejeniyar wakilci, idan wakilcin an yi ta ne saboda a biya lada. Saboda haka, bankuna ba za su zama wakilan masu ajiya wajen sanya ajiye- ajiyensu a kasuwa ba, saboda da zaran an miƙa wannan ajiya ga bankunan da aka saba da su, ya zama kuma suna lamuntar ajiyar, to abin ya zama bashi da za su iya yin tasarrufi a cikinsa, tare da wajibcin biyansa, shi kuma bashi ana mayar da shi ne da kwatankwacinsa ba tare da sharaɗin yin ƙari ba.

(c) Fa'idojin da bankunan da aka saba suke bayarwa yana cikin riba da shari'a ta haramta:

Lallai fa'idojin da bankuna suke bayarwa akan ajiya yana cikin riba da shari'a ta haramta a cikin Alƙur'ani da Hadisai, kuma wannan ne abin da ƙudurori da fatawowi

suka yi ta zuwa akansa, tun taron Musulunci na biyu da babban cibiyar binciken Musulunci ta gabatar a Alƙahira a watan Almuharram, 1385 H/ Mayu, 1965 inda masana Fiƙihu cikin manyan malaman duniya tamanin da biyar ne suka halarta, waɗanda suke wakiltar ƙasashen Musulunci talatin da biyar, inda sakin layin farko na bayanin bayan taro ya bayyana cewa: Lallai dukan nau'o'in fa'ida akan bashi riba ne da aka haramta. A kuma haka ƙudurori da fatawowi da wasicin bayan tarurruka da dama suke cigaba da bibiyan juna, a ciki akwai:

- Taron tattalin arzikin Musulunci na ƙasa da ƙasa karo na farko da aka yi a Makka, shekara ta 1396 H/ 1976, wanda sama da malamai ɗari uku daga cikin malamai da masana Fiƙihu da ƙwararru a fagen tattalin arziki da bankuna ne suka halarta, sun kuma tabbatar da haramcin fa'idojin bankuna.
- Taron cibiyoyin hada- hadar kuɗaɗe na Musulunci da aka gabatar a ƙasar Kuwait 1403 H/ 1983, shi ma an tabbatar da wannan ma'anar.
- Cibiyar Fiƙihun Musulunci ta ƙasa da ƙasa da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai a taronta na shekara- shekara karo na biyu, a Jidda a watan Rabi'ul Akhir, 1406 H/ Disamba, 1985 a ƙuduri mai lamba 10 (2/10), wanda ya bayyana cewa**:** Lallai duk wani ƙari, ko fa'ida akan bashin da lokacin biyansa ya yi, wanda ake bi bashin kuma ya gaza wajen biya, inda za a yi masa ƙari saboda ƙara masa lokaci da aka yi, haka ma ƙari, ko fa'ida akan bashi tun lokacin ƙulla yarjejeniyar bayar da bashin, duka waɗannan surori guda biyu riba ne da Shari'a ta haramta.
- Cibiyar Fiƙihun Musulunci da take ƙarƙashin ƙungiyar haɗin kan ƙasashen Musulmai a Makka, inda a taronta na shekara- shekara karo na tara, wanda aka yi a 1406 H/ 1986 ta tabbatar da cewa: Duk abin da ya zo ta hanyar fa'idojin riba dukiya ce ta haram.

- Kwamitin bayar da fatawa a Al Azhar, wanda ya tabbatar da haramcin ƙarin da ya zo akan shahadar kasuwanci (a, b) saboda yana cikin bashi da ruwa, shi kuwa bashi da ruwa riba ne, shi kuma riba haramun ne.
- Fatawar mai girma Mufti –na lokacin- Sheikh Dr. Muhammad Sayyid Ɗanɗawiy a watan Rajab, 1409 H/ Fabrairu, 1989, wadda ta bayyana cewa: lallai ajiye dukiyoyi a bankuna, ko bas u bashi, ko amsar bashi daga wurinsu da kowace irin sura akan wata fa'ita da za ta gabatar a farko haramun ne.

Bayan abin da ya gabata ma akwai fatawowin cibiyoyi na ilimi masu yawa, irinsu: Cibiyoyin Fiƙihu a ƙasashen Musulmai, da kwamitocin bayar da fatawa, da tarurrukan ƙara wa juna sani, da tarurrukan ilimi na ƙasa da ƙasa, da fatawowin malamai masana a fannonin tattalin arziki da ayyukan bankuna a ƙasashen Musulmai, dukansu sun tabbatar da wannan ma'anar, inda dukansu a haɗe suka a matsayin ijma'in wannan zamanin da bai halatta a saɓa masa ba, wato haramcin fa'idojin da bankuna suke bayarwa.

(d) Iyakance ribar kasuwanci da wani adadi na kuɗi, ko da wani kaso daga cikin uwar kuɗi (jari) a farko:

An tabbatar da cewa: cewa kwangilar lamuni da riba ta bambanta da kwangilar hasashe na shari'a, domin ribar na wanda ya ci bashi ne, hasarar kuma ta kasance a cikin rancen, amma hasashe, yana raba ribar ne kuma yana ɗaukar asarar idan ya kasance. Yana faruwa, domin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(HarajI lamuni ne)** [Ahmad]. Wato abin da ake samu na komawa, da girma, da karuwa, amma ya halatta ga waɗanda suka dauki nauyin lalacewa, da barna da gajiyawa, kuma malaman fikihu sun ciro daga wannan Hadisin sanannen ka'idar fikihu **(Riba tana da ɗawainiya)**. Haka nan, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi hani da ribar da ba ta tabbata ba.

An yi Ittifaƙi a tsakanin malaman fikihu tsawon karnoni da dama kuma a dukkan mazhabobi cewa bai halatta a tantance ribar zuba jari a cikin hasashe da sauran kamfanoni a dunkule ko kaso na adadin da aka zuba (babban jari), domin wannan shi ne garantin shugaban makarantar kuma ya saba wa ingantattun hujjoji na shari'a, kuma yana haifar da yanke shiga cikin riba, da asarar da kamfani ke buƙata da hasashe. Kuma wannan ijma'i ya tabbata, kuma ya tabbata, kamar yadda aka ruwaito ba wani saɓani a kansa ba, kuma a cikin haka Ibn Ƙudamah yake cewa a cikin Al-Mughni (34/3): "Waɗanda aka koyi ilimi daga wurinsu, gaba ɗaya sun yi ittifaƙi a kan cewa bayar da rance (hasashe) ya baci idan mutum ya yi hasashe. Ko kuma su biyun ya shar'anta wa kansa sananniyar dirhami). Ijma'i shaida ce da ke tsaye da kanta.

Kuma majalisar yayin da take bayyana hakan baki daya, ta shawarci musulmi da su samu halal, da kuma nisantar haramun da ake samu wajen yin biyayya ga Allah Madaukakin Sarki da Manzonsa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Na biyu: Basusukan da suka wuce iyaka:

(a) Dangane da abin da ya shafi hukunce-hukuncen kwangila: Majalisar ta tabbatar da hukuncin da ta yanke a baya game da hukuncin da ya ƙunsa a cikin hukuncinta a cikin Salam ta 85 (9/2) wadda ke cewa: (Ba a halatta hukuncin daurin rai da rai ba ga jinkirin mika mulki. Musulmi a cikinsa, saboda bashi ne, kuma baya halatta a shardanta Karin basussuka a lokacin jinkiri), da hukuncinsa a cikin fage na 109 (12/3) wanda yake cewa: ((Ma'anar hukuncin yana iya kasancewa a cikinsa). Duk kwangilolin kudi sai dai na kwangilolin da ainihin wajibcin bashi ne, domin wannan riba ce bayyananna, kuma a kan haka babu hukuncin hukuncin da ya halatta – alal misali – wajen siyar da kari-ka-yi saboda jinkirin mai

bin bashin da ya rage wajen biyan sauran kaso, ko saboda rashin biya ko jinkirtawa.

(b) Cibiyar ta tabbatar da shawarar da ta yanke a baya game da batun siyar da kashi 51 (6/2) a cikin sakin layi masu zuwa:

Na uku: Idan wanda ake bi bashi ya yi jinkiri wajen biyan wasu kaso daga cikin abubuwan da suka wuce kwanan watan da aka ayyana, to bai halatta a wajabta masa karin bashin da wani sharadi da ya gabata ba, ko kuma ba tare da wani sharadi ba, saboda haramun ne riba.

Na huɗu: Haramun ne ga wanda ake bi bashi wanda ya cika ya yi jinkiri wajen biyan abin da ya kamata, sai dai a Sharia ba ya halatta a biya diyya idan aka jinkirta biya.

Na biyar: Ya halatta a shari'a ga mai sayarwa ya ba da sharadi kafin cikar kwanakin lokacin da wanda ake bi bashi ya makara wajen biyan wasu daga cikinsu, matukar dai wanda ake bi bashi ya karbi wannan sharadi lokacin yin kwangila.

Na Shida: Mai sayarwa ba shi da damar rike abin da aka sayar bayan an sayar da shi, amma mai siyar zai iya ba da izinin mai siyar ya jinginar da abin da aka sayar da shi don tabbatar da haƙƙinsa na karɓar kuɗin da aka jinkirta.

(c) Buƙatar bankunan Musulunci su mai da hankali wajen magance dalilan da ke kawo tsaikon biyan basussuka, kamar ruwan ruwa na murabaha da kwangilolin nan gaba, da rashin la'akari da hanyoyin fasaha na samar da kudade (kamar nazarin yuwuwar) ba tare da la'akari ba. Don ɗaukar isasshen garanti.

Na uku: Majalisar ta ba da shawarar wadannan:

(a) Cewa bankunan Musulunci su yi riko da tafarkinsu na tsarin tattalin arzikin Musulunci da sarrafa shi, da aiwatar da gyare-gyaren fasaha da gudanarwa da suka dace don samun cigaba ta hanyar zuba jari da hadin gwiwa kai tsaye don samun cigaban tattalin arziki da

zamantakewa, wanda yana daya daga cikin mafi muhimmanci. Hadafi da manufofin bankunan Musulunci da cibiyoyin kudi.

(b) Nemo wasu hanyoyin magance matsalar basussuka a cibiyoyin hada-hadar kudi na Musulunci tare da gabatar da nazari a kansa don gabatar da shi ga majalisar a wani zama na gaba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 134 (8/14)
GAME DA SABON TSARIN DUNIYA, DUNƘULEWAR DUNIYA DA ƘUNGIYOYIN YANKI DA TASIRINSU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha huɗu, da ya gudana a garin Doha - ƙasar Kuwait, a ranakun 8 - 13 ga watan Zul ƙida, 1423 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 11 – 16 ga watan Junairu, 2003.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka miƙa wa Cibiyar Nazari game da batun sabon tsarin duniya, dunƙulewar duniya da ƙungiyoyin shiyya-shiyya da tasirinsu, da kuma sauraron tattaunawar da aka yi a kusa da shi, an cinma abubuwa masu zuwa:

Na farko: Mene ake nufi da dunƙulewar duniya da tsarin sabon tsarin duniya:

Tsarin duniya na nufin a sigarsa da bayyanarsa da saukin motsi a cikin kayayyaki da ra’ayoyi da kuma kawar da shingayen da ke tsakanin al’ummomi da ƙasashe, ta yadda duniya ta koma tamkar wani ƙaramin ƙauye na duniya sakamakon cigaban fasahar zamani da aka samu, da tsare-tsaren da suka samu, an ƙirƙira don mu’amalar ƙasa da ƙasa, gami da: ƙungiyoyin yanki na duniya, Ƙungiyar

Ciniki ta Duniya, da kamfanonin jigilar kayayyaki na nahiyoyi. Wannan ya kasance tare da cin gajiyar manyan ƙasashen duniya da tasirin wayewar ƙasashen yammacin duniya na wannan zamani na waɗannan damar da ake da su don biyan buƙatunsu, wanda ya ba su damar sarrafawa da kuma mamaye ɓangarori da dama na rayuwar ɗan Adam, maimakon haka, waɗannan ikokin sun fara aiki don jagorantar tafiyar matakai na fasaha. Cigaba da samun karin hanyoyi da tsare-tsare da za su ba su damar ƙara ƙarfinsu a daya ɓangaren, da kuma ƙara ƙarfin iko da mallake shi kan makomar rayuwar ɗan Adam a daya ɓangaren.

Wannan yana da nasaba da abin da ake kira sabon tsarin duniya, wanda ya samo asali ne daga ƙungiyoyi na ƙasa da ƙasa da kuma tarukan duniya da suka shafi batutuwa daban-daban na ilimi, tattalin arziki, zamantakewa, yawan jama'a da muhalli tare da ra'ayi mai kishin moriyar manyan ƙasashe da Turawa. Don gamammen ra'ayoyi na wayewar kayan kayan yamma na zamani.

Kasancewar duniya ta wannan hanya tana wakiltar ƙalubale ne a fili ga al'ummar Musulmi, da abin da take ɗauke da shi na saƙon Ubangiji, da kuma abin da ta kafa na wayewar ɗan Adam baligi wanda ya samu kyakykyawan yanayi da jin daxin dan'Adam a kowane ɓangare na rayuwa. Malamai da 'yan siyasa da masu tunani da jagororin al'umma a fagagen siyasa, al'adu, ilimi, tattalin arziki, yaɗa labarai da dai sauran su, suna da nauyi mai girma na ganin an samu cikakkiyar cigaban Musulunci wanda ke ingiza al'umma zuwa ga kololuwar cigaba.

Wannan yana bayyana a fagage biyu:

Na farko: Riga- kafin zuriyar al'umma da 'ya'yanta daban-daban ta fuskar ƙalubalen da ke tattare da al'adun dunƙulewar duniya a wannan zamani da ke ƙarƙashin tasirin Turawan Yamma, wanda ke buƙatar gagarumin ƙoƙari wajen gina ɗabi'ar Musulunci ta zamani da za ta iya fuskantar ƙalubale tare da fadakarwa da fahimta. Da kuma

a kan zurfin fahimtar Musulunci tare da daidaitawa da daidaitawa da daidaito, ta yadda ya haɗa ilimi da imani, da kuma tsakanin asali da zamani, da tsakanin riƙo da riƙo da budi da buxe ido ga nasarorin wannan zamani. Wannan yana wajabta kulawa sosai a cikin manhajojin ilimi, musamman ƙarfafa abubuwan da suka shafi addini, da watsi da duk wani tsoma baki a cikinsa daga wasu ƙasashen waje.

Na biyu: Jagoranci wajen tunƙarar kayan aiki da hanyoyin dunƙulewar duniya bisa ingantattun tsare-tsare masu kyau da suka shafi al'ummomin bil'Adama na wannan zamani, ta hanyar fahimta da harshen da ake fahimtar da shi daga ingantawa da fiskanci, ko taƙaitawa da gazawar nazari, ciki har da fagagen tunani, al'adu da kafofin watsa labaru, da nufin cimma ayyukan ƙirƙire-ƙirƙire da nasarorin kimiyya, da cigaban tattalin arziki da ke tabbatar da kyakkyawar rayuwa ga kowane mutum a cikin al'umma.

A cikin cikakkun tsare-tsare da aka ambata a baya, kuma bisa la'akari da cewa Musulunci addini ne na duniya wanda ya zo don amfanin mutane da jin daxinsu duniya da Lahira, Majalisar cibiya ta ba da shawarar haka;

(1) Gabatar da wanzuwar Musulunci da kuma hanyoyin magance matsalolin bil'Adama bisa manufa ta ilimi mai haƙiƙa wanda ke amfani da dukan hanyoyin da ake da su don cimma wannan.

(2) Ƙarfafa ƙungiyar haɗin kan ƙasashen Musulmi da ƙungiyoyin da ke da alaka da ita da sauran cibiyoyin Musulunci na ƙasa da ƙasa, da kuma gudanar da ayyukansu da nufin zurfafa ƙungiyar Musulunci ta ƙasa da ƙasa, musamman a fannin tattalin arziki.

(3) Buƙatar yin aiki tuƙuru don kafa kasuwannin Musulunci na bai daya da ƙarfafa ayyukan tattalin arziki da zuba jari a tsakanin ƙasashen Larabawa da na Musulunci.

(4) Yin aiki don gyara dangantakar da ke tsakanin duniyar Musulunci da sabon tsarin ƙasa da ƙasa ta yadda za a tabbatar da ‘yancin kai na ƙasashen Musulmi da mutunta ‘yancin kai da kebantuwarsu, da nufin kiyaye matsayin Musulunci na al’ummominsu.

(5) Yin aiki don ciyar da ilimin kimiyya da fasaha gaba a cikin ƙasashen Musulunci, da yin ƙoƙari sosai don gano fasahar zamani a cikinsu.

(6) Aiki don ƙarfafa alakar da ke tsakanin al’ummar Musulmi, da samun hadin kan sahu na Musulunci wajen fuskantar dukan ƙalubale.

(7) Jaddada abubuwa na asali da na zamani a cikin bahasin Musulunci, da samar da kayan aikinsa don samun fahimtar ‘ya’yan Musulmi na hankali, da gabatar da matsayin Musulunci ga al’ummar bil’Adama a kan saƙon wannan. Addini wajen samun alhairi da cigaban bil’Adama, nesantar tsattsauran ra’ayi da tsattsauran ra’ayi a daya ɓangaren, da sakaci da rugujewa a daya ɓangaren.

(8) Yin aiki da dunƙule manufofin ijtihadi a cibiyoyin ilimin shari’a a jami’o’i da cibiyoyi da majalisar fatawa da cibiyoyin fiƙihu, ta yadda al’umma za su iya tunƙarar al’amuran da suka kunno kai da matsalolin da suka kunno kai, tare da zurfin fahimtar fiƙihu. Wanda ke ba da ingantattun mafita da magunguna masu inganci.

(9) Amfanuwa da abin da hanyoyin sadarwa na zamani da hanyoyinsu suke bayarwa wajen gabatar da ingantaccen ilimi na Musulunci, da bayyanar da kyakykyawan siffar wannan addini, musamman ta hanyar tashoshin tauraron ɗan Adam da Intanet.

(10) Wajibcin daidaitawa tsakanin ƙasashen Musulmi da ƙungiyoyin sa kai da ke cikinsu a lokacin da suke halartar ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa da tarukan duniya, don

bayyana ma'anar Musulunci da aka fi sani, da kiyaye tafarkin bil'Adama daga hatsarori da munanan abubuwa da ake fuskanta.

Allah ya sa mu dace;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

SANARWA DAGA CIBIYAR FIKIHU ZUWA GA AL'UMMAR MUSULMI AKAN FALASDINU DA IRAKI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki daya.

Bayan da Majalisar Dinkin Duniya ta yi bitar yanayi mai hatsarin gaske da kasashen Larabawa da na Musulunci ke ciki, Falasdinu da Iraki akan gaba: tare da abin da mahukuntan Isra'ila da ke mamaye da Falasdinu ke yi ta fuskar ta'addancin kasa, inda ake kashe yara da mata da tsofaffi, da fararen hular da ba su da makami, da kuma kame ba-zata, kisan gilla, kai samame, lalata gidaje a kan masu su, bijirewa filayen noma da kawanyar da sojoji ke cigaba da cigaba da yi a garuruwa, kauyuka da sansanoni, musamman birnin Kudus, birnin Isra'ila. Da Mi'raj wanda ke wakiltar wani bangare na imani da imanin Musulmi, da kuma hana al'ummar Falasdinu yin sallah a Masallacin Al-Aksa mai albarka.

Tare da wannan ta'addanci, Isra'ila na da'awar zaman lafiya kuma mai laifinta mutum ne mai zaman lafiya. Kuma cewa shahidan da suka kare addininsu, da kansu, da kasarsu, da mutuncinsu, 'yan ta'adda ne.

Ko shakka babu wadannan munanan ayyuka na mamayar Isra'ila ta'addanci ne a kansu, kuma hakan keta hakkin bil'Adama ne da kuma alkawuran kasa da kasa. Duk wannan yana faruwa ne a gaban idanu da kunnuwa na

duniya, musamman a gaban ƙasashen da ke da'awar kare 'yanci, dimokuradiyya, daidaito da kare haƙƙin bil'Adama.

Kuma abin da ke barazana ga 'yan uwantaka Iraƙi na zaluncin Amurka da Birtaniyya shi ne hari kan al'ummar Musulmi, ƙasarta mai kyau da albarkatunta ba tare da yin biyayya ga kiran da Musulmi suke yi na kau da kai daga wannan wuce gona da iri ba, tare da yin watsi da shawarar da ƙungiyoyin Larabawa da na Musulunci suka fitar: na hukuma da farin jini, da kuma yin watsi da kiraye-kirayen da ke fitowa daga ƙasashe da al'ummomi masu son zaman lafiya, wannan matsayi na kin duk wata ɗabi'a da alƙawuran ƙasa da ƙasa, wanda ya saba wa alfarmar ƙasashe, filayensu da al'ummominsu.

Don haka majalisar ta yi kira ga al'ummar Musulmi da gwamnatoci da al'ummar Musulmi da su cigaba da bayar da goyon bayan da Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa mai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya wajabta, domin kiyaye rayuka da rayuka. Allah ya kiyaye, kuma ya haramta, gwargwadon faɗinsa Maɗaukaki: **(Muminai 'yan'uwa juna ne)** [Hujurat: 10], da faɗinsa**: (Muminai maza da mata dukansu masoyan juna ne, kuma masu taimakon juna; sakamakon imanin da suka yi, suna bayar da umurnin aikata abin da addininsu na gaskiya ya bayar da umurni, suna kuma hana aikata abubuwan da addini bai yarda a aikata ba)** [At-Taubah: 71] Kuma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Mumini a wurin ɗan uwansa mumini kamar gini ɗaya ne da sashe yake ƙarfafa sashe)** [al- Bukhari da Muslim], haka ma yana cewa: **(Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba ya zaluntarsa, ba ya ƙin taimakonsa, ba kuma ya bayar da shi)** [al-Bukhari da Muslim].

A bisa waɗannan ayoyi da Hadisai majalisar, baya ga abin da aka ambata a sama, ta tabbatar da haka;

Na farko: Bai halatta a Shari'a ba, a yi biyayya ga mahassada, ko kuma a taimaka musu wajen aiwatar da

munanan manufofinsu da zubar da jinin da ba su ji ba su gani ba.

Na biyu: Harin da ake kai wa kowace kasa daga cikin ƙasashen Musulmi hari ne ga al'ummar Musulmi baki ɗaya.

Na uku: A bisa shari'a an wajabta wa dukan masu mulkin Musulmi da su sauke nauyin da ya rataya a wuyansu na samun nasara da kuma gudanar da ayyukansu na addininsu da al'ummarsu da kuma ƙasarsu.

Godiya ta tabbata ga Ubangijin talikai;;

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA GOMA SHA BIYAR NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

MASƘAƊ (UMAN)

14 – 19 GA ALMUHARRAM, 1425

6 - 11 GA WATAN MARIS, 2004

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 135 (1/15)
GAME DA MAGANAR MUSULUNCI DA FA'IDA DA ƘALUBALEN DA KE GABANTA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na goma sha biyar, da ya gudana a garin Masƙaɗ - Masarautar Uman, a ranakun 14 - 19 ga watan Almuharram, 1425 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 6 – 11 ga watan Maris, 2004.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar wa cibiyar Game da maudu'in bahasin Musulunci, da siffofinsa da ƙalubalen da ke gabansa, da kuma sauraren bahasi da aka yi a kusa da shi, da kuma tunawa da abin da ya zo a cikin hiƙimar wajabcin bin littafin. Tafarkin hikima da wa'azi mai kyau wajen kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, da abin da Sunna da tarihin Annabi suka cika da shi, Nassosi na lafazi da misalai na aiki wajen la'akari da yanayin masu jawabi, da zabar hanyar da ta dace da yanayin da ake buƙata, da kasancewar bahasin Musulunci ya siffantu da daidaito da daidaito, da nau'in wanda aka nusar da shi, an tabbatar da ƙuduri mai zuwa:

(a) Abin da ake nufi da bahasin Musulunci shi ne salon magana da ke nuna haƙiƙanin Musulunci da dokokinsa a fagage daban-daban na rayuwar jama'a da na sirri.

(b) Abin da ake tahowa a kan wannan lamari a halin da ake ciki ya wajabta fayyace sifofin maganganun Musulunci da tunkuɗe shubuhohi a kai, don tunkuɗe harin rashin adalci da ake kai wa Musulunci, da tsayin daka wajen

kamfen din kafafen yaɗa labarai da ke gurbata haƙiƙaninsa.

(c) Sabunta zance na Musulunci, bisa la'akari da bin ƙa'idoji da bayanai na zamani, ba zai iya haifar da sauyi ko watsi da duk wani ƙa'idojin Musulunci ko hukunce-hukuncen shari'a ba, tana ba da shawarwari masu zuwa:

(a) Aiki kan haɗa ƙoƙarin masu wa'azi da masu tunani da suka shafi maganganun Musulunci, walau a cikin al'ummomin Musulunci ne ko na waɗanda ba Musulmi ba, don yin la'akari da abin da ake buƙata ta hanyar Alƙur'ani da Sunna wajen isar da kira da hikima. Da kyakkyawan wa'azi, da nisantar abin da ke tunkuɗe karɓar kiran gaskiya.

(b) Buƙatar yin amfani da dukan hanyoyin sadarwa da fasahohin zamani don saukaka isar da jawaban Musulunci ga al'umma daga kowane mataki.

(c) Kira ga gwamnatocin Musulunci da masu iyawa, da su kashe kuɗi da ƙoƙari wajen gabatar da jawaban Musulunci ta kafafen yaɗa labarai, musamman tashoshi na tauraron ɗan Adam da Intanet, domin a fayyace haƙiƙanin haƙiƙanin Musulunci, da kawar da shubuhohi, da ƙaryata zargin da ake yi. Kewaye da shi, da kuma yin aiki da tsarkake waɗannan hanyoyin daga dukan abin da ya saba wa Musulunci.

Majalisar ta kuma mika godiyarta ga dukan hukumomi, kungiyoyi, kwamitoci, kungiyoyi, da al'amuran da suke gudanar da ayyukan tallafawa birnin mai tsarki da kuma tsayin daka ga al'ummarta har zuwa ƙarshen mamayar wannan ƙasa mai tsarki: (**Wallahi da sannu Allah zai taimake mai taimakonsa, lallai Allah mai cikakken ƙarfi da buwaya ne)** [al- Hajji: 40].

ƘUDURORI DA BAYANAI NA TARON SHEKARA-SHEKARA KARO NA ASHIRIN DA BIYU NA MAJALISAR CIBIYAR FIƘIHUN MUSULUNCI TA DUNIYA

ƘASAR KUWAIT

02 – 05 GA WATAN JIMADAL AKHIR, 1436

22 - 25 GA WATAN MARIS, 2015

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

HUKUNCI MAI LAMBA 205 (1/22)
DANGANE DA SHURA DA KUMA DIMOKRAƊIYYA A MAHANGAR MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan tsokaci akan binciken da aka gabatar zuwa ga ƙungiya dangane da lamarin shura da dimokraɗiyya a mahangar Addinin Musulunci, sannan bayan sauraron tattaunawa da akayi akan wannan lamarin, an zartar da abubuwa dangane da hakan kamar haka :

1- Shawara ƙa'aida ce daga cikin ƙa'idojin rayuwar Musulunci,kuma tushe ne daga cikin tsarin hukunci a Musulunci, an bayar da umurnin haka a cikin shari'a, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Al'amarinsu a tsakaninsu yana kasancewa ta hanyar shawara ne)** [As-shura: 38] sannan Allah ya cewa Annabinsa abin yi wa wahayi kuma kamamme (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam): **(Ka shawarce su cikin al'mura idan sun taso idan ka yi azamar yin wani abu to ka dogara ga Allah)** [Ali Imran: 159], sannan Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya zartar da hakan mafi alhairin zartarwa, har saida sahabinsa Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda yake cewa: **(Ban taɓa ganin**

wani da yafi kowa neman shawarar abokanansa kamar Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) Ba).

2- Babu hani a shari'ance wurin amfana da tsare tsaren dimokraɗiyya ta hanyar da ake ganin ɗaiɗakun mutane da sauran jama'a za su amfani da shi, idan an cireta daga ma'anarta na falsafa, wanda yake nuni da shugabantar al'umma ba tare da yiwa shugabancin tabaibayi da shari'ar Musulunci ba, kamar dai yanda ake gani a ƙasashen da ba na Musulmai ba, tare da kiyaye ƙa'idojin shari'ar Musulunci, sannan a bi sa la'akari da tsare tsaren kowace ƙasa cikin ƙasashen Musulmai, domin kulawa da hanyoyin ciro hukunce hukunce na shari'a bisa yanayin da fiƙihun Musulunci:

Don Haka Majalisar ta bayar da abubawa masu zuwa kamar haka:

1) Mayar da hankali wurin yaɗa wayewar shawartawa da juna a cikin addinin Musulunci a matsayin abu na asali ta hanyar muhadarori da karantarwa da kuma tarrukan karawa juna sani da kafafin yaɗa labaru sannan duk wata kafa sadarwa ta zamani.

2) Ma'abota sani su duƙufa wurin bincike domin samo sababbin hanyoyi da zartarwar da abubuwa waɗanda aka tsamo su ta hanyar shawartawa, tare da taka tsan tsan wurin kiyaye ƙa'idoji na shari'a kan hakan.

Allah ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 206 (2/22)
GAME DA TAMBAYOYIN CIBIYAR BIBIYA DA ƘIDIDDIGA NA ƘASASHEN MUSULMAI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bisa la'akari da yawan zantuttkan na fiƙihu kan lamarin da yawan yamutsa hazo da tambayiyin suke tayarwa tare da yawan samun saɓanin fahimta tsakanin malamai kan lamari , sannan bisa lura da ra'ayin wakilan majajisar kan wasu abubuwan lura, majalisar ta tura da wannan lamari zuwa ga sakatariyarta domin ta samar da gamsasshen amsa kan tambayoyin sannan a sake dawowa da su ga ƙungiyar.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 207 (3/22)
GAME DA JAHADI NA NEMAN ‘YANCI DA KUMA JAHADIN KARE KAI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan tsinkaya ga wani ba’asi da aka gabatarwa majalisar dangane da jahadin neman yanci da kuma kare kai, bayan dogon tattaunawa dangane da lamarin, tare da sanyashi a ma’aunin fahimta jahadi da sakon da yake isarwa, alaka ta asali tsakanin al’ummar Musulmai da wadanda ba Musulmai ba ita ce aminci, kuma dalilin da ke haifar da yaƙi a Musulunci shine gaba da shinaddinin ko mabiyansa amma ba wai don an saba dokokin addini ba, bisa lura da saiye sauyen da aka samu ta fuskar kira zuwa ga Allah, da kuma cigaban da aka samu wurin saduwa da mutane a ƙasashensu ta hanyoyi daban daban.

Don haka majalisar ta zartar da abubuwa masu zuwa kamar haka

1. Jahadi a ma’anar na bai ɗaya: Shi ne matsa ƙaimi wurin ɗaukakar kalmar Allah tare da isar da sakon Musulunci ta dukanin hanyoyin da suka sawwaka kamar kudi da jiki, domin yaɗa adalci da aminci a tsakanin dukan al’ummu.
2. Jahadi nau’o’i biyu ne:

Jahadi Na Neman ‘Yanci: Wato shine wanda yake samarwa da kira zuwa ga Allah kariya tare da yaye dukan

wani tarnaki da ka iya kawo matsala, kamar yanda cikin manufarsa akwai kare ma su rauni da waɗanda aka zalunta a doron kasa bisa ka'idonin da malaman fiƙihu suka sanya kuma suka shardanta, manufarka hakan shine tabbatar da maslahar al'umma da kuma tunkuɗe ɓarna daga gare su. Allah mai girma yana cewa: **(Ku yaƙe su har sai babu wata fitina sannan ya zama duk wani bauta to Allah ake yiwa)** [al- Baƙra: 193], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Wai me ya sa ne ba ku son yaƙi domin ɗaukakar kalmar Allah alhali ga waɗanda aka raunata a doron kasa na daga maza da mata da ƙananan yara waɗanda ke cewa ya Ubangijinmu ka fitar da mu daga wannan alkaryar da mazauna cikinta suka kasance azzalumai)** [an- Nisa: 75].

Manufar jahadin neman 'yanci shine isar da sakon Musulunci babtare da tilastawa mutanen sai sun amshe shi ba, saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **(Babu tilasci a cikin addini)** [al- Baƙra: 256], Haka nan faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **(Babu wani abu da ke wajaba ga Manzo face isar da saƙon Allah abin bayyanawa)** [an- Nur: 54]. Haka nan faɗin Allah: **(Idan akwai wani abu akanka to bai wuce isar da saƙo ba)** [as- Shura: 48]. A bisa irin wannan nau'i na jahadi, sannan a bisa yanayin da ake ciki a yanzu, ya zama wajibi ga masu kira zuwa ga Allah su amfana da da alƙawura da yarjejeniyoyin da aka cimmawa na ƙasa da ƙasa wanda hakan ya sanya duniya ta zama gidan alƙawura na zaman lafiya, wanda hakan ya sanya ƙasashen bayar da daman tafiye tafiye domin isar da sako tare da 'yancin shiga sako da lungu kan hakan, hakanan halascin yin amfani da kafofin sadarwa na zamani, da kuma kafofin sadarwa na zamani domin yin kira zuwa ga Allah, hakanan isar da sakon Musulunci da harsuna daban daban zuwa ga al'ummu mabanbanta.

Dangane da wannan lamari wannan majalisar na tabbatar da tsayuwarta kan tabbatattun lamuran da shari'a ta tanadar kamar dai yanda hukunci da shwarwari kan haka suka gabata, kamar dai wajabcin yin tanaji tare da ƙarfafa

dakarun ƙasashen Musulmai da ba su kayan aiki waɗanda suka kamata da ke zama ƙarfin gwiwa ne garesu wanda manufar hakan shine kiyaye al'umma daga duk wani abun ki.

Jahadin Kare Kai : Shi ne abin da ya wajaba a yi na kare kai a shari'ance, wanda yake bayan yin ta'addanci akan wata al'umma ko wasu mutane ko akan addini ko ƙasa ko ɗaiɗaikun mutane, to hukuncin wannan jahadin yana gushewa ne da gushewar yin ta'addanci, tare da fitan abokanan gaba daga ƙasashen Musulmai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ku yaƙi waɗanda suke yaƙarku saboda ɗaukaka kalmar Allah, amma kada ku yi ta'addanci, domin Allah ba ya son masu yin ta'addanci)** [al- Baƙra: 190].

Don haka ƙungiya ta bayar da shawara kamar haka:

1. Samar da kotu mai adalci ta Musulunci domin raba rigima tsakanin ƙasashe da al'ummun Musulmai tare da yi mata garkuwa da dakarun na haɗaka da za a tattaro daga ƙasashen Musulmai daban daban.
2. Tabbatar da zartar da matakin da ƙungiya ta ɗauka a taronta na Bakwai mai lamba: 68 (6\7), wanda ya ƙunshi dawo da dokar samar da hukuncin kare haƙƙi a Musulunci, an tabbatar da hakanne a zama mai lamba 128 (2\14), wamdaya ƙunshi samar da wani kundi na Musulunci da tattara dokokin ƙasa da ƙasa kan kare haƙƙin bil'Adama.
3. Ɗorawa wani kwamiti na malamai ƙwararru domin samsr da manhajar karatu wacce ta ƙunshi yin bayani akan haƙƙoƙi na Musulunci a sashen alaƙar ƙasa da ƙasa wurin zaman lafiya da kuma yanayi na yaƙi, sannan manhajar zata rinƙa lura da sababbin abubuwa ta kuma yi riƙo da tabbatattun abubuwa na asali.

Allah Maɗaukakin Sarki ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 208 (4/22)
GAME DA KAFIRTA MUSULMI, DALILAN HAKAN, GURABUN HAKAN, DA YANDA ZA A MAGANCE HAKAN

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan tsinkayar wannan ƙungiya akan binciken da aka gabatar gareta dangane da lamarin kafirtawa da dalilan hakan da gurabiun hakan da yanda za a magance hakan, to bayan sauraron tattaunawa da kai komo kan lamarin, a bisa la'akari da ƙarfin halin da wasu keyi na kafirta Musulmai tare da saurin jefa Kalmar ridda ga ɗaiɗaikun mutane da kuma sauran al'ummu da ƙasashe da kuma gwamnatoci ba tare da lura da koyarwar shari'a da manufofinta da ƙa'idojinta ba.

A bisa lura da hadarin da hakan ke haifarwa bisa wannan ƙarfin halin ne na kisa da rushe rushe da fatattakan mutane daga matsugununsu.

Bayan bijiro da abin da shari'a tayi tanadi kan hakan domin kiyaye hadin kan al'ummun Musulmai da ɗaiɗaikun mutane daga hadarin kafirtawa, An ɗauki matakai da suka hada da:

Na Farko: Tabbatar da matakin ƙungiya mai lamba 152, (1/17), wanda aka fitar a taro karo na Goma Sha Bakwai (17),dangane da sha'anin Musulunci da hadin kan al'umma da mazhabobin aƙida da na fiƙihu da na tarbiyyantarwa, wanda ya ƙunshi rashin aminta da kafirta kowace irin ƙungiya ta Musulunci wacce ta kasance tana yin Imani da Allah Madaukakin Sarki, da Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), haka kuma tayi Imani da rukunan Musulunci, sanna bata yin inkarin wani sanannen abu na addini wanda hakan ke warware imanin mutum.

Na Biyu: Tabbatar da matsayin ƙungiya mai lamba 170 (1/19), dangane da 'yancin addini a shari'ar Musulunci: Ƙololuwarta da matakanta, wanda ya ƙunshi hukuncin cewa fatawar yin ridda ko kafirtawa na komawa ne zuwa gam asana ilimi wadanda aka aminta da su tare da bin matakan da malaman fiƙihu suka sanya wanda hakan ke kawar da shubuha…, sannan yake gargadin yin duk wani yunƙuri na danganta kafirci zuwa ga wata ƙungiya cikin ƙungiyoyin Musulmai, ballantana kuma kafirta sahabbai da iyayen muminai Allah ya ƙara musu yarda baki daya,ko kuma ƙasƙantar da su da rashin darajanta su.

Ƙungiya ta bayar da shawarwari kamar haka:

1- Sakatariyar ƙungiyar zata cigaba da zartar da umurni da ta bayar a baya, wacce ta yi kira a kai,wacce ta ƙunshi shirta tarurruka da ganawa da juna domin tattaunaa wasu abubuwa kamar haka:

a) Mas'alar miƙa wuya da barranta.

b) Hadisin ɓangaren da yake kuɓutacce, da abin da aka gina akai wurin samun sakamako.

c) Kafirtawa saboda rashin zartar da hukunce hukunce shari'a na Musulunci na bai daya.

Don haka ƙungiya ta bayar da wasicci kamar haka:

1. Yiwa samarin Musulmai gargadin bibiyan ma'abota karkataccen tunani da ma su shisshigi ko wuce gona da iri, tare da karkatar da su zuwa ga ingantaccen ilimi mai amfani, bisa manhajin ilimi na tsaka tsaki,sannan su yi

koyo da managartan magabata da abin da suka zo da shi daga cikin sahabbai da tabi'ai da waɗanda suka bisu da kyautatawa.

2. Dole ne malaman al'umma da masu kira zuwa ga Allah daga cikinsu su cigaba da tattaunwa da matasan tare da cigaba da gudanar da ayyukansu na kira zuwa ga Allah, sannan yin umurni da kyakkyawan aiki da hani kana bun ƙi bisa manhaji na tsaka-tsaki.
3. Ya wajaba ga hukumomi da ƙasashe su samar da hanyoyin sauƙaƙawa da gusar da wahlhalun dake hana ganawa da matasa kai tsaye domin fuskantar da su zuwa ga kyakkyawar hanya daga malamai jagororin wurin inganta rayuwar da tunanin al'umma.
4. Dole ne a samu hanyoyin amfana daga wasu ƙasashe da suka samu nasarar tattaunawa da ma'abota tunani mare kyau, daga cikin akwai gwajin da aka samu daga ƙasar Saudiyya da "Munasaha" wanda hakan ya dawo da waɗanda suka kauce hanya zuwa ga madaidaiciyar hanya.

Allah Maɗaukakin Sarki ne mafi sani;;

Da sunan Allah mai yawan rahama da jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 209 (5/22)
GAME DA HAƘƘOƘI DA WAJIBAN ‘YAN ƘASAN DA BA MUSULMAI BA DA KE RAYUWA A ƘASASHEN MUSULMAI DA KUMA YANDA SHARI’AR MUSULUNCI ZAI IYA SHAFANSU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, waɗanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan tsinkayar wannan ƙungiya akan binciken da aka gabatar gare ta dangane da lamarin haƘƘoƘi da wajiban mutum ‘yan ƙasa waɗanda ba Musulmai a ƙasashen Musulmai, da kuma yanda shari’ar Musulunci za ta iya shafansu, bayan sauraron wannan batu an samu matsaya kamar haka:

Na Farko: Lallai shari’ar Musulunci ta samarwa da waɗanda ba Musulmai ba haƘƘoƘinsu n agama gari da kuma na ƙashin kai, kamar dai yanda ta samarwa Musulmai, duk abin da Musulmai ke da shi su ma suna da shi, hakanan duk abin da ke kan Musulmai ‘yan ƙasa shi ma yana kansu, dukansu a sahu ɗaya suke wurin haƘƘoƘi da wajibai.

Na Biyu: Suna da ‘yancin bin na su tsarin shari’ar wurin yin bautarsu ko yanayin zamantakewarsu kamar aure da

makamancin haka, sannan ya halasta a naɗa alƙali daga cikinsu domin yin hukunci a tsakaninsu, sanna hukuma ta zartar da abin da alƙalin ya hukunta, bayan haka kuma hukuma na da ikon zartar da duk wani hukunci akan kowa da bisa doka ba tare da duba addinin ɗan ƙasa ba.

Na Uku: Duk abin da ya wajaba ga dukan waɗanda ba Musulmai ba da suke rayuwa a ƙasashen Musulmai, to shima ya wajaba akan Musulmai wurin kiyaye dokokin gwamnati da zamantakewa da ladubba na bai ɗaya a cikin ƙasa,tare da rashin karya duk wata doka da gwamnati ta sanya, sannan miƙa wuyansu – baki ɗaya – ya kasance ga hukumar da suke zaune ne a cikinta, kuma suna danganta kansu zuwa gareta.

Na Huɗu: Ya wajaba ga dukan kafofin yaɗa labarai su himmatu da yaɗa haƙƙoƙin waɗanda ba Musulmai ba dake rayuwa a ƙasashen Musulmai, wacce shari'ar Musulunci ta samar musu, manufar hakan shine yaɗa wayewar Musulunci da kuma rangwamen dake cikinsa da adalcinsa, tare da sanya wannan lamarin cikin manhajar karatu.

Na Biyar: Ya wajaba ga kafafen yaɗa labarai baki ɗaya su nesanci tayar da fitina ko tunzura mutane kan rikicin ƙungiyanci tsakanin 'yan ƙasa ɗaya, wanda hakan zai taimaka wurin amar da zaman lafiya da ƙarfafa tsaron ƙasa.

Allah Maɗaukaki ne maifi sani;;

Da sunan Allah mai yawan rahama da jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 210 (6/22)
GAME DA LAMARIN KAWARWA DA KUMA AMFANA DA ABUBUWA DA SUKA SHAFI KAYAN ABINCI DA MAGUNGUNA

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan ɗorawa taron ƙarawa juna ilimi nauyi yin nazari akan matsalar kawarwa da amfana da abubuwa daga sakatariyar ƙungiya an samu nasarar tabbatar da abubuwa kamar haka:

Na Farko: Dangane da fayyace ma'anar kawarwa to an samu matsaya wurin hakan a taro mai lamba: 198 (4/ 21), tare da wani ƙari da aka samu, ta inda zai kasance kamar haka: Ma'anar kawarwa wurin malaman fiƙihu shine " Canzawar abu mai najasa ko haramtacce na haƙiƙa, tare da canzawarsa zuwa wani sinadari na daban wanda ya saɓa da na baya a suna ko keɓantaka ko siffa, ana bayyana hakan ne a ma'anar Ilimi da ya shahara kan cewa shine dukan wani abu da ake iya sauya masa fasali a kimiyyance, kamar dai sauya yanayin mai da kitse ba tare da la'akari da asalinsu ba zuwa sabulai, sannan a mayar da su zuwa sinadarai daban daban da za aiya yin abubuwa da su masu yawa, kamar dai yanda ake iya sauya fasalin sinaran a kimiyyance

na nufi ta hanyoyin ilimi na fasaha, hakanan akanyi hakanne ba tare da bin tsarin da malaman fiƙihu suka sanya ba,misalign hakan shine tace abu ko ƙona shi, amma idan ya zama sauya fasalin abu na kimiyya ya ƙunshi wani sashe ne to ba a kallon hakan a matsayin kawarwa, koda kuwa sinadarin najasa zai cigaba da kasancewa a matsayinsa na haram wanda bai halasta ayi amfani da shi ba.

Amma shi "amfana" shine cusa wani abu cikin wani abu, ta inda siffarsa na Sali ke gushewa sai na ƙarshe shi ke bayyana, ta yanda zai yi wuya a iya banbance tsakanin wanna da wancan saboda yawaitar abubuwan da aka gwama su wuri ɗaya.

Hakan na kasancewa ne bisa lura da ƙa'idoji da hanyoyin da aka cimma matsaya a kansu tsakanin masana a kan duk abubuwan da suka gabata.

Na Biyu: Dangane da buluzuma "ruwan da ke haɗe da jini' wanda irinsa yazo cikin abubuwan da aka ambata abaya ɗazun, wannan ƙungiya na kallon akwai buƙatar sake yin nazari a cikin lamarin saboda samun wasu sabbin abubuwa da ke rataye da shi lamarin, don haka an samar da kwamiti domin bincike akan wannan lamarin.

Na Uku: Bisa la'akari da matakin da ƙungiya ta ɗauka wanda aka yi nuni zuwa gare shi wanda ya shafi "amfana" wanda yazo a cikinsa, amma dangane da shi kansa amfana ɗin ra'ayin ƙungiya shine jinkirta shi domin zurfafa bincike akansa.

Na Huɗu: Amma kayayyakin maye da dangoginsu tare da gusar da tasirinsu kuwa:

Haƙiƙa waɗanda suka halarci taron tattaunawa kan lamarin da yazo dangane kayayyakin da aka samar ta hanyar haramtattun abubuwa da masu najasa cikin abinci da magunguna a taron da aka yi a ƙasar Kuwait a tsakanin 22 – 24 na watan Zul Hijjah na shekarar 1415 Hijiriyya wanda ya yi daidai da 22-24 Mayu 1995 a ƙarƙashin Ƙungiyar ƙasashen Musulmai sashen ilimin likitanci dake

Kuwait, rahoton taron ya ƙunshi waɗannan abubuwa masu zuwa:

Ƙa'idoji na bai- ɗaya:

1. Ya wajaba akan kowani Musulmi ya lizimci bin hukunce hukuncen shari'ar Musulunci musamman a sashen abinci da magunguna, domin hakan shine ke tabbatar da ingancin abin da yake ci ko yake sha ko yake magani da shi. Yana daga cikin rahamar Allah ga bayinsa tare da saukaka hanyoyin bin shari'arsa lura da yanayin hali na larura, sannan da la'akari da matuƙar buƙatuwa zuwa ga bin koyarwar shari'a akan abubuwa da aka sanya, daga cikin haka akwai : Larura da ke iya halasta haram, sannan buƙata mai tsanani kan iya sauka a matsayin abu na larura matuƙar buƙatar hakan ta bayyana, saboda asalin hukuncin mu'amala da abubuwa shine halasci matuƙar ba wani dalili na haramci ne ya gufta akansu ba, hakanan asalin kallon da akewa abubuwa shine tsarkakuwarsu daga najasa, saidai fa idan wani dalili ya zo don tabbatar da najasarsu, amma fa ba a lura da haramcin cin wani abu ko shan sa a matsayin hukuncin najasarsa a mahangar shari'a, sai dai idan hukuncin cewa shi najasa ne tun asali saboda asalin alamar da ke kan abubuwa halasci ba haramci ba.
2. Sinadaran dake tattare da kayan maye da ba najasa ba ne a shari'ance, a bisa la'akari da abin da ya gabata na cewa asalin abubuwa shine halasci, shin kayan mayen madararsu ne ko kuma an surka su da ruwa.

A bisa haka, babu laifi ayi amfani da abubuwan da ke tattare da kayan maye a cikinsu a matsayin magunguna kamar dai sinaran wanke ciwo ko rauni, ko kuma magungunan kashe ƙwayoyin cututtuka, ko kuma amfani da kayayyakin ƙanshi (Na ruwa) waɗanda ake amfani da su

wurin narka sinadaran ƙamsasa wuri masu tashi sama, ko kuma ma amfani da mayukan kireem ma su kama da kitse wanda ake iya samun sinadaran kayan maye a cikinsu, amma fa giya bata cikin wannan rukunun domin haramcin amfani da ita a bayyane yake cikin shari'a.

3. Duk da cewa kayan maye sinadari ne wanda ke sanya mutum yin maye kuma an haramta ta'amuli da su,don haka akwai buƙatar al'ummar Musulmai su yi ƙoƙarin samar da wasu hanyoyi daban na sana'anta kayayyakin magunguna da babu kayan maye a cikinsu, musamman magungunan yara ƙanana da kuma na ma su ciki, to fa babu laifi ayi amfani da magungunan da da ake sana'antawa a yanzu haka wanda ake samun sinadaran mare ɗan kaɗan a cikinsu, hakan na kasancewa ne domin kiyaye magungunan ko narkarwa wanda ruwa kawai ba ya iya narkar da su, amma fa hakan yana kasancewa ne idan har ya zama babu makwafin waɗancan da ke ɗauke da sinaran sanya maye, don hakan taron ƙarawa juna ilimin ya buƙaci sashen da ke kulawa da kiwon lafiya da ya yi ƙoƙarin iyakance adadin da ake iya samu na kayan maye cikin magungunan a mahangar ilimi da dokokin samar da magunguna.
4. Bai halasta ba a ci wani abu na ci ko na sha wanda yake haɗe da wani sashe na giya komai ƙanƙantarsa, musamman ma waɗanda suka shahara a ƙasashen Turai, kamar wasu nau'uka na cakulati ko kuma kayayyakin sanyi dake da ƙanƙara a cikinsu, (kamar dai irinsu Ice kireem da dangoginsu), hakanan wasu nau'uka na lemon kwalba, wannan na kasancewa bisa lura da cewa duk wani abu da ya gusar da hankalin mutum shin mai yawa ne ko kaɗan ne to haramun ne, sanna babu wata hanya da za a iya buɗewa

mutum ita don halasta masa ita koda bisa togaciya ne.

5. Dukan kayan abincin da akae amfani da wani sashe na kayan maye a cikinsu domin narkar da su saboda ruwa baya iya narkar da su ko sanya musu kala ko kiyayesu daga lalacewa da dai abubuwa makamantar hakan, to ya halasta aci irin waɗannan kayayyakin na abinci saboda lalurar dake cikinsu gamammu ne wato an ɗaiɗaita su a ciki, sanna mafi yawansu sukan gushe a yayin sana'anta abincin ko abin shan, wannan dai ya zo ne bisa bayanin hukumomin lafiya da kula da kayayyakin abinci, tare da kwaɗaitar da samar da wasu hanyiyin da za a nesanci irin waɗannan masu kayan mayen a cikinsu.
6. Kayan abincin da ake samun kitsen alade a cikinsu wurin sana'antawa kamar su jubna da wasu Nau'o'in man girki da man shafawa da kuma man shanu da bidkit da cakuleti da aiskirem, to bai halasta a ci ko sha su ba kai tsaye, wannan yazo bayan ijima'ain malamai kan cewa alade najasa ne, don haka bai halasta a ciki namansa ba, sannan babu wata larura da zata halasta cikin irin waɗannan abubuwa.
7. Sai kuma wani abu da ake kira da suna (Jilateen) kwamitin da aka ɗorawa alhakin bayar da ba'asi akansa ya bayar da shawarar komawa da batun zuwa ga sakatariyar ƙungiya domin sake bincike akansa.

Sinaran hurmonat da inzimat:

- Shi "Hurmonat" dai sinadari ne na kimiyya wanda ake samowa daga jinni ta hanyar kurmar uwar hanji, wanda wannan sinadarin kan iya tsara hanyar tafiyar da aikin hanji da ma jikin mutum baki ɗaya.
- Shi kuma "Inzeem", wani sashe ne na frorten wanda ya fitar da wasu sinadarai da ke yiwa jiki tasiri ta

hanyar daidaita yanayin jikin da sinaran kimiyya a duk wani jiki mai motsi ba tare da ya gushe daga jikin halittan ba.

- Shi kuma "Haibarin" wani abu ne da ake cirowa daga naman alade, to bai halasta ayi amfani da shi ba sai fa a halin larura, musamman idan aka sirkashi domin samun wannan sinadarin domin amfani da shi, to irin wannan ba a lura da cewa gusarwa ne na gaba ɗaya wanda zai iya zama wani abu ne mai zaman kansa na daban da baida alaƙa da asalinsa wato alade, amma wanda ake samarwa ta hanyar fasaha ba tare da anyi amfani da wani sashe na alade ba to irin wannan babu wata matsala a ciki wurin amfani da shi.
- Shi kuma "Insolin" wanda ake samowa daga naman alade, tobai halasta ayi amfani das shi ba sai dai ahalin lalura na rashin samun makafinsa wanda yake halastacce, amma insolin da ake samowa daga jikin mutum ta hanyar kimiyya da fasaha to amfani da shi halas ne.
- Shi kuma "Maganin ciwon zuciya" wanda ake samu domin kwafe na mutum da shi domin magani na kasancewa ne kodai na ƙarfe ko na rayayyen abu, (mutum ko dabba), ya halasta ayi amfani da shim amma wanda ake samowa daga jikin alade bai halasta ayi amfani da shi ba sai dai a yanayi na lalura.

Domin haka wannan majalisar da ƙungiyar ta tabbatar da abubuwa ma su zuwa kamar haka:

- Jubuna wanda aka sana'anta daga wasu halittu :
  1. Haramcin amfani da abin da aka ciro daga alade saboda najasa ne.
  2. Idan wani sashe na jikin halitta ya zama daga dabba ne wanda ake ci namansa da aka yanka to wannan halal ne ayi amfani da shi.
  3. Amma fa idan abin da ake ciro daga dabba ba irin wanda ake yankawa bane ko daga matacciyar dabba, to mafi yawan waɗanda

suka halarci taron suna ganin rashin ingancin amfani da shi saboda rashin tsarkinsa, yayin da wasu kuma ke ganin halascinsa tare da tsarkinsa.

4. Ya halasta ayi amfani da wani sashe na hanjin da aka samo ta hanyar kimiyya wanda wasu na'aurori ke samarwa na musamman.

- **Ruwan shan da aka yi amfani da shi a tun farko:**

Ana nufin nau'in ruwan da mutum ya yi amfani da shi a baya, shin a gida ne ko kuma a wurin aiki ko a kamfani, wanda ke ƙunshe da abin da mutum ya fitar daga jikinsa, ko kuma yake cakuɗe da dagwalon masana'antu.

Amfani da ruwan da aka rigaya aka yi amfani da shi :

Majalisar ƙungiyar ƙasashen Musulmai ta yanke shawarar halascin amfani da ruwan sha wanda aka sake tacewa bayan anyi amfani da shi a wurin mu'amala, kamar dai wanke gidaje da riguna da gonaki wacce babu kayan ci a cikinsu matuƙar bas a cutarwa, amma matuwar ruwan zai iya cutarwa to bai halasta ayi amfani da shi ba gabaki ɗaya saboda gudun cutarwa.

Ya halasta ayi amfani da ruwan wurin ci k osha idan har babu cutarwa, amma bai halasta ayi amfani da ruwan a wurin ibada ba har sai an tabbatar da tsarkin ruwan.

Don haka shawar da aka bayar nag aba ɗaya ita ce:

1) Halascin yin aiki domin sabunta ruwan da akayi amfani da shi, aki koda ma ba ayi amfani da shi ba ana buƙatar hakan, wannan wajibi ne a shari'ance, saboda kawar da ɓarnar da ke iya samun mutum da mahallinsa, to wanna wajibi ne ba tare da lura da alfanun da ake iya samu ta fuskar tattalin arziki ba da yake dawowa mutum bayan hakan, koda kuwa daga koguna aka samo ruwa ko daga tafkuna, hakan na kasancewa ne bisa la'akari da maganar cewa kawar da ɓarna abin gabatarwa ne agaban jawo abu mai amfani.

2) Wayar da kan mutane kan amfani da ruwan sha a kowa ce irin fuska, shin a gida ne ko a wuraren aiki ko a gonaki, domin shari'a ta kwaɗaitar da yin hakan.

3) Bibiyan hanyoyin da zasu taimaka wurin samo hanyoyin sabunta ruwan shan da aka yi amfani da shi, musamman wanda za a kasha kuɗi mafi ƙaranta a ciki, da ƙarancin amfani da makamashi akan hakan, saboda kawar da abin da ka iya faruwa idan ba a yi hakan ba.

4) Cigaba da gwaji da bincike na ilimi da zai taimaka wurin samar da ingantaccen ruwa da aka sabunta domin amfani da ruwan ta fuskokin da suka halasta.

5) Sanya ido sosai akan na'aurorin da suke aikin tace ruwan.

6) Cigaba da kulawa da ingancin kayan amfanin gonan da aka yiwa banru da ruwan da aka sabunta da irin wannan ruwan.

7) Wajabcin sanya alamomi akan kayayyakin da ake noma su da irin wannan ruwan domin mai saye ya kwana da sanin hakan.

8) Amfana da dagwalon dake cikin ruwan da aka sabunta wurin samar da makamashi, wanda hakan zai taimaka wurin hana lalacewar mahalli.

- **Abincin dabbobi: Wato abincin da suka ƙunshi abubuwa haramtattu ta fuskar amfani da su da kuma tasirinsu.**

Majalisar wannan ƙungiya ta tabbatar da cewa ya bai halasta ayi amfani da kwalaye ko murafen da suka ƙunshi sassan mutattun dabbobi ko jinni ko naman alade da kuma sinaran da ke yaƙi da ƙuraje ko makamatan haka ba, saboda hakan na iya cutar da mutum kai tsaye.

Don haka majalisar ƙungiyar ƙasashen Musulmai na bayar da shawarar kulawa sosai da murafan abubuwa ko kwalaye da suke fitowa daga ƙasashen Musulmai domin tabbatar da cewe ba su ƙunshi ire-iren abubuwan da aka ambata a baya ba.

Allah Maɗaukakin Sarki ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 211 (7/22)
GAME DA SHUGABANCIN MACE

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar wa Cibiyar game da batun shugabancin mace, da kuma sauraron tattaunawar da aka yi a kusa da shi. ta yanke shawara akan masu zuwa:

Na Farko: Majalisar ta tabbatar da cewa Musulunci ya ba wa mata cikakken yancinsu, ya kuma ba su matsayin da ya dace da su, tare da la’akari da matsayinsu na zamantakewa, da illolinsu, da manufofinsu na uwa, ‘ya, mata da mata masu riḳon amana.

Na biyu: Majalisar ta yi la’akari da ra’ayin mafi yawan malaman fiḳihu na cewa mata ba su da wani matsayi mafi girma (shugabancin ƙasa).

Na uku: Jagorancin mata na ayyukan jama’a, kamar ɓangaren shari’a, ma’aikatu, da makamantansu, lamari ne da ke haifar da saɓani a tsakanin malaman fiḳihu na mazhabobi daban-daban, kuma babban saɓani ne. Kuma malaman fiḳihu na kowace kasa suna auna abin da suke gani daga maganganun malaman fiḳihu.

Na huɗu: A yayin da mace ta karbi wani umarni daga abin da ya gabata, to dole ne ta kiyaye ƙa'idoji da ladubban da Shari'ar Musulunci ta gindaya, musamman na abin da ya shafi tufatarwa da sauran abubuwa, da shigarta cikin waɗannan farillai ko jama'a kada ayyuka su ɓata aikinta na ilimi ga danginta.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinkai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 212 (8/22)
GAME DA GARANTIN BANKIN NA KASADAR DA KE TASOWA DAGA ƁATAR DA KUƊAƉEN ABOKAN CINIKI DA KUMA BIYANSU DIYYA KAN ƁARNAR DA AKA YI

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar wa makarantar dangane da batun bankin na tabbatar da illolin da ke tattare da almubazzaranci da kuɗaɗen abokan hulda da kuma biyan su diyya da aka samu, da kuma sauraron tattaunawar da aka yi a kusa da shi, an yanke shawarwari masu zuwa:

Na farko: Abin da ake nufi da garantin banki shi ne cewa bankin ya ɗauki alhakin ɓarna ko ɓarna (asara) na kuɗin masu ajiya da masu hannun jari.

Na biyu: Bayanin hannun bankin akan kuɗaɗen da aka ajiye dasu: Hannun bankin yana juyawa tsakanin:

1. **Hannun garanti:** Shi ne mallakar kuɗi don mallaka ko don amfanin mai shi, kamar: hannun wanda ya saya, da wanda yake riƙe da farashin sayan, mai jinginar gida, mai cin riba, mai shi, da wanda ya ci bashi.

Buƙatar ajiyar kuɗi (asusun kuɗi na yanzu) suna ƙarƙashin hannun garanti daga asusun banki.A wannan batun, Cibiyar ta tabbatar da hukuncinta mai lamba 86 (3/9) game da abin da aka bayyana a cikin adibas, sakin layi na farko, na buƙatar ajiya (na yanzu). Accounts), Ko

bankunan Musulunci suna da lamuni ta fuskar shari'a, domin bankin da ke karɓar waɗannan kuɗaɗen yana da hannu a matsayin lamuni a gare su kuma a shari'ance wajibi ne ya amsa idan aka nema.

2. Hannun amana: Shi ne mallakar kuɗi a madadin, ba mallakarsa ba, tare da iznin mai kuɗin, fili na mai ajiya, mai karɓar bashi, wanda ya ci bashi, abokin tarayya, mai hasashe, shugaban kuɗin. Kyauta, amana, da makamantansu.

Kuma tana ƙarƙashin Nau'o'in amana ne daga asusun bankin Musulunci: asusun zuba jari a bankin Musulunci, jari ce ta hasashe, kuma tanade-tanaden hasashe (bayar da ba da lamuni) a cikin shari'ar Musulunci ya shafi shi, gami da rashin halaccin mai hasashe (Bankin yana ba da garantin babban hasashe).

Na uku: Banki mai hasashe ba zai iya tabbatar da asara gabaki daya ko wani ɓangare ba a cikin asusun zuba jari, sai dai idan ya ketare iyaka, ko ya gaza, ko ya saba wa sharuɗɗan da suka dace da sharuɗɗan dokokin shari'a na gaba ɗaya, daga cikin abin da ya shafi zalunci akwai:

1. Rashin bin ƙa'idojin Shari'a da bankin ya tanada a cikin kwangiloli ko yarjejeniyoyin buxe asusun zuba jari na iri daban-daban.
2. Keta dokokin banki da kasuwanci, dokoki, da kwastam da hukumomin da ke da alhakin kula da harkokin banki suka fitar, sai dai idan sun saba wa tanade-tanaden Shari'ar Musulunci.
3. Rashin gudanar da isassun nazarin yuwuwar kuɗaɗe ga abokan ciniki.
4. Zaɓin dabaru da hanyoyin da ba su dace ba don ayyuka.
5. Rashin bin umarni da hanyoyin da bankin ya tsara.
6. Rashin ɗaukar isassun garanti kamar yadda ƙa'idojin da suka dace suka buƙata dangane da wannan.

Na huɗu: Ba ya halatta a sanya banki a matsayin mai mudaraba a cikin sharaɗi. Saboda karya sharuɗɗan

kwangilar Mudaraba, don haka ne Cibiyar ta tabbatar da abin da ya zo a cikin ƙuduri mai lamba 86, da kuma abin da ya zo a cikin ƙuduri mai lamba 30 (4/5) a Muƙarada Sukuk cewa (shi ne. Bai halatta ba ga mai yiwuwa ko Muƙarada Sukuk ya haɗa da tanadin da ke tabbatar da abin hasashe babban jari ko garantin ribar dunƙule ko wanda aka danganta ga babban birnin. Mai haƙƙin samun irin wannan riba.

Na biyar: Nauyin hujja a cikin da'awar asara ya koma banki saɓanin yadda yake a asali, matuƙar dai akwai hujjoji da suka saba wa ainihin da'awar rashin cin zarafi, da abin da ke ƙarfafa aikin wannan ƙa'ida:

- **a-** Idan an san mutane ba su yarda da maganar mai hasashe (Banki) har sai ya kafa hujja da gaskiyar ikrarinsa na rashin cin zarafi ko sakaci.
- **b-** Tabbatar da zargin da ake yi wa amintaccen: Abin da ake nufi da shi shi ne, kasancewarsa gaba ɗayan zato cewa shi (mai hasashe) ba ya da gaskiya a da'awarsa ta rashin cin zarafi ko sakaci. Kamar yadda ake sa ran mai hasashe zai ceci jarin da aka zuba daga asara, da kuma samun riba da riba.
- **c-** Shaidar sha'awar canja wurin nauyin hujja zuwa ga mai mudaraba (banki), don kare kuɗin masu zuba jari daga asarar lokacin da mai mudaraba ya yi iƙirari ko asarar kuɗin masu zuba jari.

Na shida: Ya halatta bankin da ake hasashe ya bayar da wani ɓangare na ribarsa ba tare da wani sharaɗi ba a cikin kwangilar hasashe.

Na bakwai: Hukumomin da aka damka wa alhakin tantance alhaki na rashin amfani da bankin na zuba kuɗaɗen masu hannun jarin suna da yawa, ciki har da:

1) Hukumomin sa ido irin su manyan bankunan kasar, walau cibiyar hada-hadar kuɗi ta Musulunci ko na gargajiya, suna da kwamitocin da suka ƙware a harkar bankin Musulunci.

2) Cibiyoyin sasantawa, sasantawa da sasantawa, kamar Cibiyar sulhu da sasantawa ta Musulunci ta Duniya da ke Dubai.

3) Masu binciken asusu, bisa ga abin da ya tabbata a cikin sana'ar tantancewa, kuma an yi la'akari da wannan nauyi da alhakin da ya rataya a wuyan mai binciken kuɗi na waje a cikin ma'auni na 5 na ƙa'idojin lissafin kuɗi da ƙungiyar kididdigar lissafi da kididdigar kuɗi ta Musulunci a Masarautar Bahrain ta bayar, kuma za a iya sanya lamarin ga Hukumar Kula da Shari'a.

Na takwas: Diyya ga asarar da aka yi a cikin asusun saka hannun jari yana iyakance ga lalacewa ta ainihi – shin asarar gaba ɗaya ce ko wani ɓangare ba tare da tabbatar da asarar riba ba (damar dama); Domin kawai tsammanin da ba ta dace ba.

Cibiyar tana bayar da shawarwari masu zuwa:

1. Ƙaunar bankunan Musulunci na yin taka-tsan-tsan wajen zuba jarin masu ajiya da kuma bin duk hanyoyin da hanyoyin da za su kare kuɗaɗensu da kau da kai daga gare su, da samar da kuɗi da kuma samar da tanadi da rabon da ya dace don hakan.

2. Kira ga ƙasashen Musulmi da su fitar da dokokin da suka shafi kafa cibiyoyin tabbatar da kuɗaɗen masu ajiya, ko yin gyara ga dokokin da ake da su a halin yanzu bisa tsarin inshorar da cibiyoyin hada-hadar kuɗi na Musulunci ke shiga, kuma ana gudanar da waɗannan kuɗaɗe ne bisa ga abin da aka yi mu'amala da su. Tare da Cibiyar Nazarin Fiḳihu ta Duniya a cikin ƙuduri mai lamba: 200 (21/6) dangane da tanade-tanaden Shari'a da kula da tushe na inshorar haɗin gwiwa.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 213 (9/22)
GAME DA HAƘƘOƘIN NAƘASASSU A SHARI'AR MUSULUNCI

Lallai majalisar cibiyar Fiḳihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan ta duba bincike da nazarin da aka gabatar wa Cibiyar dangane da abin da ya shafi haƙƙin naƙasassu a fannin shari'a, da la'akari da irin kulawar da Shari'a ta bayar, da kuma sauraren bahasi da aka yi a kusa da shi, an yanke shawarwari masu zuwa:

1. Naƙasa yana nufin: mutumin da ba zai iya yin aikin da yake buƙata ba (hankali, hankali ko ta jiki) idan aka kwatanta da mai lafiya.
2. Abin da ake nufi da haƙƙin naƙasassu: ƙwararrun ƙwararrun da doka ko tsari suka tsara musu, don yin rayuwa mai kyau.
3. Shari'ar Musulunci ta kula da haƙƙin naƙasassu, ta mayar da su wani ɓangare na al'umma, suna da haƙƙi daidai da sauran, kuma suna da haƙƙi daya da na sauran, sai dai abin da aka cire daga cikinta na nassi na shari'a.
4. Naƙasassu na da haƙƙi a kan iyalinsa, wadanda ake wakilta wajen ɗaukar matakan da suka takaita

faruwar nakasa tun farko, da kuma iyalan nakasassu da samar da abin da ya kamata ga nakasassu, da kuma gyara masa tarbiyya bisa soyayya da mutuntawa, da kokarin saduwa. Bukatunsa na yau da kullun kamar aure, gidaje, da makamantansu.

5. Nakasassu yana da hakkoki a kan al'ummarsa, wadanda mafi muhimmancinsu su ne: had'a shi da sauran jama'a, da kyautata masa zumunci, da girmama shi da rashin tauye shi ta kowace hanya, da sanya karfinsa da kwazonsa ga abin da zai amfane shi. Da al'ummarsa da alhairi da fa'ida.

6. Nakasassu na da hakki akan jiha, kamar haka:

- Kula da lafiyarsa ta hanyar kafa cibiyoyin kiwon lafiya na musamman don kula da shi da gyara shi, da horar da masu kula da shi kai tsaye yadda za su kula da shi.
- Ilimin da ya dace a gare shi, wanda hakan ya hada da samar masa da sabbin hanyoyi da hanyoyin ilimi, da kuma shirya malamai da suka kware wajen tarbiyya da tarbiyya.
- Aikin da ya dace da iyawarsa da iyawarsa, gami da horar da shi don ya cancanci shiga kasuwar aiki.
- Wanda ya isa ga mabukata masu nakasassu ta hanyar zakka, kyauta da kuma Bait al-Mal.
- Motsi ta hanyoyin da suka dace da shi, gami da shirya masa hanyoyin sufurin da suka dace, da samar da ka'idojin gine-gine da wuraren jama'a da ke saukaka motsi da sufuri.
- Samar da dokoki da ka'idoji masu kiyaye hakkinsa da bin diddigin aiwatar da su.

Majalisar ta ba da shawarar wadannan:

1) Yi aiki don ilimantar da dangi da al'umma game da hakkin nakasassu ta kowane hali, ta hanyar kafofin watsa labarai, ilimi, al'adu da shirye-shiryen zamantakewa.

2) Taimakawa hukumomi da hukumomi masu zaman kansu da cibiyoyin da suka shafi al'amuran naƙasassu, da ƙarfafa wuraren tallafi ga waɗannan hukumomi.
3) Gudanar da tarurruka, tarurrukan karawa juna sani da karawa juna sani da suka shafi naƙasa.
4) Ƙirƙirar karatu da cibiyoyin bincike da suka shafi al'amuran naƙasassu, da kuma amfana da su ta hanyar shirye-shiryen da aka yi wa naƙasassu.
5) Faɗaɗa tagogi na sadarwa tsakanin al'umma da naƙasassu, da kafa da tallafawa ƙungiyoyi masu kula da haƙƙoƙinsu da ɗaukar al'amuransu a matakin gida da na waje.
6) Majalisar ta tabbatar da yin duk wani abu da zai kai ga rage musabbabin naƙasa da suka hada da duba lafiyar kafin aure, allurar rigakafin cutar shan inna da sauransu.
7) Ƙaddamar da yarjejeniyoyin ƙasa da ƙasa kan haƙƙin naƙasassu ta hanyar da ba ta saba wa tanade-tanaden Shari'ar Musulunci ba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 214 (10/22) GAME DA RINJAYE DA ƘARFAFAWA A MA'AMALOLIN KUƊI: SHARI'O'IN SU, ABUBUWAN DA SUKE SARRAFAWA, DA KUMA YANAYIN TABBATAR DA SU

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan nazarin shawarwarin da taron masana kimiyya ya bayar kan batun fifiko da biyayya a cikin hada-hadar kuɗi, da shari'o'insu, da tsare-tsarensu, da sharuɗɗan tabbatar da su, wanda aka gudanar a Jidda a tsawon lokaci: 25-26 Safar 1436 Hijira, daidai da 17-18. Disamba 2014, da kuma bayan nazarin shawarwarin da kuma yin la'akari da shawarar Cibiyar da ta dace, wato ƙuduri mai lamba: (30), da ƙuduri mai lamba: (188), da mai lamba: (196), cibiyar ta gano cewa wannan batu yana buƙata daidaitawa tsakanin shawarwarin cibiyar da suka dace don sake fasalin shawarwarin taron.

Ta yi la'akari da sanya sakatariyar rukunin don kafa kwamitin ƙwararru na kimiyya, da kuma gabatar da sakamakon binciken kwamitin ga majalisar a zama na gaba.

Allah shi ne mafi sani;;

Da Sunan Allah Mai Yawan Rahama Da Jinƙai

Godiya ta **tabbata** ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga shugabanmu Annabi Muhammadu, cikamakin Annabawa, da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

ƘUDURI MAI LAMBA: 215 (11/22)
GAME DA KAMMALA BINCIKE DA NAZARIN BATUTUWAN INSHORAR HAƊIN GWIWA

Wannan yana cikin aiwatar da hukuncin Majalisar Cibiyar Fiƙihu ta Duniya mai lamba: 200 (21/6) dangane da: tanade-tanaden Shari'a da tsare-tsare na asasi na inshorar haɗin gwiwa, wanda aka yi a zaman na ashirin da daya da aka gudanar a Jami'ar Musulunci ta Imam Muhammad Bn Sa'ud, Riyad (Saudiyya) a cikin lokaci daga: 15-19 Muharram 1435, daidai da 18-22 Nuwamba 2013, tare da buƙatar gudanar da taron tattaunawa na musamman don tattauna batutuwa da dama da suka shafi haɗin kai. Inshora a shirye-shiryen ɗaukar shawarwari masu dacewa da shawarwarin da suka shafi su daga Majalisar Cibiyar.

Lallai majalisar cibiyar Fiƙihun Musulunci na duniya, da take ƙarƙashin ƙungiyar taimakekeniyar ƙasashen Musulmai, a taron ta na shekara- shekara karo na ashirin da biyu, da ya gudana a ƙasar Kuwait, a ranakun 2 - 5 ga watan Jimadal Akhir, 1436 H, wadanda suka yi daidai da ranakun 22 – 25 ga watan Maris, 2015.

Bayan nazarin shawarwarin taron ƙara wa juna sani da aka gudanar a birnin Jidda na ƙasar Saudiyya mai wannan taken, a tsakanin: 15-19 Almuharram 1435, daidai da: 18-22 ga Nuwamba, 2013, wanda ya tattauna batutuwa kamar haka:

- Ƙaddamar da Shari'a da sharuɗɗan shari'a da sarrafawa don aikin mai shari'a wanda ke aiki ga masu tsara manufofi.
- Ƙayyade dangantakar kwangilar da ke tsara kwangilar inshorar haɗin gwiwar dangane da:

- Daidaita dangantaka tsakanin masu tsara manufofi da Asusun don ƙayyade farkon dangantakar sadaukar da gudummawa; Don guje wa zato na mayar da kyautar lokacin rarraba rarar.
- Daidaita dangantakar dake tsakanin masu hannun jari da masu tsare-tsare idan asusun biyan kuɗi ya kasa aiwatar da ayyukansa (Ƙard Hasan).

- Yin nazarin rarar inshora dangane da:

- Iyakar abin da zai yiwu a cire wani ɓangare na rarar inshorar da aka samu don saduwa da haɗarin ragi a cikin asusun inshora na haɗin gwiwa.
- Iyakar abin da zai yiwu a cire wani takamaiman kashi na rarar inshorar da aka samu don fuskantar haɗarin bala'o'i.
- Ta yadda za a iya sanya diyya da aka bai wa hukumar gudanarwar ayyukan inshora wani ɓangare ko kaso na rarar inshorar, kuma hakan ya kasance a matsayin duk wani aikin da ya yi ba tare da an cire masa wani kuɗi daga cikin rajista ba.
- Matsayin da zai yiwu a haɗa kashi na adadin kuɗin shiga tare da kashi na ragi a cikin albashin da manajan inshora ya samu don mayar da ayyukan inshora, wanda zai zama abin ƙarfafawa don inganta aikin.

- Nazarin tushen bayar da inshora na Musulunci ta kowane fanni, tare da nunin dalilin da ya sa aka aiwatar da gogewar da aka yi amfani da su a cikin kamfanonin da abin ya shafa, da irin yadda wannan hanyar ta cika sharuɗɗa da ƙa'idoji na shari'a.
- Gabatar da abubuwan da suka shafi ƙasa da ƙasa game da inshorar haɗin gwiwa, da kuma gano iyakar riƙonsu da tushe da aka amince da shi a

ƙudurin majalisa mai lamba 200 (21/6) dangane da tanade-tanaden Shari'a da kula da tushe na inshorar haɗin gwiwa.

Bayan ta yi nazari tare da tattauna shi, majalisar ta yanke shawara da shawarwari kamar haka:

Na farko: Hukunce-hukuncen suna wakiltar gatari uku:

Fuska ta farko: Rarar inshora:

- Iyakar abin da zai yiwu a cire wani ɓangare na rarar inshorar da aka gane don fuskantar haɗarin ragi a cikin asusun inshora na haɗin gwiwar.
- Matsakaicin adadin takamaiman kashi na rarar inshora don fuskantar haɗarin bala'o'i.
- Iyakar abin da zai yiwu a sanya diyya da aka bai wa hukumar gudanarwa na gudanar da ayyukan inshora wani ɓangare ko kaso na rarar inshorar, kuma hakan ya kasance sakamakon duk aikin da ya yi ba tare da an cire masa wani kuɗi daga cikin rajista ba. .
- Matsayin da zai yiwu a haɗa kashi na adadin kuɗin shiga tare da kashi na ragi a cikin albashin da manajan inshora ke karɓa don gudanar da ayyukan inshora, wanda zai zama abin ƙarfafawa don inganta aikin.

